[10:18PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [ 7/8/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
~ AFRAH KO AMRAH~ 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

🏅Na🏅
Bilqis sidibe💅& Billy giro😊

🏅1️⃣🏅
Zaune yake a office dauke da kyakkyawar yarinya maqale a kafadar sa wacce shekarun ta baza su wuce four to five yrs ba sai bacci take abin ta shikuma yana faman cike ciken wasu takardu.

Gayen ya hadu sosai wanda kallo daya zakayi masa kasan dan hutu ne.
Kuma komai na sa a natse yake yinsa.

Wani gaye ne ya shigo office d'in da sallamar sa shekarun sa baza su fi 27yrs ba duk dai en tsara ne kuma da alama en uwan juna ne sbd suna dan da kama.
shigowar gayen keda wuya ya ajiye aikin da yake tare da amsa sallamar sa yayinda fuskar sa ke dauke da alamar murmushi.

Wanda ya shigo ne ke cewa "Doctor farhan sae aiki kake ta faman yi da Afrah maqale a kafada,se faman bacci take baza ka ajiye ta ka huta ba"
doctor farhan yayi murmushin da ke qara masa kyau yace "fu'ad kenan ai kasan Afrah haka take ko yaushe tana maqale a jikina har dai idan zatayi bacci ba makawa sae kan jikina take samu baccin ya dauke ta.
Kuma zancen ajiye ta na huta ko naso hakan idan baccin ta bai yi nisa ba zata farka ne idan taji zan ajiye ta,sauqi na daya Afrah bata da nauyi abin har mamaki yake bani dmn komai tsawon lokacin da nayi dauke da ita bana jin na gaji, idan kaga na ajiye ta ba wai don na gaji bane se don zanyi wani aiki.
Fu'ad ya nisa hade da fadin lallai Afrah najin dadin ta,inace dai bata hana ka sake wa da amaryar ka Amrah? Nop ko daya.
Yauwa haka nake son ji ace Afrah na bata takura kowa,ya fadi haka ne tare da d'ora ledar sweet kan desk yace ga sweet na saya ma sweet Afrah ita kadai bada Amarya ba dmn bana son a sakawa Afrah rani, idan amarya na buqata angonta ya saya mata,farhan yayi murmushi yace "bazan siya ba kuma sae ta sha na Afrah,kai ita ma zata fara sha kafin Afrah.
Fu'ad yace "cab bazan yarda da haka ba Afrah dai zata fara sha" ya fadi haka ne tare da kiran sunan Afrah kusan sau uku bata motsa ba.
Farhan yayi murmushi yace "tank God da yasa yau en jin basa kusa da ka tayar min da ita,kamar ya en jin basa kusa? Kai fu'ad kar ka ce min baka san Afrah bata ji ba she is deaf,au haba meyasa idan aka mata magana take dagawa mutum kai alamar taji?eh tana ji wani lokacin amma rashin jin ta yafi yawa kuma d'aga kan da take,
ka fahim ce ta da kyau idan kana magana bakin ka take kallo ta hakan ne take samu ta baka

amsar abinda kace,
ikon Allah to kace tana ji wani lokaci,
kenan har da magana tana yi a wannan lokaci? Bata iya magana kawai dai bakin ta na motsi kamar tace wani abu se ta kasa,amma idan tana kuka ka rantse da Allah tana ji,kukan tsaf yake fita kamar ba na deaf ba haka ma dariyar ta.

Fu'ad yace Allah sarki to baza ka kaita a duba ta ba,,fu'ad ai kasan bazan bar Afrah haka kawai ba, abun ne ya faskara amma ko yaushe cikin shan magani take,kamar Amrah.

Ka ce dai blind & deaf kake fama da su a gidan ka...kai! waye blind?ai ka fini sani, au dama cin mutunci ne ya kawo ka a office dina,wane cin mutunci ai gaskiya na fada Amrah bata gani sae da glass,to shine zaka kirata blind,bazan kirata blind ba kuwa tunda da zarar ta cire glass bata ganin komai,....wa ya gaya ma Amrah kam tana ganin shadow,....ahaf shadow din da ko ta gan shi kwata kwata bata fahimtar na mene ne,to na dai ji koma yaya ne ina sonta a hakan,ai an san kana son ta a hàkan tunda ka aure ta,ya fadi haka ne tare da miqe wa tsaye yace "ni zan tafi na san patient na can na faman jira na,idan kaje a gaida amarya,
farhan ya gyada masa kai yace inshaAllah zata ji sannan fu'ad ya fita.

Fitar fu'ad keda wuya Afrah ta fara motsawa a hankali.
Farhan ya maida ta kan cinyar sa,
tayi saurin sauka tare da jawo hannun sa tana nuna masa toilet hakan yasa farhan ya fahimci fitsari take ji.
Ya tallabeta cak yakai ta toilet tayi fitsari suka fito.
Ya dora ta kan cinyar sa tare da jawo food flask,ya zuba mata abinci ya shiga bata a hankali har taci ta qoshi ya bata ruwa tasha hade da zaro tissue ya goge mata dan qaramin bakinta.
Ya lotsa en yatsun sa kan kumatun ta se kawai naga tayi murmushin da ya bayyanar da dimple in ta,sannan ita ma ta kai hannu ta lotsa en yatsun ta a nasa kumatun shima yayi murmushin da haqoran sa farare tas suka bayyana.
Mayar da Ita yayi kan desk suna fuskantar juna ya dauko ledar sweet ya miqa mata tare da fadin uncle fu'ad ne ya ce a baki,
Shiru ta mishi tana kallon shi sbd bata fahimci me yace ba, sake maimata maganar yayi yayinda ta tsure bakin sa da kallo,a nan ta fahimci me yake cewa,yayinda ya dauko dayan sweet yana bude mata.

Cike da murmushin jin dadi irin nasu na yara ta kai hannu ta kar6i sweet din da farhan ya bude mata ya miqa mata ta kar6a.
Ta hade tafukan hannyen ta alamar thank u sannan ta saka sweet din a bakin ta se shillo take da en qafafuwanta,farhan ya kai hannu ya gyara mata tsorayen kalabar ta da ke reto kan fuskar ta.

Da dare guraren qarfe tara farhan ne da Afrah a kwance kan bed cikin shirin su na bacci suna game da waya Afrah se qyalqyatar dariya ta ke......uncle!uncle!! kiran yana fitowa cikin murya mai dadin sauraro.

Farhan naga ya tashi a natse ya nufi toilet ya same ta riqe da towel bata riga ta daura ba ta dai kare qirjinta da shi,sae faman lalabe take.

Towel ya kar6a ya daura mata sannan ya tattara sumar ta da ta jiqe shar kaf da ruwa ya mayar a baya ya shiga dube dube a toilet din bai ga abinda yake nema ba, ya jawo dan qaramin towel tare da jawota jikin sa,ya shiga tsane mata gashin kanta da ya gama ne ya dauko ta cak se kan bed kafin yake kai duban sa kan mirror ya hango eye glass din ta,yace "Amrah me yasa kika shiga toilet ba glass a idonki? Oily eyes din ta ta dago tana kallon inda take sa ran fuskar sa ce, in kaga hakan zakayi zaton tana gani sbd yanda ta saka qwayar idonta a cikin nashi wanda ni billy & Futha munyi mamakin kallon amma shi farhan da alama ya saba ganin haka shiyasa bai yi mamaki ba ko kadan
tace"uncle ina so ne na fara koyon yanda zan riqa zuwa wani gun ba sae da glass ba,yace no ki daina haka ina tsoron ya zama had'ari wata rana,ta gyada kanta kafin farhan ke tashi ya dauko mata eye glass ya saka mata.

Tace "tank u" sannan ta tashi tana tafiya cikin dabara,
farhan sae kallon qafafun ta yake cike da tausayi.

Gaban mirror taje ta shafe jikinta da turarukka masu qamshin dadi.
Sannan ta nufi wardrobe yayinda Afrah ta mirgino kan jikin farhan tayi pillow da cinyar sa tare da miqa masa wayar sa.
Gashin kanta ya shiga shafawa a hankali sbd ya fahimci bacci take ji.

Koda Amrah ta gama shirin baccin ta har Afrah tayi bacci,
qaraso wa tayi ta zauna a dayan gefen sa tare da d'ora kanta a kafadar sa, farhan ya shafo gashin kanta ya kalle ta cike da kulawa yace"ya jikin naki?duqar da kanta tayi dauke da alamar jin kunya tana wasa da zoben hannunta kafin take cewa "naji sauqi"

🏅2️⃣🏅 Murmushi yayi wanda ya qara masa kyau sbd yanayin yanda Amrah keyi idan taji kunya yana birge shi sosai,
shafo gefen fuskar ta yayi kafin yake dora Afrah kan kafadar sa da tuni baccin ta yayi nisa yaje a hankali ya shimfide ta kan d'an maidaidaicin gadon ta.
sae da ya jima yana tofe ta da addu'o'i kafin yake barin gurin.
Amrah kuwa ba abinda take face kallon sa wanda ako yaushe bata gajiya wa da hakan.
Ba ita ta daina kallon sa ba sai da yazo gab da ita ya zauna tare da jawo ta jikin sa hade da lakuto hancin ta yace wannan kallon fa sae kace yau ne farkon haduwar mu.
Bata ce dashi komai ba face lumshe idon ta da tayi hade da d'an guntun murmushi,farhan kuwa ya kashe musu wutar dakin suka kwanta sae bacci.

Da jijjihi kukan Afrah ne ya tashe su.
Farhan ne yayi saurin saukowa kan bed ya qarasa inda take ya dauke ta cikin hanzari ya nufi toilet da ita domin tayi fitsari sbd yasan ba abinda take ma kuka face fitsari sbd Afrah ta kasance yarinya wacce duk yadda take jin fitsari bata yin shi kan bed sai dai ta ajiye ma mutum kuka.
Bayan sun fito ne yayi zaune da ita kan bed,yayinda ta lafe kan jikinsa bacci na sake fizgar ta kadan kadan har ya fizge ta gabadaya.
Nan farhan ya shimfide ta wanda sai Allah Allah yake kar ta farka sbd so yake yaje masallaci lokacin sallah yayi.

Sai guraren qarfe tara Afrah ta farka daga bacci,lokacin farhan ya fito daga wanka kenan yana taje gashin kansa,
saurin kallon Afrah yayi wacce ke kuka irin nasu na yara idan sun tashi daga bacci
ganin idon ta a rufe yasa ya sauke ajiyar zuciya sbd yasan idan a bude suke da ta qyalla ido a kan shi ba makawa shine zai mata wanka gashi sauri yake sosai yana so ya hallarci meeting din da za a yi da qarfe goma,
kallon Amrah yayi wacce shigowar ta dakin kenan da alama daga kitchen ta fito sbd dauke take da trayn abinci,kallon da farhan ya mata ne yasa ta fahim ci me yake nufi nan ta ajiya tarayn da ke hannun ta ta nufi
Afrah cikin sauri ta dauke ta,
kafin Afrah ta bude idon ta har sun shiga toilet.

Koda suka fito basu sami farhan a dakin ba ya fita.
Amrah takai dubanta
gun break fast din da ta ajiye nan ta fahimci farhan ya dibi nashi kasancewar ba plate daya a cikin plates din ta ajiye.
Nan ta shafa ma Afrah Vaseline ta shirya ta cikin kayan sanyi kasancewar sanyin da ake sosai.

A 6anfaren farhan kuwa falo yaje ya zauna kan dining yana break fast sauri sauri.
Sai da ya kammala sannan ya koma gurin su amrah ya samu afrah kwance jikin pillow sai tsutsar babban yatsan ta take Amrah na riqe da plate din abinci sai faman lallashin ta take kan ta tashi taci abinci,amma mirsisi taqi tashi gashi tana jin yunwa sosai,ita ala dole farhan kadai ke bata abinci ta kar6a.
A hankali farhan ya qarasa gurin su ya zauna,Amrah ta ce "uncle nayi nayi taci abinci amma taqi"yace "dama nayi tunanin haka shiyasa naje na gaggauta yin nawa braek fast domin na samu na bata kafin lokaci ya qure min"
Yana gama fadar haka ya jawota kusa da shi ya shiga ciyar da ita har sai da ya tabbatar cikin ta ya cika.

Sannan ya bata ruwa ya tashi ya jawo suit din sa blue black in colour kallar wandon sa yayinda rigar sa ta ciki ta kasance milk haka talkalman da ke qafafunsa milk ne agogon hannun sa ma haka,briefcase din sa ya dauka hade da makullin mota,tare da fadin ni zan fita.

Nan Amrah ta tashi tare da daukar Afrah da niyar su raka shi farhan yace "a'a kuyi zaman Ku bana so taga shiga ta mota dmn na tabbatar kuka zata min sai naje da ita gashi bazai yiyu na shiga da ita taron meeting din da zamuyi sbd gabadaya likitawan state ne za a hadu wanda bansan iya tsawon lokacin da zamu dauka ba bare naje da ita na bayar a riqa min ita gun nurses,kuma gashi yau sanyi ake sosai hakan yasa nake so tayi zaman ta a gida"

Ya fadi haka ne tare da kallon agogon da ke hannun sa yaga 9:40am sannan ya maida duban shi gun afrah da ke kallon shi da alama so ta ke ya dauke ta,

bye bye kawai ya mata ya kama hanyar fita daga dakin wanda har ya bude qofar dakin ya jiyo sautin kukan ta,tsayawa yayi cak cike da damuwa sbd ko kadan baya son jin kukan ta musamman ma idan ya tuna cewa ita marainiyace kuma amana ce a gare shi.

Jiki sa6ule yaje ya kar6e ta yace bara na kai ta gun gwaggwo naga ko zata yarda ta zauna.

Nan ya fito ya nufi dayan 6angaren da muke sa ran nan ne 6angaren gwaggwor da ya ambata.

Da sallamar shi ya shiga ya same ta tana Karin kumallo ya russuna cike da ladabi ya gaishe ta sannan ya fadi buqatar shi na son Afrah ta zauna gurin ta har ya dawo.

Ba musu gwagwo ta miqa hannu domin ta kar6i Afrah,ai kuwa ta maqale kafada tana mai qara manne masa alamar baza ta je ba.

Gwaggwo tace dama shiru kawai nayi amma nasan baza ta yarda ta zauna ba kuma in banda abinka kai da kake zuwa da ita kullum yau kuma me ya kawo zancen baza ka je da ita ba?cike da damuwa ya nisa yace gwaggwo nima ba haka naso ba zuwan ne da ita ba zai yiyu ba kasancewar meeting din da zamuyi wanda tun jiya na sanar da ke irin di'n bin taron da za'ayi.....haka ne fa gaskiyar ka.

Nan ta kar6i Afrah wanda da qyar aka samu taje da kuka da komai har da su murmurje.

Farhan kuwa ya fita cike da rashin jin dadi har ya naji kamar da zai yiyu da ya fasa zuwa meeting d'in.

Futha Luv & Billy giro

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

[10:18PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [ 7/10/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

AFRAH KO AMRAH

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

Na
 Bilqis sidibe💅 & Billy giro😊

🏅3️⃣🏅
Tunda ya fita gidan bashi ya dawo daga gurin meeting d'in ba sai bayan sallar la'asar.

Shigowar sa keda wuya bai zarce koina ba sai 6angaren gwaggwo,
 da shigar sa dakin yayi tsaye cike da murmushi yana kallon Afrah kwance sae bacci take ga sweet a gefen ta zube saura kuwa duk ta watse su a tsakiyar dakin kamar yadda tsorayen kalabar ta suka barbaje akan bed.

K'arasawa yayi daga ciki ya zauna tare da gaida gwaggwo dake zaune kan sallaya tana lazimi yace "gwaggwo haka er reonon taki ta 6ata miki daki da sweets?sae da gwaggwo ta shafa addu'a tare da yaye hijabin jikinta tace"hm!ai yau ni qaramar hauka tamin sae fada take dani cikin gwallanniyar su ta kurame,farhan yayi murmushi mai hade da dariya sannan ya kalli Afrah shidai haka kawai baya son yaji an kirata a kurma duk da yasan eh kurma ce,gwaggwo taci gaba da cewa "a cikin gwalaniyar ne take dauko duk abinda ta samu tayi ta jifa da shi nayi rarrashi har na gaji haka ma Amrah tazo ta bata alawa tayi ta rarrashi amma duk d'aya wai mamaci ya karye.
   Ita da kanta ta gaji da murmujen ta a nan bakin qofa har bacci ya kwashe ta shine na dauke ta na d'ora kan gado tare da alawar da na fara tsincewa ban samu na qarasa ba naji kiran sallah shine na ajiye aikin tukun idan na qarasa sallah.

   Farhan ya nisa yace "ina ce dai bata jiwa kanta ciwo garin murmuje ba kuma bata miki 6arna ba?Aa ko d'aya bana tunanin haka,nan ya tashi tare da fadin to zanje na da'n huta na dawo na dauke ta,gwaggwo tace "to Allah hutar da gajiya" yace "Amin"kafin yake fita daga dakin.

Yana isa 6angaren su ya tarar da Amrah daure da towel gaban mirror tana taje gashin kanta.
   Ya jima a tsaye bata san da shi ba sai daga baya ne ta hango shi ta jikin mirror sakar masa lallausan murmushi tayi yayinda ya russuna a hankali ya rungumo ta tare da dora kansa a kafadar ta yana mai shaqar qamshin turaren da ke fita a jikinta, yace "my Amrah na gaji sosai"shafo sajen fuskar shi tayi tace "sorry my uncle"ta fad'i haka ne yayinda yake miqar da ita tsaye yace "muje ina son naci abinci"nan ta cire masa suit hade da fadin bari kayi wanka tukun ko...a gajiye ya kalle ta yace"ba kya da tausayi ko my Amrah sbd ke kinci kin qoshi shine ni sai nayi wanka ko zanci",,um um uncle ba haka bane ba,, haka ne man gashi har cikin ki ya tasa alamar kinci ki qoshi"ya fadi haka ne yayinda yake shafa cikin ta ya tafi har izuwa qirjinta cike da jin kunya ta cusa fuskar ta a qirijin sa ba tare da ta jaye hannun sa da yake yawo dashi kan qirjin ta ba, tace "Allah uncle ina tausayin ka kasan ulcer nake fama da ita ko naso na jira ka bazan sami damar hakan ba"
  Bai ce da ita komai ba sae aikinsa da yake na shafar jikinta wanda komai yana yinsa ne a natse a haka ne har yake qoqarin zame mata towel bata hana shi ba duk da masifar kunyar abinda yake mata da take ji sbd har yanzu bata sake dashi gabadaya ba kuma idan ta hanashi

tasan bata masa adalci ba sbd tasan turarukkan da ta shafa qamshinsu  ba xai barshi a iya kallonta kad'ai ba.
Suna cikin haka ne tayi saurin jaye jikinta daga nashi tare da daura towel d'in ta da farhan ya fara zamewa hakan yasa farhan
ya d'ago a hankali yana kallon ta,
ganin tana kallon qofar d'akin yasa shima ya maida duban sa a gun.
Afrah ya gani a tsaye riqe da sweet a hannun ta sae dai fuskar ta dauke take da fishi,murmushi yayi wanda ya nuna cike yake da farin cikin ganin Afrah.
qarasawa yayi gurin ta ganin bata da alamar qarasowa,
yaje ya durqusa tare da kama kunnen sa afrah kuwa kauda fuskar ta tayi gefe ta turo baki tare da maqale kafad'a wai bazata haqura ba,kamar qaramin yaro ya nuna kansa yace "nine baza kiyi ma haquri ba"kallon sa kawai tayi sannan ta kalli amrah da ke tsaye tana kallon su nan ta bar shi durqushe ta tafi gurin amrah tare da miqa mata sweet din da ke hannun ta Amrah ta kar6a ta bude mata sweet d'in sannan ta dauke ta,farhan ne ya qaraso gurin su yana cire buttons din rigarshi  yaje gefen gado ya zauna tare da jawo stool di'n da kulolin abinci ke kai, Amrah ce ta zuba masa abinci shi kuma sae kallon Afrah yake da ke shan sweet tana kallon shi wanda ya fahimci so take ya d'auke ta nan ya miqa hannu ya kar6e ta ya dora ta kan cinyar sa yana mai fadin an daina fishi da uncle? tsure bakin sa kawai tayi da kallo ta lafe a jikin sa tana mai wasa da buttons d'in rigar sa.

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:19PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [7/11/2016]  🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
~ AFRAH KO AMRAH ~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

Na
Billy giro😊 &Bilqis sidibe💅

🏅4️⃣🏅
Cike da kulawa farhan ke kallon Afrah da ke wasa da buttons d'in rigar shi wanda ya fahimci akwai yunwa a tattare da ita,
cire sweet d'in da ke bakin ta yayi ya zaro tissue ya goge mata bakin ta, ya zaunar da ita ta yanda zai ji dad'in ciyar da ita.
Sai da ya fara cin abincin sbd yaji idan ba wata matsala ta yaji haka,
kasancewar Afrah bata son yaji ko kadan,
ya kuwa ji abinci dai dai ba wata matsala kuma dama yayi tunanin haka bcs bai ta6a jin wata matsala a abincin Amrah ba ko yanzu ya d'and'ana ne sbd yasan d'an adam ajizi ne ya kan yi kuskure wata rana.
A hankali ya shiga fara bata abincin yayinda take bud'e d'an qaramin bakin ta tana kar6a haka shima yake bud'e d'an madaidaicin bakin sa tana saka mishi,domin Afrah  yarinya ce wacce duk abinda farhan ya mata ta kan so ita ma ta mishi haka, duk da cewa yanda take bashi abinci akwai shiririta amma haka farhan ke biye mata wanda wani  lokaci idan taje saka mishi spoon yakan d'an karkace abincin ya zuba amma sai dai yayi murmushi yasa tissue ya share ya kuma

dai dai ta mata spoon d'in ta yanda zata saka mishi a baki ba tare da abinci ya zuba ba.
Haka suka ci gaba da cin abincin su cike da sha'awa da burge duk wanda ke kallon su.
Bayan sun kammala cin abinci ne ya dauke ta yaje ya mata wanka ya dunqulo ta cikin towel ya kwantar kan bed sannan ya fice toilet domin yayi nasa wanka.
Koda ya fito har Amrah ta shirya ma Afrah cikin kayan da suka yi matuqar daukar ta sai zuba qamshi take.

Bayan wasu kwanaki farhan ne dauke da Afrah a kafadar sa dayan hannunsa kuma kaya ne niqiqi.
Amrah da ke kwance kan 3 seater ta zo cikin hanzari ta kar6i kayan da ke hannunsa suka shiga daga ciki,
Amrah na ajiye kayan Afrah ta shiga bubbud'e su cike da murna tana gwalanniyar su ta kurame tana nunawa Amrah kayan d'aya bayan d'aya,
nan Amrah ta shiga kar6ar kayan tana dubawa,
school bag ce da littafai da kuma sweets,choculate,biscuit,da school basket sannan da kuma lunch box,da ta gama gani ne ta shiga tambayar ta tana mai mata maganar kurame da hannu yayinda Afrah ke bata amsa.

Bayan ta gama tambayar ta ne ta maida dubanta gun farhan da ke jingine kan sofa idanuwansa a lumshe tace"uncle Afrah tace wae gobe zaka fara kai ta school?a hankali ya bud'e idon shi tare da gyara kwanciyar sa yace eh by tomorrow inshaAllah zata fara zuwa school"to ni zancen tawa school fa?
shiru yayi kamar ba zai ce da ita komai ba can ya nisa tare da fad'in "kar ki damu idan lokacin WAEC da NECO yayi zaki je kiyi amma baza ki koma da zuwa school ba, ba ta ce da shi komai ba,
ba wai don bata ji dad'i ba sai don ita ma haka yafi mata,jin shiru yasa ya tashi zaune tare da yaye hular da ke kansa ya kalle ta da kyau yace"yadai Amrahna baki so hakan ba ne?girgiza kanta tayi hade da fad'in "ai ni uncle haka ma da kayi yafi min"ok dauko min ruwa nasha kinji.
Nan ta tashi ta dauko masa ruwa had'e da lemu mai sanyi.

Da dare guraren qarfe goma sha biyu kowanen su bacci yake abinsa cike da kwanciyar hankali.

A hankali farhan yake bude idon shi sbd yanda yaji jikinsa kamar wanda aka d'ad'd'aure,
gabadaya yaji sa a tamke ga kuma yawan motsi da yake ji a d'akin yunqurawar da zai yi ne yaga tabbas kuwa a d'aure yake har ma ba ta yanda za'ayi ya iya wani qwaqqwaran motsi,kallon d'aurin da aka masa yake cike da tsananin mamaki shin ta yaya hakan ta faru,waya masa haka ⁉️
Idon sa yakai kan gadon Afrah wayam ba kowa ya kuma kalli gefen sa ba Amrah sosai hankalin sa ya qara tashi kan yayi wani yunquri yaji kukan Afrah an fito da ita a dayan daki aka shigo da ita d'akin da yake tare da kunna wutar dakin,
Afrah na ganin shi ta fara kuka sosai tana zille zille tare da miqo hannunta tana so farhan ya cece ta,

su kuwa sai janta suke zasu bar d'akin da ita,yayinda farhan ke yunqurin ya kunce kansa amma ya kasà gashi kad'an ya rage su fita da ita hakan yasa ya fad'o kan bed yana son yaja jikinsa da sauri yaje ya kar6o Afrah,
amma hakan ya gagare shi sbd hannayen sa a baya suke kuma a daure haka ma qafafuwansa a daure suke,
da qarfin tsiya ya yunqura hade da wani irin nishi yayinda aka kashe wutar dakin wanda yayi dai dai da tashin qarar bindiga.........kamar had'in baki farhan da Afrah suka tashi firgigit daga bacci wanda hakan ya nuna kowanen su ya tashi daga mummunan mafarki,a rikice farhan ya kai dubansa kan gadon Afrah kamar yadda ita ma Afrah take kallon nasu gadon,
Da gudu ta sauko kan gadon ta nufo gurin shi tare da fad'awa kan jikinsa,
jikinta sae qyarma yake shi kuwa farhan jikinsa ne yaji ya mutu ya qara matse Afrah a qirjin sa ya shiga shafa sumar kanta a hankali sae dai tunani ne fal a ransa yayinda yake tuna fuskokin mutanen da ya gani a cikin mafarki tabbas a zahiri yasan wad'annan fuskokin, kuma yasan mugun nufin su a kanshi,
shiyasa ya shiga fargaba sosai kar mafarkin sa ya zamo gaskiya"saukar hawaye yake ji kad'an kad'an a qirjin sa tare da jin sautin kuka,
wanda shine ya dawo dashi daga duniyar tunanin da yake ya kalli Afrah da ke lafe a qirjin sa hawaye na ta faman zarya a kumatun ta,
tana kuma fitar da sautin kuka a hankali,
sannu a hankali farhan yakai hannu yana share mata hawaye yana kuma tunanin shin ita kuma Afrah wane irin mafarki ne ya firgita ta har take yin kuka.
Gashi bai iya maganar kurame ba bare ya tambaye ta,
Amrah ce ta iya kuma bacci take.
Lallashin ta kawai ya shiga yi ta hanyar bubbuga bayan ta,
har ya samu tayi shiru ta kuma qara lafewa a qirjin sa alamar tayi bacci.

Futha luv💅&Billy giro😊

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:19PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [ 7/12/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
~AFRAH KO AMRAH ~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

Na
Billy giro😊&Bilqis Sidibe💅

🏅5️⃣🏅
Domin sae ajiyar zuciyar ta ke fita a hankali,
cike da kulawa farhan ke ci gaba da kallon er fuskar ta mai kyau wacce d'igon hawaye ke kan eyelashes d'inta,
yasa yatsan sa ya share mata tare da kwantar da ita a tsakiyar su,
cike da shagwa6a ta farka tana fad'in"uhm uhm"tayi saurin shigewa jikin sa kamar wacce ke jin

tsoro har dai yanda ta cusa fuskar ta a qirjin sa ta qudundune guri d'aya.
Addu'a ya shiga yi mata lokaci mai tsawo, sannan ya kalli matar sa Amrah wacce har yanzu bacci take gashin kanta duk ya barbarje a kan pillow har ma ya d'an rufe mata fuska,
bai yi yunqurin gyara mata ba sea surar jikinta da yake bi da kallo yana cikin haka ne yaji wani irin fad'uwar gaba wanda ya sa shi saurin daina kallon ta ya tashi a hankali yana mai karanto addu'a yaje gab da ita ya yaye mata gashin kanta da ya rufe mata fuska kafin yake zuwa toilet ya d'oro arwala yazo ya saka jallabiya kasancewar d'an guntun wando ne kad'ai a jikin sa.
Sae da ya shimfid'a carpet sannan ya kabbarta sallah.

Da asuba Amrah ce ta fara tashi miqa takeyi a hankali tare da tattara gashin kanta ta d'aure guri d'aya,
ta kai hannu ta d'auko eye glass d'inta da ke kan drawer ta saka sannan ne ta iya hango farhan da ke jingine jikin wardrobe riqe da casbi sae dai da alama bacci yake.
Yaye bedsheets d'in da ke jikinta tayi ta zamo daga ita sai er rigar ta ta bacci fara tas da ita iya guiwa mai siririn hannu.
Saukowa tayi kan gadon ta nufi gun farhan ta zauna kusa da shi tare da jinginawa a jikinsa tace "uncle ka tashi an fara kiran sallar asuba,kaji uncle"da qyar ya iya bud'e idonshi sbd wani irin bacci mai nauyi da ke fizgar shi,
ya sakad'o hannun shi ta bayan ta ya rungomo ta sosai,kamar qaramin yaro yace "my Amrah bacci nake ji sosai"to uncle ka bari idan kayi sallah sai ka koma baccin ko"gyad'a mata kai yayi kafin yake
janye jikinsa daga nata ya tashi ya nufi toilet yayi arwala ya fice masallaci haka ita ma taje tayi arwala tayi sallah.

Bayan ya dawo daga masallaci ne ya hau kan bed da niyar ya kwanta sai ya tuna yau Monday zai kai Afrah school,
hakan yasa ya fasa baccin da yayi niya,ya tashi yaje ya fara tsara littafai a cikin school bag d'in Afrah.
Amrah tazo tare da kar6ar aikin da yake tace"uncle je kayi baccin ka kawai tunda yanzu 5:40am to 7:00am sae na tashe ka yayinda ni kuma na gama had'a komai na buqatar zuwa makarantar Afrah,
Cike da jin dad'i ya gyada kansa ya shafo gefen fuskar ta tare da fad'in "tank u my wife" murmushi kawai tayi taci gaba da aikin,
shi kuma yaje ya kwanta wanda a nan take bacci ya d'auke shi.

Qarfe bakwai dai dai ta tashe shi koda ya bude idonshi har ta shirya ma Afrah cikin uniform d'in makaranta sky blue and white,
riga ta kasance fara mai dauke da necktie sky blue,aka mata stocking da skirt wanda ya kasance sky blue mai layin fari a qasan shi,
tsayin sa iya guiwa yayinda fararen socks d'in ta suka tafi har izuwa guiwar ta,se hular kanta sky blue wacce ta mata bala'in kyau har dai yanda aka d'an d'age ta gashin kanta sae ya baje a bayan ta,takalman qafafun ta kuwa tums ne baqaqe haka ma school bag d'inta baqa ce.
Ba qaramin kyau ta ma farhan ba domin ta yanda yake kallon ta kad'ai ya isa ya ganar da kai

hakan,
wanda hakan ya nuna bata ta6a masa kyau irin na yau ba.
Cike da murmushin jin dad'i ya kalli Amrah yace "sannu da qoqari my wife"ya fad'i haka ne yayinda ya dauki Afrah cak ya d'aga ta sama yana juyi da ita sae faman dariya suke, sannan daga bisani ya dora mata kiss a kumatu tare da lotsa yatsun sa akan kumatun ta wanda hakan ya qara fad'ad'a murmushin da take yi sae dimple d'inta suka qara lotsawa sosai.
Haka ita ma ta masa kiss a kumatu hade da lotsa en yatsunta a kumatun shi,
Yayi mata tsadadden murmushin da ba ko wane lokaci yake yinsa ba,
domin duk cikin murmushin da yake yi wannan yafi qara masa kyau da haiba.
Ya kalli Amrah da ke riqe da towel tana ta faman kallon su cike da murmushi,
ajiye Afrah yayi tare da kar6ar towel d'in da ke hannun Amrah ya nufi toilet domin ya gaggauta yin wanka.

Koda 7:30am tayi har ya kammala shirin sa tsaf ya ciyar da Afrah ba tare da yayi nasa break fast ba sbd gudun kar su makara da yawa duk da cewa makarantar kusa da su ta ke.

Koda suka isa makarantar sun samu ana assembly da yake founder d'in makarantar yasan da zuwan su kasancewar sa d'an uwan farhan hakan yasa yana hango fitowar su daga mota ya qarasa gurin su,farhan ya durqusa cike da ladabi ya gaishe shi wanda cikin gaisuwar ne naji ya kira sunan shi da uncle Basheer.
Sai da suka gama gaisawa ne uncle Basheer yaja hannun Afrah suka tafi sae bye bye take ma farhan kamar zata yi kuka.

Uncle Basheer na isa da ita assembly ya dora ta kan step tare da fad'in sunan ta da kuma class d'in da zata kasance wato nursery one.
Yayi haka ne sbd haka ake yi a makarantar duk aka sami newcomer akan d'ora sa a step a fad'i sunan shi da class d'in da zai shiga,akan yi haka tun daga kan d'an nursery, primary &secondary bcs makarantar ta qunshi nursery,primary & secondary.

Tun da aka d'ora Afrah kan step take kallon mutanen makarantar a wayen ce ma'ana ba wani d'ar d'ar ko noke noke akasin wasu da ko fuskar su basa bari a gani sae suyi ta faman noke noke.

Hakan da Afrah tayi ya burge mutanen makarantar sosai musamman ma wani hadadden gayen malami da tunda aka dora ta yake kallon ta har izuwa yanzu.
Kamar sa sak da founder makarantar wato uncle Basheer da alama jinin sa ne.

Ana gama assembly uncle Basheer yaja Afrah sae zuwa class d'in da zata zauna bai fito class d'in ba sae da yaja musu kunne kan kar yaji ko ya gani ana takarar ta ko nuna banbanci akan kasancewar ta kurma,
wanda duk zancen nan da uncle Basheer yayi yana kunnen hadadden gayen malamin nan,da

shima yazo ne domin shiga class d'in riqe  da attendànce register,
Sai dai jin Afrah kurma ce bai sa yaji burge shin da take ya ragu ba sae ma abinda ya qaru.
  Domin a maimakon ya zauna ya kira register sae ma daukar Afrah yayi ya dora ta kan desk  ya shafi gefen fuskar ta tare da sake mata lallausan murmushi yana mai qara jin son Afrah a cikin ransa fiye da yanda yake jin son sauran yara sbd gayen ya kasance mai son yara ne sosai.
   Kar6ar school bag in ta yayi ya fitar da littafan ta ya fara rubuta sunan ta kamar yadda yaji uncle Basheer ya ambaci real name d'in tà a gaban assembly [ 7/12/2016]
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
    ~AFRAH KO AMRAH ~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

Na
Billy giro😊&Bilqis Sidibe💅

🏅5️⃣🏅
Domin sae ajiyar zuciyar ta ke fita a hankali,
 cike da kulawa farhan ke ci gaba da kallon er fuskar ta mai kyau wacce d'igon hawaye ke kan eyelashes d'inta,
 yasa  yatsan sa ya share mata tare da kwantar da ita a tsakiyar su,
 cike da shagwa6a ta farka tana fad'in"uhm uhm"tayi saurin shigewa jikin sa kamar wacce ke jin tsoro har dai yanda ta cusa fuskar ta a qirjin sa ta qudundune guri d'aya.
  Addu'a ya shiga yi mata lokaci mai tsawo, sannan ya kalli matar sa Amrah wacce har yanzu bacci take gashin kanta duk ya barbarje a kan pillow har ma  ya d'an rufe mata fuska,
  bai yi yunqurin gyara mata ba sea surar jikinta da yake bi da kallo yana cikin haka ne yaji wani irin fad'uwar gaba wanda ya sa shi saurin daina kallon ta ya tashi a hankali yana mai karanto addu'a yaje gab da ita ya yaye mata gashin kanta da ya rufe mata fuska kafin yake zuwa toilet ya d'oro arwala yazo ya saka jallabiya kasancewar d'an guntun wando ne kad'ai a jikin sa.
   Sae da ya  shimfid'a carpet sannan ya kabbarta sallah.

Da asuba Amrah ce ta fara tashi miqa takeyi a hankali tare da tattara gashin kanta ta d'aure guri d'aya,
 ta kai hannu ta d'auko eye glass d'inta da ke kan drawer ta saka sannan ne ta iya hango farhan da ke jingine jikin wardrobe riqe da casbi sae dai da alama bacci yake.
     Yaye bedsheets d'in da ke jikinta tayi ta zamo daga ita sai er rigar ta ta bacci fara tas da ita iya guiwa mai siririn hannu.
   Saukowa tayi kan gadon ta nufi gun farhan ta zauna kusa da shi tare da jinginawa a jikinsa tace "uncle ka tashi an fara kiran sallar asuba,kaji  uncle"da qyar ya iya bud'e idonshi saboda wani irin bacci mai nauyi da ke fizgar shi,
 ya sakad'o hannun shi ta bayan ta ya rungomo ta sosai,kamar qaramin yaro yace "my Amrah bacci nake ji sosai"to uncle ka bari idan kayi sallah sai ka koma baccin ko"gyad'a mata kai yayi kafin yake
 janye jikinsa daga nata ya tashi ya nufi toilet yayi arwala ya fice masallaci haka ita ma taje tayi arwala tayi sallah.

Bayan ya dawo daga masallaci ne ya hau kan bed da niyar ya kwanta sai ya tuna yau Monday zai kai Afrah school,
hakan yasa ya fasa baccin da yayi niya,ya tashi yaje ya fara tsara littafai a cikin school bag d'in Afrah.
Amrah tazo tare da kar6ar aikin da yake tace"uncle je kayi baccin ka kawai tunda yanzu 5:40am to 7:00am sae na tashe ka yayinda ni kuma na gama had'a komai na buqatar zuwa makarantar Afrah,
Cike da jin dad'i ya gyada kansa ya shafo gefen fuskar ta tare da fad'in "thank u my wife" murmushi kawai tayi taci gaba da aikin,
shi kuma yaje ya kwanta wanda a nan take bacci ya d'auke shi.

Qarfe bakwai dai dai ta tashe shi koda ya bude idonshi har ta shirya ma Afrah cikin uniform d'in makaranta sky blue and white,
riga ta kasance fara mai dauke da necktie sky blue,aka mata stocking da skirt wanda ya kasance sky blue mai layin fari a qasan shi,
tsayin sa iya guiwa yayinda fararen socks d'in ta suka tafi har izuwa guiwar ta,se hular kanta sky blue wacce ta mata bala'in kyau har dai yanda aka d'an d'age ta gashin kanta sae ya baje a bayan ta,takalman qafafun ta kuwa toms ne baqaqe haka ma school bag d'inta baqa ce.
Ba qaramin kyau ta ma farhan ba domin ta yanda yake kallon ta kad'ai ya isa ya ganar da kai hakan,
wanda hakan ya nuna bata ta6a masa kyau irin na yau ba.
Cike da murmushin jin dad'i ya kalli Amrah yace "sannu da qoqari my wife"ya fad'i haka ne yayinda ya dauki Afrah cak ya d'aga ta sama yana juyi da ita sae faman dariya suke, sannan daga bisani ya dora mata kiss a kumatu tare da lotsa yatsun sa akan kumatun ta wanda hakan ya qara fad'ad'a murmushin da take yi sae dimple d'inta suka qara lotsawa sosai.
Haka ita ma ta masa kiss a kumatu hade da lotsa en yatsunta a kumatun shi,
Yayi mata tsadadden murmushin da ba ko wane lokaci yake yinsa ba,
domin duk cikin murmushin da yake yi wannan yafi qara masa kyau da haiba.
Ya kalli Amrah da ke riqe da towel tana ta faman kallon su cike da murmushi,
ajiye Afrah yayi tare da kar6ar towel d'in da ke hannun Amrah ya nufi toilet domin ya gaggauta yin wanka.

Koda 7:30am tayi har ya kammala shirin sa tsaf ya ciyar da Afrah ba tare da yayi nasa break fast ba sbd gudun kar su makara da yawa duk da cewa makarantar kusa da su ta ke.

Koda suka isa makarantar sun samu ana assembly da yake founder d'in makarantar yasan da zuwan su kasancewar sa d'an uwan farhan hakan yasa yana hango fitowar su daga mota ya qarasa gurin su,farhan ya durqusa cike da ladabi ya gaishe shi wanda cikin gaisuwar ne naji ya kira sunan shi da uncle Basheer.
Sai da suka gama gaisawa ne uncle Basheer yaja hannun Afrah suka tafi sae bye bye take ma farhan kamar zata yi kuka.

Uncle Basheer na isa da ita assembly ya dora ta kan step tare da fad'in sunan ta da kuma class d'in da zata kasance wato nursery one.
Yayi haka ne sbd haka ake yi a makarantar duk aka sami newcomer akan d'ora sa a step a fad'i sunan shi da class d'in da zai shiga,akan yi haka tun daga kan d'an nursery, primary &secondary bcs makarantar ta qunshi nursery,primary & secondary.

Tun da aka d'ora Afrah kan step take kallon mutanen makarantar a wayen ce ma'ana ba wani d'ar d'ar ko noke noke akasin wasu da ko fuskar su basa bari a gani sae suyi ta faman noke noke.

Hakan da Afrah tayi ya burge mutanen makarantar sosai musamman ma wani hadadden gayen malami da tunda aka dora ta yake kallon ta har izuwa yanzu.
Kamar sa sak da founder makarantar wato uncle Basheer da alama jinin sa ne.

Ana gama assembly uncle Basheer yaja Afrah sae zuwa class d'in da zata zauna bai fito class d'in ba sae da yaja musu kunne kan kar yaji ko ya gani ana takarar ta ko nuna banbanci akan kasancewar ta kurma,
wanda duk zancen nan da uncle Basheer yayi yana kunnen hadadden gayen malamin nan,da shima yazo ne domin shiga class d'in riqe da attendànce register,
Sai dai jin Afrah kurma ce bai sa yaji burge shin da take ya ragu ba sae ma abinda ya qaru.
Domin a maimakon ya zauna ya kira register sae ma daukar Afrah yayi ya dora ta kan desk ya shafi gefen fuskar ta tare da sake mata lallausan murmushi yana mai qara jin son Afrah a cikin ransa fiye da yanda yake jin son sauran yara sbd gayen ya kasance mai son yara ne sosai.
Kar6ar school bag in ta yayi ya fitar da littafan ta ya fara rubuta sunan ta kamar yadda yaji uncle Basheer ya ambaci real name d'in tà a gaban assembly wato"Zarah Sadeeq".

Futha Luv💅 &Billy giro😊

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅"Zarah Sadeeq".

Futha Luv💅 &Billy giro😊

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:19PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [ 7/13/2016] *🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅*
~*AFRAH KO AMRAH* ~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*Na*
*Bilkeesu giro😊 & Bilqis Sidibe💅*

🏅6️⃣🏅

Bayan ya gama ne yaja hannun ta yakai ta layin tsakiya seat din gaba ya zaunar da ita tare da kallon wata yarinya da ke zaune a 6angaren seat d'in, wacce kallo d'aya zakayi mata kasan tana da wayo sosai,
yace da ita"Amrah ga qawa na miki amma banda fada da tsokana sbd kan fadan ki ne yasa kowa baya son zama a kusa da ke"kan ya qarasa maganar sa wacce ya kira da suna Amrah ta wani turo baki cike da masifa tana kallon shi, tace"uncle JB........shiii! na da gai gaya miki,mtsw qaramar yarinya da ke sae masifa,cike da alamun zata yi kuka ta kalle shi ta le6ace baki tace "masifa"......no kar kiyi kuka bazan sake kira miki masifa ba amma kar kiyi fada da ita kinji,
yanzu zanje office na zauna ina hango duk abinda kike yi da zarar naga kin tsokane ta zan miki bulala kuma daga yau ba ruwana da ke na daina shiri da ke gabadaya ,girgiza kanta tayi cikin sauri ta ce"ni bazan ma tsokane ta ba,sannan ta riqo hannun Afrah tace "daga yau ke qawa ta ce ba fada a tsakanin mu ko?murmushi Afrah tayi tare da gyada kanta wanda hakan ya bawa JB mamaki,har yana magana a zuci.

Yana cewa _"wacce aka ce kurma ce ya akayi taji abinda Amrah ta fada har da su gyada mata kai"_.

Nan dai ya basar da zancen ya nufi hanyar fita class din sbd hango malami da yayi zai shigo.

Da aka tashi daga makaranta JB yaje har class din su Afrah ya jawo hannun ta yaje da ita domin ganin wanda zai zo daukar ta.

Basu wani jima a tsaye ba sai ga motar farhan ta kunno kai,
Afrah na hango motar ta saki hannun JB ta tafi da gudu kan ta qarasa har farhan ya fito daga cikin mota ya qaraso da murnar sa ya tarbe ta.
Cike da murmushi JB ya qaraso gurin su yana fad'in "'a'ah farhan na husna mai awara!murmushi farhan yayi mai cike da dariya yace"ka fara ko"JB yace to ai gaskiya na fad'a ya fadi haka ne yayin da ya riqo hannayen Afrah yana wasa da su yace " a ina ka samo hadaddar yarinyar nan?kai JB Amanata ce fa ko ka manta da ita?oh sorry Allah ba mantawa nayi ba kawai dai ban ta6a ganin ta ba sae yau,
Farhan yace "haka ne fa inace yanzu ka ganta da kyau kar wata rana kace min baka gane ta ba...na isa bare a yanzu da ta zamo d'aliba ta, nan gaba kuwa mata ta zata zamo inshaAllah,,sosai farhan yayi dariya yace wace ce zata zamo matar ta ka?"Zarah mana" cewar JB wanda ya fadi haka ne yayinda ya nuna Afrah yaci gaba da cewa "ko baza ka bani auren ta ba?Farhan ya girgiza kansa yayinda yake ci gaba da dariya yace "JB baka rabo da abin dariya"JB yace "nifa da gaske nake yi daina kiran zancen da abin dariya"...hm to naji zaka iya jiranta kenan har ta girma?qwarai ma kuwa ai kasan idan ina son abu zan iya yin komai a kansa,farhan yace "to Allah ya nuna mana lokaci sae musha biki....bikin da ba a ta6a irin sa ba ma kuwa cewar JB yayinda farhan ya riqo hannun Afrah yace kaga mu zamu fice domin idan nace na biye ma zamu jima a nan,ni kuwa gashi bana so Afrah ta gaji da tsayuwa har taje ta

fara jin yunwa,JB yace "ok a gaida gwaggo da kuma amarya Amrah kafin yake kallon Afrah yace"bye my wife,Allah nuna mana ranar auren mu"wanda hakan yasa farhan ya shiga mota yana dariya domin duk a tunanin sa da wasa JB keyi ga shi kuwa har ga Allah JB ke zancen.

JINJINA GARE KI *AISHA NUCLEAR*(MAMAN FADEEL) MUNGA SAQON WAQAR DA KIKA MA ONLINE HAUSA WRITERS MUNGODE ALLAH YA BAR ZUMUNCI YA RAYA FADEEL AKAN SUNNA.
ONLINE HAUSA WITERS KECE MIKI LUV U ALL😘

*Futha Luv💅 & Billy giro😊*

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:19PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [7/14/2016] Billy giro😊: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
~*AFRAH KO AMRAH* ~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*Na Bilqis Sidibe💅 & Bilkeesu giro😊*

*Note:*
Ku danna *read more* domin ci gaban page.
_(Munyi haka ne domin wasu basu san da hakan ba)_

🏅7️⃣🏅
Tsaye JB yake yana ma Afrah bye bye har sai da ya daina ganin su sannan shima yaje ya shiga tashi mota.

Yayinda muka bishi domin ganin shi d'an gidan waye.

Unguwàr New G. R .A ya nufa da ke cikin garin baucci layin farko gida na uku,
horn yake tun kan ya qarasa,
cikin hanzari kuwa mai gadi ya wangale masa qatoton gate.

Da shigar sa ya parker mota ba ma a inda ya da ce ba wanda cikin gudu gudu ya qarasa shiga cikin gidan tare da kiran mom!mom!!mom!!!
Oh no momma! wai ina kika shiga ne?

Wata mata muka hango tana saukowa kan staircase mai kyau da ita wacce kallo d'aya zakayi mata kasan tabbas wannan matar manya ce.

Kan taqaraso take fadin lafiya my son wannan kira haka?
Da sauri yaje ya riqo hannayen ta ya kai ta kan kujera ya zaunar ya durqusa kan guiwoyinsa yana mai fuskantar ta yace "mom albishirin ki yau na samo matar da zan aurà daga yau sae ki huta da min qorafi, da murnar ta tace"wow! gud story my dear son, er gidan wace ce?may be kin santa momma,Zarah ce wacce farhan ke riqo,cike da rashin fahimta take kallon shi tace "wace Zarah ce farhan ke riqo? oh no momma to Afrah nake nufi.... Kaddai kace min Afrah er gidan marigayi Alhj Sadiq wacce shekarunta baza wuce shekara biyar ba... Aha momma ita ce wlh... Mtsw Allah ya shirya min kai junaid,cike da shagwa6a
Yace "momma me kuma nayi? Haba my son ya zaka kawo min er shekara biyar kace min ita kake so ka aura nida banqi a cikin satin nan ma a maka aure ba,amma idan kace sae ka jira ta ban san iya lokacin da za'a dauka ba kenan, wata qil ma bana raye,jikin JB yayi sanyi ya wani 6ata fuska kamar qaramin yaro yace"momma ai kinsan mace ce saurin girma ne da ita,cike da alamun rarrashi tace "kaga my Son kayi haquri ka ajiye zancen yarinyar nan ka samo wata dai dai da kai kaji, fuskar nan tashi kamar zai yi kuka ya tashi daga durqushen da yake tare da sakin hannyen maman shi ya kalli mahaifin sa da ke tsaye a bakin qofa wato uncle Basheer yace "father kaji abinda momma take fada ko,
shike nan ni duk na kawo yarinya ace bata yi ba na nemo wata,kuma kullum a dame ni da qorafi naqi na kawo yarinyar da zan aura.
Mamansa ta girgiza kai hade da murmushi domin tasan JB bai ta6a kawo yarinya yace gata da sunan zai aura ba sae a wannan karon da shine na farkon sa.
Mahaifin dai nasa shima murmushi yayi yace "junaid ai yau ne farkon kawo zancen zakayi aure a gidan nan,kuma zancen naka kamar da wasa a cikin sa yarinya er shekara biyar kuma kurma ce fa..... Ni Abba ko ta had'a da makafta ina son ta a haka kawai dai kace min ka amince na jira ta idan ta girma a mana Aure, kaji dad, don Allah Father kar ka ce a'a wlh ni kadai nasan irin yanda nake ji a game da ita duk da cewa qaramar yarinyar ce,amma tun lokacin da ka d'ora ta a gaban assembly na sami kaina da jin sonta fiye da yanda nake jin son sauran yara,kuma ina ji a jikina rayuwa da ita alhairi ne a gare ni,wanda na tabbatar idan ban same ta ba zai iya haifar min da matsala.
Uncle Basheer dai tsaye kawai yayi da mamaki yana kallon JB na zuba masa rashin kunya,
JB yaci gaba da cewa"Father kar ka ce nayi rashin kunya abinda nake ji ne na gaya maka wanda ina jin hakan zai sa ka tausaya min,pleeease! father.
Uncle Basheer ya nisa yana mai ci gaba da kallon JB wanda ya fahimci tabbas da gaske JB keyi yace"nayi maka alqawari junaid indai har yarinyar nan tana sonka idan ta girma to zan aura maka ita
Him!zo kuga JB a wannan lokaci wanda kan tsananin murna sakin baki yayi yana kallon mahaifin sa domin bai zaci abin zai zo masa da sauqi haka ba,dunqule hannyen sa yayi ya jimqe kamar wanda zai naushi wani abu tare da fadin "wuhuu! Father na gode sosai! yaje ya rungume mahaifiyar sa tare da bata kiss a kumatu yace "momma ki qara min godiya a gun Father zan je na kaiwa Granny labarin farin cikin da nake ciki a yau"yana gama fad'ar haka ya fita da gudu yayinda uncle Basheer ya sami guri ya zauna,wanda tun kan ya zauna mahaifyar JB ke kallon shi da mamaki tace "Abban junaid ya zaka biye ma yaron da yau kamar ba a kan hankalin sa yake ba,
Umman junaid ba wani baya kan hayaccin sa,kin fi kowa sanin halin junaid idan ya qwallafa

abu a ransa wanda idan bai sami abin ba kin san babbar matsalar da ke biyo wa baya,kuma kin san irin son da nake yiwa junaid kasancewar shi kad'ai ne d'a a gare mu.
Amma Abban junaid kasan yarinyar nan fa kurma ce bata ji,indai wannan ne mai sauqi ne domin zan iya yin komai na ganin cewa ta dawo normal sbd dama can ba kurma ba ce wata matsala ce tasa ta daina ji domin yanzu haka wani sa'in jin ta yakan dawo mata magana ne kawai da bata iya wanda inshaAllah idan aka fitar da ita qasashen waje zata samu lafiya, kawai abinda nake so da ke ki mana fatan nasara.....to Abban junaid Allah ya sa ayi nasara.

*Futha luv💅 & Billy giro😊*

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:19PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [ 7/16/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
~*AFRAH KO AMRAH* ~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*Na*
*Bilqis Sidibe💅 & Bilkeesu giro*😊

🏅9️⃣🏅
Yakai hannu zai cire mata pant,Afrah ta qanqame jikinta sosai tana kuka tana kuma ci gaba da kallon abinda ke tsakiyar qafafunshi a cikin yanayi na mugun tsoro kamar wacce ke masa kallon qatoton maciji.
ganin abin yana qoqarin ta6a cinyoyinta ne yasa ta daddage ta buga wata uwar kuwar da tasa farhan ya wani irin tashi a firgice ya kai duban sa a gun,wanda hakan ne yasa firgicin sa ya qaru sosai ganin tsirif ya rage a lalata masa rayuwar Afrah,
Da qarfin tsiya ya nufi mutumen ya masa uwar mazgar da tasa ya fad'i qasa wanwas.

Haka shima farhan fad'uwa yayi sbd wani irin tari da ya tunkaro shi ya durqushe nan gurin tare da tofar da baqin jini,daga nan bai sake yin tari ba sae dae gabadaya jikin sa ya saki baya iya ta6uka komai sae numfashi da yake sama sama.

Afrah ta zo da gudu ta fad'a jikinsa tana kuka mai tsima zuciya jikinta sae qyarma yake.
Da qyar farhan ya iya kai hannu ya rungumota hawaye masu zafi na fita a idanun shi yayinda yake gyara mata pant,qara rungume ta yayi yana fitar da ajiyar zuciya mai nauyi kamar yadda Afrah ta rungume shi tana fitar da ajiyar zuciya.....uncle! uncle! ya d'aga kansa cikin sauri

domin ganin Amrah da ke kiranshi,yayinda luqeqen mutumen da Farhan ya mazga ke cewa ku kwantar min da ita idan ya hana ni da qaramar zanyi da babbar.
A rikice yace "don Allah kar ku ta6a min matata ku min ko ma mene ne amma kar ku ta6a min Amrah da Afrah"

Sam basu bi ta kan farhan ba sae qoqarin kwantar da Amrah suke.......

"Ku dakata!cewar wani gaye da tun shigowar su yake zaune kan sofa ya d'ora qafa kan qafa yana shan sigari cikin kwanciyar hankali.
Tashi yayi yaje gun farhan ya durqusa yana mai ci gaba da shan sigari yana busawa Farhan hayaqin sigari a fuska, Afrah da ke maqale a qirjin farhan ta qara cusa fuskar ta sbd ko kad'an bata son ganin fuskokin su.
Yace da Farhan "kaine silar mutuwar mahaifin mu don haka dole ka za6i d'aya daga cikin matan nan,
wacce zamu dauki fansa a kanta domin yau na lashi takobi baza mu bar gidan nan ba har sai munyi kisa a gaban idon ka domin kaji irin zafin da muka ji a lokacin da kasa aka kashe mana mahaifi a gaban idon mu.
Farhan yace "Habib ni ya kamata ku dauki fansa akaina ba akan su ba"

Gayen da farhan ya kira da habib ya shiga kallon farhan cikin yanayi na ka ma raina min da wayo.
Sae dai bai ce da shi komai ba face sigarin sa da ya zuqa yayinda hayaqin sigarin ke fitowa ta bakin sa da hanci cikin yanayin qwarewa,sannan yace "tun farko kai kasa kanka abinda bai gano ka ba,hakan yasa bazan ta6a tausaya maka ba ko na canza ra'ayi,don haka na baka minti biyu ka fad'i *AFRAH KO AMRAH* wacce zamu d'auki fansa akan ta idan ba haka ba wlh zan harbi wacce naga dama ko kuma na kashe su gabad'aya!

*Futha Luv💅 & Billy giro😊*

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:19PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [ 7/15/2016] Billy giro😊: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
~*AFRAH KO AMRAH* ~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*Na Bilkeesu giro 😊 & Bilqis Sidibe💅*

🏅8️⃣🏅
Sai dai da alama ta fadi haka ne kawai don ba yanda zàtayi, amma ko kadan bata ji dadin hukuncin da Uncle Basheer ya yanke ba,bcs sae magana take a ranta,tana mai cewa:

_ni da na matsu naga en jikoki na amma ace sae ya jira er qaramar yarinya har sae ta girma_....uncle Basheer ya katse ta da cewa "ina buqatar ruwan sha bata iya tashi ba sae mai aiki da ta shiga qwalawa kira domin ya bata haushi ba kadan ba,
har ma bata jin zata iya kawo masa ruwan da kanta.

Bayan wasu kwanaki da faruwar hakan, farhan ne zaune a bedside daure da towel iya qugu yayinda Amrah ke bayan sa durqushe akan guiwoyinta tana riqe da d'an qaramin towel tana goge masa gashin kansa har izuwa gashin qirjin sa da yasha ruwa ya kwanta luf,
ita ma towel ne a jikin ta da alama wanka suka fito domin kowannen su yana dauke da digo digon ruwa a jikin sa.
Da ta gama tsane masa ruwan jikin sa ne ta wani lafe a bayan sa kamar wata er baby,ta sakado hannayen ta akan qirjin sa tana yawo da su slowly slowly yayinda idanuwan ta suka fara lumshewa alamar bacci take ji.
Farhan yakai hannu ya shafo gashin kanta yace "yadai Amrah ya akayi? cikin muryar ta wacce ako yaushe baya jin ya gaji da sauraren ta tace"uncle na gaji da yawa ga bacci da nake ji sosai, jawota yayi ya maida ta gefen sa ya zaunar tare da dora kanta a qirjin sa yana mai ci gaba da shafar sumar kanta, yayinda yake kallon fuskar ta cike da kulawa,yace"inace komai kin packer mana wanda zamu buqata?komai na packer uncle, sae dai naji dazun kana waya wanda a cikin wayar da kayi na fahimci kamar ba mu kadai zamu yi tafiyar ba, eh ba kowa bane face JB,
sae dai ban san me zai kai shi ba.
Kawai dai yaji naje ma uncle Basheer da zancen ina so ya hada ni da abokinsa qwarraren likita ne fanni ido da kunne yana zaune a qasar India kasancewar sa ba'indiye,
shine yake ce min dama kuwa yaso yamin zancen akai Afrah gurin shi ko za'ayi nasara tunda dama can ba kurma bace, sae gashi na riga shi zancen , shine yake ce min ba ma likitan kad'ai zai had'a ni da shi ba zai d'auki nauyin komai na ganin ta sami lafiya nace da shi a'a ya barshi domin ba ita kad'ai zan kai ba har da ke sbd kema idanuwanki sun sami matsala ne a sanadiyar ulcer.
To shine fa JB yace zai je ya raka matar shi wato Afrah amma nasan da wasa yake akwai dai abinda zai kai shi.
Uhm bare kasan JB da abin wasa yake,
Lallai wasa yake domin yasan Afrah *Tawa ce* ni kadai bada kowa ba,domin bana jin zan iya bawa kowa *Amanata,*
cike da shagwa6a Amrah ta masa wani kallo tare da bugo qirjin sa tace"uncle ka fara ko"farhan yayi murmushi tare da girgiza kansa ya tashi ya dauko musu kayan bacci ya bata nata sannan ya saka nashi ya nufi gadon Afrah da tuni baccin ta yayi nisa,
Addu'a yayi mata kamar yanda ya saba yi mata a kullum, sannan yaje ya kwanta tare da jawo Amarah a qirjin sa ya rungume suka shiga baccin da ma'aurata kawai keyin sa bada gwauraye ba😜lol!.

Cikin baccin su ne da yayi nisa kuma da alama yana musu dad'i sosai.

Akasin Farhan da yayi minti shida a farke sbd wasu alamomi da ya ke ji a cikin gidan wad'an da ba dai dai ba,kuma abin sae qaruwa yake hakan yasa ya janye Amrah a hankali daga kan jikin sa yakai hannu domin lalubo ma6allar wuta....kamar daga sama Farhan yaga mutum a gaban sa ya hura masa wata farar powder a cikin hançi da ta saka shi tari a nan take ba qauqautawa.

Hakan bai hana
farhan ya kunna wutar dakin ba, gaban sa ne yayi wani irin mugun faduwa ganin taarin mutanen da ke zagaye da shi,wadanda sak sune suka bayyana a cikin mafarkin sa da yayi a kwanakin baya sae gashi a yau sun bayyana a zahiri.

Tarin da farhan keyi ne yasa Amrah ta farka tare da kiran sunan shi yayinda take lalubo eyeglass d'in ta da take ajiye wa kan drawer idan zata shiga bacci,wani irin mugun bugu d'aya daga cikin su ya kaiwa hannun ta wanda yasa ta saki qara sosai tare da sakin eyeglass d'in da ta dauko,

Ya fizgo ta da qarfi sae lalabe take tana"uncle!uncle!!uncle help me!!!

Allah sarki farhan ko kansa ya kasa d'agowa bare yaga halin da take ciki sae dai yana jin kuwar kiran sa da take ta faman yi wanda kan tsananin tarin da yake yasa ya kasa ko d'ago kansa bare ya iya ceto ta.

Amrah bata daina ihun da take ba hade kuma da ci gaba da lalubar eye glass d'in ta cikin sa'a kuwa taji ta taki eyeglass d'in wanda hakan yasa tayi saurin kai hannu ta dauko ta kafa a idon ta nan ta shiga firgici sosai ganin wanda ke riqe da ita kafin take kai idon kan

Wani luqeqen mutum baqiqirin da shi ya nufi gadon Afrah wacce ihun Amrah ne ya tashe ta,ta shiga yin kuka a firgice tana kallon farhan da ke ta faman tari jini na fita a bakin sa.

luqeqen mutmin nan yayi tsaye yana qarewa Afrah kallo wacce ke sanye cikin er fincikar farar rigar baccin ta da ta mata kyau sosai,ga gashin kanta da ya zagaye fuskar ta ya sauko har kan kafad'un ta,sea hasken fuskar ta ya qara bayyana.

Da ya qare mata kallo ne yace"yarinya da ke sae bala'in shiga rai"ya fadi haka ne yayinda yake zare belt d'in wandon sa yace "yau dole kema na gwada aiki na akan ki".

Yana gama zare belt ya bude zip d'in wandonsa ya nufi Afrah gadan gadan kamar wanda yaga cikakkiyar budurwa,

Ya kama rigar baccin ta ya yage tun daga sama har qasa ya jefar ya rage daga ita sae pant,

Afrah kuwa sae kuka take tana ja da baya sbd ta firgita da ganin abin da ya fitar a cikin wandon sa.

Ga shi da Amrah har farhan ba wanda yasan abinda ke shirin faruwa sbd tuni suka cire ma Amrah eyeglass farhan kuwa tarin da yake yi sae abinda ya qaru wanda yanzu kan tari har ya kai kwance dafe da qirjin sa idanuwan sà sunyi jajir,jini se ci gaba yake da fitowa a bakin sa.

Duk irin kukan da Afrah keyi da ganin cewa yarinya ce bai sa wannan gardin yaji tausayin ta ba sae jawo ta da yayi da qarfin tsiya ya manna ta a jikin sa tare da bude mata qafafu.

*Futha Luv 💅 & Billy giro😊*

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

[10:20PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [7/18/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
~*AFRAH KO AMRAH* ~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*Na*
*Bilqis Sidibe💅 & Bilkeesu giro😊*

🏅🔟🏅
Farhan ya kalli Habib da mamaki had'e kuma da ganin son kanshi yayi yawa yace"Habib kenan to ni kana nufin mahaifi na da kuka kashe da kuma matar da kuka harba bata ji ba bata gani ba kun ci bulus kenan.
Habib yace "kwata2 ba sa hannun mu a wannan kisa wata qungiya ce da taje fashi gidan sa suka kashe shi ba mu ba,amma wannan matar ni na harbe ta da kaina sbd zafin kashe mana oga da kuka yi wanda muka dauke shi tamkar mahaifi, amma kuka masa kisan da bai ji ba bai gani ba, bcs fitowa yayi domin jin qarar harbi sae kawai kasa aka harbe shi.
Kaga kuwa ba qaramin taimaka maka nayi ba da har nace ka za6i d'aya, amma idan kasa wasa sae na aiwatar da aiki na a cikin rashin tausayi.

Shiru farhan yayi yayinda gumi ke karyo masa ta ko ina, yana tunanin ta yanda zai shawo kan Habib ya haqura,ya za6i wani abin amma banda kashe, *AFRAH KO AMRAH* domin bai shiryi jin mutuwar ko waccen su a ciki ba, har dai a yanda ya d'auke su matsayin amana.

Shin waye *Farhan*?
kuma ya akayi Afrah da Amrah suka kasance amana a gare shi?

Muje zuwa domin jin labarin.

*Farhan* ya kasance maraye ya tashi ne a hannun gwaggwo koda ya tashi bai san su waye iyayen sa ba kasancewar duk sun rasu yayinda suka bar masa tarin dukiya mai yawa sbd shi kadai ne d'a a gun iyayen shi.
Mahaifin farhan yana da qannai guda biyu,
Alhj usman(mahaifin fu'ad) sae gwaggo ita ce qarama a cikin su domin har yanzu ba wasu shekaru ne da ita ba sbd bata haifi warin farhan ba asali ma bata ta6a haifuwa ba,duk tsawon shekarun da tayi da mijinta kafin ya koma ga mahalicci.
Uncle Basheer wato mahaifin JB,ya kasance yaya a gun mahaifiyar farhan.

Marigayi Alhj Sadiq cewa da mahaifin Afrah maqwabci ne a gun su farhan,kuma abokin mahaifin farhan ne sosai,wanda tun daga kan karatun farhan na primary har izuwa high school da yayi a qasashen larabawa shine ya dauki nauyi,duk da irin dukiyar da iyayen farhan suka bar masa bai yarda aka ta6a ko sisi a ciki ba,acewar sa abar masa abinsa idan ya girma ya mallaki hankalin kansa ya fara juya abin sa ta hanyar kasuwanci.

Kuma Alhj Sadiq ya kasance mai tausayin talakawa da taimakon jama'a duk unguwar kowa ya shaida.
Sae dai yana
da kishiyar uwa da duk abin nan da yake bata gani duk da cewa gabakidaya 'ya'yanta har jikokin ta da ita kanta ba abinda zasu nema a gurin shi su rasa,amma kullum cikin rashin gode masa ta ke,
gashi kusan ince rabin neman sa su yake ma sbd ba shi da d'an uwa ko d'aya kuma mahaifiyar sa bata raye,yana dai da mata qwaya d'aya tal Hajiya Zarah da yake matuqar sonta duk da cewa bata ta6a haifuwa ba kusan shekaru goma da sukayi aure amma kwata2 bai nuna mata damuwar sa ko ya nuna buqatar qaro aure sam ba hakan a ransa ya riga ya barwa Allah komai yayinda suka dage da addu'a shida matar sa Hajiya Zarah.

Hajiya Zarah ta kasance tana samun tsangwama sosai a gun en uwan mijinta sbd rashin haifuwar ta,a yanda suke mata gori kwata kwata kamar sun manta cewa Allah ke bada haifuwa,wanda cikin zagin da suke mata har cewa suke juya baki ganin Annabi,baki haifo ba kin hana shi ya qaro aure ya haifo,
kin magance mana d'an uwa baya ganin kowa da gashi indai zancen ya qaro aure ne sai dai yace haifuwa ta Allah ce shine mai bayarwa,haka duk dukiyar nan tashi sae abinda kika ce yake bamu.
Tun abin baya damunta har yazo ya fara damunta wani lokaci ta shige d'aki tayi ta kuka tana roqon Allah yasa tana da rabon samun haifuwa a duniya,ko zata huta da tsangwamar da dangin mijinta keyi mata.

Da yawan addu'ar da take yi ne wata rana ta tashi cikin tsananin zazza6in da yasa Alhj Sadiq ya shiga damuwa sosai yaje ya kira likita,koda likita yayi en gwaje gwajen sa ya fahimci Hajiya Zarah na dauke da juna biyu.
Sosai Alhj Sadiq yayi farin ciki da jin zancen domin har sadaka sai da yayi.

Tunda dangin sa suka ji labari sukayi baqin ciki sosai domin ba da gaske suke suna son d'an uwan su ya haifu ba,bcs basa son ya samu magaji,
so sukayi su tursasashi ya auri wata er uwar su domin su riqa tatsar sa sannu sannu har dukiyar ta koma hannun su.
Sae dai basu nuna masa baqin cikin su ba sae ma gud'a da suka tarbe shi da ita a lokacin da ya kai musu labari.

Hajiya luba wato Kishiyar uwar sa fantsama tayi gurin bokaye ita da 'ya'yanta domin su samu su zubar da cikin da ke jikin Hajiya Zarah wacce yanzu komai kawo mata suke na marmari,yayinda Hajiya Zarah ke kar6a tana ci domin ganin take yanxu ba wata qiyayya a tsakanin su kuma bata tunanin cewa suna saka mata wani abu a ciki.
Duk irin barbaden da sukeyi mata a cikin abinda suke kaimata bai sa cikin ta ya zube ba sbd Hajiya Zarah mai yawan addu'a ce ita da mijinta.
Cikin ikon Allah kuwa cikin har ya kai wata tara yayinda en uwan mijinta ke ci gaba da faman

fad'i tashi gurin bokaye na ganin cewa an haifu abin bai zo da rai ba.

Ranar wata litinin Hajiya Zarah ta tashi da wata matsananciyar naquda,wanda cikin gaggawa Alhj Sadiq ya kaita asibiti, sae dai tasha wahala sosai kafin ake samu ta haifu.

Cike da murna Alhj Sadiq ya shiga dakin da aka kaita domin hutawa,murnar sa ce ta qaru ganin har 'ya'ya biyu kwance kusa da ita.

Sae dae d'ayar tafi kama da Hajiya Zarah da kuma kyau da qiba ga shiga rai hakan yasa ya kai hannu had'e da bissimilla ya dauke ta yayi mata addu'o'in neman tsari.

Da ya gama ne ya ajiye ta zai dauki dayar,sai wayar sa ta shiga qara yayi saurin barin dakin domin kar ya tashi Hajiya Zarah da ke bacci.

Bai san cewa wayar na fara ringing ta farka ba, wanda binshi kawai tayi da ido har ya fita daga d'akin.

Takai hannu ta shafi kan 'ya'yanta hade da basu kiss a goshi,d'agowar da zatayi ne ta had'a ido da wata mata da ke leqen ta ta window, matar sae kallon jarirran take tana murmushi yayinda hawaye ke sauka a kumatun ta.

Hajiya Zarah tace "baiwar Allah lafiya? murmushi kawai tayi ta share hawayen ta da gefen zanin ta da ta yafa sannan tace"ba komai 'ya'yanki ne kawai suka bani sha'awa,Allah ya raya miki su akan sunna,sae da ta kalli yaran kafin take cewa "amin"

Ta dago domin sake kallon matar sae wulgawar ta kawai ta gani.

Alhj Sadiq ya d'an jima kafin yake dawowa,
yana shiga d'akin ya shiga tsananin rud'u ganin wuqa da6e a cikin Hajiya Zarah kuma babu jaririya d'aya.

"Innalillahi wa inna ilahi raji'un shine abinda ya shiga maimatawa"yana ja da baya yayinda miyon bakin sa ya tsinke gabadaya sae wani irin gumi da ke keto masa ta koina.

En uwan sa ne sukayi kici6is da shi a bakin qofar dakin wanda sae yanzu ne shigowar su asibiti.

Sosai sukayi mamakin ganin abinda ya faru da Hajiya Zarah wanda har ba a iya fahimtar farin ciki sukayi ko baqin ciki.

Gun Alhj Sadiq kuwa kallo d'aya zakayi masa kasan ya shiga tashin hankali sosai.

Bayan wasu kwanaki da faruwar hakan anyi iya bincike na ganin cewa an gano wad'an da suka kashe Hajiya Zarah da kuma sace jaririya d'aya da akayi amma ba a gano komai ba.

Sae wani shirme da yaji a gun nurses d'in da suka kar6i haifuwa cewa wae Hajiya Zarah ba 'ya'ya biyu ta haifa ba d'aya ce,bai ce da su komai ba domin tunda aka binne Hajiya Zarah bai sake cewa da kowa komai ba sae jimami da yake fama da shi, kuma zancen su ya dauke shi a shirme da kuma rashin sanin wacce suka kar6i haifuwar ta.

🏅1️⃣1️⃣🏅

Da kwana hud'u ne farhan ya dawo daga qasashen waje domin ya kammala karatun sa na likita.
Sae dai yayi baqin ciki sosai da ya riski mummunan labarin da ya saka shi kuka domin Hajiya Zarah ya dauke ta tamkar mahaifiya kamar yadda ya dauki Alhj Sadiq mahaifi.

Tunda aka bawa farhan jaririya domin ya ganta kallo d'aya yayi mata ya fashe da kuka yayinda tausayin ta ke qara shiga a cikin zuciyar sa.

Ranar suna ba wani biki aka yi ba yarinya taci sunnan mahaifiyar ta wato "Zarah" aka yi mata laqami da suna"Afrah"

Tunda aka yi biki ako yaushe zaka sami farhan dauke da Afrah domin ji yake kamar qanwar sa ce ta jini, har ma baya son wani abiñ da zai raba su, amma dole idan lokacin bacci yayi yakan miqa ta gun mahaifin ta.

Shekarar Afrah d'aya Farhan ya fara zuwa da ita duk inda zai je, shiyasa Afrah ta saba da shi sosai har ba ta son azo kar6ar ta sbd yanzu mahaifin ta yayi aure yayinda ya auri er uwar su wacce dangin sa ke son ya aura, shiyasa da dare yayi se ta matsa a mayar da Afrah wanda bata yin haka sae a gaban Alhj Sadiq domin kawai yace tana da kulawa.
Farhan baya mai da ta sae tayi bacci domin yasan irin kukan da take idan yaje maida ta bata yi bacci ba.
Gashi ko kad'an baya son jin kukan ta domin idan tana kuka wani abu yake ji a tsakiyar zuciyar sa mai zafin gaske.

Farida shine sunan matar da Alhj Sadiq ya aura wacce ta biye ma en uwan sa ta shiga tatsar kudin sa son ranta wani lokacin ma bata tambayar sa kudi sae ta d'ebi abinta shi kuwa ba ganewa yake ba.

Abinda yake d'aure mata kai da dukiyar shi duk irin dibar da take yi ma dukiyar sa bata raguwa sae qaruwa ta ke, gashi yanzu ba qananan kudi take kar6a a hannun sa ba sbd qaryar cikin da ta masa shiyasa baya jin shamaki ko nawa ta tambaye shi bata yake.
Kuma duk abin da ya bata da wanda ta d'iba sae ta kaiwa su Hajiya luba wai acewar a riqa tarawa har a kar6e dukiyar gabad'aya.

Ganin sunyi shekara biyu suna tatsar sa amma dukiya kamar qaro masa ake abin ya d'aure musu kai sosai suka tafi gurin bokan su, domin ya duba musu kodai dukiyar tsafi ce Alhj Sadiq ke fama da ita.
Boka ya gama duban sa yayinda yake sanar da su,cewa "ba wani tsafi a cikin dukiyar sa,kuma indai dukiyar sa ce basu ma d'ibi komai ba.

Haka suka koma gida yayinda ko wannen su ke dauke da tunani kala2 a cikin zuciyar sa,wanda kafin su shiga bacci sae da sukayi meeting.

Washe gari farhan ne a cikin mota yayinda hancin motar sa ke qoqarin shiga gate d'in asibitir da yake aiki.

Sae dube dube yake can ya hango wasu tafe mabarata guda biyu uwa da er ta suna tafe yayinda er ke riqe da sandar mahaifiyar ta tana mata jagoran ci.

Wani irin lallausan murmushi farhan ya sake ya fito motar ya nufi inda suke, ya kar6i sandar da ake mata jagoranci yace"haba mama ya akayi kuka makara da zuwa har na zaci baza ku zo ba,

Hawaye ne zar suka fito a fuskar matar,

farhañ yayin saurin kalloñ er ta yace"Amrah me ya sami mama? Kauda fuskar ta tayi gefe tana tattara hijabin ta da gabaki dayan sa ya yage da zarar ta sake shi zai iya fad'uwa,cike da tausayi farhan ke kallon yanda hawaye ke d'iga a hannun ta,ya kalli tun daga kan wuyan hijabinta har zuwa inda ya tsaya a tsage yake kuma yana da tabbacin jiya ba haka yaga hijabin ba,yace"Amrah me yake faruwa ya akayi hijabin ki ya yage, bata iya cewa komai ba sae sautin kukan ta da ke son fitowa"maman tace" wani yaro ne ke takura ta sosai kullum idan ta dawo daga makarantar boko sae ya tare ta wai shi sonta yake ya kama fada mata maganganu marar sa dad'in ji,kullum bata kula shi,shine yau ya nemi ya tozar ta ta,ta hanyar yaga mata tufafin jikinta wanda har ya fara yaga mata hijabi ne yana qoqarin yaga mata rigar jikinta Allah ya cece ta ta fizgi jikin ta tazo gida ba ko hijabi a jikinta,sae da zamu fito ne gashi bata da wani hijabi da zata saka dole muka bi wannan hanyar ko zamu ga hijabin,ba ta ga hijabin ba sae yaron da ke takura ta ta gani yazo ta gaban ta tare da yafa mata hijabi yana qoqarin jan hannun ta yayan shi ya hana shi hade da fadin indai wannan yarinyar ce ya kwantar da hankalin sa yau zai kai mai ita da dare.

Tana kawo wa nan tayi shiru tare da share hawaye tace "dan Allah d'an nan ka taimaka min kar su sace min ita,

ita kadai ta rage min wacce nake jin sanyi a gun ta, da ita nake yawon neman abinda muka sawa cikin mu.

Idanuwan farhan suka ciko tap da hawaye sbd wani irin tausayin su da yaji ya kalli Amrah tare da fadin kinsan sunan yaron?cikin muryar kuka ta ce "eh"sunan shi "J" yayan shi kuma Habib, dama kin san su ne? Eh sbd gabadaya anguwar ba wanda bai san su ba, shi ke nan Ku kwantar da hankalin ku zanje unguwar ta ku na musu magana inshaAllah ba abinda zai faru.

Nan mamn ta mishi godiya yayinda wata mota ta shiga yiwa motar farhan oda da ya bari a bakin gate.

Farhan yace da su "ina zuwa mama"

Yaje ya shigar da motar shi tare da parker ta gurin da ake parker motoci.

Ya fito kenan cikin mota wani gaye da ke sanye da kayan likita wanda shima Parker motar sa yayi yace da farhan "wai kai a ina kasan mutanen nan da kullum sae ka tare min hanya a kan su? Dan guntun murmurshi farhan yayi yace "wani taro aka gayya ce mu nida wani aboki na a wata makaranta kan wani quize competition da za ayi, to acan ne naga er kasancewar ita ce tazo over roll position,kuma nine wanda ya bata kyauta,but d way yanda ta kar6i kyautar cike da ladabi da biyayya ya bani sha'awa sosai har na sami kaina da qara mata tawa kyautar.

Sae gashi ranar bayan an tashi daga school ni kuma zan shigo asibiti na gansu tana janye da mahaifiyar ta na dauka cewa zasu je ganin likita ne nace su shigo mota na rage musu hanya domin kafin su qarasa daga cikin asibitin da nisa, sea er tace "min uncle ba likita zamu je gani ba dama muna bara ne a bakin asibitin"da mamaki nace "bara ina kudin da kika samu a kyautar da aka baki"sae da tayi shiru kafin take bani amsar cewa "mun biya kudin haya da ake bin mu na wata biyu sannan na biya kud'in makaranta" nace, "yanzu kenan ko kud'in abin ci ba ku da shi? gyada min kai kawai tayi yayinda na zaro three thousands na basu sbd su kadai ne a aljihu na kuma na manta ATM card d'ita a gida shine nace "don Allah gobe suyi haquri su zo ina so zan gansu" to shine d next day suka zo abin takaici na dauko ATM card kan sauri na manta da ita kan bed, to shine na qara basu haquri kan suzo yau shine ka gan mu a tsaye.

Gayen yace Allah sarki wlh har sun ban tausayi, kuma inshaAllah gobe zan baka tawa gudunmuwar sae ka basu,sbd yanzu bana da wasu isasshin kud'i,
farhan "yace yayi ba matsala sun gode sosai.

🏅1️⃣2️⃣🏅
Kafin daren wannan ranar sae da yaje unguwar su Amrah yayin da ya cika bayan motar sa tap da kayan abinci bayan maqudan kudin da ya basu a d'azun.

Sosai mahaifiyar Amrah tayi farin ciki har kuka sai da tayi.

Farhan bai bar anguwar ba har sae da yaje yaga "J"da kuma yayan shi Habib yayi musu magana cikin lalama kan don Allah su tausaya musu ko don halin da suke ciki na rashi.

"J" da Habib tamkar basa gurin yayinda farhan keyi musu magana domin sau d'aya suka d'ago Kansu suka kalle shi basu sake kula shi ba sae zuqar sigarin su da suke.

Hakan yasa farhan yaji haushi yace duk suka kuskura suka ta6a lafiyar er mutane sae sun gani domin sae yasa an d'aure su,nan ya baza musu qurar motar shi ya fice.

Da dare Alhj Sadiq na bacci shida er sa Afrah da ko yaushe tare suke baccin su yaji ana tayar da shi.

Ya bude idon sa yayinda yake fitar da addu'a a bakin sa,sae kawai yaga an dauki Afrah tare da kunna hasken dakin,mutane biyar ya gani a zagaye da shi ogan ne ya dauki Afrah ya d'ora mata bindiga a kunne ya kalli Alhj yace "dukiya ko er ka ka za6i daya"

Alhj Sadiq na qoqarin furta magana,ogan ya katse shi da cewa"idan ka furta kalma d'aya zamu harbe er ka da kai kanka kuma mu kwashe kaf dukiyar gidan nan.

Alhj Sadiq yayi shiru yayinda yake tunanin cewa tabbas Afrah tafi masa komai a duniya kuma idan ta mutu ta mutu kenan ba zata ta6a dawo masa ba amma ita dukiya Allah kan iya dawo masa da ita fiye ma da wacce yake da ita yanzu.

Ganin ya jima bai ce da su komai ba ogan ya kai hannu gun ma6allar bindiga yana qoqarin ya danna Alhj Sadiq yayi saurin cewa"ku dakata na amince ku bani 'yata ku dauki dukiya.

Ogan yayi wata irin kafurar dariya yace ka kuru ashe kana son er ka! nan ya jefa masa Afrah wacce sae tsala ihu ta ke.
Yace oya ka fita daga gidan nan domin gidan ya daina zama naka har abada.
Ba musu Alhj Sadiq ya tafi sauri sauri har yana had'awa da gudu ya fita daga gidan, su kuwa kome suka tuna sae bin bayan shi sukayi da gudu

Farhan yana cikin baccin sa da bai riga yayi nisa ba ya tashi firgigit kamar wanda aka tsakura.
Ya figi jallabiyar sa ya saka yaje ya shiga mota bai zarce koina ba sae gidan su Amrah koda yaje ya sami mamar sae kuka take tana kururuwar aka wo mata agaji sun sace mata 'ya,
gabadaya farhan ya shiga rudu kan jin abinda take fad'a gashi ba halin ya tambaye ta inda suka nufa tunda makauniya ce.
Cikin sauri ya saka ta mota bai zarce koina ba sae police station,yayin da aka had'a shi da motar en sanda domin gaggawar nemo inda suke kafin su aiwatar da mugun nufin su akanta.

Tafe suke cikin gudu yayinda motar en sanda ke ta faman jiniya.

A wahale Alhj Sadiq ke gudu yayinda shedar sa ke neman d'auke wa,
ya hango motar sae hannu yake mata yana mai waiwayar bayan sa a rikice.

Kafin su farhan su dakata domin ganin wanda ke neman taimako sae qarar bindiga suka ji an harbi Alhj Sadiq nan ya fadi shida Afrah wacce ta saki wata irin qara cike da firgici ta sume a nan gurin.

Da gudu farhan suka qaraso shida police,
Sosai farhan ya shiga rudu ganin Alhj Sadiq wanda a nan take idanuwan sa suka rikid'e zuwa ja,d'agowar da zaiyi ne ya hango wanda yayi harbin nan farhan yace da en sanda shoot him!ba wasa kuwa d'ayan d'an sanda ya kai maisa harbi wanda ba don duqewar da yayi ba da a qafa za'a same shi sae aka same shi a wuya ai kuwa nan take ya fad'i qasa matacce yayinda suka ji kururuwa mai qarfin gaske had'e da fad'in father!!sae duk en fashin suka fito a ma6oyar su, suka yo kan ogan su da aka harbe,cikin zafin nama d'ayan su ya aiko harbi wanda yayi dai dai da fitowar mahaifiyar Amrah sbd ihun Amrah da taji,nan harbin ya sauka akan qafar ta wanda hakan yasa en sanda suka tafi da gudun su, kan su qarasa har en fashin sun d'auke gawar ogan su suka saka a mota suka bar gurin a tsiyace ba tare da sun bi takan Amrah da ta fito a cikin motar ba,
Amrah kam taje da gudu ta fad'a kan mamar ta tana kuka mai tsima zuciya.

Farhan kuwa hankalin sa ne ya rabu gida gida duk ya rikice ga Alhj Sadiq kwance cikin jini ga Afrah a some ga kuma mahaifiyar Afrah da aka harba.

Farhan na qoqarin tashi Alhj Sadiq ya riqo hannun shi yana numfashi a wahale ya riqo hannun Afrah ya had'a da na farhan yana mai cewa "Farhan ga qanwar ka na baka amana bana so ta rayu tare da kowa face kai,domin kai kad'ai ne wanda nafi yarda da shi a duk duniya,

yana kawo nan kawai ya shiga yin Kalmar shahada sae kawai hannun sa ya saki komai nasa ya daina motsi.

Nan farhan ya shiga jijjiga shi yana kiran Abba! Abba!!Abba!!!ina rai ya riga yayi halin sa,nan farhan ya shiga yin kuka kamar mace.

Da safe Farhan ya ajiye Amrah a asibiti wanda kallo d'aya zakayi mishi kasan yayi kuka bana wasa ba.

Kudi ya zaro ya miqa wa Amrah da har yanzu kuka take yace"Amrah kiyi haquri takai ci na d'aya rashin nasarar cafko su da ba'ayi ba Amma in Allah ya yarda mama zata ji sauqi, tun da kinga yanzu za'a shiga theater da ita wanda naso ace da ni ciki amma bazan samu shiga ba sbd jana'izar da zanje.

Gyada kanta tayi tare da yi mishi godiya sannan ya fice.

Sae da ya jima kafin yake dawowa jiki sa6ule ya qarasa gurin Amrah da ya hanga sae faman rusar kuka ta ke farhan yace"Amrah lafiya ina mama?cikin kuka tace uncle wai mijin mama yazo ya tafi da ita ba tare da an mata aiki ba, dama mama tana da miji ne?gyada masa kai tayi kafin yake cewa to meyasa bai je da ke ba?sbd ni ba er sa ba ce?farhan yayi shiru kamar mai son cewa wani abu sae kuma ya fasa,

Sae tunani yake yanda abubuwa suka cakud'e masa lokaci d'aya ga mutuwar Alhj Sadiq ga shi an nemi en uwan Alhj Sadiq an rasa sun gudu gabakid'aya har matar shi da kuma dukiyar sa kaf,ba kuma wannan kad'ai ba yanzu kwata kwata Afrah bata ji tun lokacin da ta farfad'o daga doguwar sumar da tayi,kukan da Amrah ke ci gaba da yi ne ya dawo dashi daga dogon tunanin da yake yace"ki daina kuka nasan idan hankalin mama ya dawo zata dawo ta d'auke ki,yi shiru ki daina kuka kinji,nan yaci gaba da rarrashin ta wanda da qyar farhan ya samu Amrah ta daina kuka tabi shi gidan su.

Bayan sati daya da faruwar hakan Amrah kam sae bud'ar ido take mamar ta tazo amma shiru wanda hakan ne yasa ta qara shiga damuwa kullum cikin kuka bata cin abinci.

Ko yanzu kwance take cikin d'akin da aka bata masauki sae faman rusar kuka take.

Farhan ya shiga da sallama ta amsa yayinda take share hawaye ya samu guri ya zauna tare da Afrah dake maqale a kafad'ar shi.

Yace"Amrah a gaban idon ki ne mijin mama yazo ya d'auke ta? Aa na d'an d'aga dana dawo ne likitawa ke sanar dani kan cewa ba yanda basuyi ba kan ya haqura har a mata aiki yace a'a, olryt inace kinsan garin da mijin mama yake ko? Eh na sani,that's gud ki shirya zanje na kai Afrah asibiti idan na dawo sai mu je.

Nan ya fita daga dakin yayinda gwaggwo ke qoqarin shiga dauke da abinci.

Koda farhan ya dawo ya samu har ta shirya shi kadai take jira.

Sae dae zuwan su garin bai anfana musu komai ba sae baqin ciki,sabida labarin da suka ji kan

cewa tuni mijin mama yabar garin yau kusan shekara d'aya kuma ko garin da ya koma baya can sbd kasuwanci yake baya tsayi guri d'aya.

Amrah kuka take tun kan hanya har suka zo gida sbd bata da wasu en uwa da zata je gurin su mahaifiyar ta kad'ai ce kuma yanzu ta rasa ta.

Farhan kuwa sae lallashin ta yake haka ita ma goggwo ta kama mishi.

Amma Amrah tamkar rarrashi qara mata kukan yake wanda har akayi kusan sati uku Amrah bata daina aikin kuka ba,
ba dare ba rana kuma duk yadda akayi da ita bata cin abinci,wanda rashin cin abinci ne ta shiga ganin bishi bishi har tazo bata gani,koda akaje asibiti suka ce tabbas yunwa ce ta mata illa domin dama can tana tare da yunwa.
Ba yanda farhan bai yi ba na ganin ta warke amma abu ya faskara kamar yadda ita ma Afrah abu ya faskara sae magani da suke ta faman sha kullum.

Kwanaki sun ja yayinda lokaci yake qara tafiya zaman da Amrah take a gidan su farhan ya kawo so da shaquwa tsakanin farhan da Amrah.
Sae dai wani abu da kowa bai sani ba shine Kusan kullum sae Habib ya turowa farhan text na barazana akan sae ya d'auke Amrah da kuma daukar fansa kan ogan su da aka harbe.
Farhan sae dai yayi tsaki,yayinda yake cike da son ya gano ma6oyar su ko hukuma zata yi nasarar cafke su.

Sanin cewa da gaske zasu iya sace Amrah domin har tare ta sun ta6a yi wani lokaci da ta je kasuwa wanda jin haka ne yasa farhan ya nemi a gaggauta d'aura musu aure ba tare da ta kammala secondary school ba.

Haka ko akayi domin cikin sati d'aya farhan ya angonce da matar sa Amrah.

Wannan kenan.

A nan muka kawo qarshen labarin.

sae ku biyo mu domin jin yanda farhan zai qarasa da su Habib.

*Billy giro😊 & Futha Luv💅*

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:20PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [7/19/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
~*AFRAH KO AMRAH* ~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*Na*
*Bilkeesu giro😊 &Bilqis Sidibe💅*

🏅1️⃣3️⃣🏅
Farhan ya dawo daga dogon nazarin da yake ya kalli Habib yace"kayi haquri Habib a bisa rashin sani ne yasa na ce a harbe shi domin duk a tunani na shine ya harbi Abba...Farhan kenan tun farko da baka kira motar police ba da duk hakan bai faru ba.
Kasani nasan cewa nine ka daukowa motar police sbd na dauke Amrah.
Tun lokacin da ka fito gida kaje gidan su Amrah ku ka fice police station duk ina sane.
Sa'a kawai kuka ci kai da motar police d'in,
domin ba don Alhj Sadiq ya tare ku kan hanya ba,da kuna kawo wa saitin ma6oyar mu baza ku kai labari ba har abada,domin tarkon da muka had'a muku ba wanda zai rayu a cikin Ku.
Kuma shisshigin da kayi na raba Amrah da J hakan zai sa bazan ta6a lamunta maka ba.
Sbd tun lokacin da ka aure amrah ka lalata min rayuwar qane na, ya zamo ba yada wani amfani sae kwanciya, kwanciyar da bazai iya tada kan shi ba sae an tayar.
Wanda ba don jinyar sa da nake ba da tuni na manta cewa na dauki fansa a kan ka.
Ka had'a min zafi biyu a lokaci d'aya ka kashe mana oga kuma Amrah ta koma hannun ka, kasani J ya fika son Amrah fiye da yanda kake tunani!domin J bai ta6a son wata 'ya mace da har yaji yana son aurenta kamar Amrah ba.
Domin ko dauke ta da mukayi ba muna nufin cutar da ita ba sae don a d'aura mata aure da J,sbd na fahimci da gaske yake sonta shiyasa na jajir ce na ganin ya mallake ta.

Amma sae kazo ka lalata mana lissafi.

Qyar farhan ke kallon Habib da yayi shiru alamar ya kawo qarshen zancen sa.
Yace "naji J da aure yake son Amrah amma haka kawai kai tsaye ake d'aura aure ba yardar yarinya ba izinin iyayenta.
Sannan kasan irin halin da Amrah zata shiga ita da mahaifiyar ta na aura mata yaron da baya da halin  kirki kuma baya da niyar gyara hali,wanda idan ya aure ta lalata mata rayuwa kawai zai yi,domin Amrah yarinya ce wacce duk namijin kirki zai so ta kasance matar shi.

Habib koda ace ban auri Amrah ba,ba shi zai sa ka samu damar auradda ita ga J ba,domin indai ina raye bazan ta6a bari J ya auri Amrah ba.

Wani  fari da ido Habib yayi yana mai ganin tirzawa irin ta farhan yace"lallai farhan wuyan ka yayi qwari kai da kake neman na haqura shine har ka sami damar gayan min wannan zancen.

Kauda kansa kawai farhan yayi yana mai cike da jin haushin Habib wanda har jin yake da yana jin qarfi a jikin sa da sae dae ya fafata da shi ba zancen bashi haquri,sae dae kash sun riga sun kashe masa qarfin jiki da sinadarin powder da suka shaqa masa.

Hakan zai sa ya haqura yaci gaba da bashi haquri duk da cewa bada haquri ga azzalumin mutum baya daga cikin tsarin sa.
Amma zai yi hakan ko don kare lafiyar Afrah da Amrah.

Maida duban sa yayi gun Habib da yaje kan sofa ya zauna tare da d'ora qafa kan qafa ya kunna sigari.
Wanda sae da ya zuqi sigari ya busar sannan yace "farhan lallai yau zan nuna maka ni ba mai imani bane.
Idan tantama kake to yau zaka fahimci hakan da gaske.
Sbd ka ta6o ni inda ba a ta6o ni.

Farhan ya nisa ya lumshe idon sa cike da damuwa yace"na roqe ka Habib kar ka ta6a min lafiyar *Afrah ko Amrah*ko ma me zakayi ka aiwatar da shi akaina.

Cike da murmushin mugunta Habib ya sauke qafar sa da ya d'ora kan d'aya,
yace "na yafe maka laifi d'aya amma bazan yafe maka d'aya ba.
Gama fadar hakan keda wuya ya saita bindigar sa yayinda wutar gidan ta d'auke d'if wanda yayi dai dai da tashin qarar bindiga.
Afrah da ke jikin farhan ta buga wani irin razanannen ihu.

Yayinda dariyar Habib ke fitowa.

A firgice farhan ke lalubar Afrah da yaji ta saki gabad'aya bata motsi,sae wani d'umi da yake jin yana sauka kan jikin sa.

*Futha Luv💅&Billy giro😊*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:20PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [ 7/20/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
~*AFRAH KO AMRAH* ~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*Na*
*Bilqis Sidibe💅 & Bilkeesu giro😊*

🏅1️⃣4️⃣🏅
Ga kuma wani nishi da yake jin yana fitowa ta bayan sa.
Wanda hakan ya qara rikitar da shi,yayi yunqurin tashi domin neman fitila.
Bai riga ya tashi ba haske ya bayyana a d'akin,ya kai duban sa cikin sauri gun Afrah da ke kan jikin sa, wacce ya shiga dube dube a jikinta ba alamar harbi, somewa ne kawai tayi domin tsorata da jin qarar bindiga har ta masa fitsari a jiki.
Ajiyar xuciya ya sauke mai nauyin gaske,

sannan ya d'ago idon shi domin kaiwa Habib duba sae yaga wayam ba kowa a d'akin duk sun fita,har Amrah ma bai ganta ba.
A rikice ya tashi yakai Afrah kan sofa ya kwantar,
juyowar da zai yi ne ya hango Amrah kwance dafe da gefen cikin ta.
Kan bed ya hau tare da tallabo ta jikin sa,
yakai hannu ya yaye mata sumar da ke kan fuskar ta tare da 6alle abin da suka rufe mata baki da shi,
a hankali ta shiga bude idanun ta yayinda bakin ta ya fara motsi kadan kadan,
wanda da qyar ta iya furta "un..cle" hade da fitowar hawaye zar a idonta.
Cike da damuwa farhan yace"my Amrah"...
sae kuma ya kasa cewa komai sbd hannun sa da yaji ta d'ora kan inda suka harbe ta,idanun sa ne suka ciko tap da hawaye yayin da ya tsure gurin da kallo sae jini ke fita a gun,bakin sa na rawa haka ma duk jikin sa ya d'auki rawa yace"my Amrah bari nazo muje asibiti kinji"riqo hannun sa tayi ta girgiza mishi kai tace"no uncle,ni fuskar ka kawai nake son gani" a hanzarce ya tashi ya nemo eyeglass d'in ta a tsakiyar d'aki ya saka mata,
Kallon fuskar shi take ba ko qyaftawa,kamar yadda shima farhan ke kallon ta,
a hankali ta d'ago hannun ta da ke dauke da jini sha6e sha6e,ta shafi gefen fuskar shi yayinda idanun ta suka fara lumshewa hawaye kuwa sae rigangan fitowa suke"forgive me uncle"shine abinda ya fito daga bakin ta.
Saurin jijjiga ta yayi yace"no Amrah don Allah kar ki rufe idon ki, ki bari muje asibiti kinji"....ka yafe min uncle ni bazan rayu ba...waya gaya miki my Amrah zaki rayu har ma ki haifo min 'ya'ya...mutuwa zanyi uncle,kuma inaji a jiki na ummana zata zo nema na idan tazo kace ta yafe min,hawaye ne suka zubo sha6e sha6e a kumàtun sa,
ta share masa hawayen tace"ba kuka nake so ba uncle,ni addu'a nake so ka min"ta fadi haka ne yayinda take kallon wani gefe dauke da murmushi a fuskar ta.
Ashe Afrah ce ke qarasowa gurin su,tazo sae rarraba ido take tana kallon farhan da ke kuka, sae kawai d'an qaramin bakin ta ya bud'e a hankali tace"uncle meyasa kake kuka anti bata da lafiya ne? Da mamaki farhan ya kalli Afrah yace"Afrah magana kike yi please kice da Aunty kar ta tafi ta bar mu kinji.
Afrah ta kalli Amrah da ke kwance, sae
dae bata ce da ita komai ba face Amrah da ta riqo hannun ta ta had'a da na Farhan tace"uncle ina son rayuwar ka da Afrah,n i Luv u uncle I luv u so much!" daga haka bata sake cewa komai ba sae bakin ta da ke motsi kamar mai addu'a,ta rufe idonta ruf,sae kawai ta saki hannayen su, a rikice farhan yace "no Amrah I Luv u more please dont leave me!
"Amrah!!Amrah!!!jijjiga ta yake sosai yana kiran sunan ta,wani irin kuka ne ya qara zo masa ya rungume ta sosai.
"Uncle" cewar Afrah ganin mutanen da ke shigowa d'akin.
Gwaggo ce,dasu Habib had'e da en sandan da ke bayan su.
Gwaggo taje da qyar ta 6an6are Farhan daga jikin Amrah,tana mai lallashin sa, do'ra kansa yayi kan kafadar gwaggo yana kuka kamar qaramin yaro yana mai cewa"gwaggo kinga Amrah ta tafi tabar ni shike nan daga yau bazan qara ganin ta ba,gwaggo shike nan bazan sake jin sautin muryar Amrah ba.
Hawaye ne suka zubo a idanun gwaggo yayinda take shafa kan farhan,tace "farhan kayi

haquri dama haka rayuwa ta ke, idan kaine yau gobe ba kai ba ne.

D'aya daga cikin police ne ya qarasa gun gawar Amrah yayi dube duben sa yaga tabbas lallai ba rayuwa a tare da ita nan ya girgiza kan shi had'e da jawo bedsheet ya rufe gawar.

Sannan suka tasa qewar su Habib gaba wad'an da hannayen su har qafa duk an sanya musu sarqa gudun kar su gudu.

Tun da gwaggo ta fara lallashin farhan had'e da yi mishi nasifa, sae yayi shiru kukan ya daina zo masa gabadaya,
sae kallon gawar Amrah yake wacce aka rufe da farin bedsheet ya kafe idon shi guri d'aya wato gefen cikin ta da aka harba wanda har jini ya 6ullo kan farin qyalle da aka rufa mata.
Ganin baya da niyar daina kallon gurin yasa gwaggo ta jawo hannun shi dana Afrah suka bar dakin.

*Futha Luv💅 & Billy giro😊*

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:20PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [ 7/21/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
~*AFRAH KO AMRAH* ~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*Na*
*Bilkeesu giro😊& Bilqis Sidibe💅*

🏅1️⃣5️⃣🏅
Washe gari bayan an dawo daga gurin jana'iza.

Mutanen da suka zo ma gwaggo gaisuwa sae jimamin yanda abin ya kasance suke.
A nan gwaggo take musu bayani ko ita ta tashi sallar dare ne sae taji a ajikin ta gidan kamar ba lafiya,har tana jin kamar hayaniya a 6angaren su farhan koda taje sae taji duk irin abubuwan da ke shirin faruwa tsakanin farhan da en fashi,wanda hakan yasa tayi hanzarin komawa ta dauki waya ta kira police sae dae koda suka iso har sun aiwatar da nufin su.

A 6angaren farhan kuwa tunda aka dawo daga gurin jana'iza yaji komai ya dawo mishi sabo har ma ya kasa zaman kar6ar gaisuwa ya shige d'aki ya had'e kai da guiwa sae kukan zuci yake.
Yana cikin haka ne sae ga JB riqe da Afrah,ya shigo da sallamar sa.
Farhan ya d'ago idanuwan sa da sukayi jajir cikin raunin murya ya amsa sallama, yayinda JB ya sami guri ya zauna,yace"farhan kayi haquri kazo muje gurin zaman kar6ar gaisuwa bai kamata ace mutane na zuwa basa samun ka ba.

Farhan ya kalli Afrah da ke kallon shi kamar wacce zatayi kuka,wanda tun jiya yake ganin yanayinta haka, duk da cewa yasan bata san meye mutuwa ba amma yanayin ta kamar wacce tasan mutuwa, yace da JB ka maida Afrah cikin gida sae kazo muje.

JB yace "zarah zo muje gun gwaggwo"maqale kafada tayi tace"um um uncle ka tafi kawai ni gurin uncle d'ina zan zauna"farhan ya nisa tare da jawo hannun ta yace"ki bishi kinji,an jima zan je gurin gwaggo na d'auko ki.

Nan ta gyd'a kanta JB yaja hannun ta suka fice.

Koda JB ya dawo ya sami fu'ad yazo gurin farhan a tare suka fice gurin zaman kar6ar gaisuwa.

Sae guraren qarfe goma farhan ya sami komawa cikin gida sbd sae a wannan lokaci en kar6ar gaisuwa suka watse.

Yana zuwa ya shiga toilet ya watsa ruwa ya fito kenan ya sami Afrah tsaye cikin kayan baccin ta,tana riqe da d'an qaramin silver flask,

d'ayan hannun ta kuma tana riqe da teddy.

zuwa tayi ta miqa masa flask bata ce dashi komai ba sae cup da taje ta d'auko ta bashi, bud'e flask d'in yayi ya zuba mata tea mai kauri,sannan ya zauna ya dora ta kan qafafun sa,

Ya kai cup a bakin ta,ta girgiza kanta, tace"uncle kamanta cewa kai ke fara sha kafin ni,farhan yayi shiru can yace"poppy luv" _*ya kan kira ta da wannan sunan ne sbd poppy sunan wani plant ne mai dauke da red flower wanda Afrah ke mugun so domin duk suka shiga garden bata da aiki sae tayi ta tsinko flower tana wasa da shi,har ma tana sawa a gashiñ kanta,shiyasa yasa mata poppy luv shine idan ta motsa masa wani lokaci sae ya kira ta da sunan*_

Farhan yaci gaba da cewa"poppy luv ni bazan iya cin komai ba yanzu"kallon shi tayi tace"uncle idan baka sha ba nima bazan sha ba"farhan yayi shiru yana kallonta,shi dai baya jin zai iya cin komai damuwar sa kad'ai ta ishe shi, sae dae baya iya barin Afrah da yunwa domin yasan idan bai sha ba,baza ta sha ba.

A hankali yakai cup a bakin sa ya kur6a kadan,

sannan ya bata tasha,da yake shegen wayo ne da ita duk ya bata tasha bata yarda ta sake sha sae yasha domin ita ma ke riqa cup din ta kai a bakin sa,da haka har suka shanye tean gabad'aya har sauran da ke cikin flask basu rage ba sbd dukkan su yunwa suke ji.

Gwoggo ce ta shigo da sallamar ta dauke da abinci ta ajiye abincin tare da fad'in "nasan cewa yau duk baka ci komai ba,

don Allah kayi qoqari ka sawa cikin ka wani abu kafin ka kwanta"ai yanzu muka gama shan tea nida Afrah"wannan d'an tean ne zai ishe ku"Allah gwaggo ba don Afrah ba da bazan iya sawa baki na komai ba,kuma tean kauri ne dashi sosai shiyasa ya ishe mu"ai dama tean ku biyu na had'a ma shi,sbd tana ganin zan had'a mata tace na had'a har da uncle"kawai dai nayi tunanin cewa ba zai ishe ku ba sbd kun yini da yunwa domin ko ita yau bata ci komai ba,

duk nayi mata zancen abinci sae tace sae da kai zata ci, ba yanda banyi ba amma taqi ci, hakan yasa yau duk bata sha maganin ta ba,cikin sanyin murya wanda dama tun d'azun haka

yake maganar sa yace"ai gwaggo a ajiye zancen shan maganin ta domin kinga taji sauqi,to idan ta daina sha baza a koma er gidan jiya ba?a'a gwaggo dama abinda na fahimta shi ne ihun da tayi tun a lokacin da aka harbi Abba(Alhj Sadiq) shine ya kawo mata matsala a cikin dodon kunnen ta har ta daina ji,sae gashi jiya tana jin qarar bindiga tayi razanannen ihun da nake sa ran shine ya kauda wannan matsalar farko ma'ana ya dawo mata da jin ta,amma duk da hakan zamu je asibiti a duba ta.

Gwaggo ta nisa tace"ikon Allah ni kam tun jiya nake ta mamakin yanda take magana ashe haka abin yake,Allah yasa samun lafiyar kenan, kai kuma Allah ya baka ikon haqurin rashin da mukayi na Amrah, yace Amin kafin take fita daga dakin.

Sae da Afrah tayi bacci sannan ya kai ta gurin gwaggo.

Ya dawo shi kad'ai cikin d'aki abin tausayi wanda kallo d'aya zakayi masa kasan shi kanshi yana jin tausayin kanshi,

duk da cewa ba'a wancan d'akin yake ba,domin tunda aka fitar da gawar Amrah bai sake leqa d'akin ba.

Sanin cewa ba zai iya yin bacci ba bai ko gwada kwanciya ba yaje ya d'oro arwala ya shiga jero salloli inda duk yayi raka'a biyu sae ya jima sosai yana karanto addu'o'i.

A 6angaren su Habib kuwa hukuncin d'aurin rai da rai aka yanke musu tare da horo mai tsanani a bisa rashin sanin iya adadin ran da suka kashe garin yawon su na fashi da makami.

Bayan sati 1

Haka rayuwar farhan ta dawo so lonely,

sea dae sauqin sa d'aya yawan ibadar da yake da kuma addu'a duk sae komai ya fara masa sauqi wato damuwar da yake ciki ta fara rage mishi,domin yanzu har ya koma kan aikin sa wanda sae ya kai Afrah school ne yake ficewa asibiti.

*Futha Luv 💅 & Billy giro😊*

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:20PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [ 7/23/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
~*AFRAH KO AMRAH* ~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*Na*
*Bilqis Sidibe💅&Bilkeesu giro😊*

🏅1️⃣6️⃣🏅
Sannu Sannu lokaci keta ta tafiya domin yanzu Afrah har tana primary 2 inda take tafka rashin ji a school son ranta ita da qawar ta Amrah
(wato wacce JB ya had'a ta da ita tun a nursery)
duk makarantar an san da zaman su kan rashin jin su,ga kwanya da Allah ya musu sae ma ka rasa wacce tafi qoqari a cikin su, hakan yasa suke zowa first position ma'ana bracket sukeyi.

Riqe take da towel d'an qarami dai dai ita pant kadai ne a jikin ta, tana tsaye a bakin qofar toilet sae kuka take cike da shagwa6a yayinda take kallon gwoggo da ke had'a mata tea ta sanya madara kenan sae ga farhan ya shigo,ya kalli Afrah tare da girgiza kanshi domin inda sabo ya saba sbd kullum idan za'a je school sae Afrah tayi kuka.

Sae da ya gaida gwaggo ya qarasa gurin Afrah da ta qara fitar da sautin kukan ta, farhan yaja hannun ta suka zauna kan sofa,ta wani narke masa a jiki tana ci gaba da kuka.

Farhan ya shiga lallashin ta inda yake cewa"poppy luv meyasa kullum roqon ki nake akan ki daina kuka amma kullum sae kinyi kuka"a shagwa6e ta share hawayen ta tace"to uncle kullum ni bana baccin safe tun bacci bai ishe ni ba ma ake ta she ni"kiyi haquri poppy luv haka boko yake sae da haquri,mararaicewa tayi tace "to uncle zaka bar ni yau kar naje?...no poppy luv kin manta yau friday saurin tashi ake?cikin 6acin rai mai d'auke da shagwa6a ta kalle shi kafin take tashi kan jikin sa tare da jefar da towel d'in da ke hannun ta, tace "oh no uncle! uhm uhm"nan ta shiga bubbuga qafafunta a qasa kafin take zama dirshan kan tiles ta had'e kai da guiwa ta fara rera sabon kuka, farhan yayi shiru yana kallon ta da alama kukan yana masa zafi a rai ,ya kira sunan ta kusan sau biyu bata amsa mishi ba,yace "ba ruwana dake idan baki zo mun shirya ba"yana gama fadar haka ya jingina a jikin sofa tare da lumshe idon shi.
Afrah ta d'ago kanta tana kallon shi,wanda tayi 15 secnds a haka,jin ta daina kuka yasa farhan ya bude idon shi a hankali ya sauke su kan Afrah, kunnen ta ta kama tace "sorry uncle"sannan ta share hawayen ta tace "na daina kukan kar kayi fishi dani kaji, kaji uncle, murmushi farhan yayi yace"oya zo kiji wani albishir"da hanzarin ta taje inda yake rad'a mata abu a kunne Afrah ta daka tsalle cike da murna tace shike nan yau bazan tsokani kowa ba na maka promise uncle,farhan yace "yauwa my poppy luv ko ke fa to mu tafa ko,nan suka tafa tare da lotsa kumatun junan su, wanda hakan ke qara sa kowannen su ya qara fadada murmushin sa.
Gwaggo dai sae murmushi take tana kallon su inda sabo ta saba,domin kullum haka ke faruwa sae da wayo ake samu taje school ba kuka.

Sae da tasha tea sannan gwaggo ta shirya mata suka fice.

12:20pm ya koma domin ya dauko ta sae sauri yake sbd a 12 ya kama ta yaje dauko ta se ya had'u da go slow kan hanya.

Da shigar sa makarantar sai dube dube yake ya ga sauran yaran da ba a zo daukar su ba sae dae ba Afrah a cikin su ,qarasawa yayi gurare n classes,Afrah ya hango da gudu duk

hannuwanta ca6a2 suke da wani abu kamar kala har ma fuskar ta duk shine, cin karo tayi dashi yayinda ta 6ata masa fararen kaya tayi saurin dago kanta domin ganin waye,tana ganin shi ne ta rufe fuskar ta da tafin hannun ta tare da fad'in"oops sorry uncle"ta kuma qanqame shi tana mai cusa fuskar ta a jikin sa sae duk ta qara 6ata mishi kaya,a maimakon ranshi ya 6aci sae ma yayi dariya yace"Afrah meye haka a jikin ki har kika 6ata min kayan juma'a? Dariya takeyi yayinda ta dago fuskar ta kafin tace wani abu sae ga JB wanda shima dariya yake, JB yace kasan me wai fa Auntyn su ce suka je suka tarar a staffroom sae bacci take tare da birthday cake kusa da ita,wai ni take jira nazo muyi celebrate d'in birthday ko meye dalilin ta oho,shine fa suka ci mai isar su sannan sauran suka ya kuta shi,ita kanta ma basu bar taba domin duk sun 6ata mata fuska har cikin gashin kanta duk cake ne, ita kuwa wai duk bacci take bata san meke faruwa ba,hango ni da sukayi ne yasa kowa yabi tashi hanya suka gudu,,
Shine kake dariya abin ka musu fad'a,,,wlh farhan abun ne da dariya domin kallo d'aya nayi wa Auntyn se na ganta kamar black monkey shine abin ya ban dariya sosai,farhan ya kalli Afrah yace"Afrah ashe har anti kike tsokana ko, turo baki tayi tace "uncle ita ce kullum idan tazo class din mu sae ta kar6e mana sweets da chewing gum d'in mu nida Amrah,wai mun fiye ciye ciye a class, kuma shi ke nan baza ta bamu ba,,jan hannun ta kawai farhan yayi sukayi sallama da JB.
Da shigar su mota Afrah ta hango Aunty ta fito a hargitse sae neman su take domin tasan ba wanda zai mata aikin sae su.
Afrah ta kwashe da dariya tare da nuna ta tace"uncle see d way she look like crazy bird!sosai abin ya bawa farhan dariya domin tabbas tayi kama da mahaukaciyar tsuntsuwa sae dae saurin 6oye dariyar sa yayi yaja motar, yana mai kwa6ar Afrah da kar ta sake yiwa auntyn ta haka ba kyau, amma tamkar ba da ita yake zancen ba sae kallon antyn take tana ci gaba da dariya har tana duqewa qasan seat wai duk dariya ce.
can tayi shiru ta kalli farhan da ya maida hankalin sa gun driving tace"uncle zaka koya min mota"poppy luv yanzu kinyi qanqanta sae idan kin girma na koya miki,um um uncle ni yanzu nake so ka koya min, kaga ita Amrah da mashin Abbanta ke zuwa d'aukar ta kaga idan na iya mota,sae na riqa kawo kaina school har ma na riqa maida Amrah gida ba sae Abban ta yazo d'aukar ta ba,kaji uncle ka koya min bazan yi rashin ji ba
...yauwa uncle ina alqawarin da kamin yau da safe? Ai kin 6arar da alqwarin tun da dama cewa nayi sae idan baki tsokani kowa ba.....Allah uncle ba wanda na tsokana a yau indai a class d'in mu ne,other classes ne kawai sae Aunty,ta fadi haka ne yayinda ta turo baki, farhan yace "oh poppy Luv I mean gabad'aya school kar ki tsokani kowa,cikin muryar kuka tace"to uncle kai ne kace min class baka ce min school ba,ok naji ni nayi kuskure don haka daga yau kar ki sake tsokanar kowa a school kinji, ya fadi haka ne yayinda Afrah tayi saurin bude glass d'in motar sbd wata er makarantar su da ta hango kan gaban mashin da alama yayanta ne a tare da ita,yarinyar sae gyangyadin bacci take, nan Afrah ta bud'e murya sosai tace Sleeping sickness!firgigit yarinyar ta farfad'o tana ganin Afrah ba shiri ta jefo mata facing cap Afrah tayi saurin rufe glass d'in motar,
ji kake qwal hular ta bugi glass,Afrah "tace kai! kai!....farhan yayi saurin riqe hannun Afrah ganin tana qoqarin sake bude glass,tace Allah uncle sae na rama...
kafin farhan ya riqo d'ayan hanun ta tuni ta bude glass har ta cire school facing cap din ta, ta jefa sae a goshin yarinyar,yarinyar ta wangame baki zuwa kuka Afrah kuwa ta kece da dariya hade da yi mata gwalo.

Tuni wanda ke tare da yarinyar ya harzuqa ya sauko a mashin sbd duk abin nan da ke faruwa tsaye suke bcs of traffic calming.
Kan ya qaraso har farhan ya fito daga cikin mota ya samu da qyar ya lallashi mutumin.
Sannan ya koma ya tada mota ya fice sbd traffic light ta basu dama.
Kallon Afrah yayi wacce har yanzu bata daina yiwa yarinyar gwalo ba,yace Afrah!!da murmushi ta juyo tare da fad'in sorry uncle, girgiza kanshi kawai yayi sbd ya riga yasan idan tayi nasara gun fad'a to ko tsawar me zai mata ranta ba zai ta6a 6aci ba,shiyasa ma ya gwammaci ya mata a lalama.
Yace Afrah meyasa ba kya iya zama baki tsokani kowa ba?langwa6ar da kañtà tayi tace "idan ka koya min mota zan daina uncle.
Allah ya shirya min ke my Afrah ya fadi haka ne dai dai sun iso gida.

Da shigar su gida yakai Afrah 6angaren gwaggo ya tafi nashi 6angare domin ya canza tufafi.

Koda ya dawo ya samu har an ma Afrah wanka sae jiran shi take suci abinci.
Suna gama cin abinci ya d'auki makullin mota,Afrah ta marairai ce tace"uncle inazuwa"no Afrah masallaci zanje ki bari idan na dawo sae muje inda nace miki kinji,"uncle please" ta fadi haka ne yayinda idanun ta suka ciko da qawalla,durqusawa yayi ya riqo hannun ta yace "to shike nan amma a mota zan bar ki kin yarda?da sauri ta gyada mishi kai domin ganin take da ya fita ba zai dawo suje yawon da yace ba.

Tafe suke kan hanya sae surutu Afrah ke mishi ita sae ya kowa mata mota har tana fad'in uncle ai na ma ga yanda kake yi zan koya da kaina,,farhan jin ta kawai yake har suka zo masallaci.

Bai riga ya parker mota ba sae ya hango wani abokin sa da suka jima basu had'u ba yayi saurin fita ba tare da ya kashe motar ba bare zancen cire key.
Yana wuce wa Afrah ta koma seat din driver da murnar ta inda ta shiga ta6e 2,tana kwatan ta duk yanda taga farhan nayi, ta dora qafafuwan ta inda taga yana dora nashi tare da danna gun da qarfi,wanda hakan yasa motar ta tafi ba shiri,
Yayinda farhan ya gama gaisawa da abokin sa,abokin ya fice shi kuma ya juyo,ai kuwa ya tafi da sauri har yana had'awa da gudu,yayi nasàrar riqo gambu,yakai hannu cikin sauri ya kashe motar,a tsoràce Afrah ta fad'a kan jikin sa cikin kuka dafe da goshi da alama buguwa tayi a gurin,cike da damuwa farhan ya jaye hannun ta yaga gurin har yayi lolo yayi ja,nan ya shiga murza mata, sautin kukanta ne ya qaru ta rirriqe hannun shi tare da cusa fuskar ta a qirjin sa, jikin ta sea rawa yake sbd ta tsorata sosai da jin yadda motar ta tafi da qarfi, bubbuga bayan ta ya shiga yi a hankali, ya kalli mutane sae sauri suke zasu shiga masallaci.
Nan ya shiga dube dube yana tunanin yanda zaiyi da Afrah gashi ana qoqarin tada sallah.
Kamar daga sama yaji "ance idan ba damuwa ko zaka bani ita na riqa ma,
Farhan ya kalli inda maganar ke fitowa wata er matashiya ya gani ba laifi akwai kyau sae dae ba shape, kafin yace komai tace"ganin nayi kana ta faman dube dube ni kuma zan wuce kan hanya naga ya kamata na tsaya na taimaka maka,farhan bai kawo komai a rañsà ba yace

"haka ne gasky na gode fa" ya fadi haka ne yayin da ya miqa mata Afrah,wani lallausan murmushi ta mishi tace" ai ba godiya a tsakanin mu sbd tamkar qanwa ta ce, nan farhan yayi murmushi ya dan kai bakin sa saetin kunnen Afrah wacce bata ko dago ta kalli wacce ta kar6e ta ba yace"my poppy Luv zan tafi na dawo kinji" ya shafi bayan ta tare da yi mata peck a gefen fuska, wanda duk abin nan da yake yarinyar sae kallon shi take da alama komai na farhan birge ta yake, domin bata daina kallon shi ba har ya shiga masallaci,sannan ta iya daga qafafunta taje cikin motar ta ta zauna yayinda Afrah ke maqale a qirjin ta, a hankali takai hannu ta shafo dai dai inda taga farhan ya shafa a jikin Afrah ta kuma dora lips dinta a dai dai inda farhan ya ma Afrah kiss,bata dago ba sae da tayi nata kiss, tace "Luv u guy"

*Futha Luv 💅& Billy giro😊*
®NWA✍🏻
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:20PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [7/25/2016] Billy giro😊: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*~AFRAH KO AMRAH ~*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*Na*
*Bilkeesu giro😊 & Bilqis Sidibe💅*

🏅1️⃣7️⃣🏅
Cike da murna ta d'auko wayar ta tayi dialling number yayinda mom farida ya bayyana a screen.
Ringing daya biyu aka d'aga tace"mama yau akwai labari mai d'adi sae dae naxo zaki ji.
Ta kashe wayar tana saqe saqe a cikin ranta har aka fito daga masallaci.
Farhan ne yazo ya same ta tayi nisa gun tunani sallamar da yayi ne tayi far da ido,ba tare da ta amsa sallama ba tayi murmushi tare da fadin har kun fito,gyada mata kai farhan yayi yana mai kallon afrah sbd koda ya shiga masallaci cike ya ke da damuwar ganin yanda goshin ta yayi lolo yayi ja,har ma ya qagu ya fito.
Yace tayi bacci ne? Bazan iya ce maka eh ko a'a ba sbd tun lokacinda na kar6e ta bata d'ago kanta ba har yanzu,
Eyyah my poppy Luv inaga gurin yana matà zafi sosai,nan ya kai hannu ya kar6e ta, ya dago fuskar ta yana mai kallon gurin cike da damuwa yace"oh poppy luv meyasa kaudin ki yakai har kika jiwa kan ki ciwo haka,that's y bana son rashin jin da kike wlh just bcs of irin wannan ranar, yarinyar dai sae kallon farhan take wacce ta fahimci har cikin rai yake jin zafin jimuwar da Afrah tayi,ta d'an kauda kanta kad'an tana mai jin haushin yanda yake kula Afrah ita ya bar ta a tsaye...."wash uncle zafi ka daina murza min"maganar ta fito a bakin Afrah yayinda tayi ta cike da alamar zata yi kuka.
Yarinyar ta juyo a hankali ta kalli Afrah wacce taji sautin muryar ta mai taushi da dad'in saurare like flute, domin tun da take bata ta6a jin murya mai dad'in sauraro irin wannan ba,duk da tasan qaramar yarinya ce amma ta jinjina ma zaqin muryar ta,
Farhan kuwa kukan da yaga Afrah na qoqarin yi ne yasa ya daina murza gun,sae iskan

bakin sa da yake d'an hura mata a hankali, yayinda Afrah ta wani lafe a qirjin sa,sae yarinyar ta gansu perfect match kamar su tabbata a hakan,amma tafi son ya kasance ita ce a qirjin farhan ba Afrah ba.... Farhan ne ya katse ta da banzan tunanin da take,yace"am sorry pls nagode fa"sauke ajiyar zuciya tayi mai nauyi had'e da gyad'a kanta,ta shiga mota shima ya nufi tashi mota ya shiga,tare da bud'e drawer mota ya bude er qaramar first aid kit dake ciki,ya dauko magani wanda da qyar ya samu Afrah tasha sannan suka bar gurin.

Sannan ita ma ta iya tuqa motar ta ta wuce,

Tana isa gida jiki sa6ule ta zauna kan kujera, matar da ta fito ce ta bamu mamaki sosai domin kuwa Farida ce matar marigayi Alhj Sadiq wato Baban Afrah.
Zama tayi tare da fad'in leesa lafiya kin shigo jiki mace bayan kin kira ni da murna har ma kina ce min akwai labari mai dad'i,hmm mom farida na tsorata da ganin yanda yake bawa qaramar yarinya kulawa, ba ma shi ba mom ko suna na fa bai tambaya ba,,, mtsw wannan ne kawai na ma zaci wulaqan taki yayi,inace dai kin samo number sa..mtsw mom gayen fa bai ko sake min fuska ta yanda zan sami damar tambayar sa wani abu ba,domin kwata kwata hankalin sa na kan wannan qaramar yarinyar, wai kan d'an wani qaramin jin ciwo da tayi duk yabi yasa kansa a damuwa...hmm ai indai farhan ne kadan kika gani, yanzu abinda nake so da ke shine gobe zan miki kwatàncen gidan sae kije a matsayin kinje dubata,
to na tabbatar in yaji kan Afrah kika je zai fara sake miki fuska har ma ki sami damar samun number sa,ni kuma a cikin kwanakin nan zanje qauye domin na kar6o mana maganin da nace miki za'a turara ma wani abun da zai ci,sae dae maganin yana da sharad'i domin a ranar da aka turara shi a ranar ake so aci wannan abun,idan ba a ci a ranar ba ba kuwa zai yi aiki ba, amma idan yaci to ina mai gaya miki zai ji a duk duniya ba wacce yake so kamar ki domin ko Afrah da kike gani ba zai qara kallon ta ba sae da izinin ki.... Au haba mom!Allah kuwa domin ko bacci ba zai iya yi ba har sae yazo ya ganki, nan leesa ta ba farida hannu suka tafa cike da murna suna shewa.

A 6angaren farhan kuwa duk yabi yasa kansa a damuwa sbd tunda suka koma gida Afrah take kwance har zuwa marece tama daina zancen zuwa yawon da ta qwallafa a ranta sbd jikin ta duk yayi zafi.

Farhan ne zaune a bedside yana kallon Afrah cike da damuwa... Gwaggo tace"ni kuwa meyasa baza kayi mata allura ba, d'an guntun murmushi farhan yayi ya d'an kauda kansa gefe yace"wlh gwoggo kukan ta ne bana son ji,ko fa bata magani ya na qarasa bare allura,gwaggo dai kasa cewa komai tayi ta rasa mene ne farhan keji idan Afrah na kuka wanda tun tana jaririya har yanzun bai daina ji ba.

Da dare farhan na kwance yana bacci Afrah ta shigo dakin riqe da er teddy,
tana sanye da rigar bacci peach in colour iya guiwa,ta hau kan gadon taje nesa da farhan tana wasa da teddy.
Cikin baccin sa yake ji a jikin sa kamar Afrah na kusa dashi hakan yasa ya bud'e idon shi a

hankali yaga ashe da gaske tana kusa da shi, ya tashi da hanzarin sa tare da jawo ta kusa dashi yace"my poppy Luv kinji sauqi?eh uncle,gwaggo ta baki magani kinsha?eh,ina ce bakiyi kuka ba ko?shiru ta mishi, wanda shima yasan tambaya kawai yayi amma kuka kam ba fashi,yayi murmushi tare da shafo gashin kanta yace "to me yasa har yanzu baki koma bacci ba?shiru ta mishi domin ita kanta bata san dalilin da yasa ta kasa komawa bacci ba bayan tana jin sa sosai.

Haka shima farhan yayi shiru yana tuna cewa Afrah bata iya bacci fa sae kan jikin sa,nan yace "sorry my Afrah ban san zaki farka ba da na jira ki har ki sake komawa bacci,kuma nima baccin yazo min ne ba shiri,, hmm farhan kenan sae magana yake da Afrah kamar wata babba, nan ya jawota jikin sa,yana shafa jikin ta a hankali yayinda yake ta kallon fuskar ta harde zara zaran eyelashes din ta da ya qure da kallo kamar mai wani tunani,cikin minti biyar tayi bacci abin ta,sae da ya tabbatar baccin ta yayi nisa sannan ya maida ta gurin gwaggo.

Da safe gurarен qarfe 11 farhan ne da Afrah cikin qananan kaya riga da wando three quarter kala d'aya,riga black wando fari, sai sukayi kyau sosai sbd kayan sunyi dai dai da jikin su,ga qamshi mai dad'i da ke fita a jikin su,yayinda suke zaune kan resting chair farhan na karatun jarida Afrah na jingine a jikin sa tana riqe da poppy flower guda biyu sannan ta soka d'aya a gefen gashin ta sae tayi kyau kamar ba indiya har dai yanda gashin kanta yasha gyara aka zubo shi a baya.

Fresh air ke bugo musu cike da natsuwa gurin yayi tsit ba mai magana a cikin su sae kukan tsuntsaye da ke tashi kasancewar cikin garden suke,Afrah sae kallon tsuntsayen take yanda suke shawagi a cikin d'an kejin su,ko kad'an bata yarda tayi wani dogon motsi ba sbd duk rashin jinta idan ta fahimci farhan na buqatar natsuwa to kuwa shiru take yi da bakin ta.

Suna cikin haka ne suka ji sallama farhan ya fara dago idon sa ya sauke su kan leesa ya amsa sallama yana mai son ya tuna inda yasan fuskar,leesa ta fahimci haka yayinda take qoqarin zama kan dayar kujerar da ke dubin su had'e da sakin murmushi tace"suna na "Khaleesat amma anfi kirana da leesa nice wacce muka had'u jiya har na kar6i Afrah ka shiga masallaci, farhan ya sake mata murmushi na alamar ya gane ta, tace "dama tun jiya na biyo bayan ku da niyar na ga gida domin na samu nazo naga ya Afrah taji da jiki, abin na raina tun jiya har ma naso ace nazo kafin yau.

Sosai farhan yaji dad'i domin shi dai ba abin da yafi masa dad'i irin ka nuna damuwar ka akan Afrah.

Yace " naji dadi na kuma gode sosai da kulawar ki..ah ah ba komai ai yiwa kaine,ta fad'i haka ne tare da fad'in Afrah zo muga gurin"Afrah ta kalli farhan, yace jeki kinji,nan ta tashi ta nufi gurin leesa, leesa kuwa sae magana take a ranta"

_yarinya zaki gane kuren ki ne,domin kin kusa zama shara a gun farhan sae yanda nayi dashi_

Ta tsaida zancen yayinda Afrah ta qaraso,ta jawo Afrah jikinta tare da shafo kan ta,ta kalli goshin Afrah tana mai nuna damuwa a fuskar ta, tace "Allah sarki Afrah sannu kinji,Afrah ta gyada kanta tana mai kallon leesa,kafin leesa ke tambayar farhan abinda yaji wa Afrah ciwo, nan farhan ya sanar da ita, tace "Allah ya tsare gaba"sannan ta furta a ranta " _ina ma ace kin mutu a cikin motar_"

Kamar Afrah taji me tace ta jaye kan jikin ta ta koma gurin farhan,

Yayinda leesa ke ci gaba da magana tana mai kallon Afrah da taje kan jikin farhan ta lafe _kin kusan yin na qarshe yarinya domin kwanaki kad'an ya rage ki daina zuwa ko kusa da shi bare zancen kwanciya a jikin sa_

Nan ta daina zancen ta koma jan farhan da fira,har ta samu ta kar6i number shi.

Sae da ta d'an jima kafin take barin gidan tare da bawa Afrah sweets,chocolates & Biscuits cike da wata er matsakaiciyar leda.

Haka ma washe gari sae da taje gidan inda ta qara zuwar ma Afrah da kayan maqulashe ciki har da ice cream.

Gidan ta yini a 6angaren gwaggo wanda hakan yasa Afrah ta sake da ita sbd Afràh yarinya ce mai saurin sabo.

Bayan ta koma gida ne farida ta tarbe ta da Albishir d'in cewa ta kar6o magani yanzu aiki ya rage nata, leesa ta kar6i maganin cike da murna tace"in Allah ya yarda gobe muna zaune zaki ga dan aike farhan yazo nema na,domin gobe Leda biyu zanyi ta chocolates naje har makarantar su Afrah na bata.....ha a! wannan shirmen fa leesa?mom farida ba shirme a ciki zuwan nan da nayi na kwana biyu a gidan su na fahim ci bata fara cin wani abu sae farhan yaci....to ai ba su biyu ake so suci ba shi kadai ake so yaci,eh ai shiyasa nace leda biyu zanyi dayar ita ce wacce zan turara ma magani wato ta farhan,dayar wacce bata da komai ita ce ta Afrah,idan naje school d'in su ni nasan yanda zanyi mata bayanin cewa ga nata ga ta farhan..... Hmmm amma dai akwai ki da shirme... Ba wani shirme mom, yarinyar tana da ganewa sosai domin zuwan da nayi na samu farhan yana koya mata karatun islamiya sae kinji yanda qira'a ke fita a bakin ta, kuma duk tambayar da yayi mata kai tsaye take bashi amsa.... Naji tana da ganewa amma meyasa baza ki bashi da kanki ba? Mom baki ga yanda ya dauki abin da ya fito hannun ta da muhimmaci ba, shiyasa nake so ta bashi domin na tabbatar idan ta bashi zai ci.

To shike nan ke kuma ki tabbatar kin turara maganin da kyau.

To mom farida.

Washe gari kasancewar ranar Monday ce Afrah na school yayinda suke ta guje guje ita da Amrah kasancewar lokacin break fast ne.

Leesa da ke tsaye sae kallon su take,ta dan ya mutsa fuskar ta kadan tare da fadin abin tausayi Afrah daga yau ba kya da wani sauran nishad'in da zaki ci gaba da wasa da qawaye sae dai wasu suyi ba ke ba.

Nan ta qarasa gurin su tare da bayyana murmushi a fuskar ta,Afrah ce ta fara hango ta tazo da gudu ta tarbe ta,tace "Aunty ina uncle"Afrah ai ke zan tambaya uncle,ko tunanin kike tare muka zo?a'a yace idan ban tsokani kowa ba zai zo ya kawo min ice cream, kuma yau ban tsokani kowa ba nida Amrah kawai ke wasan mu,,uhm to ki ajiye zancen ice cream ga chocolate & Biscuit na kawo miki, ta fadi haka ne yayin da ta fitar da Leda biyu, tace wannan ledar wato white colour itace ta uncle, pink colour ce taki,kar kici yanzu ki bari sae kinje gida, idan kika bawa uncle nashi sae kici naki,amma ki tabbatar kunci a yau domin zai iya lalacewa

idan ya kwana....Aunty yaushe biscuit ya fara  lalace wa a kwana da'ya, nifa wanda uncle ke saya min yana kwanaki bai yi komai,, _kaih! yarinyar nan akwai baqin wayon tsiya_ta fadi haka ne a ranta kafin take fitar da biscuit wanda da gani zai yi dad'i da tsada ta nunawa Afrah tace"uncle d'inki ya ta6a saya miki irin wannan? Turo baki tayi tace"wanda uncle ke saya min yafi wannan girma da kyau.

 Duk da Ieesa taji haushi hakan ta dake tace"nima zan riqa saya miki irin wanda uncle ke saya miki, amma kici wannan a yau kinji,
 haka shima uncle,ok Anti zamu ci a yau,yauwa Afrah to je ki adana su a cikin jakar ki but wanne ne na uncle? White one na uncle pink one nawa... That's gud my dear je ki dawo sae na baki wani  keda qawar ki.
    Da gudu Afrah taje har tana had'awa da tsalle.
   Ba jimawa ta dawo, Ieesa ta dauko sweet ta ba Afrah sannan ta ba Amrah, Afrah tace"anti Amrah bata shan sweet,chewing gum take ci, ok ina da chewing gum bari na bata,bayan ta bata ne ta wuce tana mai yi musu bye bye sae fatan nasara take a cikin ranta.

Da dare farhan ya fito daga wanka ya sami Afrah sae game take da game tab,tana jin ya fito ta watsa mishi idanun ta masu shegen haske da kyau, tace"uncle har yanzu ba muci biscuit d'in da Aunty ta ba mu ba"tayi maganar ne a shagwa6e bcs tana gudun kar yace dare yayi baza su ci ba, ba musu yace ok je ki d'auko mana kafin na gama shiri sae muci.
   Da murnar ta taje ta d'auko ta kawo, ta bashi white leda ta d'auki pink.
   Sae da ya gama shirin sa sannan yayi lokacin bud'e ledar ya dauko biscuit ya bude yayin da ya tsure biscuit d'in da ido yana mai jin baya son saka komai a bakin sa sbd yayi brush amma haka ya zaro d'aya ya saka a bakin shi.

*Billy giro😊 & Futha Luv💅*

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:20PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [7/26/2016]  🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
      *~AFRAH   KO AMRAH ~*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*Na*
*Bilqis Sidibe💅 & Bilkeesu giro😊*

🏅1️⃣8️⃣🏅
Amma hakañ ya zaro d'aya ya saka a bakin shi had'e da yin "bismillah"
   Bai wani  ci da yawa ba ya ajiye sbd baya son zaqi sosai.

Haka ita ma Afrah ta ajiye nata sbd bacci take ji.
Har tana qoqarin kwanciya farhan yace "tashi muje muyi brush.
Koda suka dawo suka sami wayar farhan sae ruri take, farhan ya dauki waya yaga leesa na yawo kan screen, yace "Afrah zo ga Antin ki"
Sae da yayi receiving ya bata,bayan sun gama gaisawa ne,leesa tayi shiru tana tunanin ta yanda zata gane cewa sunci biscuit,can tace"Afrah inace biscuit d'in da na baki akwai dad'i sosai ko?eh shine ma muka gama ci yanzu nida uncle se mukayi brush zamu kwanta, shi kad'ai yaci nashi ko har da ke? Shi kadai yaci nashi nima naci nawa, yauwa inace baki masa canjen leda ba, fara kika bashi ko?eh Anti, that's gud!haka nake son ji,bye my dear,,, ok bye Aunty.
Ta juya ta kalli farhan da yayi kwance kan bed idanun sa a lumshe da alama bacci yake ji sosai.
Jin ta gama waya yasa ya bud'e idon shi tare da sakar mata murmushi yace "zo kiyi bacci na maida ke gurin gwaggo kafin nayi bacci"
Nan ta hau kan bed ta shige jikin sa,sae ta dawo er fincika a cikin faffad'an qirjin sa, da yake dama bata da girman jiki sililiya ce.

A 6angaren leesa cike da murna ta daka tsalle,taje da gudu ta fad'a wanka,ta fito tayi zaune ba tare da tayi kwalliya ba acewar ta sae yazo sannan zatayi kwalliya ta nemi tufafin sawa sbd taja nata aji.

Farhan kam tuni bacci ya kwashe su shida Afrah.

Tun abin qarfe goma leesa ke sauraren zuwan farhan har 11:30 ba alamar farhan sae duk hankalin ta ya fara tashi wai ko da gaske yaci biscuit d'in.
Tana cikin haka ne sae ga farida ta shigo tace "ya naji shiru ko har yazo ya tafi?bai zo ba tukuna amma nayi waya da Afrah tace min sunci" yauwa dama wasu turarukka nake son baki ki shafa kafin kije,to shike nan zanzo na kar6a.

Gwaggo ta gama sallah tana lazimi ta kalli agogon bango har sha biyu tayi farhan bai kawo Afrah ba,
tashi tayi taje 6angaren shi,ta samu sae bacci suke shida Afrah ta wani qara shigewa jikin sa kamar wacce ke shan mamma, girgiza kan ta tayi tace"Afrah akwai aiki in kin girma domin bansan ya zakiyi da wannan sabo da farhan ya miki ba.
Nan taje sannu ta jaye Afrah kan jikin farhan ta d'ora ta a kafad'a,, da sauri ya bud'e idon shi yace"gwaggo keda kanki bari na kai miki ita, a'a yi zaman ka kawai dama so nake ka rufe 6angaren ka kar ya kwana a sake.
Nan farhan yabi bayan ta ya rufe 6angaren shi yaje ya kwanta kafin yake addu'ar shiga bacci.

Leesa kuwa rabon ido take har safe ba farhan ba alamar sa😂.

Tun da safe leesa ta shirya tsaf inda ta shafe jikin ta da kalolin turarukkan magani.
Ta fito gidan ba tare da sanin farida ba.
Bata zarce koina ba sae makarantar su Afrah,wanda yayi dai dai da isowar farhan,taji dad'in da ya tsaya a bakin gate bai shiga daga ciki ba domin ba kowa ake bari ya shiga da mota ba sae wane da wane, bata bari ya ganta ba domin bata so ya ganta.
Kallon shi take ya zagaya ya bude ma Afrah gambu sae lallashin ta yake akan ta daina kuka, afrah kuwa sae qara shagwa6e masa take tana maqale kafad'a ita baza ta shiga school ba.
Nan ya dauke ta ya dora a kafad'ar sa yana ci gaba da lallashin ta.
Leesa kuwa takaici yazo mata iya wuya domin ta tsani ganin farhan da mace ko me qanqantar ta kuwa, bare a yanda taga yana ji da Afrah har wani fargaba take ji a ranta da ita kad'ai ta barwa kan ta sani.
Wata er qaramar kwalba ta fitar tare da bud'e murfi yayinda wani baqin suracin hayaqi ya shiga fitowa a hankali bai zarce koina ba sae gun farhan ya shiga cikin idanuwan shi, wanda hakan yasa farhan yaji wani irin jiri mai qarfi ya d'ebe shi yayi saurin sauke Afrah kan jikin sa ya dafa jikin mota yayinda yake fitar da "bisimillah" a bakin sa had'e da karanto addu'o'i.
Sannu sannu ya fara daina jin jiri har ya dawo normal,sannan ya kalli Afrah wacce tun lokacin da ya sauke ta sae kallon shi take tace"uncle baka da lafiya ne"girgiza kanshi yayi yayinda ya durqusa yana share mata hawaye yace "lafiya ta qalau poppy luv"
JB ne ya qaraso gurin su bayan sun gama gaisawa da farhan yace "my little wife ya akayi kika makara yau tun d'azu nake dubin hanyar ki,, farhan "yace yau na kasa ciyo kanta ne har muka makara,
kuka take tun gida sae yanzu na samu ta daina, kan makarar ma yasa ban shiga daga cikin makarantar ba na tsaya a gate.
To ai gani nazo sae mu tafi ko, nan yaja hannun ta sae bye bye take yiwa farhan shima haka har sae da suka shige sannan ya shiga mota.
Leesa na kallon shi yana qoqarin cusa hancin motar sa a cinkoson motocin mutanen da ke kawo 'ya'yan su makaran ta.
Sai mamaki take yanda turaren ya shiga idon sa amma bai sa wani abu ya canza a tsakanin sa da Afrah ba, sae dae ta lura da lokacin da yake addu'a wanda yasa ta fahimci cewa kenan ko biscuit d'in jiya akwai addu'ar da yayi kafin yaci,hakan yasa maganin bai yi tasiri a jikin sa ba.
Tace"lallai farhan idan kasan wata baka san wata ba"nan ta jefar da turaren hannun ta ya tarwatse ta shiga mota ta tafi hasale.

*Futha luv 💅& Billy giro😊*

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:20PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [ 7/28/2016] Billy giro😊:
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*~AFRAH KO AMRAH*~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*Na*
 *Bilqis Sidibe💅 & Bilkeesu giro*😊

🏅1️⃣9️⃣🏅
Leesa na komawa gida  ta shiga d'aki had'e da jefar da d'an yalalon gyalen ta,ta shiga rawayar daki tana tunanin mafita.
   Farida ce tazo ta same ta tace"tun jiya nake sauraren kije min da kyakkywan labari amma naji shiru.
 Shiru  Leesa tayi tana tunanin me zata ce da ita.
    Ya kinyi shiru ba amsa kinsan fa ni aiki na ba wanda za'a tsaya wasa bane so nake na kwashe dukiyar nan kafin Hjy luba da 'ya'yanta su ankara.

  Idan baku manta ba Hajiya luba ita ce kishiyar uwar Alhj Sadiq (wato baban Afrah,) kuma ina fatar kun fahimci farida ita ce matar da Alhj Sadiq ya auro bayan rasuwar Hajiya Zarah (wato mamar Afrah)🤔

Farida taci gaba da cewa sanin kanki ne ba abinda ya dawo da mu garin nan sae don mu samu sauran kadororin sa su koma hannun mu,sbd wannan karon baza mu iya yin yanda mukayi gurin mallakar sauran ba, sbd da sa hannun sa ne,wanda don na iya sa hannun sa ne yasa muka mallake su,har ma muka kwashe kud'ad'en sa da ke banki,amma wannan karon hakan ba zai yiyu ba sbd takardun filayen sa da gidajen sa duk da sunan Afrah ne kuma dole sae da sa hannun farhan muke iya mallakar su,kuma ni kad'ai nake son na mallake su bada wad'an can munafukan mutanen ba,shiyasa bana son ku jima kuna wata soyayya da farhan so nake da ya fara sonki kiyi qoqarin ganin yasa muna hannu sbd kinsan da maganin ya kama shi duk  abinda kika ce yayi zaiyi ne ba tantama.

 Rai 6ace leesa ke kallon farida"tace mom farida ni fa gaskiya kallo d'aya nayi ma farhan naji ina son shi kuma da aure ba guntuwar soyayya nake sonyi da shi ba,,hm amma leesa kin san dalilin da yasa na zo da ke ko, sanin kanki ne da zan iya wannan aikin ba abinda zai sa nazo da ke,domin ko giyar wake nasha bazan yi soyayya da farhan ba,asali ma bazan ta6a yarda ya ganni a cikin garin nan ba.
   Don haka idan baza ki iya ba tun wuri ki gaya min na nemo wata.
   Shiru leesa tayi tana tunanin fa matsayin 'ya take a gurin farida wato farida qaunar mahaifiyar ta ce da suka fito ciki d'aya amma tasan indai akan dukiya ne ba ruwan mom farida da dubin hakan  zata iya nemo wata ta fita batun ta,kuma ko ta nemo wata shawo kan farhan zai yi wuya sbd addu'ar da yake yi,ko ba hakan ba ma baza ta ta6a yarda wata mace ta ra6i farhan ba domin ko Afrah yau d'in nan zata raba ta  da farhan....da ke fa nake magana, amsar ki nake jira.
   Leesa ta nisa tace"mom farida baza ki gane bane farhan fa ya tsare kansa da addu'oi wanda ba kai tsaye ake shawo kansa ba,shiyasa nake so ki bari abi abun a hankali ba sai an saka gaggawa a ciki ba sbd kinsan cewa da yanzu kun mallake duka kadarorin bcs kunyi aje da  'yan fashin da kuka tura gidan Alhj Sadiq kan cewa sae Alhj Sadiq ya saka wa kowace takarda

hannu kafin su bashi damar fita daga gidan,sae suka yi komai a gaggauwa ce har suka manta da zancen sa hannu,kuma koda suka tuna har ya fita,
binshi da sukayi baiyi wani amfani ba sbd jin motar police yasa suka harbe shi ya mutu ba tare da sun sami abinda suke so ba,
that's y yanzu nake son nayi komai a natse amma ina mai tabbatar miki da cewa yau yau d'in nan zan raba farhan da Afrah sbd ita ce babbar matsala ta domin na fahimci kulawar da yake bata ne kesa ba ya kula mutane, kin ga idan na raba shi da ita dole sannu sannu zai haqura ni kuma sae na fara qoqarin cusa soyayya ta agare shi.
Idan har ma taqama yake da addu'a to aiki na na yau ba boka ba malam.
Kamar ya leesa? Leesa taja hannun farida tace "mom farida zauna kiji"ina son ki bani number mutanen ki domin da yamma zanje gidan su farhan na d'auki Afrah muje yawo in yaso daga can na miqa musu ita suyi gaba da ita wanda har abada baza a qara ganin ta ba, ni kuma zanje asibiti gurin Dr Bilal yamin aikin da duk wanda ya ganni zai zaci naji rauni da gaske,acewar kidnappers na hadu dasu kan hanya suka kar6e Afrah ni kuma suka min rauni, kinga kuwa dole farhan ya haqura da qaddara domin ta tafi kenan ba zai sake ganin ta ba, nan farida ta ba leesa hannu suka tafa tace "ashe dai 'yata mai kwanya ce,, au duk a tunanin ki zaman da nayi a bariki na banza ne,,hmm to ke kina ganin Dr Bilal ba zai tona mana asiri ba..ya ma isa! shine fa gayen da nace miki mun had'u har kullum yana zowa muna d'ebewa juna kewa, jiya ne fa kawai bamu had'u munyi ba sbd hankali na ya karkata kan Farhan,farida ta bugo leesa cike da dariya tace dad'i na dake baki da kunya,to meye abin kunya mom farida koke fa kina damawa da naki Alhazzan.

" wa iyazu billah ya Allah ka shirya bayinka"

Da marece kuwa leesa ta shirya tsaf ba ta zarce koina ba sae gidan su farhan.

6angaren gwaggo taje ta shiga da sallamar ta,ta gaida gwaggo sannan ta gaida farhan da ke zauna kan sofa, ita ma ta nemi guri ta zauna ta kalli Afrah dake kwance jikin gwaggo wacce kallo d'aya ta yiwa leesa ta kauda kai, leesa ta ce"Afrah me aunty ta miki da baza ki tarbe ta ba? gwaggo tace"ita da uncle d'in ta ne,koda yaje d'auko ta makaranta ya samu tana fad'a da wani yaro,shine ya mata fad'a ya hana ta rama dukan da yaron ya mata,to fa tun sannan take faman fishi da shi taqi ta haqura taqi cin abinci taqi yarda na mata wanka,,, oh my dear Afrah zo qyale uncle muje yawon mu bada shi ba ko, zo kinji.
Afrah da shegen son yawo tazo da murnar ta,nan leesa ta cire mayafi kamar wata er gida taje ta mata wanka gwaggo ta bata tufafi ta shirya ta tsaf.

farhan dai sae kallon su yake wanda ya dauki fitar da wasa sae yaga ashe da gaske ne.

Har mota farhan ya rakasu ya riqo hannun Afrah ya d'an rage tsawon sa kadan yace"puppy luv haka zaki fita baki ci abinci ba... Kar ka damu idan mukaje zan samar mata abinda zata ci.

leesa tayi maganar

yayinda Afrah ta fizge hannun ta daga riqon da farhan ya mata, sbd har yanzu fishi take dashi,dan guntun murmushi farhan yayi ya kama hanya yana mata bye bye yana mai jin kewa kamar wacce zata tafi guri mai nisa, Afrah kam kallon sa kawai take dauke da fishi a fuskar ta ba tare da ta mishi bye bye ba.

Har zasu shiga mota Afrah ta juyo yayinda farhan ya juya,tace"uncle! ta kira shi ne cikin"daga murya sbd ya dan yi nisa da su,hakan yasa farhan ya juyo,nan Afrah ta sake masa murmushi tace"bye uncle"shima yayi mata murmushi yace "bye my Afrah"kallon su yake har suka fita daga gidan,bai koma daga ciki ba sae da yace"Allah ya tsare min ke my Afrah".

Suna cikin tafiya hadari ya had'u sosai suna isa Temako  Super market ruwa suka fara sauka kamar a bakin qwarya,
leesa ta sami guri ta Parker mota.
Lema ta dauko ta kalli Afrah tare da shafo gefen fuskar ta tace"my dear Afrah kinga ruwa ake yi sosai ki zauna zanje na siyo miki ice cream,chocolate,biscut har ma da kayan wasa kinji,maqale kafad'a tayi tace"um um duk ina da su a gida ni yawo kawai nake so"oh Afrah bana son ruwa su ta6a ki kije kiyi rashin lafiya kinga uncle ba zai ji dad'i ba.
Turo baki tayi tace Allah anti sae kinje dani ai ga umbrella nan a hannun ki bazan jiqe ba.
Leesa taji kamar ta shaqe wuyan Afrah kan takaici  ta dake tace"ok ina zuwa kinga an kira ni a waya bata jira me Afrah zata ce ba tabar gurin da nisa sannan ta d'aga waya tace"yauwa dama kuwa yanzu nake qoqarin kiran ka,nayi nawa aikin saura ku,
kuzo ga yarinyar nan a cikin mota ku tafi da ita kuma motar ta zama taku hade da dubu dari biyar d'in da ke ciki.
Ajiye wayar keda wuya ta hango shi tafe cikin kaftani kamar na kirki bai zarce koina ba sae cikin motar da Afrah take zaune yana shiga ya ja gambu ya rufe.

*```Futha luv💅 & Billy giro😊```*

®NAW✍🏻
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:20PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [ 7/31/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
~*```AFRAH KO AMRAH```* ~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*Na*

*Bilkeesu giro😊 & Bilqis Sidibe💅*

🏅2️⃣0️⃣🏅
Yana shiga ya dorawa Afrah bindiga a goshi, ta juyo tana kallon shi a tsorace har tana qoqarin fara kuka yace"shiiii!ba abinda zan miki ni abokin uncle din ki ne yawo xamu je na siyo miki

kayan wasa daga nan mu wuce gurin uncle.
Da yake Afrah mugun tsoron bindiga ne da ita bata bi ta kan abinda yake fada ba ta shiga kuka tana kiran "Anty"
Leesa kam tuni ta 6uya sae dae tana hango duk abinda ke faruwa.
Ganin yanda Afrah ke kuka har tana qoqarin tona mai asiri yasa ya 6oye bindiga domin ya fahimci ya yi babban kuskuren nuna mata ita.
Ya jawo ta jikin sa domin ya samu ya lalla6ata ya gudu da ita cikin kwanciyar hankali.
Afrah kam ta riga ta tsorata da shi sae fizgar jikin ta take yayinda sautin kukan ta ke qara fitowa,ta manna masa uban cixo a hannun sa da ya rufe mata baki.
Cikin zafin nama ya kai mata mari sbd jin zafin cizo.
Nan tayi baya kanta ya bugi gambun mota sae kawai gambun motar ya bude ta suntu6a waje, da yake dama gambun motar a bude yake shine bai san da hakan ba.
Sosai ya shiga rudu bcs Afrah na faduwa wata mota ta tsaya close to Afrah.
Rudun sa ne ya qaru hango wanda ke ciki, ai ko ba shiri ya rufe gambun motar ya tafi agurguje.
Farhan ne ya fito daga motar ya nufi Afrah cikin hanzari ya dauke ta sae kuka take yayinda jini ke fita a gefen bakin ta.
duk ta rikice ta qanqame farhan sosai tana ci gaba da kuka.
Idanun farhan sukayi jajiri sae kallon motar da wuce yake ko zai gane wanda ke cikin motar.
Leesa ce tazo da gudu yayinda farhan zai saka Afrah a mota, sbd ko kadan baya son ruwan sama su ta6a ta sabida zazza6i suke sata.
Bai saka Afrah a mota ba sae wani mugun kallo da ya bi leesa da shi har sae da yasa hantar cikin ta kadawa ta saki lemar da ke hannun ta.
Yace"wane irin shashanci ne zaki bar min Afrah gurin wani bnza can har yana qoqarin hallaka ta!
Wata irin ajiyar zuciya ta sauke a 6oye sbd ta fahimci bai gane ainihin abinda take shirin aikatawa ba.

Nan ta shiga fitar da hawayen munafurci wanda duk ruwan da ake kelawa kana hango gangarowar da suke kan kumatun ta.

Cikin murya kuka tare da qara marairaice murya tace"wlh farhan ita kadai na bari a mota sbd ruwan da naga anayi,sai na tafi ni kadài, ban ko qarasa ba na hango wani ya shiga motar yana qoqarin guduwa da Afrah shine nazo da gudu, amma wlh *Ban sanshi ba*gashi ya gudu da mota ta da kuma maqudan kudin da ke ciki.
Sae dae ba damuwa ta bane tunda anyi sa'a bai je da Afrah ba,amma don Allah kayi haquri da nasan hakan zai faru da bamu zo ba.
Farhan yayi shiru yana son gasgata zancen leesa har dai yanda take kuka tana ci gaba da roqon sa.
Nan yaji ta bashi tausayi ya zaro kudi a aljihu ya bata yace kiyi haquri a halin da Afrah take ciki bana jin zan iya biya wa wani guri.

😂zo kuka leesa a wannan lokaci sororo tayi ta saki baki tana kallon farhan ko godiya ta kasa

mishi har ya shiga mota ya tafi ya bar  ta nan tsaye ruwa na faman dukan ta,
ga lema tabi iska kuma gurin ba alamar zata sami taxi sbd ruwan da ake.

😂zafi biyu kenan buqata bata biya ba tasha kashin ruwa.

Farhan na isa gida ya dauki Afrah dake kuka tana rawar sanyi ya tafi da ita 6angaren gwaggo ya cire mata kayan jikinta da suka jiqe,
gwaggo tace"lafiya me yake faruwa da ita naga jini a gefen bakin ta kuma sae kuka take tana rawar sanyi?
 Cike da damuwa farhan ya bawa gwaggo Afrah yace don Allah gwaggo a gasa mata jikin ta da ruwa masu zafi tukun.

 Nan gwaggo ta shiga da ita toilet, farhan ya tafi ya canxo tufafi ya dawo yana da sintiri a bakin qofar toilet kyace wanda yakai patient asibiti yana jiran fitowar doctor.
   Sae da gwaggo ta d'an jima kafin take fitowa dauke da Afrah dunqule cikin towel, farhan ya amshe ta yana kallon fuskar ta  da ya fahimci marin qwarai aka mata dmn yatsu sun kwanta tsaf kuma har gurin ya kumbura.
   Sosai yaji ta bashi tausayi yaje da ita kan bed ya zauna ya shafa mata mai ya saka mata tufafi sannan ya shiga yiwa gwaggo bayanin abinda ya faru.
   Gwaggo tayi taslima tace"ni har naga rashin haqurin ka da kace zaka bi bayan su hankalin ka bai kwanta ba, ashe wani mummunan  abu ke shirin faruwa, oh Allah ya qara tsare ki Afrah,,amin gwaggo,na rasa meyasa yanzu mutane ba tsoron Allah a ransu,, ai zamanin yanzu sae addu'a, gwaggo ta fadi haka yayinda take miqowa farhan tea mai zafi sae qamshin ginger ke tashi a cikin sa.
   Sae da farhan ya kur6a yaji zafin dai dai sannan ya shiga lalla6a Afrah har  ya samu tasha ya kuma bata magani.
  Nan bacci mai nauyi ya kwashe ta farhan ya shiga shafa magani a hankali kan gefen fuskar ta da ya kumbura.

A 6angaren leesa kuwa akan ta ruwa suka qare tayi yawon neman taxi har ta gaji, ga cajin wayar ta ya qare bare ta kira mom farida azo a dauke ta.
   Sae da ruwa suka dauke tsaf sannan ta sami abin hawa,ta tafi cike da tunanin wata mafita kala kala a cikin ranta.

Tana shiga gida ta hadu  da mom farida tana saukowa kan staircase ta kalli leesa da jiqe sharkaf da ruwa duk ta galabaita kamar kazar da tasha kashin ruwa.

Farida tace"ya haka keda nake ta  sauraren kiran ki na aika miki mota....bari kawai mom farida gayen ya mugun hallakani ashe kwata kwata bai san aikin sa ba wlh! ban san me yasa yazo shi kadai ba ya kuma tsaya er qaramar yarinya tana ja'inja da shi har ta bude gambu mota ta fado,wanda hakan yayi dai dai da isowar farhan, dole ya gudu buqata bata biya ba.

Kuma wani  abin takaici nan farhan ya barni,duk da irin kukan da na mishi ina bashi haquri abinda ban ta6a yiwa wani d'a namiji ba, amma ya tafi ya barni wai shi ba zai iya biya wa wani guri ba sbd halin da Afrah take ciki,shine ya wani bani kudin taxi bayan ba alamar taxi a gurin.
   Amma lallai farhan din nan shi bai lura da ba abin hawa ba ko kuma ya manta cewa idan ana ruwan sama abin hawa wuya yake....mom farida Ta ya zai fahimci hakan bayan gold dissa na cikin matsala.
   Gashi shi kuma dan iskan gayen can nayi kiran shi a waya yafi a qirga akan kiran sa ne ma cajin wayata ya qare bai d'aga ba, daga qarshe ma sae yayi rejecting, wanda hakan ya nuna min ya gudu da mota da kuma kudi ba tare da ya biya min buqata ta ba.
   Hm ai mutanen basu da kirki domin tunda naji kince shi kadai yaje nasan bai sanar da sauran ba don kawai yaci kudin shi ka dai.
   Hake ne man,gashi yanzu zafi uku uku kenan bana ga mota da kudi bana ga biyan buqata na kuma sha kashin ruwa a banza, ,kuma wai duk akan er qaramar yarinya hakan ta faru dani,amma na rantse... Mtsw mom bari kawai na watso ruwa na dawo na gaya miki wata mafitar!

Hm ko ce mata akayi idan Allah ya kare bawansa akwai wani mahaluqi da ya isa ya cutar da shi.
   Muje zuwa dai muga abinda leesa ke shirin yi wanda take tunanin Allah zai bata sa'a.

*```Futha Luv💅& Billy giro😊```*

®NWA✍🏻
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:20PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [ 7/31/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
    ~*```AFRAH KO AMRAH```* ~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*Na*

*Bilkeesu giro😊 & Bilqis Sidibe💅*

🏅2️⃣0️⃣🏅
Yana shiga ya dorawa Afrah bindiga a goshi, ta juyo tana kallon shi a tsorace har tana qoqarin fara kuka yace"shiiii!ba abinda zan miki ni abokin uncle din ki ne yawo xamu je na siyo miki kayan wasa daga nan mu wuce gurin uncle.
   Da yake Afrah mugun tsoron bindiga ne da ita bata bi ta kan abinda yake fada ba ta shiga kuka tana kiran "Anty"
  Leesa kam tuni ta 6uya sae dae tana hango duk abinda ke faruwa.
 Ganin yanda Afrah ke kuka har tana qoqarin tona mai asiri yasa ya 6oye bindiga domin ya

fahimci ya yi babban kuskuren nuna mata ita.
Ya jawo ta jikin sa domin ya samu ya lalla6ata ya gudu da ita cikin kwanciyar hankali.
Afrah kam ta riga ta tsorata da shi sae fizgar jikin ta take yayinda sautin kukan ta ke qara fitowa,ta manna masa uban cixo a hannun sa da ya rufe mata baki.
Cikin zafin nama ya kai mata mari sbd jin zafin cizo.
Nan tayi baya kanta ya bugi gambun mota sae kawai gambun motar ya bude ta suntu6a waje, da yake dama gambun motar a bude yake shine bai san da hakan ba.
Sosai ya shiga rudu bcs Afrah na faduwa wata mota ta tsaya close to Afrah.
Rudun sa ne ya qaru hango wanda ke ciki, ai ko ba shiri ya rufe gambun motar ya tafi agurguje.
Farhan ne ya fito daga motar ya nufi Afrah cikin hanzari ya dauke ta sae kuka take yayinda jini ke fita a gefen bakin ta.
duk ta rikice ta qanqame farhan sosai tana ci gaba da kuka.
Idanun farhan sukayi jajiri sae kallon motar da wuce yake ko zai gane wanda ke cikin motar.
Leesa ce tazo da gudu yayinda farhan zai saka Afrah a mota, sbd ko kadan baya son ruwan sama su ta6a ta sabida zazza6i suke sata.
Bai saka Afrah a mota ba sae wani  mugun kallo da ya bi leesa da shi har sae da yasa hantar cikin ta kadawa ta saki lemar da ke hannun ta.
Yace"wane irin shashanci ne zaki bar min Afrah gurin wani  bnza can har yana qoqarin hallaka ta!
Wata irin ajiyar zuciya ta sauke a 6oye sbd ta fahimci bai gane ainihin abinda take shirin aikatawa ba.

Nan ta shiga fitar da hawayen munafurci wanda duk ruwan da ake kelawa kana hango gangarowar da suke kan kumatun ta.

Cikin murya kuka tare da qara marairaice murya tace"wlh farhan ita kadai na bari a mota sbd ruwan da naga anayi,sai na tafi ni kadài, ban ko qarasa ba na hango wani ya shiga motar yana qoqarin guduwa da Afrah shine nazo da gudu, amma wlh *Ban sanshi ba* gashi ya gudu da mota ta da kuma maqudan kudin da ke ciki.
Sae dae ba damuwa ta bane tunda anyi sa'a bai je da Afrah ba,amma don Allah kayi haquri da nasan hakan zai faru da bamu zo ba.
Farhan yayi shiru yana son gasgata zancen leesa har dai yanda take kuka tana ci gaba da roqon sa.
Nan yaji ta bashi tausayi ya zaro kudi a aljihu ya bata yace kiyi haquri a halin da Afrah take ciki bana jin zan iya biya wa wani  guri.

😂zo kuka leesa a wannan lokaci sororo tayi ta saki baki tana kallon farhan ko godiya ta kasa mishi har ya shiga mota ya tafi ya bar  ta nan tsaye ruwa na faman dukan ta,
ga lema tabi iska kuma gurin ba alamar zata sami taxi sbd ruwan da ake.

😂zafi biyu kenan buqata bata biya ba tasha kashin ruwa.

Farhan na isa gida ya dauki Afrah dake kuka tana rawar sanyi ya tafi da ita 6angaren gwaggo ya cire mata kayan jikinta da suka jiqe,
gwaggo tace"lafiya me yake faruwa da ita naga jini a gefen bakin ta kuma sae kuka take tana rawar sanyi?
 Cike da damuwa farhan ya bawa gwaggo Afrah yace don Allah gwaggo a gasa mata jikin ta da ruwa masu zafi tukun.

 Nan gwaggo ta shiga da ita toilet, farhan ya tafi ya canxo tufafi ya dawo yana da sintiri a bakin qofar toilet kyace wanda yakai patient asibiti yana jiran fitowar doctor.
   Sae da gwaggo ta d'an jima kafin take fitowa dauke da Afrah dunqule cikin towel, farhan ya amshe ta yana kallon fuskar ta  da ya fahimci marin qwarai aka mata dmn yatsu sun kwanta tsaf kuma har gurin ya kumbura.
   Sosai yaji ta bashi tausayi yaje da ita kan bed ya zauna ya shafa mata mai ya saka mata tufafi sannan ya shiga yiwa gwaggo bayanin abinda ya faru.
   Gwaggo tayi taslima tace"ni har naga rashin haqurin ka da kace zaka bi bayan su hankalin ka bai kwanta ba, ashe wani mummunan  abu ke shirin faruwa, oh Allah ya qara tsare ki Afrah,,amin gwaggo,na rasa meyasa yanzu mutane ba tsoron Allah a ransu,, ai zamanin yanzu sae addu'a, gwaggo ta fadi haka yayinda take miqowa farhan tea mai zafi sae qamshin ginger ke tashi a cikin sa.
   Sae da farhan ya kur6a yaji zafin dai dai sannan ya shiga lalla6a Afrah har  ya samu tasha ya kuma bata magani.
  Nan bacci mai nauyi ya kwashe ta farhan ya shiga shafa mata magani a hankali kan gefen fuskar ta da ya kumbura.

A 6angaren leesa kuwa akan ta ruwa suka qare tayi yawon neman taxi har ta gaji, ga cajin wayar ta ya qare bare ta kira mom farida azo a dauke ta.
   Sae da ruwa suka dauke tsaf sannan ta sami abin hawa,ta tafi cike da tunanin wata mafita kala kala a cikin ranta.

Tana shiga gida ta hadu  da mom farida tana saukowa kan staircase ta kalli leesa da ta jiqe sharkaf da ruwa duk ta galabaita kamar kazar da tasha kashin ruwa.

Farida tace"ya haka keda nake ta  sauraren kiran ki na aika miki mota....bari kawai mom farida gayen ya mugun hallakani ashe kwata kwata bai san aikin sa ba wlh! ban san me yasa yazo shi kadai ba ya kuma tsaya er qaramar yarinya tana ja'inja da shi har ta bude gambu mota ta fado,wanda hakan yayi dai dai da isowar farhan, dole ya gudu buqata bata biya ba.
 Kuma wani  abin takaici nan farhan ya barni,duk da irin kukan da na mishi ina bashi haquri abinda ban ta6a yiwa wani d'a namiji ba, amma ya tafi ya barni wai shi ba zai iya biya wa wani guri ba sbd halin da Afrah take ciki,shine ya wani bani kudin taxi bayan ba alamar taxi a gurin.
   Amma lallai farhan din nan shi bai lura da ba abin hawa ba ko kuma ya manta cewa idan ana ruwan sama abin hawa wuya yake....mom farida Ta ya zai fahimci hakan bayan gold dissa na

cikin matsala.
Gashi shi kuma dan iskan gayen can nayi kiran shi a waya yafi a qirga akan kiran sa ne ma cajin wayata ya qare bai d'aga ba, daga qarshe ma sae yayi rejecting, wanda hakan ya nuna min ya gudu da mota da kuma kudi ba tare da ya biya min buqata ta ba.
Hm ai mutanen basu da kirki domin tunda naji kince shi kadai yaje nasan bai sanar da sauran ba don kawai yaci kudin shi ka dai.
Hake ne man,gashi yanzu zafi uku uku kenan bana ga mota da kudi bana ga biyan buqata, na kuma sha kashin ruwa a banza, ,kuma wai duk akan er qaramar yarinya hakan ta faru dani,amma na rantse... Mtsw mom bari kawai na watso ruwa na dawo na gaya miki wata mafitar!

Hm ko ce mata akayi idan Allah ya kare bawansa akwai wani mahaluqi da ya isa ya cutar da shi.
Muje zuwa dai muga abinda leesa ke shirin yi wanda take tunanin Allah zai bata sa'a.

*```Futha Luv💅& Billy giro😊```*

®NWA✍🏻
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:20PM, 11/30/2016] Billy Geeero: : [ 8/1/2016]
~*AFRAH KO AMRAH* ~

*Na*
*Billy giro😊 & Bilqis Sidibe💅*

🏅2️⃣1️⃣🏅
Bayan Leesa ta fito daga wanka ne, take ce ma, mom farida"ni shawarar da na yanke itace"dole zan koma gurin boka sbd na fahimci duk inda Afrah ta shiga farhan na biye da ita hakan kuwa zai min wahalar sace ta kuma asiri na zai iya tonuwa tunda ko yanzu ban san cewa yabi bayan mu
Don haka abin da naga yafi sauqi zan je gurin wani boka na da ke min aiki domin bai ta6a min aiki bai ci ba,kuma ba magani yake ba mutum yayi aiki da kansa ba,
Shi da kansa yake aikin domin aljani yake turama wanda za'a yi ma aikin,kuma da ya tura aljanin komai ya kammalu,,amma akan Afrah za'ayi aikin ba farhan ba, domin Afrah yarinya ce ba addu'a ta sani ba,don haka nake so ya tura mata baqin aljani lokacin da taje makaranta ta 6ace 6at aljanin ya kai ta wata uwa duniya ko kuma a mata kurciya tabi duniya!
Shike nan matsala ta ta tafi!shi kuwa farhan ko zai iya ganin aljanin yabi bayan shi oho!
Mom farida ta kwashe da dariya tace yaga me!ai daga ranar shida afrah sae dae a mafarki ko zai gan ta.
Bare ma nafi son ayi aikin kafin a tashi daga school koda zai je daukar ta sae dae ya samu bata nan"leesa tayi maganar kafin suke tafawa ita da mom farida.

Sae da akayi kwana biyu sannan leesa ta tafi qauyen da bokan yake,cike da murna ta dawo domin ganin take har aikin yayi,sae sauraren gobe take sbd sae gobe yace mata za'ayi aikin.

Haka ko akayi domin washe gari farhan yaje daukar Afrah da wuri wanda yana ma tsaye aka buga tashi,

amma koda yaje class d'in su bai ganta ba, har kowa ya watse farhan na ta faman neman Afrah shida uncle Basheer wanda sunyi kusan awa d'aya suna neman ta basu gan ta ba kuma duk inda ake tunanin yaro mai rashin ji na shiga bata can.

Nan farhan yace da uncle Basheer ko dai JB ya dauke ta? Bana tunanin haka sbd junaid tun kafin a tashi ya fita.

Ai kuwa nan hankalin farhan ya tashi sosai dmn Afrah bata ta6a mishi haka ba duk yazo daukar ta yana samun ta.

Bai bar makarantar ba sae ma zama da yayi cikin mota tare da dora kansa a sitarin mota.........unce!firgitgit ya dago kanshi ya fito cikin motar da sauri,yayinda Afrah tazo da gudu ta fada jikin sa, ya qanqame ta sosai kamar wanda ya shekara bai ganta ba.

Ya kalli JB da ke tare da su yana faman murmushi yace"Afwan ba haka naso ba wlh"

Ba wani gsky kasa na tsora ta kasan fa abinda ya faru da Afrah bayan kwana biyun nan,shine ka fita da ita kafin a tashi da school don kawai hankali na ya tashi....yi haquri na manta da waya ta ne da na kira ka na sanar da kai,to me ya fitar da ku ba'a ko tashi ba?wlh Afrah ce yau rashin jinta ya motsa... Farhan yayi dariya yace"waya gaya ma motsawa yake ai kullum tana tare da rashin ji,,,a'a my little wife kam tana jin magana yau dai ne,,,farhan dai murmushi kawai yayi domin ya fahimci Jb baya son ana ce ma Afrah bata ji, yace"to naji tana jin magana amma kuma yau wa ta tsokana?ita da wata ce suka qullah ko er me.... Keep and go only me! cewar Afrah,JB yace to kaji, to da suka qulla ita Afrah kullum akace mata keep and go bata ajiye wa ko kallon kirki ma baza ta ma ta ba, amma ita Afrah da tace dole a ajiye taci, to shine yau qawar ta wacce suka qullah abun, ta gaji sae da ta bari Afrah taje break fast ta kwashe kaf sweets din da ke cikin jakar Afrah ta cinye gasu da yawa fa,nan fada ya hadu tsakanin su sae da nace tazo muje na siyo mata wani sweets,,,farhan ya bude ido yace kace sweet din da yawa?sosai kuwa ba kai ke bata ba?JB kasan Allah wlh bana ba Afrah sweets da yawa bcs bana son tana shan zaqi sosai...cab ai kuwa duk makarantar nan Afrah tafi kowa shan sweets, domin har suna aka sa musu ita da qawar ta Amrah,Afrah sweet,Amrah chewing gum haka ake kiran su, domin ko yaushe ka gansu even during class ma zaka sami Afrah da sweet a bakin ta Amrah kuwa chewing gum, not only break fast time.

Cike da damuwa farhan ya lumshe ido yace"oh Allah"sannan ya kalli Afrah wacce ta noke fuskar ta a cikin jikin sa,wanda ya fahimci ko yanzu sweet ne a bakin ta,ya fara magana cikin fada yace "poppy luv! Kinsan bana son ki dauki abu ba tambaya,amma shine kullum kike yi!meyasa! nace me yasa!?dago idon ta tayi wanda har hawaye sun fara fitowa dmn ko kadan bata son fada har dai idan farhan ke mata shi, kama kunnen ta tayi tace"please uncle am sorry"wace ce qawar ki Amrah?motar JB ta nuna mai, wanda yayi dai dai da fitowar Amrah ciki domin tun dazu bacci take sae yanzu ta farka, farhan yace"that's y ashe wannan Amrah ce qawar ki shiyasa rashin jin ya hadu guri daya, Amrah da bata san me ake ciki ba tazo da

murnar ta gurin farhan tace"lah uncle dama Kaine uncle din Afrah"nine Amrah ina dad da bai zo daukar ki ba? Mun hadu  dashi kan hanya  uncle JB yace da shi idan ya siyo mana sweets zai maida ni gida, to meyasa ba a maida ke ba bayan an siyo? Afrah tace tana son taje gidan mu shine yace mu fara zuwa school tukun muga idan kazo, farhan ya kalli Afrah wacce tayi saurin nokewa kan jikin sa tana ci gaba da kuka.
   Yace da Amrah ok muje na maida ki gida.
   Nan sukayi sallama da JB  suka wuce.
   Har aka kai Amrah gida suka zo gida Afrah bata sake cewa komai ba duk da cewa ta daina kuka,ta dai qi magana ne sbd farhan yaqi sake mata fuska.

Da shigar su farhan ya wuce 6angaren shi Afrah ta wuce 6angaren gwaggo.

Sae da yayi wanka ya tafi 6angaren gwaggo ya samu ita ma Afrah an mata wanka nan ya jawo musu abincin su suka ci.

Da suka gama cin abinci ne Afrah ta kalli farhan dake fira shida gwaggo cike da nishadi, nan taji qarfin cewa"unce a ina kasan Abban Amrah....a gidan ku na sanshi!nan Afrah ta le6a ce baki zuwa kuka ta tafi da gudu ta fad'a jikin gwaggo.
   gwaggo tace"yau kuma kai ke fada da Afrah abinda ban ta6a gani ba,,Afrah ba taji gwaggo wai ace ta debi sweet bata sanar da ni ko ke ba, tabi'ar da na tsana a rayuwa ta shi Afrah keyi,sweet din da ba kullum nake bari taje da shi ba,ashe aikin banza nake har qarawa take akan wanda na bata....ya isa farhan kaga sae kuka take,, haba gwaggo bafa tabi'a mai kyau bace,kamar halin 6era ne wanda  zai iya bin ta har girma.

 Haka ne kuma,ke kuma Afrah kar ki sake yin haka ba kyau,, shidai farhan bai ce komai ba ya tashi zai fita,cikin kuka Afrah taje ta tarbo gaban shi, tace"pls uncle kayi haquri bazan sake ba"farhan yayi tsaye yana kallon ta wanda kallo d'aya zakayi masa kasan yana jin zafin kukan da take yana jurewa ne kawai.
  Sauke ajiyar zuciya yayi yace shike nan,idan kika sake... kamin dukan tsiya har sae nayi kukan jini,gwaggo ce ta fara dariya kafin  farhan yace"lallai akan ki zan sayi bulala na ajiye, ya fadi haka ne yayinda ya ja hanun ta suka zauna ya shiga share mata hawaye,yace idan kika sake rashin ji kuma zan kai boarding school ne,girgiza kanta tayi tace"Allah uncle bana son boarding school nayi qanqanta,ai ba yanzu zan kai ki ba sae kin shiga secondary,maqale kafada tayi tace"gsky uncle bana so,amma idan na sake tsokanar wani na yarda,haka kike ce?eh,,
 to shike nan gwaggo ki zama shaida.
  Gwaggo dai murmushi kawai tayi amma tasan da wuya Afrah ta daina tsokana, farhan kuwa bazai iya rabuwa da Afrah  na en kwanaki ba bare zancen boarding school.

*Billy giro😊&Futha Luv💅*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:20PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [8/4/2016] Billy giro😊: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
   ~*AFRAH KO AMRAH* ~

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*Na*
*Bilkeesu giro😊&Bilqis Sidibe💅*

🏅2️⃣2️⃣🏅
A 6angaren leesa kuwa tun lokacin da farhan ya fito da su Afrah school har suka je gida tana biye da su.
Inda kanta ya daure sosai na ganin Afrah tare da farhan kuma tana da tabbacin boka ya turo baqin aljani sbd tun da farar safiya taje qauyen gudun kar ya manta wanda a gaban idon ta taji boka yayi magana da baqin aljani ya tura shi gun Afrah.

Cike da baqin ciki ta koma gida sae dai kuma tana isa gate ta kasa shiga sae juya akalar motar ta tayi zuwa qauyen da bokan yake.

Da zuwan ta bokan ya tarbe ta da maganar domin duk abinda ke faruwa baqin aljani ya sanar da shi.
Dogon bincike ya shiga yi a cikin qwayar tsafin sa yayinda ya shiga kallon rayuwar Afrah tun lokacin da aka haifi Afrah har izuwa yanzu yana ganin komai tamkar video.
Long time da qare binciken sa yayi shiru,sae zufa ke karyo masa ya kasa ce ma leesa komai domin tabbas a cikin rayuwar Afrah ya hango wani abu da ke sa duk mugun nufi baya fadawa akanta ,amma ba zai sanar da leesa ba har sae ya qara shan romonta ko zai iya sanar da ita daga baya,leesa ta katse shi da cewa"lafiya dai boka ko da wata matsala ne?akwai er matsala domin wannan yarinya da kike gani aiki daya baya yi da ita,
kamar ya?ina nufin sae mun maimata abin da mukayi jiya,gaban ta ne ya bada ras domin ko kadan bata son maimata abin da sukayi jiya,ko fama da doyin jikin sa aiki ne bare kuma wani baqin garin magani da yake yi yana shafa mata a gaban ta.
Cike da damuwa ta kalli bokan tace"ba wata hanya ne sae wannan? Inace tun jiya na sanar da ke,ba wata hanya sae ita, domin kusan ta ta dake tamkar muna kusan to rabuwar Afrah da Farhan ne,, haka ne kuma ka gaya min,, amma ki sani wannan karon bayan haka ta faru zamuyi wanka a tare da mazubin ruwa daya, ina fatar kin fahimta.
Shiru leesa tayi ita wankan ba matsala bane a gurin ta irin hada jiki da shi amma tabbas idan zai kawo rabuwar Afrah da farhan zata yi koma me ne.
Nan tace"da bokan na amince,nan boka ya washe wargazazzun jajayen haqoran sa har ana hango wani yauqi a bakin sa sbd daud'a.
Daga nan suka shiga daki domin aikata mummunan aiki.

Wa iyazu billah.

********

Haka rayuwa taci gaba inda lokaci ya tafi sosai domin su Afrah har an kammala primary school.

Yayinda leesa keta rabon ido na ganin 6acewar Afrah amma shiru har anyi shekaru.

ga boka sae yaudarar ta yake yana sheqe ayar sa da ita a duk qarshen wata wanda yaso ace kullum yake samun hakan, sae dae karatun da ta fara yi ne a Abuja bazai basu wannan damar ba.

Leesa har ta fara gajiya ganin aiki yaqi ci yaqi cinye wa hakan yasa ta fara tunanin ko wata mafita zata nemo.

Zaune take sae tunanin mafita take, mom farida ce tazo ta same ta.

Fuskar ta a daure tace"leesa nifa na gaji da shirmen da kuke keda bokan ki, wane irin abu ne kusan shekaru hudu magani bai ci ba,wai kuma sae faman abu d'aya ake ba canji.

Nima mom farida abun yana damuna sosai kullum sae yace min aiki ya kusa ci tsirif ya rage amma shiru har na gaji, shine yanzu nake tunanin wata mafita..

....mtsw ni yanzu na gaji da jin shawarar ki ace yanzu duk yanda kuka shaqu da farhan har ya dauke ki kamar er uwa ace kin kasa masa kissar mata ki kai masa takardu ya sa hannu kin tsaya sake da baki wai sae ya fara sonki!

Haba mom farida koda ace farhan ya fara sona ta ya zan kai masa tarkadu ya sa hannu ko takardu wadan da idan ya gansu na gama yawo tunda akan hayyacin sa yake dole ya fahimci takardu waye......lallai yanzu ke dama duk a tunanin ki sae ya san takardun mene ne zai yiwa signing,ke mace ce fa kina iya kai masa takardu a matsayin wasu takardun asibiti ne,tunda kema karatun asibiti kike, se ki samu ki jashi da fira har ya sa hannu ki kar6i abinki bai san yayi ba.

Hmm mom farida wlh farhan na daban ne komai akan tsari yake yinsa ba a yanda kike tunani ba....to lallai kuwa zanyi aikin da kai na idan ke baza ki iya ba, ga hanyoyi da dama sunzo har dai yanzu da Afrah ta fara girma ko mutuwa farhan yayi bani da baqin ciki sbd Afrah zata iya sa hannu akan tarkardun tunda dama mallakin ta ne.... A'a don Allah kar ki sa a kashe farhan ki qara bani lokaci zanyi duk abinda kike so.... gaskiya leesa sae dae kiyi haquri da son farhan domin son da kike mishi bashi zai sa na fasa aiwatar da abinda nayi niya ba!tana gama fada ta fice.

Yayinda leesa ta shiga tension tasan ba makawa mom farida zata iya sa a kashe farhan ta kuma sa a kama Afrah tayi signing akan dole.

Kut "dole na hana faruwar hakan domin don son farhan kadai nake wannan yaqin ba don ki mallaki dukiyar ba"

ta fadi haka ne a fili kafin take barin falon.

🏅2️⃣3️⃣🏅
Afrah ce kwance kan bed sai sharar bacci take,wacce yanxu zata kai 12yrs ta qara kyau fiye da yanda take yarinya domin kamar yanzu ne asalin kyanta ke fitowa.
Ta dan qara jiki ba kamar da da take sililya ba yanzu dai dai take ba qiba ba rama.

Farhan ne ya shigo cikin sauri yana fad'in poppy luv! yana hango ta kan bed yayi saurin rufe bakin sa yace da gwaggo da ta sallame sallah"ashe bacci afrah keyi nake faman kiran ta,, gwaggo tace"ai da ka tashe ta da kar ka tashe ta kasan farkawa zatayi tunda ka shigo dakin"saurin fita zanyi kafin ta farka dama so nayi muje a siyo kayan makarantar ta,bcs ban sani ba ko akwai wani abinda zata buqata....wai Farhan da gaske kake zancen kai Afrah boarding school,eh mana gwaggo kinsan rashin jin Afrah sae abinda ya qaru gashi kuma har yanzu bata daina kukan zuwa school ba,shine abun ke damuna sosai...amma farhan bata yi qanqata ba kuwa, no akwai iren iren ta a can, kuma ko ban kai Afrah boarding ba dole na canza mata school bcs of *JB international school* din nan da take ciki kwata kwata JB ya shagwa6a ta duk abinda ta ga dama yi take,wanda ba don gifted ce ba da sae dae ta riqa cije bindi kan shiririta.

Haka ne kuma da har na so nace kabar ta school din tayi boarding a ciki tunda makarantar akwai borders amma bayanin da kamin na fahimta, sae dai kasan JB ba zai ji dad'i ba har dai a yanda suka shaqu shida Afrah, haquri zai yi domin bana son rashin jin Afrah ya kai ta ga ta6ar6arewar tarbiyarta.
Ni zan fice ina sauri sbd zan koma asibiti anjima gashi da safe ne zamuyi tafiyar.
Nan ya kama hanya zai fita....Afrah wacce tun dazu ta farka taji duk abinda suke fadi, tace"uncle wlh bana son boarding school, at all bana son a canza min school, jiki sa6ule yaje ya zauna kusa da ita cikin muryar lallashi yace"poppy luv haquri zakiyi, sbd gaskiya ba zan ajiye zancen boarding school ba bcs na gaji da rashin jin ki kuma keda kanki kika ce idan baki daina rashin ji ba akai ki boarding school kin tuna...uhm uhm no uncle i cant remember ,please kar ka kai ni boarding school,ta fadi haka ne yayinda ta kwanta kan cinyoyinsa tana ci gaba da kuka.
Am sorry Afrah na riga na yanke hukunci ba kuma zan canza ba,, hawaye sha6e2 ta dago tana kallon shi tace"yanzu uncle so kake naje inda ban san kowa ba, ba kai ba gwaggo ba Amrah ba uncle JB ni kadai ban san kowa ba kamar wacce aka tsinta"
tayi maganar ne cike da muryar kuka had'e da shagwa6a har ma ba a gane me take fada sosai.
Komai farhan ya kasa ce mata sbd duk kukan da take bai ta6a jin zafin da yake ji a ransa kamar yanda yake ji yanzu ba.
Nan ya tashi ya fita ya bar Afrah sae kuka take yana jin tana roqon gwaggo kan ta roqa mata shi.
Gwaggo dai haquri kawai ta shiga bata.

Sosai ya jima kafin yake dawo wa dauke da kaya niqi niqi Afrah na ganin shi ta turo baki tare da kauda kai akasin kullum da take tarbo shi da gudu ta kar6i kaya.

Gwaggo ce ta taimaka masa ta kar6i wasu kayan sbd sunyi masa yawa a hannu ga kuma wasu

kayan da mai gadi ya shigo da su.

A gajiya farhan ya zauna kusa da Afrah da taqi yarda ta kalli ko gefen da ya zauna, yace duba kiga na siyo miki duk abinda kike so,har da wani sabon chocolate na siyo miki kingan shi, Afrah kam kamar ba da ita farhan ke magana ba ko kallon chocolate din taqi, yace"to albishirin ki"nan ma ta masa shiru, yace"Afrah ni kike sharewa,, uhm uhm ta fadi inaji"sae kin duba sayayyar da na miki tukun,
nan Afrah ta shiga duba komai da taga kamar na mutum biyu ne,tace"uncle siyayyar kamar ta mutum biyu ce"lumshe idon shi yayi yace"keda Amrah zaku je.... Yeee! uncle thank u!ta fadi hakane yayinda ta maqale shi,tana murna nan take kuma idon ta suka ciko da qwalla tace "but uncle I gonna miss u"no my Afrah zan riqa zuwa miki visit every month kinji... Maqale kafada tayi tace"ni kullum nake so kaje"...ba zai yiyu ba Afrah,yana fadar haka ta fashe masa da kuka yace"um um my Afrah stop crying idan ba so kike ko a month kar naje ba.
Kuka take ji sosai amma haka ta haqura ta share hawayen ta domin tana son ya riqa zuwar mata.
Wayar farhan tayi qara ya daga wayar yayi magana ta en mintina ya bawa Afrah tare da fadin ga Amrah kuyi magana ita ma taji labari a bakin abban ta sea murna take ke kinxo kina kuka.
Nan ta kar6i wayar wanda sun jima suna wayar hakan yasa damuwar Afrah ta d'an ragu.

Farhan ya kalli agogo yace gwaggo bari naje na shirya na tafi asibiti..... Zanje uncle, ok to...kash sorry JB ya kira ni a waya yace zai zo ki kaima mamansa yawo bcs yaji zanjen zan kaiki school gobe shine ya buqaci haka,ok uncle yaushe zai zo?inaga yana kan hanya ki shirya kafin ya qaraso.

Kafin farhan ya fita har Jb yazo a tare suka fita inda farhan ya nufi hanyar asibiti Jb ya nufi hanyar gidan su.

Suna shiga Jb ya hadu da wata er uwar shi wacce bazata wuce 15 yrs ba tazo da gudu ta tarbe shi, ta kalli Afrah sau daya ta kauda kai.

Suna shiga falo umman JB na ganin shi da Afrah ta bala'in sha mai toka.
Afrah ta gaishe ta, ta amsa mata ciki ciki.
ta wuce fuuu zuwa upstairs, nan Jb yabi bayan ta suka je daki,inda ta shiga yi masa fada sosai kan cewa tun dazu Nina tazo tana faman jiran ka amma kayi zaman ka shine da zaka shigo kawani kwaso Afrah kuka zo tare don kawai ka nuna min baka da buqata da Nina ita da ma ar er uwarka..mom ba haka bane wlh tafiya Afrah zatayi gobe to boarding school,
shine na kawo ta bcs bata ta6a zuwa nan gidan ba kullum nace zan kawo ta sae kice min a'a... But about Nina inace kina zancen ne kawai shiyasa ban dauki abun serious ba bcs kinsan da zancen Afrah,, junaid ni qaramar yarinya ce da kullum zan zauna ina maka zancen da bashi bane, haba mom gsky ni Afrah nake so kuma zan iya jiran ta... Ni kuma bazan iya jiran ta ba junaid domin na matsu na ga en jikoki na, inace qaramar yarinya kake so ka aura ai ko Nina

yarinya ce...no mom nifa ba zancen qaramar yarinya nake ba kawai dai Afrah nake so... bari kaji in gaya ma dole sae ka auri Nina in yaso daga baya ka iya auro Afrah... gasky umma bana ra'ayin mata biyu...to ko mahaifin ka da ya fika cijewa ya amince da zance na, don haka tun wuri ka sani Nina na kammala makarantar ta za'a daura auren ku,,JB ya kalli umman sa cike da son yayi kuka ta qara da cewa kuma yanzu yanzu nan kaje kuyo shopping kai da Nina domin ban kwana tazo mana gobe zata koma Abuja sbd hutun makarantar su ya qare.

Ba yanda Jb ya iya haka yaja Afrah da Nina domin zuwa shopping.

Sae dai tun da suka shiga mota ran Junaid ya qara 6aci har dai yanda yaga Nina ta shige gaban mota ta bar Afrah baya,kuma sae faman hararar Afrah take ta jikin mirror se dai shi bai lura da hakan ba, sae Afrah da ta lura wacce jin take idan nina ta matsa da hararar ta zata iya dambe da ita ba ruwan ta da ganin nina ta girme ta domin ko kadan bata daukar raini nan tace"uncle JB ni ka maida ni gida"shopping zamu je yi Afrah ki bari idan muka dawo....no uncle ni ina son na koma gida, jB da baya son ganin 6acin ran Afrah nan ya garzaya ya maida ita gida.

Amma da sukayo shopping sae da yakai mata tulin kayan da ya siyo mata wanda hakan ya qara sa Nina ta qara jin haushin Afrah.

Da dare gwaggo ce ta packer musu komai Abban Amrah ya kawo ta nan gidan ta kwana sbd jirgin safe zasu bi zuwa abuja bcs a cikin garin Abuja farhan ya nema musu makaranta.

Da safe Afrah na tashi tayi arba da kayan su da aka packer,

ai kuwa tayi zaune tana ta rusar kuka da qyar gwaggo ta rarrashe ta taje tayi wanka ita ma Amrah tayi wanka suka shirya,

farhan yazo sukayi break fast sae kallon Afrah yake wacce tayi suka suku.

Suna gama cin abinci suka kama hanyar airport.

Koda suka sauka garin Abuja wata mata wacce ake kira da"Hajiya saudah wato mahaifiya ga fu'ad"

da yake dama fu'ad mazauna garin abuja ne aiki ne yakai sa garin bauci.

Itace ta tarbi su farhan suka je har makarantar a tare sbd itace VC din makantar abu ga mai galihu har hostel farhan ya bisu bcs duk student na class, shida kanshi ya za6a musu room dinda zasu zauna wanda bai wuce daukar mutum biyu ba,wanda ba don galihu ba da sae dae su zauna dogon room.

Farhan ne ya tsara musu komai yanda ya dace kamar wani mace wanda yayi haka ne don kawai ya samu Afrah ta sake,duk da haka bai hana Afrah taci kuka kafin ya bar makarantar ba.

Tafe yake cikin garin bauci ya fito daga airport sbd har jirgin su na dawowa ya sauka.

Leesa ce keta faman sheqa gudu tana biyar farhan a baya duk tabi ta rikice tana ta faman kiran farhan ta waya sai dai line busy bcs a lokacin waya yake da Afrah wacce har yanzu kuka ta ke.

Leesa da qyar ta samu wayar farhan ta shiga, sae dae
Hankalin ta ne ya gama tashi hango tayoyin motar farhan da suka fara juyi kafin kace me har tayar gaba ta cire inda motar ta shiga juyi da farhan wanda sae faman salati yake yana qoqarin ganin motar ta tsaya amma ina! tuni ta fada daji tana kaurar itatuwa long time kafin take haduwa da wani qaton dutse ta tsaya se hayaqi ke fita a cikin ta.

Leesa kuwa tana qarasowa ta fito mota da gudu,
sosai ta shiga rudu hango motar farhan yanda tayi daqa daqa kamar ba d'an Adam a ciki.

Taro ya hadu sosai sbd hanyar ta kasance ta mutane,tambayar leesa suka shiga yi ko dan uwan ta ne amma tamkar da statue(gunki) suke zancen, hakan yasa wasu daga ciki suka tafi domin bawa farhan taimakon gaggawa,kafin a samu a kira en sanda,

Anyi minti talatin kafin ake samun fitar da farhan a cikin motar, fararen kayan sa duk sun rine zuwa ja.

Nan en sanda suka nemi sanin en uwan
sa inda mutane suka nuna leesa acewar suna sa ran er uwar sa ce,da qyar en sanda suka samu tayi magana inda ta basu numbar gwaggo.
Ta tsure farhan da kallo wanda yake sheme ba ya motsi sae jini da ke ta fita a jikin sa,gaban ta sae dukan uku uku yake bata son aje asibiti taji labarin cewa farhan baya raye.

Police kuwa ana basu numbar gwaggo suka kira ta suka sanar da ita halin da ake ciki.

Ba jimawa suka zo a rikice ita da uncle Basheer da JB wanda yayi dai dai da isowar ambulance.

Ana shiga asibiti su fu'ad suka kar6e shi zuwa theater room gabadaya hanklin fu'ad ya gama tashi ganin fuskar wanda yake shirin treating,hakan ya dake ya danne kukan sa ya shiga bawa Farhan taimakon gaggawa.

Su uncle Basheer suna waje sae faman sintiri suke suna jiran fitowar su fu'ad.

Wayar gwaggo ce tayi qara yayinda umman fu'ad ya bayyana a screen jiki sanyaye ta d'aga wayar sae dai muryar da take sa ran taji ba ita taji ba,muryar Afrah ce taji wacce da ji tasha kuka tace"gwaggo meyasa uncle ya kashe wayar sa, ko yayi fishi dani ne don naqi daina kuka? please gwaggo kice yayi haquri na, daina kuka,ina so nayi magana da shi,gwaggo meyasa kika

yi shiru ko yaqi haqura ne?da qyar gwaggo ta tsaida kukan da take ji yayinda ta shiga tunanin abinda zata ce da Afrah can tace"farhan baya kusa ya d'an d'aga"ok bye gwaggo i wiil call u letter before i back to hostel.

*Futha luv💅&Billy giro😊*

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:20PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [7:15AM, 8/7/2016] Billy giro😊: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
~*AFRAH KO AMRAH* ~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*Na*
*Bilkeesu giro😊& Bilqis Sidibe💅*

🏅2️⃣4️⃣🏅
Nan gwaggo ta kashe wayar jiki sanyaye, tana tunanin ko me za'a fito a sanar da su game da farhan.

Sun jima sosai sannan aka fito dashi,
Fu'ad ne ya nufo gurin su gwaggo,kafin ya qaraso gwaggo ta tafi cikin sauri tace"ya ake ciki,inace dai bai mutu ba ko"
Gwaggo ki kwantar da hankalin ki farhan yana raye sae dae unconscious koma nace ya shiga coma,inda ya sami raunuka da kariya biyu a qafar sa ta hagu,amma kar ki damu gwaggwo sauqi zai zo inshaAllah.
Gwaggo tayi shiru tana fadin"innalillahi wa inna ilaihi raji'un ya Allah ka tashi kafadar farhan.
Fu'ad yace amin kafin yake zuwa dasu dakin da aka kai farhan.

Duk wanda ya shiga sae ya zubar da qwallah bcs gabadaya jikin farhan bandage ne se kussuwar hancin sa kadai sae idanun sa ake gani.

Jikin kowa a mace suka sami guri suka zauna.
Leesa kam kasa zama tayi tana tunanin rashin karamci irin na mom farida domin ita ce tasa akaje har aiport aka banye ma farhan tayar mota, sbd taji hakan da kunnen ta a lokacin da take waya da wanda yayi aikin.
Qarasawa tayi gab dashi tana ci gaba da kallon shi,
fatar ta d'aya kar farhan ya sami wata naqasa a jikin sa,domin dama zubin kyaun sa ne yaja ta.
Nan kuma ta shiga wani tunani idan mom farida taji farhan bai mutu ba zata iya sa azo a qarasashi.nan ta shiga maganar zuci.

_ya zama dole naje na san yanda zanyi da mom farida kar ta sa a qarasa shi, idan kuwa har dukiya take buqata zan bata wasu qadarorin da mahaifina ya mallaka min_
Nan tace da gwaggo Allah ya sauwaqe ni zanje gida na dawo
Gwaggo ta gyda mata kai.

Fitar leesa keda wuya wayar gwaggo ta shiga ruri kallon wayar ta shiga yi tana tunanin me kuma zata ce da Afrah domin bata son tasan wani abu ya faru da farhan.
D'aga wayar tayi tace har yanzu fa bai dawo ba"to gwaggo zan sake kira anjima.. a'a Ku koma hostel haka... Why gwaggo ko dai wai uncle fishi yake dani shine kike 6oye min?a'a ba wani fishi da yake da ke, to gsky ni bazan koma hostel ba sae nayi waya da uncle, shiru tayi tana kallon farhan wanda ba a ma san yaushe ne zai farfad'o ba....kinji gwaggo don Allah ki bar ni na zauna na en minti, da nayi waya da uncle zan koma hostel... haquri zakiyi Afrah.
Kuka ta fashe ma gwaggo dashi cikin shagwa6a tana mai fadin Allah gwaggo dana koma hostel baza a barmu mu fito ba ko yanzu mama ce ta fito da mu, kuma ni bazan iya bacci ba idan banyi waya da uncle ba... Gwaggo kasa ce mata komai tayi tana tunanin dama tasan wataran sae hakan ta faru wannan sabo da farhan ya ma Afrah zata wahala ne wani lokaci....JB ne ya katse ta da cewa gwaggo bani wayar na lallashe ta,
Nan ya qar6i wayar ya qara a kunnen sa tare da fadin Afrah, da sauri ta share hawayen ta cike da jin d'adi tace"yes uncle please kayi haquri ka daina fishi da ni kaji,,Afrah nine uncle JB ba farhan ba...to ina uncle? uncle ya daga kiyi haquri ki koma hostel kinji,nan dai JB yayi ta lalla6ar ta har ya samu ta yadda zata koma hostel.
Nan fu'ad ya kar6i wayar ya sanar da mahaifiyar sa halin da farhan ke ciki don tasan yanda zata riqa yiwa Afrah wayo kar ta sake kira har a samu Allah ya farfado da farhan.
Sosai umman sa ta cika da jimami kafin suke ajiye wayar.

Cike da tausayi umman fu'ad ta qara lalla6ar Afrah sannan suka fice hostel ita da Amrah.

Da dare bacci ya gagari Afrah sbd kwanciyar da ta saba yi kan cinyar farhan kafin ta samu bacci ya dauke ta.
Haka tayi ta juyi tana kallon Amrah wacce tuni tayi baccin ta sharkaf.

Ganin da gaske ta kasa bacci gashi tana jin tsoron kasancewar ta ita kadai a farke,
Nan ta dauko teddy ta wacce ke cike da qamshin turaren farhan wacce farhan ke mata wayo da ita idan ya fahimci baccin ta bai yi nauyi ba kuma yana buqatar ya tashi se ya dauko teddy ya shafe ta da turaren sa ya kwantar da ita kusa da Afrah shi kuma yaje zuwa aikin sa.

Rungume teddyn tayi tana mai shaqar qamhin turaren farhan har ta soma jin tamkar shine a kusa da ita,daga haka kuwa bacci mai nauyi ya kwashe ta.

*Billy giro😊&Futha Luv💅*

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:21PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [8/10/2016] Billy giro😊: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*~AFRAH KO AMRAH ~*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*Bilqis Sidibe💅 & Bilkeesu giro😊*

🏅2️⃣6️⃣🏅
Bala'i!cewar Nina wacce ta d'aga hannu zata kai wa Afrah mari,Afrah ta riqe hannun!tana qoqarin fara dame da Nina.... dakata Nina!kar ki yadda ki had'a jiki da ita zata rainaki banni da shegiya na ci ubanta yanzu na mata dukan tsiya dama ina da cikin ta"
cewar senior wacce suka sami sa6ani da Afrah dazu da safe.

Tana gama fadin haka tayi d'amara tayo cikin Afrah da bulala zata fara dukan ta,
Afrah ta duqa ta kwashi qafafunta sae ga senior qasa tumus, nan Afrah ta haye ruwan cikin ta ta shiga kai mata duka ta koina.

Nina tazo da gudu, Amrah ta tattare ta tana ta bata haquri, yayinda Afrah ke ci gaba da dukan senior wacce ta kasa yunqurawa ta tashi sbd yanda Afrah ta d'obo qasa ta watsa mata a ido ta kuma cika mata baki da ita tana ci gaba da kai mata naushi duk bakin ta yayi jini.

Wannan senior wacce ta ja Afrah da safe ko yanzu ita ce tazo ta ja Afrah,
Wanda yayi dai dai da Nina ta bangaje Amrah tayo cikin Afrah..... Ke! ke!lafiya me yake faruwa"cewar VC wacce ta shigo ganin lafiyar hostel.

Nina bata bi takan Vc ba sae qoqarin take kaiwa Afrah duka,
vc tace"ke Nina ba magana nakeyi da ke ba,me ya had'a ki da Aleesa har kika mata jina jina kuma kina qoqarin had'awa da er qaramar yarinya tahowar jiya jiya.

Nina tace"mama er qaramar yarinyar da kika kira tahowar jiya jiya ai ita ce tayi ma Aleesa jina jina ba ni ba...bana son shashanci Nina na fa san halin ki ta yaya Afrah zata yi wa Aleesa haka ko kunyar fada ba kya ji ace Afrah ce tayiwa Aleesa haka!wlh mama ita ce,
Vc ta kalli Afrah wacce ta wani tunzuro baki kafin
tace wani abu Afrah tace"mama ai sune suka fara tsokana ta"afrah kenan da gaske ke kika yiwa Aleesa haka?eh mama
ita ce wai sae ta dake ni.

Ya salam ikon Allah Afrah ,yanzu er qarama dake kika iya fad'a da babba haka kuma wa ya gaya miki ana dukan senior.....ai barta mama wlh mama yau sae ta sha kashin tsiya... Nina a gabana kike fadin haka ban hana Ku dukan yaran mutane ba bare Afrah er j.s.s one da ba komai suka sani ba....mari na fa tayi mama, kai Nina wai meyasa ba kya iya zama sae kin ma mutum sharri,mama ki tambaya kiji fa ai shine silar fad'an su da Aleesa..... Mama ruwan arwala muka zo d'iba ina tara buta ta ta buge min sae da ta watse,
 ta fad'i haka ne a shagwa6e, Vc taja Afrah jikin ta tana lallashi tace kar kiyi kuka Afrah, ya isa inace Nina yau kun fahimci abinda nake sanar da ku  ko yaushe duk makarantar nan ba wanda yafi Ku yiwa senior rashin mutunci,, sae gashi kun had'u da wacce ta fi ku har tana yin dambe da ku,kuma kar inji kar ingani kuce zakuyi wa Afrah wani  abu,,kema Afrah ki kiyaye dukan siniyo ba a yin haka kinji, sannan ta kalli wacce Afrah ta bawa kashi,idanu sunyi jajir sae fitar da ruwan hawaye suke, ga baki duk ya sundule yana fitar da jini,
tace ke kuma Aleesa ki jira ni yanzu muje clinic a duba ki.
 Nan mama taja su Afrah da Amrah zasu fice, Nina wacce ta kai qololuwar suquwa  tace"haba mama wlh Allah wannan hukun cin baiyi ba, Nina ni kike gaya ma haka, in banda rashin hankali wa zai biye wa d'an j.s.s one,ai sai dai kuyi ta fahimtar da su har su fahimci yanda zaman makaranta yake ba wai da sunyi abu ku dake su ba,kuma bari kiji in gaya miki duk naji wani tashin ta shina sae na sanar da Abbanki ai kinsan abinda ke nan.
  Vc na gama fadin haka ta wuce Nina ta kalli Aleesa tace"hm cab!ke kin yarda j.s.s. one tayi miki dukan tsiya a banza,taci bulus kenan... Kan Bala'i !kina wasa dani Nina sanin kanki ne bana cewa komai a gaban mama domin kar ta hana ni abinda nayi niyya,na fison idan na aikata tukun ko zata ji,
domin wlh ni idan baki na kadai ta fasa to ni zan manta ubanshi ne,yanzu mama kawai nake jira ta fita daga hostel d'in nan zan farfasa mata jikin ta ne na kuma sa juniors su mata wanka da ruwan gishiri,ta yanda zata fahimci ruwa ba sa'an kwando bane kuma ta gane da farkon sa'a ce kawai tayi bai wai qarfin ta ko dabarar ta yasa ta min haka ba.

Vc na shiga dasu Afrah d'akin su,
 Afrah ta marairaice tace"mama wai uncle bai kira ba har yanzu?Afrah waya ta ba caji kuma ki kwantar da hankalin ki ai farhan ba zai share ki haka kawai ba.

*Note*
Idan baku manta ba nayi muku bayani a page 10 cewa mahaifin farhan yana da qannai guda biyu da suka fito ciki d'aya, wato gwaggo da Alhj usman,Alhj usman shine mahaifin fu'ad,wannan vc da kuke ji  itace matar Allhj usman (Abban fu'ad) wato mahaifiya ga fu'ad.
  Wanan kenan ina fatar wad'an da suka manta sun tuna.

Afrah tace"to mama mu haka za mu riqa yin komai da ruwan sanyi....to Afrah haka school life take but kar ku damu zan had'a ku da wata innar da zata riqa taimaka muku da ruwan zafi, amma yanzu kuzo muje gidana kuci abinci kuyi sallah,
ta fad'i haka ne sbd cike take da tausayin Afrah kan had'arin da farhan yayi wanda har yanzu

bata ji ance ya farfad'o ba.

Nan taja su suka wuce tare da Aleesa wacce aka ajiye clinic amma bata d'auka cewa Vc dasu Afrah zata je gidan ta ba,
ta d'auko rakiya sukayi ma vc zasu koma hostel ne,domin sae qisa yanda zata ci uban Afrah take da ta koma hostel.

A 6 angaren su leesa kuwa.

Sorry I can't continue let tomorrow please.

*Futha Luv💅&Billy giro😊*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:21PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [ 8/9/2016] Billy giro😊: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
~*```AFRAH KO AMRAH```* ~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Bilqis Sidibe💅&Bilkeesu giro😊```*

🏅2️⃣5️⃣🏅
washe gari Afrah na farkawa taga cikin dakin da take kuka kawai ta shiga rerawa sbd mafarkan da tayi tayi sae yayi mata kamar tana gida.

Amrah ce ta farka ta same ta ta dora kai kan guiwa tana ta rusar kuka kamar wacce aka yiwa mutuwa.

Cike da damuwa Amrah tace haba Afrah me kike ma kuka tun da asuba haka? Allah uncle bai kyauta min ba nace masa bana son boarding school amma shine ya kawo ni.

Ajiyar zuciya Amrah ta sauke tace"kinga sannu sannu zamu saba kinji yanzu muje muyi sallah.
Nan ta samu da qyar taja ta suna fito wa gaban house.
Afrah taja birki tace wai ke Amrah ina zamu je haka kina fama da bokitayya,har da wata buta? Ruwa zamu je diba mana mu sami na wanka da na arwala....dibar ruwa fa? Eh man idan bamu dobo ba wa kike tunanin zai ba mu?

Afrah bata ce komai ba nan Amrah taja ta sae fanfo.
Afrah na ganin layin mutane tace"kai! yanzu duk layin nan a gaban mu suke kuma har sae mun

jira sun d'iba?eh amma zamu bada butar mu ne su en muna na arwala koda zamu gama sallah layi ya kai kusa kai gare mu cos kinga ba mutane sosai.
Turo baki kawai tayi tana kallon mutanen da suka tsura mata ido, cike da tsiwa tace"to kije ki tara butar mana kinga sae faman kallon mu suke da idanun su kamar mujiyoyi.

Da mamaki Amrah tace"Afrah...to qarya nayi kalle sufa,wlh Allah duk d'iya bata daina kallo na ba sae munyi ta tunda ba ubanta ne ya kawo ni makarantar ba....ke! mind ur tongue ko kuma wlh yanzu na hora ki"
cewar wata senior wacce ke zaune gaban fanfo tana cika bokitayya tana bawa junior suna kai mata kwana.
Afrah ta kalle ta sama da qasa ta watsar tace"horo sae kace wata masa,
ki dai hora wad'an da kike horawa su da suka dauka,wawaye kawai kuna ganin kanta kamar gijen shirwa amma kun wani bi mata layi kamar bayi tana baku ruwa kuna kai mata bayan duk abu d'aya kuka zo yi a makarantar....cikin 6acin rai senior ta miqe ta nuna Afrah da yatsa tace ke!kin san abinda kike fad'a kuwa,a da nayi niyar raga miki ganin ke new comer ce baki san komai ba amma wlh yanzu sae kin gane kuren ki!
Amrah tace"don Allah sister kiyi haquri wlh bata san makari ba ne.... Am not ur sister!ta nuna juniors din da take ba ruwa suna kai tace"sune sisters dinki domin sune tsaran ki!ni dole ki kirani da Anti.... Ai gwai Amrah! ji yanda wannan abar ta wani gwasale ki!
Tana fama da rama kamar wata figaggiyar kaza har taga bakin cewa a kira ta da Aunty.... Fuuu senior tayo cikin Afrah,Amrah tayi saurin shiga tsakanin su tayi ta bata haquri gurin duk ya cika da student ana kallon ikon Allah yanda junior ke zagin senior har tana fadin Amrah da kin barta wlh na kakkarya lenge lengen jikin nan nata,
senior kuwa sae zillo take tana son ta cafko Afrah.

Da qyar aka samu wata senior taja Afrah inda waccen senior ke fad'in yau duk wanda zai miki tsaye a cikin makarantar nan sae nayi discipline dinki!

Suna shiga daki senior tayi ta fahimtar da Afrah ba a yiwa senior haka respect ake basu tamkar aunty ki ta gida,Afrah jin ta kawai take ita ina taga Anti bare ta san da hakan.
Nan senior ta fita ta dawo,
sae gata tare da junior dauke da ruwa aka ajiye ma su Afrah.

Bayan sunyi wanka sun shirya cikin uniform,
su kazo gun Kari, Amrah ce ta had'a musu tea ta ba Amrah nata.

Afrah na kur6awa ta furzar tace"Amrah lafiyar ki zaki mana tea da ruwan sanyi!
To Afrah ina kike tunanin zamu sami ruwan zafi baki ga da ruwan sanyi mukayi arwala da wanka ba.
Nan Afrah ta le6ace baki zuwa kuka kamar taga uncle d'inta kusa tace"wayyo Allah uncle ka kashe ni,nayi arwala da ruwan sanyi nayi wanka da ruwan sanyi sannan kuma nasha tea mai

sanyi uhm uhm uncle ka kashe ni da ka kawo ni boarding school,nan ta hau bakin ta ta fara rera kuka iya qarfin ta duk house a na jin ta.

Wata senior ce tazo ta leqa dakin tana fadin wace ce ta cika mana house da kuka sae kace gidan da akayi mutuwa!cike da masifa Afrah ta d'ago domin ganin wace ce, mamaki tayi ganin Nina wacce suka had'u da ita gidan su JB, ita ma Nina tayi mamakin ganin Afrah nan ta ya mutse fuska kamar wacce taga kashi tace" wai dama kece mtsw ta buga tsaki ta wuce.

Afrah ta yunqura zata tashi Amrah tayi saurin rirriqe ta tace"please Afrah kar kija mana wani bala'in....bana so Amrah! bana so kina hana min abinda nayi niyya!
kinsan bana son raini yaza tazo har dakin mu tana fama da guntun gashi kamar bindin akuya ta watsa min banzan kallo ta wuce!

Yi haquri Afrah...

Mtsw ni tashi mu wuce da Allah!

Nan suka wuce zuwa area class ba tare da kowannen su yasha tean ba.

Bayan sun dawo sunje fanfo dibar ruwan arwala,

Afrah ta hango Nina tsaye a bakin fanfo ta tasa junior gaba suna d'ibar mata ruwa.

Nan Afrah ta

fizgi butar da ke hannun Amrah tace"bani ki ga".

Afrah na zuwa bakin fanfo bata damu da bokitin da ke tare ba,
Kawai ta tara butar inda rabin ruwa na shiga ciki rabi na bin jikin butar suna sauka cikin bokitin da ke tare kuma tana sane tayi hakan.... Nina ta buge butar har saida ta kufce a hannun Afrah duk ruwan da suka fara shiga suka watse, ba wata wata Afrah ta kai

mata wawan mari wanda yayi da isowar senior da suka sami sa6ani da safe.

*```Billy giro😊&Futha luv💅```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:21PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [ 8/12/2016] Billy giro😊: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

~AFRAH KO AMRAH ~

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

Na Bilkeesu giro😊&Bilqis Sidibe💅

🏅2️⃣7️⃣🏅
Leesa na zuwa gida ta sami mom farida ta gama waya kenan rai 6ace,tana ganin leesa ta hau ta da masifa tace"wato shine sae da kika je domin hana faruwar hakan to qwalelen ki domin lokaci ya qure miki.... Haba mom farida kinsan yanda nake son farhan amma kika sa aka mishi haka bayan na roqe ki kan ki bari wannan karon wlh zanyi duk yanda kike so na ganin yasa hannu a takardun....kinga dakata yanzu dai kowa tasa ta fishsheshi ai naji labarin farhan ya na asibiti to wlh indai bai mutu ba,lallai kuwa zaki ji labarin mutuwar sa a daren yau... A'a mom farida don Allah kar ki min haka indai dukiya kike so nayi miki alqawarin zan baki kadarorin da mahaifi na ya mallaka min.... kin kuwa san irin dukiyar da Alhj Basheer ya barwa Afrah, duk dukiyar nan da kika ga muna damawa cikin ta kad'an kika gani domin cikin kashi dari na dukiyar sa,kashi ashirin muka sami damar ci domin tamanin d'in duk ya mallaka su da sunan Afrah!ta yaya kike tunanin er dukiyar da kike son mallaka min zata amfane ni,
keda mahaifin ki dukiyar da yake taqama da ita iyakar shi sahun farko a masu kudin garin kaduna amma Alhj Basheer tsaf za'a jero shi a sahun farko na masu kud'in Nigeria ....mom farida ai bance baza ki mallaki dukiyar ba nidai abinda nake so dake kar kisa a qarasa farhan don girman Allah... ke Allah kika sani da zaki wani had'a ni da shi!
ki sani tuni na fahimci soyayyar farhan tafi damunki ba wai ganin na mallaki dukiyar ba.

Don haka kowa tasa ta fishsheshi.

Tana gama fad'a ta wuce leesa ta bi ta har zuwa dakin ta tana ci gaba da roqon ta.

A 6angaren su gwaggo kuwa ita kad'ai aka bari a d'akin tana sallar isha'i su uncle Basheer sunje masallaci.

Leesa ce tazo ta same ta ta sallame sallah kenan,
wanda sae da gwaggo ta kammala addu'oin ta sannan suka gaisa da leesa.
Sukayi shiru na d'an wani lokaci leesa ta katse shirun da cewa"ni kuwa gwaggo me zai hana a fitar da farhan qasashen waje sbd ya sami kyakkywar kulawa, gwaggo ta nisa tace"ai leesa asibitin nan da kike gani suna da komai na kayan aiki kuma suna da qwararrin likitoci, zai sami kulawa fiye da yanda kike tunani,amma gwaggo ganin nike kamar can zai fi kuma ko don Afrah bana son taji labarin wani abu ya faru da farhan hankalin ta zai tashi sosai gashi tana school, amma idan aka fitar da shi waje za'a iya ce mata tafiya yayi, ai leesa kinsan zata iya damuwa kan sae tayi waya da shi da ya na garin da baya garin,haka ko dazun mukayi ta fama da ita da qyar aka samu Jb ya lalla6ata.
Leesa tayi shiru tana tunani domin hankalin ta yafi kwanciya idan aka dauke farhan da qasar nan, duk da cewa ta samu ta shawo kan mom farida amma bata tunanin ta haqura da gaske,ko

kuma taje ta canza ra'ayi bata sani ba,hakan kuwa zai iya sa taji mutuwar farhan kai tsaye.

A 6angaren su Afrah kuwa sae da marece suka koma hostel dauke da flaks din ruwan zafi da suka samo gidan Vc da kuma kular abinci.

Da dare sunyi shirin bacci,suka dauko kular da suka zo da ita, faten dankalin turawa ne mai zafin gaske suka zuba a plate zasu fara ci,
sae ga Nina da Aleesa sun shigo d'akin,kowacce da zabgegiyar bulalar ta.

Futha Luv 💅&Billy giro😊
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:21PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [8/16/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
~AFRAH KO AMRAH ~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

Na

Bilkeesu giro😊&Futha luv💅

🏅2️⃣9️⃣🏅
Tashi dai ka zauna my dear sbd nasan bayan ka yayi ciwo sosai kana buqatar tashi zaune.
Nan farhan ya tashi zaune wanda yayi dai2 da shigowar gwaggo.
Murna ta shiga yi sosai tana godewa Allah, sae ga su Alhj Basheer,Jb,fu'ad sun shigo nan suka shiga taya gwaggo murna yayinda suka tambayi leesa yaushe ya farfad'o.
Nan ta sanar da su yanxu ne farfadowar sa.

Fu'ad ya duba shi yace a bashi ruwa yasha, leesa ce tayi saurin tsiyayo ruwa a cup inda ta fakaici idon kowa ta zuba garin wani magani fari qal da shi.
Taje ta bawa farhan har ya kar6a,
gwaggo ta kar6i ruwan a hannun farhan tace"ai leesa ba a bawa mara lafiyan da ya jima bai farfad'o ba abu haka kawai yana da kyau ayi addu'a tukun.
Tana gama fad'ar ta tofe ruwan da addu'a ta bashi yasha.
Ran leesa yayi mugun 6aci idanuwan ta sukayi jajir.
Fu'ad ya nemi a kawo ma farhan abinci ,gwaggo ta debo ta shiga bashi abincin da kansa.
Sae dae tun shigowar su farhan bai ce komai ba sae kallon su yake.
Da ya gama cin abinci Fuad ya keka shi zuwa toilet sbd yayi wanka, amma farhan ya kasa yin komai sae da fu'ad yayi masa wanka da brush inda ya shiga tunanin akwai matsalar da farhan

ya samu domin baya yin komai sae ance yayi.

Sae dae bazai sanar da su gwaggo ba har sae yayi bincike ya gano inda matsalar take.

A washe gari ne ya gama binciken sa inda ya gano matsala biyu farhan yake dauke da ita, d'ayar matsalar cikin qwaqwalwar sa take,
komai ba zai iya yi ba har sae an bashi command an kuma nuna mai yanda zaiyi,tamkar wanda ya manta abubuwa.
D'ayar kuma abu ne da ya d'aga mishi hankali sosai wacce baya jin zai iya sanar da kowa.

Cike da damuwa ya sanar da su gwaggo matsalar da farhan ya sami ta rashin yin komai har sae ance yayi.
Sae dae ya nuna musu ba wata matsala ba ce idan ana nuna mishi sannu sannu zai dawo normal.

Duk da haka sae dae sukayi jimami sosai.

A 6angaren sau Afrah kuwa sati biyu da suka wuce.
Suna samun kulawa sosai a gun inna Adama wacce Vc ta hada su da ita haka ko Aysha tana iya qoqarin har yanzu domin tana kan nuna musu yanda ake zaman school.

Sae dai Afrah duk tabi ta rame sbd rashin waya da farhan amma tana waya da su gwaggo inda suka ci gaba da lalla6a ta kan cewa farhan yayi tafiya ya manta wayar sa amma in ya dawo zai kira ta,
*hakan ya faru ne tun kafin farhan ya farfad'o*

A 6angaren su gwaggo suna cikin jimami ne wayar gwaggo ta shiga ruri, tana ganin Vc tasan Afrah ce,
nan ta d'aga wayar se kuwa taji Afrah cikin kuka tana tambayar uncle nan gwaggo ta miqa wa farhan waya,kallon gwaggo kawai yake riqe da waya har sae da ta nuna mishi yanda zai yi,,bayan an nuna mai ya kuma yi shiru Afrah na magana bai bata amsa.

Cike da tausayi JB ke sanar da shi abinda zai ce ma Afrah kamar qaramin yaro.
Da haka aka gama wayar Afrah kam da farin ciki ta yini har ta kwana.

Sannu sannu kwanaki na tafiya yayinda farhan ke samun sauqi kuma dai2 gwargwado ana nuna mishi yanda zai yi abubuwa har ya fara yin wasu abubuwa da kanshi.

A 6angaren leesa kuwa ba abinda ta matsu irin lokacin zuwa visiting yayi sae damun gwaggo take kan cewa aje da farhan ko Afrah zata fi farin ciki,gwaggo tace"farhan da baya iya taka qafar sa zuwa wani guri,leesa tace amma gwaggo ya kamata aje da shi ko akan wheelchair ne, to Allah dai ya nuna mana lokaci muna masu rai da lafiya.

Yau ce ranar visiting Afrah sae murna take zata ga uncle,gashi har yanxu bata san yayi had'ari ba.

Gwaggo,JB,Fu'ad,Baban Amrah,leesa sune suka d'unguma zuwa visiting,fu'ad ne ke tuqa motar inda ya zarce cikin makarantar se staff quarters ya tsaya qofar gidan vc wato mahaifiyar sa.
gidan shine na farko ba nisa da gate.

fu'ad ne ya taimakawa farhan ya fito,ya jingina shi a jikin mota zai d'auko Wheelchair wanda in kaga farhan a jikin mota tsaye tamkar lafiyar sa qalau.

Su Amrah ne tafe sun fito daga hostel zasu je gate sbd en class d'in su ne messengers.
Amrah ce ta hango su duk sun fito daga mota tayi saurin ta6o Afrah cike da murna tana nuna mata su Farhan, wani ihun murna ta saki har sae da idon mutane yayo kanta taje da gudu ta fad'a jikin farhan, da qarfin tsiya farhan ya ture ta har sae da ta fadi,gwaggo tace subhanallah! farhan me yake faruwa Afrah ce fa....gwaggo ban santa ba kuma bana son ganin ta,don Allah mu bar nan gwaggo,ido na zai fashe idan na sake kallon ta.

Mamaki qarara a fuskar Afrah wacce ta tashi tsaye tana kallon farhan da yasa tafukan hannyensa ya rufe idon sa gam yana qoqarin ganin ya shiga mota.

Cike da murna leesa ke kallon alamarin yayinda kan kowa ya d'aure musamman Afrah da ta dasqare guri d'aya hawaye wani na bin wani.

Futha Luv💅&Billy giro😊

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:21PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [8/21/2016] Billy giro😊: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
~AFRAH KO AMRAH ~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

Na Billy giro😊&Bilqis Sidibe💅

🏅3️⃣0️⃣🏅
Cikin kuka tace "me nama ka ne uncle da har zaka ce baka sanni ba kuma wai baka son ganina don Allah uncle koma mene ne kayi haquri wlh Allah daga yau bazan sake ba please uncle, ta fadi haka ne yayinda take matsawa kusa da shi,shi kuma sae sauri yake zai rufe ganbun

mota,yana fad'in idona zai fashe gwaggo don Allah muyi mu bar gurin nan.
Leesa ce ta jawo ta jikin ta tana"haba Afrah ba kya jin me yake fad'a ne sae qoqarin matsawa kike kusa da shi, ki tausaya ma uncle d'in ki mana"Aunty uncle yana fishi dani ne ba wani idon shi da zai fashe don Allah Anty kice yayi haquri Allah bazan sake ba.
Leesa ba tace da ita komai ba sae lallashin ta take yayinda take wata magana a cikin zuciyar ta,
gwaggwo taje gurin farhan da ke roqon su kan suyi su bar gurin tace"kaga farhan wannan wasan ya isa haka jibi yanda kasa Afrah ta dauki abun da gaske sae kuka take ta faman yi,don haka fito daga cikin motar muna so zamu shiga daga ciki.

Nan gwaggo ta matsa mishi kan ya fito cikin motar, tayi 2 dashi amma yaqi nan ta fahimci fa da gaske yake bayan son ganin Afrah.
Kan ta ya d'aure sosai haka ma kowa cike suke da mamaki tace"innanlillahi wa inna ilaihi raji"un! yau me nake shirin gani da rana ido biyu ba a cikin mafarki ba.
Gwaggo ina ga kamata yayi ayi a sallami su Afrah domin a gaggauta zuwa asibiti a duba shi aga kodai wani abu ke damun idon shi domin ni kaina abin ya d'aure min kai sosai,,leesa ce tayi maganar yayinda Afrah ta qara fashewa da kuka tana fadin"allahumma ajirni fi musibati....haba kukan ya isa kiyi haquri kinji,leesa ce ta fad'i hakan wanda tayi haka ne domin kar Afrah ta qarasa addu'ar.
Amrah ta lura da hakan domin a cikin sauri leesa ta rufe mata baki sae dai kuma bata fahimci me leesa ke nufi da hakan ba.
Nan suka shiga gidan vc yayinda suka sanar da ita abin al'jabi domin sun dauke shi kamar al'ajabi.
Basu jima ba leesa ta matsa kan suje fa an bar farhan a mota nan suka sallami su Afrah wacce sae kuka take suna lallashin ta inda har suka bar gidan Afrah kuka take.
Bayan sun koma leesa taje gida da murna tana labartawa mom farida duk abinda ya faru tace"mom farida bari gaskiya aikin sabon bokan nan yana ci sosai sae dai matsalata dasu sun fiye addu'a amma kuma dad'i na da bokan yasan aikin shi ko yaushe yana kan qwaryar tsafin sa wanda da addu'ar su ta karye maganin zae d'ana wani.
shiyasa hankali na ya d'an kwanta kinga ko da sun fahimci sammu ne yasa farhan ya tsani Afrah ko sun karye shi aikin banza ne domin boka na kan aikin shi.
Ni yanzu fal farin ciki nike ciki zanyi aure da farhan cikin kwanakin nan sae ki fara shirye shirye... Au kin kar6o turaren kenan,na kar6o amma yana da sharadi bcs sae da yammacin la'asar zanje na masa shi kuma sae idan yana bacci kuma idan na masa turaren zan kasance daga ni sae shi a d'akin sbd ba a so ya fara had'a ido da kowace mace face ni, idan kuwa nayi kuskuren barin shi ya had'a ido da wata mace wai fa koda uwar sa ce to kuwa da ita za'a d'aura auren bani ba...he lallai turaren nan yanayi, ai bari kawai mom farida har da wani kaskon tsafi ya bani kuma ki kwanta kiyi bacci abinki domin da na auri farhan wlh tamkar dukiya ta dawo hannun ki,ta fadi haka ne yayinda suka tafa.

A 6angare su Afrah kuwa kan kukan da take yasa ta kamu da zazza6i mai tsanani.

Hakan tayi ta fama da shi kusan kwana 4 bata iya komai.
Dole Vc ta yanke shawarar mayarda ita gida sbd magani da allura ba wanda bata sha ba amma ciwon sae qaruwa yake sbd yanda tasa damuwa a ranta sosai.

A 6angaren leesa kuwa zaune take a d'akin gwaggo tana taya ta jimami kan yanzu ko sunan Afrah farhan baya son yaji an ambata kuma sunje asibiti ba a gane komai akan matsalar idon sa ba.

Sae da suka d'anyi shiru leesa tace"farhan d'in yana nan kuwa naga tun lokacin da na shigo ban ganshi ba? inaga bacci yake domin tun da ya dawo masallaci ban sake jin d'uriyar sa ba.
Tace to gwaggo zanje naga idan farke yake sae mu gaisa kafin na wuce.
To a gaida gida,
cewar gwaggo kafin leesa ke fita.

Leesa na zuwa 6angaren farhan bata zarce koina ba sae d'akin farhan ta same shi sae sharar bacci yake.
Nan tayi hamdala tare da fitar da kaskon turaren ta na tsafi wanda gawayi ke laqe a jikin sa basa moving,sae da ta furta wata kalma kafin take hura iskan bakin ta sae kawai gawayin sukayi jajir har suna fitar da belar wuta.
Nan ta zuba turare tana kewaye farhan da shi duk dakin ya surnuqe sannan ta nufi toilet wanda yayi dai da shigowar Afrah wacce kallo d'aya zakayi mata kasan tana jin jiki.
Bata damu da yanda taga d'akin ya cika da hayaqi ba sae qoqarin zuwa gurin farhan take wanda ya fara motsi alamar zai farka,
sannu a hankali ya bude idon shi ya sauke su kan Afrah.

Masu karatu kuyi haquri zamu dakatar da yin Afrah ko Amrah na d'an wani lokaci sbd wani dalili.
Tagwayen marubuta kece muku Luv u all😘

Billy giro😊& Futha Luv💅
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:21PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [9/18/2016]
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*~AFRAH KO AMRAH ~*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*Na Billy giro😊 & Bilqis Sidibe💅*

*🏅31🏅*
Fad'awa tayi kan jikin shi tana kuka nan farhan ya fara jin wani abu na fizgar shi wanda ya sàmi kanshi da fara shafar jikin Afrah......qarar fashewar wani abu suka ji da sauri suka tashi suna kallon leesa wacce ta fito daga toilet tazo fuuuu ta fizge Afrah da ke kan jikin farhan ta ingiza ta da qarfi har sae da ta fad'i ,nan farhan ya tashi kamar wani zautacce yaje ya tada Afrah ya kalli leesa cikin 6acin rai yace" me matata ta miki da zaki kada ta!... Matar ka?eh mata ta ce.... Afrah ce fa ,kallon Afrah yayi yace"ko ita ce fa ai mata ta ce...kai wawa ne yaushe ta zamo matar ka?kaji ta yanzun nan mana......fuuu tayi cikin Afrah ta fara dukan ta tana fad'in er iska kin lalata min komai da yanzu nice matar shi amma kinzo kin 6ata min lissafi baqar makira kawai!haka tayi ta maganganu tana dukan Afrah wacce tuni farhan ya kare ta dukan na sauka kan jikin shi, leesa kuwa bata ma san wanda take duka ba idon ta ya riga ya rufe........Aa! Aa! Lafiya me yake faruwa haka da kike faman dukan su!? cikin kuka leesa tace"gwaggo ki taimaka a kar6e Afrah daga hannun shi so yake ya lalata mata rayuwa.....lalata rayuwa kamar ya farhan ne fa......to ai gwaggo yanzu na same su kan gado yana qoqarin raba ta da kayan jikinta dana hana shi yace na barshi wai Afrah matar sa ce don haka kar na qara shiga sabgar su kuma tambaye shi ma kiji,
Wai haka farhan? Eh gwaggo mata ta ce .....ikon Allah ,Allah ya taimaka da kika zo da anyi 6arna, kai fa farháñ baka gane ta bane Afrah ce fa,
ba marigayiya Amrah ba don haka sake ta ta muje ta sami abinda taci bata ko da lafiya yanzun ne dawowar ta,,,nan gwaggo taja hannun Afrah, Afrah ta marairai ce tace "Gwaggo ni ki bar ni gurin uncle ba abinda yake min "naji muje kici abinci sae ki dawo kinji,to gwaggo amma da uncle zanci abincin...."kinga Afrah uncle d'in ki bai yi sallah ba ki bar shi yayi sallah ke kije kici abinci"

Cewar leesa wacce ta danne zuciyar ta ne kawai tana magana.

Farhan yace "gaskiya gwaggo baza a je min da mata ta koina ba"
komai gwaggo kasa cewa tayi yayinda al'amarin Farhan ya fara bata mamaki yanda yake abubuwa kamar wani wawa ,nan tayi ta lalla6a shi kan ya saki hannun Afrah da xarar taci abinci zata dawo amma yaqi sae ma qara riqe mata hannu yake, leesa tace"kinga Afrah yi masa magana ko zai sake miki hannu ba musu Afrah tace"uncle ka bari na tafi idan naci abinci zan dawo kaji"to matata amma kar ki jima kinji, bazan jima ba uncle .
Nan aka samu ya saki hannun ta,
gwaggo ta tafi da ita.

Ihu ne kawai leesa bata saki ba sbd tsananin abinda take ji na baqin ciki kallon agogon d'akin tayi ta fizgi jikin ta kamar wacce ta zauce ta kwashi kayanta ta bar gidan a guje.

Farhan kuma kasa haqura yayi domin ji yake kamar za'a fizge ransa idan Afrah bata kusa da shi

hakan yasa ya tafi 6angaren gwaggo yayi zaune kusa da Afrah tare da riqe hannun ta kamar mai gudun kar ta tafi ta barshi ,gwaggo tace"wai kai ba sallah zakayi bane?gwaggo na fayi sallah kafin na kwanta.
Daga haka gwaggo ta shiga kallon ikon Allah yanda farhan ya d'ora Afrah kan cinyar shi sae lalla6a ta yake yana ciyadda ita kamar ba shine kwanaki yace ya tsani ko jin sunan ta ba.

Ba abinda ya qara d'aure mata kai irin Afrah na son shiga toilet amma yace sae tare zasu shiga baza ta tafi ta barshi ba gawaggo tayi juyin duniyar nan amma yaqi haka suka kwashe kusan awa d'aya yaqi bari Afrah ta d'aga ko nan da can ga fitsarin da take ji sae qoqarin kufce mata yake,ga farhan sae wasu abubuwa yake mata kamar wanda ke shirin ràba ta da tufafin jikin ta.

Ganin haka gawggo ta kira fu'ad a duba shi domin abinda yake ya wuce aikin hankali.

Da fuad yazo gwaggo ta mishi bayanin komai ya kuma gani da idon sa ya nisa kafin yake cewa "lallai al'amarin nan da mamaki sae dai kuma ni a gurina bazan yi mamaki ba sbd dama akwai wata matsala da ban gaya muku cewa farhan na d'auke da ita ba sbd gudun kar na tashi hankalin Ku inda a cikin magungunan da yake sha akwai maganin wannan matsalar wanda nake sa ran idan yana shan shi daily matsalar zata rage sae gashi naga matsalar tana qoqarin yi masa karaf d'aya wato matsalar ita ce qwalqwalwar farhan ta sami matsala wacce ako yaushe zata iya bugawa ya haukace kuma da kamar wuya ya iya dawowa normal....cikin tashin hankali gaggwo ta miqe zumbur ,fu'ad yayi saurin cewa "kar ki damu akwai wani abu da na fahimta yanzu a game da Farhan wanda inshaAllah idan akayi masa yanda yake so za'a ji sauqin shawo kan matsalar......koma mene ka fad'a inshAllah ni mai yi masa yanda yake so ne,, gwaggo ba wani abu bane face aure farhan ke so.... Aure kuma?eh gwaggo ki dube shi da kyau ki ga abubuwan da yake yiwa Afrah duk wanda ya kalle sa sau d'aya zai fahimci aure yake buqata har dai Kalmar nan d'aya da yake ta furtawa
*"mata ta"*kuma ko ba haka ba farhan mutum ne da ya kamata ace ya buqaci aure sbd tun rasuwar Amrah bai sake yin wani aure ba.
Haka ne fuad amma aure yanzu ba a shirya ba ta ina ma z'a fara wanda ko nema banji ya fara yi ba ,,, haka ne gwaggo amma matsàlàr da yaké ciki za a dubà domin ina tsoron kar yawàn tunànin son aure ya masà yawà har qwaqwalwar shi ta kasa dauka aje abinda ake yiwa gudu ya faru sae dai
kuma samuñ wacce za'a aura masa ne matsala ba ma auren ba but yanzu gwaggo ba wata wacce kika yaba da hankalin ta kuma of course zata so farhan....ni kuwa ina zan sani fuad yanzu kai a gurin aikin ku nan asibiti ba wata wacce kake ganin jinin ta ya had'u da farhan?gwaggo kinsan fa farhan mutum ne da baya kula mace bare har shiri ya shiga tsakanin sa da ita but wannan yarinyar leesa fa wacce ke yawan zuwa gurin Ku me zai hana a tuntu6e ta muji ko zata iya auren farhan a halin da yake ciki.....shine fa amma kuma kana ganin zata

yadda ta aure shi idan taji matsalar shi ?ba mamaki zata amince sbd naga kamar tana tausaya mishi kuma idan aka yi auren ina ga ba wata matsala tunda aka yi masa abinda yake so wanda inshaAllah qwaqwalwar shi zata sami natsuwa ,
in yaso bayan aure a fita waje da shi zuwa asibiti.... Eh lallai kayi magana inshaAllah kuwa zamu zauna nida mahaifinka da kuma kawun shi Basheer duk abinda suka ce sae na tuntu6i ita leesa kafin muje ga iyayen ta.

To gwaggo bari na masa allurar bacci domin ita kad'ai ce tafi sauqi a samu ya saki Afrah .

Bayan yayi masa allura ne ya fita daga gidan yayinda gwaggo ta zauna tana ta nazarin maganganun fu'ad.

Afrah kuma ta tafi toilet a gurguje tayi fitsari wacce bata fito ba sae da ta watsa ruwa.

A 6angaren leesa kuma tana fita gidan bata zarce koina ba sae qauyen da take zuwa gurin boka taje mai da bayanin abinda ya faru tana buqatar in da wata hanya yayi gaggawar karye wannan magani, nan boka ya nuna sam ba wata hanya  inda da kukan ta da komai take roqon sa ya dai duba amma yace sae dai tayi haquri domin kuskuren d'agawar da tayi har Afrah ta riga ta had'a ido dashi yaja mata don haka ba fashi  yau sea an d'aura auren Afrah da farhan muddin d'ayan su yana numfashi a doron qasa,
cikin tsananin takai ci ta bar qauyen wanda tana cikin driven sae kawai kalmar boka ta fad'o mata a rai kalmar ita ce
 *"Ba fashi a yau sai an d'ura auren Afrah da Farhan muddin d'ayan su yana numfashi a doron qasa"*
Ta furta a fili cewa "kenan hakan na nufin idan na kashe d'ayan su ba zancen aure,gud idea ba makawa zanyi abinda nake ganin shine dai dai domin kuwa zan sa ayi taron mutuwa a maimakon na d'aurin aure.
 Nan ta qara wa motar ta wuta bata zarce koina ba sae gidan su Farhan tana fitowa ta had'u  da taro a bakin qofar gidan sae rarraba  goro ake bata san lokacin da jakar hannun ta ta sa6ule qasa ba sbd  jin sunan wacce aka d'aura aure da ita wanda hakan yasa tayi mamaki.

To masu karatu muje zuwa muga shin meyasa leesa tayi mamaki da jin sunan wacce aka d'aura aure da ita shin sunan ta ne taji ko kuwa na Afrah?

*Futha Luv💅&Billy giro😊*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:21PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [9/19/2016]

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*~AFRAH KO AMRAH ~*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*Na Bilqis Sidibe💅&Billy giro😊*

*🏅32🏅*
Qafafun ta ne taji sun kasa d'aukar ta ta samu da qyar ta shiga cikin gidan da shigar ta tace"gawggo me nake shirin ji a bakin qofar gida? D'aurin Aure ne Ieesa d'aurin auren da yazo mana kai tsaye na Afrah da farhan....ihu ta saki ta d'ora hannu a ka tace"na shiga tara! shike nan shike nan gwaggo kun auradda Afrah ga Farhan!
ha! wayyo Allah na! .....gwaggo tace"ah ah Ieesa lafiyar ki kina qoqarin tara mana jama'a haka....wlh Gwaggo dole ne Afrah ce ta ban tausayi qaramar yarinya ayi mata auren wuri haka wacce ko qidan dangi yanzu ne ta fara.

Nan gwaggo ta nisa ta ja hannun Ieesa suka zauna tace"Ni kaina na tausaya ma Afrah matuqa kuwa don dai ba yanda zamuyi ne kawai abu ne da ya riga yazo domin farhan ya rikice mana kamar wani mai aljanu shi sae anyi masa aure da Afrah duk yabi ya hauka ce mana har sae da aka kira malamai duk wanda yazo sae dai yace a gaugauta yi masa auren shi yafi ,
ba yanda muka iya dole aka gaggauta d'aura auren.

Amma shine gwaggo ko a sanar da ni ko Allah zai sa na samo malamin da zai duba shi ko ayi dai dai.....
ko da yake ni ba kowa bace a gurin ku ina faman cusa kaina ne kawai.

Ba haka bane Ieesa kina fita gidan nan abun ya fara rikicewa sae da Fuad yazo ya masa allurar bacci amma kamar ba a yi ba domin ko minti biyar ba a yi ba ya tashi,shine fa tun daga lokacin bamu sake samun natsuwar sa ba sae da aka d'aura auren nan,,,

Shiru Ieesa tayi yayinda take magana a ranta cewa
_"lallai sae yanzu na qara tabbatar da aikin bokan nan yana ci tamkar yankan wuqa,sae dae kuma aikin nasa ya fad'a inda bai dace ba a bisa kuskuren da na aikata wanda ya zama dole na gyara kuskure na ta hanyar ganin cewa wannan auren bai d'ore ba_"

Bayan ta gama tace"amma dai gwaggo da mamaki aji cewa kun aura masa er qaramar yarinya kamar Afrah me zai gane da ita face kawai ya lalata mata rayuwa,
ni a gani na gwaggo da raba auren nan a kayi domin za a cuci rayuwar Afrah ne kawai".....ta

yaya kike ganin za a raba auren nan leesa?
Cike da zumud'in samun nasara ta share hawayen ta tace"gwaggo indai aure farhan keso a gaskiya ba Afrah ya kamata a aura masa ba cikakkiyar budurwa ta dace da shi domin yaji dad'in d'ebe qishirwar da ya jima yana d'auke da ita kuma ko ba haka ba Afrah ba komai take iya yi na aikin gida ba kuma karatun ta fa tayi yaya da shi naga kamar zai yi mata wahala da aure a kanta,,,haka ne leesa amma......
Amma me gwaggo fisabilillah ko ni kuka tuntun6a bazan aure shi ba duk da cewa ina da tsayayye wanda zan aura kuma ina matuqar son shi amma akan farhan zan iya haqura da duk wani d'a namiji sbd kawai na taimaka masa yaji dad'in rayuwa yanda kowa keji sbd ni a matsayin en uwa na d'auke ku bana jin akwai wani abu da zaku nema a guna da baxan iya muku shi ba,wanda ko yanzu a shirye nake da na aure shi indai har za a rava auren sa da Afrah domin shine yafi dacewa da kowanen su ,
shi ya samu ya auri wacce zata iya da lalurorin shi ita kuma Afrah ta samu ta qarasa karatun ta cikin sauqi,
ko ya kika ce gwaggo?

Sosai gwaggo ta nisa kafin take cewa "sosai kinyi tunani leesa sae dai mun riga ki yin wannan tunanin amma muka haqura da hakan sbd farhan ba aure kad'ai yake so ba
Afrah dai ce yake so ya aura ba wata ba wanda idan muka ce mu raba auren to komai zai iya faruwa sbd yanzu qwaqwalwar Farhan ba kamar ta kowa bace abu qalilan zai iya sa qwaqwalwar shi ta kasa d'auka ya haukace,
shiyasa muke ta kaffa kaffa da shi ,
kuma zancen karatun Afrah ba matsala bane sbd za a fita da farhan qasar indiya zuwa asibiti yayinda zasu samu masauki a gun wani abokin mahaifin sa inda za'a nemawa Afrah makaranta a can taci gaba da karatun ta....shin gwaggo kin manta cewa idan farhan yaji sauqi dole zai koma ga aikin shi ko kuwa zai zauna ba wani aikin yi ne?a'a zai dai nemi aiki a can har sae Afrah ta kammala karatun ta sae su dawo sbd dama a can yayi karatu har suka so su d'auke shi aiki ya nuna yafi so yayi aiki a qasar su,amma har yanzu suna son ya koma qasar su domin su d'auke shi aiki.
kinji dalili.

_"haqiqa rayuwar mata da miji abin sha'awa ce har dai idan ka sami miji mai sonka da gaske,ya rabbi ka bani miji na gari irin farhan ka kuma bani damar cire son wanda bai san ina yi ba wanda akan sa naqi kula kowa bayan nasan ko yace zai aure ni bazan yarda ba sbd bana jin zan iya kasancewa butulu koda kuwa zan mutu akan son sa._

Knocking d'in da akayi ne ya katse ta tayi saurin goge en sirarin hawayen ta sannan ta bud'e qofa.
Farhan yaje ya dire Afrah kan gado tace"sannu uncle baka gaji ba? Hancin ta ya lakato yace "da me zan gaji wannan jikin naki da ba nauyi bare yinin yau duk baki ci abinci ba"
Murmushi kawai tayi yace"oya je kiyi wanka ko kuma a d'aki na zaki je sbd kinga Ko Amrah tana so tayi.... Ai tun a mota nace nice first d'in wanka don karma tace ta riga ni,,,Uhm Afrah kenan ki wahalda ita kuma kice kece first d'in wanka to ke Amrah kin yarda da hakan?hm banni da ita uncle wai ita shegen wayo ne da ita amma zan rama....yanzun ma kuwa zan taya ki ki rama domin zan riqe miki ita ne sae kinyi wanka kafin tayi,
Afrah najin haka ta tafi da gudu sae toilet wanda da shigar ta ta jefo doguwar rigar jikin ta tare da fad'in"wlh kar ki shigo na tu6e"
Farhan yace"nidai ke shirin shigowa yanzu" nan ya nufi hanyar toilet ,
Afrah tayi saurin saka key tana bashi haquri kan kar ya shigo, sae da ya d'auke rigar da ta jefo yace"to yi sauri kiyi ki bata guri kuma da kun gama ku tabbatar kunci abinci after that kizo d'aki na ina son ganin ki"tace"tom"kafin yake fita.
Bayan sunyi wanka sun ci abinci still Afrah na jin jikin ta cike da gajiya, hakan yasa ta koma bayi ta shiga ruwa masu zafi domin gasa jikin ta ko zata rage jin gajiyar,
da haka ne bacci ya kwashe ta a cikin ruwan.

Ta d'au lokaci kafin take fitowa a gurguje tana d'aura towel tace "Amrah ashe bacci nayi.....au haba? Allah kuwa gashi nasan uncle na can yana jirana Allah yasa kar yayi fushi" tana gama fad'ar haka ta fita.

Koda ta shiga d'akin farhan ta same shi ya gama waya kenan kallo yabi ta dashi sbd wani musulmin kyau da ta mishi kan gyaran gashin da ke saman kanta irin gyarn nan da ake mimmird'e suma wato curly hair style wanda duk da hakan bai hana gashin ya sauko har kan kafad'un ta ba.
yayi scnd 10 yana kallon ta inda kai tsaye ya fara jin wani abu shiyasa yayi saurin kauda idon sa a kanta.

Afrah da ta zaci fushi yayi ta kama kunnen ta tace"sorry uncle bacci ya d'auke ni shiyasa kaga banzo kan lokaci ba"
ta qarasa gurin sa sbd murmushin da ya mata yace "ba komai"
Zaman ta keda wuya ya shiga shafar sumar kanta yana tura hannun sa a cikin gashin sae yaba gyaran yake tace"thank u"tare da kwantar da kanta a kafada'ar shi tace"uncle ka fad'a min dalilin kirana ina so na koma bacci"da yamman nan Afrah... ta wani marairaice fuska tana kallon shi tace"dan Allah uncle ka bar ni nayi ko na 20mnt wlh na gaji sosai bana jin na ta6a wahala irin ta yau"ai bazan hana ki ba domin na fahimci yanda kike ji akan shi ne nace ki zo domin na miki tausa,,,,tace"ni kuma uncle bayan kayi min a d'azu"ai wannan soma ta6i ne don haka kwanta na miki tausa kiji dad'in bacci kafin ayi magrib, wai ma tukuna kunyi sallolin da ake bin ku?ai ba a biyo mu ko d'aya ba bcs a shagon wata balarabiya muka samu mukayi sallah,, ok to kwanta na miki tausar ya fad'i haka ne yayinda ya kwantar da ita sae duk taji kunya ganin yanda yake mata wani kallo ta rufe fuskar ta da tafukan hannayen ta tace" nidai uncle ka bar ni kawai naje nayi bacci na ai na gasa jiki na da ruwan zafi"
ba dai dana fara ba,
ya fad'i haka ne yayinda yake tausa mata qafafuwan ta har izuwa cinyoyinta .
Afrah kuwa duk ta qara jin kunya har dai idan yaje kan conyoyin ta sae taji kamar wani salon yake mata hakan yasa taji dad'in tausar sosai wanda daga haka tayi bacci.
Ganin tayi bacci farhan ya jaye mata hannunwan ta da ta rufe fuskar ta sannan ya juya mata kwanciyar ta sbd yana son ya tausa mata bayan ta,sae da ya jaye sumar da ta d'an rufe mata baya sannan yaci gaba da yi mata tausa a hankali, ita kuwa sae sauke ajiyar zuciya take.

Sae gab da magrib ta tashi daga bacci ta shiga miqa a hankali cike da jin dad'in d'an baccin da ta samu tayi inda a hankali take ziro en qafafun ta a kan gadon wanda yayi dai dai da fitowar farhan kan ya qaraso wani qamshi ya daki hancin ta kan wani body mist da yake shafawa a qirjin sa.
saurin d'auke idon ta tayi sae kuma ta sake kallon qirjin sa da taga ba suma ko qwaya a d'aya qirjin very smooth akasin wani lokaci da take ganin qirjin dauke da suma luf,
kauda fuskar ta tayi ta d'an 6ata fuska tace"ni uncle ka daina aske suman jikin ka yana min kyau"su6ul taji fitowar maganar kai tsaye ai kuwa duk taji mugun kunya tayi saurin tashi xata var d'akin yayi sâurin riqo hannuñ ta da qrfi har sae da ta fad'o masa kan qirji,
ya d'ora hancin sa akan nata suna shaqar numfashin juna ya kalli yanda taqi yarda ta had'a ido da shi yace"meye abin kunya dan kin fad'i ra'ayin ki kan mijinki"

Qoqarin jaye jikin ta take yace"sorry na daina,amma zan tambaye ki yanzun qirjin nawa bai yi kyau bane?komai kasa cewa tayi yayinda taqi yarda ta kalli qirjin sa kamar yanda ya buqata, sae body mist d'in da ke hannun shi ta kar6a tana kallo sbd qamshin sa yayi mata dad'i sosai,
yace"kema kina so na shafa miki?sae a lokacin ta kalle shi tace"ina dai son ka saya min" ya kar6i turaren tare da d'ora hannunta akan qirjin sa yana yawo dashi sannan yace"zan saya miki amma sae kinji idan yayi miki dad'i a jikin ki,, kmr ya uncle?kamr haka ,
ya fad'i haka ne yayinda ya kai hannu kan qugun ta ya qara manna ta a jikin sa yana shafa mata shi kan cikin ta,da mamaki Afrah tayi saurin kallon shi domin kai tsaye taji hannun sa cikin towel d'in ta sae duk ta tsorace sbd shi kad'ai ne a jikin ta gashi hannun shi sae yawo yake kan cikin ta sae Allah Allah take kar ya wuce gun domin ta fara jin alamun haka ta yanda yake qara zuwa da yatsan shi sama yana wani salo kamar mai zana mata wani abu a jiki har dai da yakai kan tsakiyar mammanta wanda hakan yasa qirjin ta ya shiga up and down kan wani irin fad'uwar gaba da take ji kuma ta kasa yin komai sae kallon yanda hannun sa ke yawo take cike da tsoro da mamaki wanda cikin hikima taso ta qwaci kanta amma ta kasa sbd yanda ya matse ta sosai.

Muryar ta na rawa tace"uncle meye haka kake min? qara rungume ta ma yayi ya fara zuwa da hannun shi qasan cikin ta,
ai kuwa ba shiri ta ture shi daga jikinta ta shiga ja da baya kmr wacce taga zaki tafe, farhan kuwa sae qarasowa yake kusa da ita yana mata wani kallo d'auke da idanun shi da suka soma canza kala.
A rikice ta kame jikin qofa sbd yzo gab da ita hakan yasa wasu hawaye masu zafi suka sauko a gurguje kan kumatun ta tace"na roqe ka uncle dan girman Allah kar ka ta6a ni"cak ya tsaya domin yana girmama sunan Allah"
Nan ta samu ta fita a gurguje,
farhan ya shiga kiran ta amma ina tuni ta kai d'akin su.
Tana shiga ta saka key ta xube nan bakin qofar tana kuka mai ciwo .
Amrah tazo a rude tana fad'in "lafiya me yake faruwa ne? Knocking dinda aka shiga yi ne yasa Afrah tayi saurin kallon qofar taja Amrah sukayi quryar d'aki"da mamaki Amrah tace"ke uncle ne ke knocking ba kowa ba.
ba kiji muryar shi yana kiran ki ba?nasan shine amma don Allah kar ki bud'e masa....fizge hannun ta tayi tace"akan me! Allah ni bazan iya masa haka ba,bata jira me Afrah zata ce ba taje ta bud'e masa qofa sae dai tana bud'e qofar ta kauda idon ta sbd bata ta6a ganin shi d'aure da towel ba.
Nan ta bashi hanya ya nufi gun Afrah wacce wannan karon bata yi tunanin guduwa ba sbd tasan idan ba hauka yayi ba bazai ce ya mata wani abu a gaban Amrah ba sae dai fatar ta d'aya kar Amrah ta fita ta bar su.
Saurin noke hannun ta tayi da yake son riqowa ta maida su baya wacce still hawaye na sauka kan kumatun ta,
yace"haba Afrah meye na kuka nifa mijinki ne ko kuwa don ban ta6a miki irin haka ba"please uncle ka daina cewa haka, ta yaya na kasance matar ka idan aure kake so ba sai kaje kayi ba"ba wani kin fa san cewa ni mijinki ne kawai dai ki gaya min idan sona ne ba kya yi! da farko yayi mata tsawa sae kuma ya sassauto muryar sa kmr zai yi kuka yace"
pls Afrah ki gaya min kinji wlh bana so na takura ki"

ni fa uncle ba wani  aure da ke tsakanin mu,qarya zan miki ne Afrah? Baza ka min qarya ba uncle sae dai zan gaya maka gaskiya bana son ka a matsayin miji domin bana jin zan iya,sbd ina da wanda nake so nayi rayuwar aure dashi.
Tamkar saukar guduma yaji maganar ta dirar masa a kunne yayinda komai  nasa ya daina motsi domin har numfashin sa neman d'aukewa yake sae kallon Afrah yake wacce tun kafin ta furta maganar ta runtse idunun ta gam hawaye se wasan tsera suke akan kumatun ta.

*Billy giro😊Futha lurv*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:21PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [10/13/2016] Billy giro😊: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futhalurv.WordPress.com*

*``` 🏅47🏅 ```*
Tafukan hannayenta ta had'e ba tare da ta bud'e idanuwan ta ba.
Tace"dan Allah uncle kayi haquri ka fita"
Da qyar farhan yaga ya iya jan qafafun sa ya bar d'akin.
Yana fita Afrah ta durqushe ta fashe da wani  sabon kuka tace"am sorry uncle! Har sau uku tana fad'in haka.
Sannan ta kalli Amrah wacce tun lokacin da Afrah ta furtawa farhan bata son shi a matsayin miji take mata kallon mamaki ba ko qyaftawa.
Afrah tace"Amrah wlh qarya na yiwa uncle ni ina son shi a matsayin miji kuma bana jin zan iya rayuwa da wani  d'a namiji face shi,
amma kuma ina da wani  buri da nake son cikawa wanda na fahimci auren nan yana son ya hana min cika burina,

shiyasa nafi buqatar ya sauwaqe min in yaso idan na cika buri na sae na dawo ma auren.
Cike da rashin fahimta Amrah ta qarasa gurin ta, tace"ni kuwa wane buri ne wannan da yafi aure muhimmanci a gurin ki? Ba wai yafi aure muhimanci bane,asali ma muhimancin auren yasa nake jin idan inada aure bani da lokacin komai,domin aure abu ne mai matuqar muhimanci a gurina da bana son had'a shi da da duk wani abu, kan hakan yasa nake son auren ya fita a kaina har sae na cika burina.
Hm Afrah kenan wannan wane irin buri ne haka? Buri na shine na nemo wad'an da sukayi sanadiyar raba ni da mahaifiya ta tun ina jaririya na kuma nemo wad'an da suka raba ni da mahaifina tun ina er shekara biyu,wato en uwan mahaifina da kuma matar sa ta biyu.
Nayi baqin ciki sosai a lokacin da uncle ya sanar da ni wannan labarin duk da cewa bani da wani wayo sosai amma tun a lokacin na qudur ta a raina sae na nemo su indai har ina raye haka suma muddin suna raye wlh bazan bar su ba sae nasa an musu hukunci dai dai da su.
Iska mai zafi Amrah ta furzar kafin take cewa"Amma Afrah na tabbatar a labarin da uncle ya baki ba zai rasa sanr da ke cewa shima yayi bincike akai ba"
Haka ne Amrah ya sanar da ni amma ni ban gamsu da binciken da akayi ba sbd ba a gano su ba sun gudu, daga haka kuma aka daina zancen neman su kinga haka da akayi yana iya qara bawa azzalumi damar yaci gaba da zalunci sa.
Sae dai Dan Allah Amrah bana son kowa yasan dalilin da nake son aure na ya rabu da na uncle sbd ko kad'an bai so sanr dani labarin iyayena ba nice na matsa masa sbd yanda nake ji a school kowa na fad'in "daddy mommy" amma ni bani da su bare nayi zancen su, shiyasa na nemi naji meyasa ni banda su ,
wanda kan irin kukan da nake ina matsa masa da tambaya yasa ya sanar da ni.
Sannan kuma ina so kimin wata alfarma guda d'aya wato ita ce,don Allah Amrah ki auri uncle"zumbur Amrah ta miqe tace"me kike cewa? Abinda kika ji dai shi na fad'a kan cewa ki auri uncle sbd na tabbatar idan na rabu da uncle ba zai zauna haka kawai ba zai yi aure sbd a yau yayi matuqar bani tausayi,domin na fahimci aure yake so,ni kuma ina baqincin uncle ya auri wata mace amma ke zan iya haqura ya aure ki sbd kusan nace tare muka taso mun san halin juna......ki dakata da zancen ki haka domin bazan ta6a amincewa da hakan ba, kuma ni ina da wanda nake so bana jin zan iya rabuwa da shi! Wane ne wannan wanda ban sani ba keda nasan ba kya kula kowa.
Shiru Amrah tayi, Afrah tace "baza ki sanar da ni wane ne ba? Bazan iya sanar da ke ba..... Sbd me? sbd uncle Farhan ne ba kowa ba wanda na taso da son shi tun ina qarama kan yawan taimakon da yake kaiwa mahaifina a matsayin sa na lebaran uncle,sae gashi ya kasance mijinki hkan yasa dole bazan iya auren sa ba ko a mafarki kuwa,kuma koda shi kad'ai ya rage cikin maza bazan iya auren sa ba sae dai na mutu banyi aure ba kan na had'a kishi da ke.
Duk maganar tana yin ta ne a cikin zuciya.
Afrah tace"dake nake nace meyasa? sbd ko shi wanda nake so bai san ina yi ba ,shiyasa bana jin zan iya sanar da ke,,,ni bana ma buqatar naji wane ne tunda naji bai ma san kinayi ba duk da cewa banji dad'i ba domin nasan ba qaramar azaba keda hakan ba kana son mutum bai san kana yi ba,amma dan girman Allah Amrah ina son ki girmama sunan wanda na had'a ki da shi ki taimaka min ki janye son wanda bai san kinayi ba ki saka na uncle koda kad'an ne,ki kuma yarda cewa zaki aure shi,to wlh idan kika min haka bani da wata babbar masoyiya a duniyar nan face ke.....idan kuma naqi fa? Baza ki zamo maqiyiya ta ba amma wlh tamkar kin

rugaza min tsarin rayuwa ta ne sbd idan uncle ya auri wata ba ke ba bana jin zan iya sake auren sa.

Afrah ki ma daina kuka da durqusa min kina roqo na sbd a gaskiya ke ke shirin ruguza tsarin rayuwar ki muddin kika yarda auren uncle ya fita akan ki zai auri wata ce bani ba domin a gsky bazan aure shi ba don haka ki ma daina zancen rabuwar auren ku sbd ban fara mafarkin mun sami sa6ani da ke ba domin idan na auri uncle nasan yau da gobe sae Allah.

Da mamaki Afrah tace"yanzu a yanda muke har kina tunanin don kin auri uncle zamu iya samun sa6ani.....hm bari kiji in gaya miki Afrah koda ace mu hanta da jini ne idan muka had'a miji d'aya dole watarana muyi fad'a sbd shi kishi abu ne da yakan rufe ido da kunne baji ba gani.....naji Amrah kuma na fahimci akan kar mu sami sa6ani ne yasa kike gudun auren uncle.....bashi kad'ai ba ne har da kunya ina ji ace duk amintar mu na aure miki miji....haba Amrah dan Allah ki daina d'auko wani banzan zance ni dai dan girman Allah nake roqon kimin alfarma idan kuma ba kya dubin girman Allah shike nan,,, Afrah rashin amincewa buqatar ki bashi zai sa ya zamo bana girmama Allah ba, amma kuma..... Sae tayi shiru tana wani nazari, bayan ta gama ta tayar da Afrah dake durqushe a gaban ta,ta share mata hawaye kafin take cewa"nima ina da wata alfarma wacce sae idan kin min ne zan yarda da taki,,, fad'i ina jinki,, Alfarmar ita ce ba wani abu bane face kije ki bawa uncle haquri kan abinda kika masa ki kuma snr dashi gsky kina son sa a mtsyn mji ,,meyasa Amrah?bazan baki amsa ba sae idan kinje kin dawo to kuwa duk kika dawo min da zancen na auri uncle zan amince na aure shi, nayi miki alqawari,, da gaske? Da gaske...na gode Amrah kar ki sake min godiya domin mun wuce yiwa junan mu godiya abin kunya ne ma don na miki abu kice kin gode sbd mun riga mun zama d'aya.
Yanzu sae ki tashi muyi sallah sae kije ki bashi haquri.

Bayan sunyi sallah Afrah taje har d'akin farhan sae dai bata same shi ba,bata yi mamaki ba sbd tasan yana masallaci.

6angaren Amrah kuwa Afrah na fita ta fad'a ruf da ciki kan bed tana rusar kuka, sbd tsananin sonda take yiwa farhan wanda ko muryar sa taji sae taji wani abu kmr fad'uwar gaba,bare idan ta ganshi kai tsaye take jin bugun zuciyar ta ya canza, duk akan son shi amma bata jin zata iya amincewa buqatar Afrah duk da wani 6angaren zuciyar ta nace mata wata dama ce ta same ta a sauqaqe da zata mallaki abinda take matuqar so,amma haka ta dake tana hana zyr ta.

Tana cikin kuka ne taji shigowar Afrah cikin sauri ta share hawayen ta ba tare da Afrah ta lura ba.

Tashi tayi zaune tace"ya akayi kika dawo da sauri haka? Baya nan yana masallaci kinsan sae bayan isha'i yake dawowa"

Amrah tace"dama so nayi sae kinyi wanka kafin kije kinga dama ta samu sae kije kiyi wankan ko"

Amrah shi bawa uncle haquri har sae nayi wanka? nidai kije kiyi indai har kina so na amince da buqatar ki, ba musu Afrah taje ta fad'a wanka wacce ta jima sosai kafin take fitowa.

Amrah ce ta shiga shirya ta da kanta duk d'akin ya qamsashe sbd turaren da ta mata wanka da shi.
Ta kuma nemo wasu kayan bacci masu kyau ta bata ta saka sae dai kafin tasa sae da tace"Amrah nifa ban gane ba shirin bacci tun yanzu kuma kin wani shafe ni da turare"ai inace kinji ana sallar isha'i da kinyi sallar ba wani abu zakiyi ba face cin abinci sae shirin bacci kinga ai banyi sauri ba.
Amrah dai bata ce mata komai ba domin ita to 9 take shirin baccin ta.
Nan ta zuba hijabin ta har qasa domin tayi sallah.

Tana gama addu'a kenan taji shigowar farhan .
Amrah tace"tashi kije gashi nan ya dawo.
Da qyar Afrah ta iya miqewa ta cire hijabin jikin ta sae fad'uwar gaba take ji da tunanin yanda zata ba farhan haquri kan abinda ta masa da bata ji dad'in sa ba ko kad'an.
Ta fara tafiya suku suku kamar wacce aka cirewa lakka hr ta kai bakin qofa ta tsaya tace"Amrah ina tsoro domin ji nake kmr wani abu zai faru da ni"name kenan Afrah keda zaki bawa uncle haquri me kike tunanin zai faru da ke?nima ban sani ba.
To zo muje na raka ki ba abinda zai faru da ke sae alhairi.

Bakin qofa ta kai ta ta juyo.

Afrah ta shiga knocking a hankali cike da fargaba.
Kanta a qasa koda farhan ya bud'e qofar yayinda ta shiga jin kamar ta nutse cikin qasa kan abinda ta masa wanda ta fahimci ya girgiza sosai sbd kallo d'aya zaka yi masa kasan yana cikin matsananciyar damuwa, domin in ma a kace mata yayi kuka bata musu sbd yanda taji muryar sa yana cewa"ya akayi ne Afrah?kasa ce masa komai tayi yace"shigo daga ciki idan magana gare ki"
Bata musa masa ba ta shiga taje kan sofa ta zauna ta kame guri d'aya kmr wata munafukar baquwa.

Tayi kusan minti hud'u zaune tana tunanin kalmomin da zata had'a ta bashi haquri can tace"Dan Allah uncle kayi haquri da abinda na maka wlh fad'a kawai nayi ni bada gaske nake bana sonka ba, dan Allah kayi haquri kaji bazan sake ba"kallon ta kawai farhan keyi domin tun lokacin da ta furta cewa bata son sa a matsayin miji yaga sai da ta rufe ido kafin ta furta hakan,tun a wannan lokacin yasan cewa bada gaske take ba, sae dai tunanin sa me ya d'ebe ta ta furta masa hakan.
Jin yayi shiru bai bata amsa ba ta sulale qasa ta fara masa kuka tana bashi haquri.
Shi da kanshi ya tayar da ita ya shiga share mata hawaye kafin yake cewa"amma Afrah meyasa kika min haka, ko kuwa dan ina shafa jikin ki ne, ko kowa dan kinji hanuna a qasan cikin ki ne shi yasa kikayi tunanin zan kai hannu inda bai dace ba.
Duk tamboyoyin nan da yayi mata guda uku tana girgiza masa kai amma sae ta qarshen tayi

shiru taqi cewa komai ,yace "Afrah ba ina nufin na kai hannu na inda kike tunani ba domin nasan shiyasa kika ture ni daga jikin ki",,,yi haquri uncle wlh na tsorata ne sbd ba komai a jiki na sae towel kad'ai kasancewar na fito daga toilet kenan nazo d'akin ka.

Ba komai Afrah ya wuce, kunci abinci ko kuwa? Aa ,to tashi kuje kici abinci sae Ki dawo kinji? Nan ta gyad'a mishi kai ta tashi ta fita.

Bata jima ba ta dawo take sanar da shi  Amrah tace fresh milk kawai zata sha ta kwanta, yace"to kefa?nima bana jin zan ci wani  abu sbd kasan ba mu jima da cin abinci ba...um um ke kam zaki ci wani  abu ,meyasa uncle? Kawai dai nace zaki ci kuma banda musu, ai bazan maka ba,, sbd kina gudun na zane ki ba... ai nasan kana sona baza ka zane ni ba,ko baka sona... Aa qaunar ki dai nake,ya fadi haka ne yayinda ya lakato hancin ta yace "je ki debo abinci muci.

Bayan ta d'ebo ya kalli rigar baccin jikin ta yace"ya kamata ki cire rigar nan ta sama domin kiji da'din cin abinci,

A nan tsaye ta cire rigar  sama wanda ta ciki ta ma fi kyau dai dai jikin ta mai d'an siririn hannu iya guiwa sae dai ana hango jikin ta ba sosai ba.

Idon farhan ne yakai  kan qirjin ta yayi saurin d'auke idon shi dmin yasan da ya qara minti d'aya zai iya hango komai.

A kunyace Afrah ta kalli rigar sbd bata san yanda rgr take ba, cikin siyayyar Amrah take.

Kunya taji sosai ganin ta hango qirjin ta nan ta kama kame kame tana d'an jan wuyan rigar kamar wacce wuyan rgr ya ma yawa bayan kuwa d'as yake a jikin ta tace"uncle ka bari na mayar da rigar sama sbd naga kamr baza ta takura ni gun cin abinci ba sbd material d'in ba mai nauyi bane.

Dariya ta soma bashi wai ita wayo,bai yi dariya ba yayi murmushi yaja hannun ta ya zaunar da ita gefen shi yace"ni kuma sae gashi haka nake son ganin ki sbd rgr tayi miki kyau sosai.

Bata iya ce masa komai ba sae d'an kame kame take ci gaba dayi har ya fara bata abinci tana ci, wanda har sukayi rabin cin abinci bata saki jikin ta ba sae daga baya,koshi ganin tayi farhan baya kallon jikin ta face fuskar ta.

Da suka gama shi da kanshi yakai  kwanukan abinci sbd shi ya buqaci hakan.

Koda ya dawo ya sameta takure ta had'e qirjin ta da guiwa kamr wacce kejin sanyi,kashe splt yayi domin shi har ga Allah ya zaci sanyi take ji.

Kallo ya kunna musu can Afrah ta gaji da faman takure kanta tace"uncle ni zan koma d'aki"meyasa baza ki taya mijinki bacci ba yau gashi har Amrah ta rufe qofa ta zaci a nan zakiyi bacci,,,ai baza ta iya bacci ita kad'ai ba,,to naji amma sae anjima ko zaki koma,,,bata sake cewa komai ba sae kallon rgr ta take wacce ta bari kan sofa tana ji kmr taje kawai ta saka rgr amma tana gudun 6acin ransa kuma kar yace bata jin magana tunda yace haka yake son ganin ta.

Kallo suke yi amma hankalin sa na gun Afrah kar bacci ya soma d'aukar ta domin idan yaga hakan baya jin zai iya takura mata.

A hankali ya kai bakin sa kan saitin kunnen ta yace"Afrah kin fara jin bacci"tukuna uncle"
Nan yaja hannun ta yace"yauwa muje to muyi arwala muyi nafila da zaman nan na banza"

Bayan sun gama farhan ya nemi da su hau gado suyi fira hakan yasa ya kashe TV da wuta ya var dim light kawai,ya shiga yi mata fira inda cikin firar ne ya bata body mist ta shafa mishi,
shi kuma ya shiga shafa jikin ta cikin hikima har yana wasa da hannun rgr ta,
Afrah dai sae binsa take kamar raqumi da akala ita dai kar ta 6ata masa rai,duk da ta fara jin abun nason yafi qarfin ta,amma haka ta dake tana ci gava da shafa mishi body mist kan faffad'an qirjin sa,wanda farhan jin shafar yake tamkar susar qadangare sbd slowly slowly take yi kamar wacce ke gudun taji masa ciwo.
Nan ya riqo hannun ya manna ta a qirjin sa yana mata wani salo wanda ni Billy giro nace ba sae an sanar da ku ba domin kunsan komai.
lol

Ya jima yana gwada mata iyawar shi wanda a sauqaqe ya rava ta da rigar jikin ta sbd ya riga ya kashe mata jiki bata da wani kata6us sae ma taya shi take kan duk abinda ya mata sae kace remote control, cike da natsuwa ya had'e bakin su guri d'aya sbd yanda yaji ta fara masa alamar kuka.
_"Bismillahi, Allahumma jannabna shaitan wa jannabi shaitana ma razaqana._"
Shine abinda ya furta yayinda ya zare bakin sa daga nata.

Fas! Kake jin qarar fashewar wani abu inda a rikice leesa ta saki qwaryar tsafin da ta fashe a hannun ta,ta shiga lalaben d'akin tana fad'in"na shiga uku mom farida ido na bana gani!

*Billy giro😊 & Futha lurv💅
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:21PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [10/14/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futhalurv.WordPress.com*

*```🏅48🏅```*
A 6angaren Afrah kuwa wani irin  ihu ta saki har sai da Amrah ta jiyo wacce ke d'aki zaune kan sallaya.
   Hawaye ne suka silalo a hankali kan kumatun ta yayinda ta furta cewa"Alhmdlh buqata ta ta biya saura d'aya ya Allah ka amsa min".

Farhan kuwa duk ya rud'e da jin ihun Afrah bayan yasan a hankali ya mata sae dai tuna cewa jinin ta mai saurin jin zafi ne komai qanqantar abu sae taji ciwon sa hakan yasa ya bita a hankali sosai amma hakan bai hana tayi tayi masa kuka ba.

Bai fi 40 mnt akanta ba ya barta, kuma Alhmdlh ya gamsu dari bisa dari.
   Nan yake qoqarin rarrashin ta amma tuni Afrah ta fizge jikinta ta bar d'akin.

Tana zuwa ta qwanqwasawa Amrah ta bude mata,ta shiga tare da bedsheets d'in ta da ke ta faman bibiyar ta a baya.

Farhan da ya biyo ta yayi dai dai da Amrah ta maida qofa ta rufe, yayi kamar ya qwanqwasa amma kuma yana jin nauyi sbd yasan dole Amrah zata fahimci wani  abu ya shiga tsakanin sa da Afrah.
   Hakan yasa ya juya ya koma d'akin shi.

Washe gari Amrah ce zaune a bedside tana kallon Afrah wacce tun jiya da tazo cikin kuka ta kwanta bacci ya kwashe ta har yanzu bata ta shi ba gashi anyi sallar asuba.

 Sak Afrah kejin yanda Amrah ke tashin ta amma tayi kmr bata ji ba sae ma tunanin abinda ya faru tsakanin ta da farhan take, tana mamakin kanta da kuma tsananin jin kunya yanda ta biyewa farhan tana maida masa martani a lokacin da yake romancing d'inta har take tantama wai ba mafarki take ba kuwa,sae dai zafin da take ji a qasan ta da yanda jikin ta ke ciwo shi ke bata damar gaske ne sae duk ta shiga tunanin yanda zata sake iya had'a ido da uncle ai sai yace tana buqace tunda har ta kama masa byn bata san yanda akayi ba ma.

Amrah da ta fahimci idon Afrah biyu tace"wlh idan baki tashi kinyi sallah ba zan kira uncle"
A rikice ta tashi tace"haba Amrah ya zaki min haka don Allah kar ki kira shi"
To tashi, cikin dabara ta tashi tare da bedsheets d'in da take famn rufe jikin ta"ta wani turo baki tana kallon Amrah da ke kallon ta tace"to meye kina wani kallo na"sosai abin ya bawa Afrah dariya ta shiga dariya har tana duqawa qasa, Afrah taji wani haushi tace"ai duk kece kuma wlh sae kin min nawa alqawarin!
Tana gama fad'ar haka ta tafi toilet inda tun a toilet corner ta saki bedsheets.

Tana shiga sae ga Farhan ya shigo d'akin ya sami Amrah sae dariya take, yace"keda waye ne haka?uncle wlh Afrah ce ta ban dariya.... Kuka takeyi ne?Aa,ta fad'i haka ne yayinda take qoqarin fita daga d'akin,sae da yaga fitar ta sannan ya shiga toilet sbd yana son ya sanar da Afrah sae fa tayi wanka kafin tayi sallah.

"Innalillahi hava uncle"haka ta fad'i yayinda ta ganshi kai tsaye,shiyasa tayi saurin shiga gurin wanka inda ba lallai bane ya iya hango ta.
Sae dae da shigar ta ta fara ihu, da sauri farhan ya shiga gurin ya same tsugunne sae yarfi take da hannu, wanda duk halin da take ciki bai hana ta ajiye masa rigima kan sae ya fita ba,,yace"Afrah yanda kika kame jikin ki ta yaya zan iya ganin ki nidai kawai gaya min me kike ma ihu....ba shiri ta sake wani ihu ta tashi ta qanqame shi sae fad'in take"wayyo Allah uncle ka kashe ni gshi ynzu bazan iya fitsari ba, zaki iya mana tsugunna muga...to rufe idon ka, yana rufe ido ta tsugunna da sauri sbd fitsarin ya matse ta sosai, amma kuma ta kasa yi sae wani ihu ta sake saki ta damqi hannun farhan tace"uncle bazan iya ba ciwo,Afrah ki daina raki mana kiyi fitsarin....wato ma raki nake yi bayan duk kaine...naji yi hqr, rufe idon ki a hankali sae kiyi fitsarin ni kuma sae na murza miki bayan ki ta yanda zaki ji sauqi, ni bazan rufe ido na ba shike nan sae kaje ka kalle ni ban sani ba,nyi miki alqawari bazan bud'e idona ba, ba musu kuwa ta rufe nata idon ta qara damqe hannun shi yayinda ta fara fitsarin ta wani matse cinyoyin ta fitsarin ma sae da qyar yake fita sae fad'in take "wayyo uncle zan mutu"da kulawa yake murza mata bayanta yana fad'in yi a hankali"ai a hankali nake yi amma har cikin raina nake jin ciwo,, to ya isa daina surutu haka.
Da qyar ya samu ta kammala fitsarin taqi miqewa tsaye a cewar sae ya fita,yace"zan fita amma ki tabbatar sae kin gasa jikin ki kafin ki fito,idan na fahimci ba kiyi ba zan miki da kai na ne,ya qara da cewa"hope kinsan sae kinyi wakan tsarki kafin ki fito?bata ce masa komai sbd kunya ,yayi murmushi ya fita daga toilet d'in.

Haka tayi wankan ta ba tare da ta gasa jikin ta ba ko ta manta ne oho.

Ta fito d'aure da towel ta same shi jikin wardrobe yana fitar mata da kayan da zata saka.
Tun kafin ya juyo yace "meyasa baki gasa jikin ki ba kika fito? Oh ni uncle ya akayi ka sani

bayan baka toilet d'in ko leqe na kake yi? na leqe ki ni munafuki ne, kawai dai yanda kika yi saurin fitowa ne ya bani tabbacin baki gasa jikin ki ba,don haka mu koma daga ciki,marairaice masa tayi tace"wayyo uncle dan Allah kayi haquri...ai kinsan nace idan ba kiyi ba zan miki da kaina,dan haka rashin jinki ya ja miki,kukan shagwa6a ta fashe mishi da shi tace" uncle idan na shiga ruwan zafi mutuwa zanyi kuma shike nan baza ka qara gani na ba.... Wa ya gaya miki ko kin manta inada photon ki a waya bayan wanda nake da shi a d'aki....to ai bazan yi motsi ba bare na maka magana....ai zanyi mafarkin kina min magana har ma muna wasa.....Uhm Uhm ashe baka sona ban sani ba tunda har kake son na mutu,, rungume ta yayi yana rarrashi yace"so kuwa har da qauna  don akan haka ne yasa nake son ki gasa jikn ki sbd nasan idan ba kiyi ba zuwa anjima zazza6i zai iya kama ki sbd kinsan halin jikin ki,
cizon sauro ma se ya saki zazza6in kwana uku bayan kumburin da gurin yayi....nidai uncle bana son shiga ruwan zafi a daina zancen....ai kuwa jikin ki zai gaya miki,....dukana zakayi?da wane dalilin,kawai dai idan baki gasa jikin ki ba nake nufi.
  Ba abinda zai faru sae alheri,, Allah yasa  domin kmr kinsan na qagu na ga baby na,mugun kunya taji tayi saurin ture hannun sa da ya d'ora kan cikin ta tace"nifa wlh bashi nake nufi ba Alherin Allah nake nufi... to ai shima Alherin  Allah ne babba ma kuwa,kai amma fa naji dad'in addu'ar nan taki,har ma kinci kyauta,
 nan ya d'an qara jawota jikin sa yana mai kallon cikin idon ta yace"gaya min idan kinji alamar ciki ya shiga ne a daren jiya domin nasan irin kyautar da zan qara miki, na kuma ji dad'in gaya wa gwaggo a daren jiya Alherin Allah ya same mu,duk yana mata abubuwan ne cikin tsoka na.
  kuka ta ajiye mishi da gaske ba wai na shagwa6a ba tace"Allah uncle zan nutse ka daina fa"idan kika nutse sae na biki kinga sae muyi soyayyar mu ba mai ganin mu bare ya takura mu.
  Qafafunta ta shiga bubbugawa a qasa tana fad'i dan Allah uncle ka daina sani jin kunya wlh ni fa alherin da nake nufi daban,shike nan tunda kince Allah na kuma daina but idan kin shirya kinyi sallah ki same ni a d'aki......me kuma zaka min idan naje d'akin ka?dariya ta bashi sosai yanda ta 6ata fuskar nan had'e da tsoro kmr wacce ke neman guduwa,,,
ya jawo ta ya rungume yana dariya kamar baya mutuwa, irin dariyar da ya jima bai yi ba,yace"abinda kike tunani bashi zan miki ba"
ita dai kallon sa kawai take domin ya burge ta sosai yanda yake dariya sae ya qara mata kyau da haiba,har ta sami kanta da d'anyin murmushi tare da duqar da kanta kmr wacce taji kunya har tana wasa da en yatsun ta, kiss ya d'ora mata kan yatsun ya fita daga dakin yana fad'in kiyi sauri kar ki makara sallah.

*Billy giro😊&Futha luv💅*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:21PM, 11/30/2016] Billy Geeero: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```~AFRAH  KO AMRAH ```*~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*NA Billy giro 😊& Bilqis Sidibe💅*

*Futhalurv.WordPress.com*

*🏅49🏅*

*Back to Ieesa*

Ieesa ihu take sosai har sai da masu gadin gidan suka jiyo wanda a gurguje suka shigo yayinda ita ma mom Farida ta fito da gudu har tana hard'e qafafu.
Suka same ta ido rufe sae lalabe take tana fad'in "na shiga uku mom Farida ga ido na bud'e amma bana gani komai sae duhu"
Kmr ya bayan idanun ki a rufe amma kina fad'in a bud'e suke........ da gske mom Farida da gske idanuwa na a rufe suke? to zan miki qarya ne ki bud'e idanun naki kiga, duk kinbi ki wani tayar mana da hankali a banxa.
A hankali ta shiga bud'e idanun ta har ta ware su gabada'ya wani irin ajiyar zuciya ta fitar mai qarfi tare da dafe qirjin ta ganin ta ga mom farida da ke gefen ta,
Sannan ta kalli masu gadi tace"lafiya kun wani zo kun mana circirko sae kace kiran ku akayi"
Sum sum suka fice, mom Farida tace "kya kore su bayan ihun ki ne ya kawo su, to dan nayi ihu sae aka ce suxo banda gulma, ai dole suxo wannan ihun da kika kurma sae kace wacce aka cirewa ido..... Mom Farida dole ne kinsan abinda na gani kuwa Farhan ne fa ke qoqarin kusantar Afrah bayan boka ya sanar dani zai hana faruwar hakan idan har na daina sallar asuba da ta magrib kuma sanin kanki ne na kiyaye kuma dama ba sallar nake yi ba sae ta min dad'i bare har nayi kuskuren yin su, amma sae gashi a banza domin har addu'ar saduwa da iyali naji yana yi wanda ita ce tayi sanadiyar sa qwaryar tsafina tayi duhu har ma d'akin ya d'auka gabad'aya bana ganin komai da ga qarshe sae kawai nji ta fashe inda qarar fashewar ne ya qara rikitar da ni har na fito a gurguje sae naga shima gidan ba hske kmr yanda na baro d'aki.

Mom Farida ta nisa tace "kar ma ki tashi hankalin ki a yanda naga aikin bokan nan na ci ba yanda xa a yi Farhan ya iya kusantar Afrah, har ma kike cewa yayi addu'ar saduwa da iyali ke addu'ar saduwa da iyali kika sani ne keda tun tashin ki ba kya xuwa islamiyya bare xancen karatn littafan addini,haba mom Farida na fa dad'e da sanin wannan addu'ar tun ina primary nake jin duk abinda Abba da mom keyi har yana karanta wannan addu'ar sbd a d'aki d'aya muke bacci nida su.

_(kunji illar kwanciya da 'ya' ya guri d'aya sea suji duk abinda kukeyi)_

Shiyasa hankali na ya tashi sosai domin nasan komai ya gama wakana a tsakanin su.

Ki ajiye wannan tunanin wata qil addu'ar kawai yayi amma yana can ya kasa biyan buqatar sa da ita don haka yi hanzari ki shirya muje gun boka muji meye gskyr abinda ke faruwa.

*Back to Afrah*

Bayn tayi sallah ta shirya sae ga Amrah ta shigo,
Afrah tace"ina kika shiga da safen nan? Wai falo nje na d'an kwanta shine fa bacci ya kwashe ni "oryt ya xancen magnr mu ta jiya? Da mamaki Amrah ta kalle ta tace" wai still kina kan bakar ki? Eh man akan wane dalili ma kike tunanin zan janye?hm Afrah rufin asirin ki shine ki daina xancen nan..... Um Um dan Allah kar ki soma kuma kar kice min baxa ki yi ba sbd kin riga kimin alqawari tun jiya.
Shiru Amrah tayi domin duk a tunanin ta duk macen da tasan meye kwanciya da miji ba zata so ace mijin ta na kwanciya da wata ba face ita koda kuwa auren ta yayi zata ji kishin hakan sosai, amma sae gashi taga Afrah bata ma damu ba.

Nida futha dai munce
may be qurciya ke cinta.

Afrah tace"kinga tunanin me kike bayan tun jiya mun gama maganar komai har kika sa naje gun uncle gashi har kinsa avinda bana son ya shiga tsakani na dashi ya faru.... Meyasa ba kya so bayan mijinki ne? sbd idan hkn na faruwa tsakani na dashi yau da gobe zan iya samun ciki ni kuma ba son hakan nake ba kuma family planning baya cikin tsarin rayuwata shiyasa nake son ki aure shi.

_Allah yasa ma kin sami cikin_

Shine abinda Amrah ta furta a ranta ko meye dalilin ta oho .

Kice wani abu mana Amrah uncle yana jira na a d'aki',, shike nan kije ki snr da uncle idan har ya Amince magana ta qare, dad'i taji sosai tace "ai nasan uncle zai yarda har dai idan na nace masa da xancen"

Ta fita sae murna take Amrah dai sai binta tayi da kallo wacce ke ta roqo a cikin ranta "Allah yasa kar uncle ya yarda"

Sbd har ga Allah duk son da take yiwa Farhan bata jin zata iya auren shi sbd Afrah, da dai wata ce zata iya cusa kanta na ganin ta mallake shi.

Afrah na shiga d'akin Farhan ta same shi yana linke kayan baccin ta da ta bri.
Yi tayi kmr bata gani ba, Farhan yazo da kayan ya riqo hannuwan ta ya d'ora su a Kai

yace"ga kayan baccin ki da kika bari garin gujewa miji "
Zubadda kayan tayi tace"wai uncle baza ka daina ba ko? Sorry amma bana son kina jin kunyar nan nafi so ki saki jikin ki kmr ba abinda ya faru tunda an riga an zamo d'aya,, ni bazan haqura ba sae ka amince da xancen da zan gaya maka yanxu " Ina jin ki ko sae mun zauna? Eh sae mun zauna kuma sae kace ka amince kafin na fad'a.
Hannun ta yaja suka zauna yace" bazan ce na amince ba sae naji xancen tukun "ni kuma bazan fad'a ba sae kace ka amince" a'a ba a yi haka ba haquri zakiyi ki fad'a domin bansan wane irin zance ba ne nje nace na amince sae kin fad'a naji ba haka ba azo ki ajiye min rigima ki kuma d'auka ko bana da mutunci, ai nasan kana da mutunci za ma ka amince da abinda zan fad'a ,to ina sauraren ki.
Sae da ta kalle shi ta kuma duqar da kai tana wasa da en yatsun shi sannan ta fara da cewa " uncle dama ba wani abu bane so nake dan Allah ka auri Amrah tunda kaga tare muka taso shiyasa nake son muci gaba da rayuwar mu a tare har mutuwa kuma kaima nasan zaka so hakan sbd ka san halin Amrah kmr yanda ita ma tasan naka, bana tunanin xa a sami wata matsala a tsakanin ku amma kai me ka gani? Ta fad'i haka ne yayinda ta tsure shi da ido tace "me ka gani uncle? Abinda na fahimta dai shine yunwa kike ji har kina wani xancen can daban"
Me kake nufi uncle wlh zanxen gaskya nake kuma mai muhimmanci, qwarai na fahimci yana da muhimmanci amma da alama idan kika ci abinci zaki fi bashi muhimmanci sa, cin abinci da safe haka nida nake son ma na koma bacci, to naji kisha fresh milk kafin kiyi bacci, nifa kace wani abu tukun, to ai so nake kisha fresh milk sae mu qarasa zancen, ya fad'i haka ne yayinda ya tashi ya tsiyayo mata fresh milk a cup yaje yana bata.
bayan ta gama ya d'auko magani zai bata tace"me kuma zai sa nasha magani byn lafiya ta qalau? sbd rashin gasa jikin ki da bakiyi ba idan kuma ba kya sha sae ki tashi muje agasa jikin.....gsky ni bazan yi ko d'aya ba, cak taji ya d'auke ta ya nufi hanyar toilet da ita yace "dole kiyi d'aya yarinya"naji dan Allah sauke ni kar ka sani a ruwan zafi zan sha maganin" ba musu ya koma da ita suka zauna ya bata magani ta kar6a kmr tayi kuka tasha yace "yauwa dama abinda yasa nace kixo kenan dan haka sae ki kwanta kiyi bacci........wane baccin bayan kasan magana muke ka tursasa ni kan sae nasha fresh milk....... ai wannan daji sambatun yunwa ne kmr yanda na yanxu ya kasance sambatun kinci kin qoshi..... Uhm Uhm wai uncle me kake son mai da ni ne,Allah ka duk san da gske nake yin zancen nan amma kake wani basarwa, ni ko nasan da gske kike yi tunda gaki a gaba na ba mafarki nake ba amma kinsan wani lokaci idan dad'i yayi wa mutum yawa haka kawai sae ya fad'i wata magana don yaji dad'in bakinsa yayinda mai saurare idan yana da hankali ba zai biyewa mgnr ba.
Daga haka yayi kwanciyar sa ya kuma rufe idanun sa,nan ta wani 6ata fuska cikin muryar kuka ta ajiye masa surutn da ba makari don kawai kar yayi baccin da ta fahimci yana so yayi.
A hankali ya bud'e idon shi ya jawo ta ya kwantar kan jikin sa yana bubbuga bayan ta kmr wata er baby yana fad'in "shi yaro idan kaga ya cika rigima kuma baya tare da yunwa gashi kuma lafiya qalau ba wani ciwo to bacci yake ji" to ai ni ba yarinya bace "naji ya dai isa haka idan ba so kike mu 6atawa junan mu rai ba ki lalata mana amarci" daga haka tayi shiru tana kuka ciki ciki,nan Farhan yayi ta lallashin ta har sukayi bacci.

Sae guraren qarfe goma suka tashi Afrah taje d'akin su ta watsa ruwa kamar yanda Farhan ya shiga nasa toilet .

Zuwa 11am sun gama break fast kan dining su duka uku Amrah ta tashi ta wuce d'aki Afrah kuwa ta wani marairaice fuska tana kallon Farhan, cike da kulawa ya zaunar da ita kan cinyar sa yace "wa ya ta6a min ke",,,uncle ne,, wane uncle?kai mana,,, ni d'in da kai na? eh man,, to amin afuwa ... Maqale kafad'a tayi tace" ni bazan maka ba sae idan ka amince da zance na.
Afrah zan miki tambaya amma ina son ki fad'a min gaskiya domin kinsan bana son qarya,,,naji uncle, meyasa kike son na auri Amrah da wane dalilin? Yanda na maka bayani da farko dai d'in ne ba wani dalili,,, banda qarya fa nace Afrah,, ai uncle ba qarya na maka ba.... Hm Afrah ni fa ba yaro bane da zaki mayar irinki dan haka ki fito ki gaya min gaskiyar dalilinki may be ma idan naji na amince da buqatar ki.
Uncle nifa bani da wani dalili kawai dai ina ra'ayin muyi miji d'aya nida ita.
Ajiyar zuciya ya sauke ya miqar da ita suka tashi tsaye, inda a hankali ya d'ora mata kiss kan goshi yace"zan fita bazan dawo ba sae bayan la'asar,
ku tabbatar kun shirya kfin na dawo sbd kinsan fita zamuyi domin qarasa sayayyar da ba muyi ba.
yana kawo nan yasa kai zai fita tace "uncle meye haka muna magana zaka fita? Ki bari idan kin shirya fad'a min gskyr dalilin ki sae na tsaya na saurare ki.
Bai jira me zata ce ba ya fita.
Cikin kuka ta haura zuwa d'akin su, Amrah da ke packing kallon ta kawai tayi bata ce mata komai ba sbd dama tayi tunanin Farhan ba zai yarda ba.

Ana gama sallar la'asar sae ga Farhan ya dawo yaje d'akin su Afrah yayi knocking, Amrah ce ta bud'e masa kasancewar Afrah sallah take yace "Ina ftr kun shirya? Shiru tayi ta duqar da kai,
yace" Afrah bata shirya ba ko? Eh nayi nayi da ita ta shirya tace baza ta je ba, Ina take ne? Sallah take,, to idan ta gama kice ta same ni a d'aki.

Yana zuwa d'aki ya cire kayan jikin sa ya d'aura towel sae ga Afrah ta shigo da sallamar ta, sae da ya kalle ta kafin yake amsa sallamar.
tsayin ta tayi a bakin qofa shi yaje ya same ta yace "puppy luv yi haquri ki shirya muje kinji,,! Um um uncle kuje kawai don ni ko wanka banyi ba,, ai nima yanxu zanyi wankan zo muje muyi tare,, da mamaki ta kalle shi ta yaya ma zata iya wanka da shi, sae dai bata ce komai ba sae girgixa kanta tayi.
Yace "olryt idan Baza ki iya wanka dani ba je d'akin ku kiyi amma kiyi sauri kinji" ,, nifa ba inda zanje ku tafi kawai,, to saqon gwaggo fa? zan ba Amrah ta saya mata, Afrah nasan kina son fitar nan amma fushin da kike yi dani yasa kika ce baza ki je ba,kiyi hqr ki shirya muje kinji,, cikin muryar kuka tace nifa uncle nace maka bazan je ba, cike da son ya rarrashe ta ya qara matsawa kusa da ita tayi saurin bud'e qofa ta bar d'akin.

Har suka shirya zasu fita kuka take Farhan yazo yayi rarrashi har ya gaji taqi shiru haka suka fita shida Amrah ya biya 6angaren su Amir ya kira shi kasancewar tare zasu je.

Afrah kuwa njin tashin motor su ta qara fashewa da wani sabon kuka sbd taso fitar ba kad'an ba amma fushi irin nata yasa ta dake kan bata zuwa.

Har washe gari Farhan bai sake sa Afrah a ido ba sbd jiya tana jin sun dawo ta shige toilet ya vawa Amrah saqo kan in ta fito ta same shi a d'aki amma da Amrah ta snr mata sae taqi zuwa.

Sai yanxu da zasu je airport suka had'u kallo d'aya tayi masa ta kauda kai haka shima Farhan kallon ta kawai yayi yaci gava da sallama da su Baban Amir .

*Nigeria*

Har suka isa kuwa ba wanda yace da wani qala hakan yasa ran Afrah ya qara 6aci ai kuwa suna shiga gida ta fad'a jikin gwaggo tana kuka,kallon ta farhan keyi wanda da gani kukan na qona masa zuciya sosai.

*Billy giro 😊&Futha lurv 💅*

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:21PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [16/10/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futhalurv.WordPress.com*

*```🏅50🏅```*
Gwaggo tace"Aa lafiya Afrah keda muka jima ba mu had'u ba amma shine kika tarbe ni da kuka, ko kukan murna ne, kai wannan kukan kmr ba haka bane,me aka yi mata ne farhan?
d'an guntun murmushi yayi yace"
kinsan halin ta gwaggo rigima ce kawai"
Oh ni shatu da girman ki Afrah gashi kinyi 6ul 6ul kin wani qara haske da kyau kmr balarabiya sae kace don kiwon ki kadai kuka je Oman,daina kuka gaya min wa ya ta6a ki na rama miki?
Komai bata ce ba tayi shigewar ta d'aki.
Farhan ya bita yana fad'in Afrah ba ke ji ne gwaggo na miki magana shine kika share ta kmr ita ce ta miki laifin!
Saurin dakatawa tayi ta fasa shiga toilet d'inda tayi niya sbd jin yanda farhan yayi magana ransa a 6ace.
Tace"yi hqr uncle ba wai share ta nayi ba fitsari ne ya matse ni..... Shut up! wane fitsarin bayan kafin mu iso sae da kikayi fitsari!....wlh uncle....shiii je ki bata haquri!
Tako d'aya tayi ta tsaya cak tana sauraren saukowar fitsarin da ya kufce mata,a tsorace tayi saurin kallon farhan
da ya fara tako a hankali yana kallon fitsarin,ai kuwa kai tsaye ta katse fitsarin tana ja da baya tana fad'in"dan Allah uncle kayi haquri kar ka daken wlh bada sani na ba ya fito min..... Wayyo gwaggo ki bashi haquri yana qarosowa zai daken.
Gwaggo tace"hava farhan yi haqyri mana tunda kaga da gaske dai ne fitsarin take ji, kuma ba gayya bace sbd sanin kanka ne tun tana er qanqanuwa duk yanda fitsari ya matse ta bata yinsa a jikin ta.
Sosai gwaggo ta bashi mamaki da har take bashi haquri wai kar ya daki Afrah, ta yaya ma zai iya dukan Afrah wanda ko fad'an nan da yayi mata jarumta ne, kuma shi tausayi ma ta bashi da yaga tayi fitsari sae duk yaji bai kyauta ba kan fad'an da yayi mata.
Yace"gwaggo nifa ba dukan ta zanyi ba kawai zan ja hannuta ne muje toilet ta qarasa fitsarin"to jata kuje ni na samu na gyara gurin kafin Ku fito......um um gwaggo ki barshi kawai na gyara "
cewar Afrah wacce har yanzu bata yadda idan sun shiga toilet farhan ba dukan ta zai yi ba.
Bai kula yanda taqi yarda da hakan ba kawai yaja hannun ta yana fad'in "gwaggo ki bar mata gurin ta gyara tunda haka take buqata .

Suna shiga toilet Afrah ta shiga bashi haquri har tana qoqarin jiwa kanta ciwo garin guduwa.
Farhan ne yayi saurin jawota ta fad'a jikin sa, nan ta shiga qarasa fitsarin a jikin ta kan yanda ta tsorata da jawo tan da yayi sbd ita bata ma san cewa zata jiwa kanta ciwo ba.
Farhan ya kalli yanda ta qanqame shi kmr wacce ke shirin yaga masa riga kan damqar da ta masa ta wani cusa fuskar ta a cikin qirjin shi jikin ta sae wani rawa yake tana sauraren saukar duka.
A hankali ya kira sunan ta, ta d'ago kamr wata farar kura yace"kin gama fitsarin? gyad'a masa

kai tayi yayinda hawaye ke silalowa a hankali kan kumatun ta.
Riqo kumatun nata yayi kmr wanda zai share mata hawaye se lumshe idon sa tare da matsawa a hankali ya had'e bakin su inda ya jima kafin yake zare bakin nasa, ya rungume ta yana magana qasa qasa kmr mai rad'a yace"Afrah me yasa kike tunanin zan iya dukan ki da har kika firgita da yawa haka sae kace na ta6a dukan ki"
Afrah wacce ke ta famn sauke ajiyar zuciya ta qara shigewa jikin sa tace"sorry uncle"
D'ago fuskar ta yayi yana share mata hawaye yace "to muje ayi wanka ko?
Samun kanta tayi da kasa yi masa musu gashi mugun kunyar take ji ya mata wanka sae dai toilet d'in ba wani haske dim light ne.

Bata iya ce masa komai ba kuwa har ya shiga cire mata tufafin jikin ta sae dai bata bar ya cire mata riga ba sae da ta juya masa baya wanda koda ya juyo da ita ta rufe qirjin ta da hannuwa , nan ya d'auke ta ya had'a mata ruwa a baho ya saka ta a ciki, sae dai still har ya fara mata wanka hannuwan ta na kan qirjin ta, dad'in wanka da gajiyar zaman jirgi suka tara mata guri d'aya har bacci ya soma kwasar ta.
Bayan ya gama yi mata wanka ya had'e hannun ta da nashi ya murza a hankali wanda hakan yasa ta farka daga baccin da take Yace"sae ki tashi an gama wankan,kunya taji sosai da taga hannuwan ta basa kan qirjin ta nan tayi saurin kai d'ayan hannu ta rufe d'ayan kuma ta rufe fuskar ta tace"uncle ka tafi kawai zan fito"murmushi kawai yayi ya fita ya sami gwaggo ta gyare gurin tsaf ta jera musu abince kala kala.

Yace"sannu da aiki gwaggo"ai kune da sannu kuda kuka sha hanya, yauwa wai ya ban ganku da Amrah ba?Gwaggo ai Amrah tawaye ta mana tunda taga Abbanta yazo tarbar mu tace baza ta biyo nan ba sae gobe zata zo ta gaida ki,,, to ai banga laifin ta ba tunda dama gida ya kamata ta fara zuwa taga iyayen ta tukun,,, haka ne kuma,, ni zanje na d'an watsa ruwa na rage gajiyar da nakeji idan Afrah ta fito taci abincin kawai ba sae ta jira ni ba...au ya bata fito ba, ko fushi take
shine taqi fitowa ? ba fushi take yi ba zata fito ne ynzu.

Daga haka ya fita.

Afrah dake la6e a bakin qfr toilet tana jin kunyar fitowa ta d'an fito kad'an tace"gwaggo ya tafi ko?
waye?
uncle,,, hm shi kuma uncle d'in ake kunya,bata dai ce komai ba ta fito tayi zaune zaman cin abinci

Gwaggo tace" d'aure da towel d'in zaki ci abinci,,, ni gwaggo yunwa nake ji sosai, to ai gaki nan gashi.

Har ta bude kula sae tayi saurin tashi kmr wacce ta tuna wani abu tazo ta rungume gwaggo a hankali tace"dan Allah gwaggo kiyi haquri wlh dazun fitsari ya hana na miki magana ba wai fushin da nake yi ba"ai ba komai jeki kici abinci"

Har taci abinci ta kammala farhan vai shigo ba .

farar vest ta nemo ta saka da baqin wando three quarter taje kan jikin gwaggo sae fira suke cikin nishad'i sae ga farhan ya shigo da sallamar shi Afrah tayi saurin 6oye fuskar ta jikin gwaggo tayi kmr bacci take ,girgiza kansa yayi domin yaga lokacin da ta 6oye fskr ta .

Gwaggo tace"wai kuma yanzu kai take kunya ko me ya faru ne oho.

Sae da farhan ya zauna sannan yace"ai gwaggo tun lokacin da ta fara girma sae kawai naga ta fara kunya ta sae kace bani ke mata wanka ba har ta kammala primary, shine yanzu wai don na mata wanka take wani jin kunya ,,,, kai ko dai farhan dole taji kunya yanxu fa an girma ga d'an gaba nan duk ya taso ya cika guri gwanin sha'awa.

Cikin jin kunya Afrah ta qara shigewa jikin gwaggo,farhan yace"nifa ban ma wani ganta ba sbd dim light amma shine har bata son had'a ido dani"ai kasan kunya adon mace ce.

Nan sukayi shiru ba wanda ya sake cewa komai inda farhan ya maida hankali yana cin abinci.

Har farhan ya kammala cin abincin sa Afrah na 6oye jikin gwaggo yace"gwaggo Afrah tayi bacci ne ?tana jinka yanzu haka sae wasa take da hannun ta kan jikina,, Yace"Afrah zo na tambaye ki mana, ba musu ta tashi taje kan jikin sa ta lafe sae kace mage.

Hakan da ta masa ba qaramin juriya yayi ba domin shi kad'ai yasan abinda yake ji wanda kmr kar ya mata wanka ya fara jin kansa da buqatuwa.

yace"zan tamvaye ki zaki kwana a 6angare na yau ko sae gobe idan kin tare? Nidai uncle a daina wannan zancen tukun kace ka amince da buqata ta shine abinda nake so naji,,,,gsky Afrah bazan ce na amince ba sbd ni mace d'aya ta ishe ni,sannan ita Amrah ce miki tayi ta rasa mijin aure ne....ba zancen haka bane uncle nidai dan Allah amincewar ka nake buqata.

Afrah meyasa ke kam ba kya jin kishin mijinki har ke da kanki wai kike cewa na auri wata, ai ni bansan meye kishi ba bare har nayi, to zan gaya miki meye kishi,

kinga zaki ji ko kad'an ba kya son na ambaci sunan wata mace bare zancen na tsaya kusa da ita muna masu firar soyayya har ta kai mu ga yin aure muna masu kwanciya a gado d'aya yayinda mu'amalar aure zata shiga tsakani na da ita,ma'ana wannan abun da ya faru tsakani na dake har kika ta min kuka zaki so ya faru tsakani na da wata ba ke ba?turo baki tayi ta wani 6ata fska tace"to ni ina ruwana ba sae kaje kuyi tayi ba, kawai dai idan baza ka amince ba ka daina cika ni da surutu"yanzu Afrah kina son wata ta san sirri na da ke kad'ai nake son kici gaba da sanin sa......Uhm Uhm nidai ka bar ni haka tunda baza ka amince ba kuma daga yau ma ba ruwana da kai kar ka sake min magana .

Daga haka sautin kukan ta ya qarasa fitowa gaggwo wacce duk mgnr nan da sukeyi bata jin su sae lazimi take kuma ko banza qasa qasa sukeyin magana sae yanzu ne taji kukan Afrah tazo kan jikin ta ta kwanta.

Farhan yazo ya durqusa kusa da ita yace "tashi muje 6angaren mu dare yayi,,,ture hannun sa tayi tace"ni bazan je ba"oh oh gwaggo dan Allah ce ya daina ta6a ni me ya shafe sa dani ma wai da ba zai yi tafiyar sa ba ,Afrah yau kuma uncle ne fa,uncle d'in wasu ne ba nawa ba na yafe shi tunda baya son abinda nake so....ikon Allah me take so ne farhan?gwaggo mayi maganar gobe sbd yanzu wani irin bacci nake ji,,,To shi kenan Afrah tashi kuje mana,,maqale kafad'a tayi tace"ni anan zanyi bacci"yi haquri Afrah kizo muje kinji...um um bazan je ba... Afrah ba kyau yiwa miji gardama fa,gwaggo ce ta fad'i hakan, Afrah tace"aini na daina yin miji dashi daga yau"

To gwaggo ni kan zan tafi tunda vata zuwa,,to Allah ya tashe mu lafiya,,,Yace"Amin kafin yake fita.

Gwaggo tace"Wai Afrah da gaske baza ki je ba kuwa...nidai gwaggo ki daina min maganar uncle kwata kwata daga yau ba ruwa na da shi ,
wlh kuma da gske nake idan yaqi ya amince.

Gwaggo ta bi ta da kallon mamaki domin ta fahimci da gaske dai Afrah ke zancen ba zancen shagwa6a a ciki to sae dai mene ne take son farhan ya amince da har yaqi.

Nan Afrah ta tashi tana share hawayen fuskar ta taje d'aki kan bed ta kwanta.

Haka shima farhan yana zuwa d'aki ya nemi guri ya kwanta sae juyi yake cike da son kasancewar Afrah Kusa da shi sae yaji duk baccin da yake ji ya tafi yayinda ya shiga mamakin kansa shida bai fiye buqata ba ya kayi yanzu kwana biyu kacal har yaji yana son wani abu ya sake shiga tsakanin sa da Afrah ko don ya jima baya tare da mace ne.

Haka ya qaraci tunanin sa wanda tunanin sae qara masa buqatuwa yake har dai idan yana tuna surar afrah a lokacin da yake mata wanka,hakan ya qara masa jin baya iya bacci bai same ta ba.

Nan ya tashi ya koma 6angaren gwaggo da niyar ya qara lalla6a Afrah sae ya samu har gwaggo ta rufe 6angaren ,
akan dole ya juya wanda yana shiga 6angaren sa yaje yayi arwala ya shiga yin nafilfili.

*Billy giro😊&Futha lurv💅*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:22PM, 11/30/2016] Billy Geeero: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```~AFRAH KO AMRAH ```*~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*NA Billy giro 😊& Bilqis Sidibe💅*

*Futhalurv.WordPress.com*

*🏅51🏅*
Washe gari guraren qarfe goma Farhan ne ya shigo 6angaren su gwaggo ya sami Afrah ta fito daga wanka kenan tana d'aure da towel iya cinya ,
kallon ta yake yana yi ma gwaggo ina kwana.
Bayn sun gama gaisawa da gwaggo ya nemi guri ya zauna yace " Afrah ba gaisuwa? Kmr yayi magana da dutse sae da gwaggo tace" ba kya ji Afrah"
Gwaggo ai nayi miki Ina kwana , ai bani ake magana ba uncle d'inki da baki gaida ba.
Vaseline kawai ta d'auka Kan dressing mirror ta koma falo ta zauna.

Gwaggo ta kalli Farhan da ya soma shiga damuwa tace " wai me take son kayi mata ne kai Kuma kaqi? Mtsw gwaggo wai wani shirme naji tana fad'a wanda ba tasan naji duk abinda take gaya ma Amrah ba kan cewa wai sae ta nemo wad'an da suka kashe iyayenta byn tun a lokacin ba irin binciken da ba'ayi ba amma ita tace sae tayi nata shine ta d'auko wani banzan shirme na na auri Amrah a cewar ita binciken da zata yi ba zai bata damar kula ni ba.
Hm hankalin ta d'aya kuwa ko Kuma dai wani abu take so ta fake da hakan, ba wani abinda take so gwaggo har ga Allah so take ta nemo en uwan Abbanta domin a yanda take ma Amrah bayani tana kuka zaki fahimci da gaske take but ai wannan aikin ko ni mai yinsa ne rashin sanin makamar inda xa a fara neman su ne matsala sbd su neman su bana bugawa da jarida bane ko a yad'a a media dmn idan aka yi hakan ganin nake idan suka ji zasu iya guduwa ba tare da an gansu ba, sannan shekaru da yawa haka ya ma nasan ta inda zan fara vare ita Afrah, shin tukuna ma ko suna raye ko basa raye duk ma bamu sani ba.... Shi na gani gwaggo rigima ce kawai irin ta Afrah wlh tunda tasan ba anan zamu tabbata ba tayi haquri mana har zamu je inda xa a bawa kowa haqqin sa kan duk wanda ya zalunci wani Allah ba zai bar shi ba sae ya hukunta ta shi.
Sannan kuma nayi tunanin ba abinda ta nema ta rasa bare nace ko dukiyar ta take son kar6owa.
To ka ganar da ita hakan mana ko zata fahimta, zanyi qoqari na gani domin gsky bana jin zan amince ma shirmen ta .
Yana gama fadar haka yaga giftawar Afrah yace da gwaggo "kingan ta tana ma jin abinda muke fad'a nasan ko naje baza ta sauraren ni ba sae ma wata rgmr da zata taso min da ita,,,kaje dai ka rarrashe ta ko zata janye wannan ra'ayin.

Koda yaje ya same ta ko Vaseline d'inda ta d'auka bata shafa ba ya zauna a hankali kusa da ita yace "tabi'ar da kika d'auko kenan Afrah ana magana kije ki la6e kina saurare, ki daina irin haka ba kyau kinji "
En hawayen da suka cika mata ido ne suka shiga silalowa tayi saurin share hawayen zata bar gurin, Farhan ya riqo hannun ta ya zaunar da ita sae kawai ta fashe mishi da

kuka, kmr wanda ake hurama wuta a cikin zuciyar sa yake jin kukan yayi saurin jawo ta ya rungume yana rarrashi cike da son tayi shiru ko zai daina jin abinda yake ji, amma sae ma qara fitar da sautin kukan take.

Yace "dan Afrah ki daina kukan nan wani abu nake ji a zuciya ta,bata kulashi ba taci gaba da yin kukanta gashi yanda take ci gaba da kukan hakan yake qara jin abun na qaruwa.

Buttons d'in rigar sa ya bud'e ya jawo hannun ta ya zira a cikin rigar shi ya d'ora hannun ta gefen hagu dai dai 6angaren zuciyar sa, d'agowa tayi tana kallon shi sbd yanda taji zuciyar sa na bugawa yace "kinji ko kinji abinda zuciya ta keyi idan kina kuka ji nake kamar zata fashe, ko so kike ta fashe na mutu ki daina gani na,saurin girgiza kanta tayi wanda hakan yasa hawayen da ke maqale a kuncen ta suka qarasa saukowa,ta bud'e d'an qaramin bakin ta wanda idan tayi magana ba ka cewa ciki ta fito sbd kad'an take bud'e shi amma Kuma sae mganrta ta fito dai dai yanda take so yayinda mai sauraren zai ji abinda ta furta ba tare da yaji maganar ta maqale ba.

Tace "ni uncle bana so ka mutu ka barni" to ki daina kuka kinji "nan ta shiga share hawayen ta ya shiga taya ta, sannan ta wani marairai ce tace" but pls uncle..... Yatsan sa ya d'ora Kan lips d'inta tare da girgiza mata kai yace " na roqe ki da Allah kar ki furta maganar da kike da niya" kan dole tayi shiru amma taso ta sake roqon sa ko zai amince amma zata bar abun har wani lokaci.

Nan ta sami kanta da kwanciya kan qirjin sa takai hannu a hankali kan gefen zuciyar sa tana saurare,murmushi ne ya su6uce mata tace "lah uncle zuciyar ka ta daina bugawa sosai a yanda take yi dazun lokacin da ina kuka yanxu shike nan baza ta fashe ba ko? Baza ta fashe ba,,,to ni uncle ina tawa zuciyar take?sae da ya kalle ta da d'an murmushi sannan ya d'ora hannun sa kan mamman ta na hagu ba tare da ya zare mata towel ba ya d'an tafi da hannun sa qasan mamman ta kad'an, duk da taji mugun kunya amma haka ta dake sbd tana son tasan inda zuciyar ta take , tace "uncle nima tana bugawa?eh tana bugawa amma normal bugawa ne wanda ko yaushe take yinsa, kawo hannun ki kiji amma ki saurara da kyau

Nan ya riqo hannun ta ya d'ora dai dai inda shima ya aza yace kinji ko? Naji kad'an kad'an amma ba irin naka ba da naji a d'azu, to muje dama kiji,, nan suka koma kan mamman ta na dama yace "me kika ji ? Banji ko kad'an d'in da nake ji a gefen hagu na ba,ryt ba ya bugawa sbd ba zuciya a gurin domin ko wace hallita zuciya d'aya take da ita ina ce yanxu kin fahimta? eh amma yaushe ne zata daina min motsi ta huta? Sai idan kin mutu, kmr tayi kuka tace ni uncle bana son na mutu, meyasa? sbd bana son na daina ganin ka,,,da gaske? Allah kuwa, to meyasa ba kya son ki daina gani na? Sai da rufe fuskr ta da tafin hannun ta tace "sbd ina sonka bana son na daina ganin ka har abada,sosai yaji dad'i ya jawota ya rungume, tare da zira hannun sa a hankali cikin towel d'in ta ya tafi da shi gefen mamman ta na hagu yana shafawa yace" nima ina son ki shiyasa bana son wannan zuciyar ta daina aiki.

*Futha lurv 💅&Billy giro😊*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

[10:22PM, 11/30/2016] Billy Geeero: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```~AFRAH KO AMRAH ```*~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*NA Billy giro 😊& Bilqis Sidibe💅*

*Futhalurv.WordPress.com*

*🏅52🏅*
Kame jikin ta tayi tana fad'in "uncle ka daina wani abu nake ji"
Zare hannun sa yayi a hankali ya kai babban yatsan sa yana shafa lips d'in ta yayinda yake kallon cikin idanun ta cikin wani salo ,
yace "gaya min me kike ji" kunya taji ta tashi ta bar gurin.
Jingina bayan sa yayi ya lumshe ido had'e da fitar da ajiyar zuciya a hankali sannan ya tashi yabi bayan ta. yana shiga yace da gwaggo ni zan fita sae na dawo,to a dawo lafiya.
Ya kalli Afrah kmr zai ce wani abu sae kuma y fita.
Gwaggo tace "ke Afrah baki ga Farhan zai fita bane,da baza ki raka shi ba" gwaggo nida bama kaya a jikina, kije ko bakin qofa ne mana ki masa Allah ya kiyaye sai ki dawo.
Ba musu kuwa ta fita har tana had'awa da sauri kar ya fita bata same shi ba.
A nan falo ta had'u da shi yana gab da fita sae kawai taga ya tsaya ya juyo yana kallonta yace "zo man Afrah ba rakiya kika zo yi ba, da murmushi ta qaraso gurin sa ,kanta ya shafa tare da d'ora mata kiss kan goshi yace" ni zan fita me kike so na dawo miki da shi? kallon sa tayi ta kauda kai tna wasa da en ytsunta kafin take cewa "kazo min da ice cream sannan da Oat choco" su kad'ai? Eh, to ni baki min nawa kiss ba,,hannun sa ta
riqo da niyar d'ora masa kiss akai yace "ni a nan nake so kimin" lips dinsa ya nuna yaga kmr baza ta iya ba ,yace "to yi min a inda na miki"
nan ya d'an russuna ta riqo kumatun sa shi Kuma yana riqe da hannayen ta ta d'ora masa kiss kan goshi tare da fad'in " a dawo lafiya uncle"
Nan ya mata bye bye ita ma tana mishi har ya fita.

Kafin ya fita gidan ya had'u da Amrah sae da suka gaisa sannan ya wuce wanda koda ya shiga mota yana jiyo ihun Afrah da ke murnar ganin Amrah sae kace ba jiya jiya ne aka rabu ba.

Bari mu koma 6angaren su leesa muji ko ya suka kasance.

Ba wani 6ata lokaci leesa ta shirya suka tafi sae dai rai 6ace suka dawo da alama sunji irin rashin nasarar da sukayi wanda da shigar su gida leesa ta fara fad'in "hava mom

Farida ki daina wannan xancen wlh bazan dangana ba sae nasa kowa ya tsani farhan na kuma tsiyata shi tsiya tsiya ta yanda ko ita kanta Afrah sae ta guje masa bare har wata mace tayi tunanin ra6ar sa,kuma tunda na rasa shi wlh sae na raba sa da duk wani farin cikin sa, na kuma raba sa da duniya tunda boka ya sanar da ni ba aure tsakani na da shi har abada to kuwa banga amfanin zamn sa a duniya ba.

_hm my lady kinji me leesa ke fad'a shin ko akawai wani abunda bawa zai yi ma bawa wanda Allah bai masa ba?ko d'aya my lady domin duk abinda ki ga ya sami bawa to kuwa nufi ne na ubangiji da kuma jarabawar sa sbd ba wani mai iko sae shi, haka kuma ba wani mai rahama sai shi kinga kuwa ba wanda ya isa yaye rahama ga wanda Allah ya yiwa haka kuma ba wanda ya isa ya arzita wani bare yace zai iya kar6ewa ko ya aikata wani mummanan abu a kansa_

*******

Nan Amrah ta yini har dare bayan ta wuce Afrah ta sake dawo ma Farhan da wata savuwar takurawa akan se ya amince ya auri Amrah, shi kuma ko kad'an yaqi ya saurare ta da qarshe ma ya bar gidan bashi ya dawo ba sai guraren qarfe goma wanda duk a tunanin sa Afrah tayi bacci shine yazo dmn ya lalla6a ya kaita 6angaren su ba tare da ta sani ba , sae ya samu idon ta biyu sae fira suke ita da gwaggo.

tana ganin shi ta had'e girar sama da ta qasa ta wani sha toka kmr wacce tun tashin ta bata ta6a fara'a ba.

Farhan yaje ya durqusa saitin kunnen ta yace " Afrah ki daina fushi dani ba kyau nifa mijinki ne" ture shi tayi kusa da ita tace "ni ka daina matsowa kusa dani tunda ba ka son abinda nake so" yi haquri tashi muje 6angaren mu mu shirya kinji "nan yaja hannun ta tace" uhm uhm gwaggo ce ya daina ta6a ni tunda bana shiri dashi, to ai so nake ki tashi muje mu shirya kinji,,, tace"gwaggo, gwaggo, gwaggo kina jina fa... Afrah me kike so nace miki tunda naga abin naki sae ke,meyasa kin fiye liqewa ne ke kam ? To gwaggo ai shine yaqi ya amince da yanxu ma na daina maganar. Farhan yace ni gwaggo ba ma shi ba ni so nake tatashi mu koma 6angaren mu dare yayi.... ko yau a nan zanyi bacci na ba inda zanje, kallon gwaggo yayi cikin damuwa yace " gwaggo kin ji ta gashi ni yau wlh.... Sae kuma yayi shiru dmn vaya jin zai iya snr da ita abinda yake ciki, gwaggo da ta fahimta tace "ai sai ka tallabe ta kuje tunda ba a harkar aziqi da ita... Ba shiri Afrah ta tashi ta matsa nesa da Farhan tana kuka tace" gwaggo yanxu nice ba a harkar aziqi dani ai wannan baki ne kike so kimin "daga haka ta ajiye musu kuka ba na wasa ba taje can kusa da jikin gina ta zauna ta hade kai da guiwa tana ci gaba da aikin kukan ta.

Nan farhan yaje yayi ta rarrashin ta amma taqi shiru da qarshe yace" hava my Afrah pls help me and go to za aza room mana "

Dariya ce ta su6uce mata ta rufe baki tace"lah uncle har da kai kana koyon Baba buhari ko " hannun ta yaja zasu bar d'akin yana fad'in "ba dole ba ina ji ina gani mata zata qiya min" tace "to ai shi Baba buhari manufar sa daban amma se mutane suka canza masa"

Gwaggo da ke jin su murmushi kawai tayi tace " kai mutane kuma.

Suna zuwa 6angaren Farhan, inda da shigar su aza room lol😜ya fara nuna mata

abubuwa masu nauyin fad'a ga makaranta wanda tun suna tsaye suka kasa jurewa suka zauna daga haka suka bawa gado amana inda kowanen su ya shiga faranta ran d'an uwan sa musamman Farhan da yake jefawa Afrah manyan manyan saqonnin da suka rikita qwaqwalwar
ta,
sun jima suna faranta ran juna inda gab yake da jefa qwallo a raga, Afrah ta miqe zumvur ta jawo bedsheets ta rufe jikin ta tana neman kayan baccin ta,Farhan yace "Afrah lafiya me yake faruwa ne? Ni bacci nake ji uncle zan koma 6angaren gwaggo, daga haka ta shiga mayarda kayan ta, Farhan na tsaye yana kallon ta har ta gama yace" Afrah ina ce kin fahimci yanayin da nake ciki amma shine zaki tafi ,kiyi haqri dan Allah ko minti ashirin ne, da sauri take qoqarin varin d'akin sbd kukan da take ji kan tsananin tausayin da ya bata amma haka ta dake ta fita tana ji sae faman roqon ta yake kmr zai yi kuka.
Tana fita 6angaren ta samu guri ta zauna taci kuka mai isar ta sannan ta tashi sae kallon 6angaren take tana ji kmr ta koma sbd tunanin halin da ta bar shi sae dai tafi son taci gaba da yi masa hakan ko zai amince ya auri Amrah.

Farhan kuwa zama yayi ya dafe kansa yana karanto addu'o'in neman sauqi bila adadin.

Cikin dare sosai ya tashi firgigit yana qoqarin tuna wasu kalmomi a cikin mafarkin sa.

_Kar ka bar maraya a cikin damuwa ka saurari me yake son snr da kai domin baka san me ya gani a cikin mafarkin sa ba_

Sai da ya maimaita maganar sannan ya shiga nazarin ta lokaci mai tsawo.
Nan ya sami kansa da tashi ya nufi 6angaren gwaggo ba tare da ya dubi daren da ake ciki ba spare key d'in da ya riqo ya sa ya bud'e 6angaren, yayi turus cikin mamaki da fargabar ganin Afrah waje bakin qofar falo ta had'e kai da guiwa tana ta kuka
ji yake kamar mafarki yake amma haka yaje gab da ita ya zauna inda a tsorace Afrah ta d'ago,
tana ganin shine ta qanqame shi tana kuka tana fad'in "Dan Allah uncle ka amince na samu na fara binciken nan wlh kullum sae nayi mafarkin Abbana yazo yana ce min " na tashi naje gare su kafin suzo gare mu "haka yake ta fad'a kullum sae dai a yau cikin tsawa ya min maganar har sae da na firgita ,, ta qarasa maganar cikin muryar kuka mai ban tausayi ,,,,jikin sa ne yayi sanyi ya qara rungume ta tsam a qirjin sa yana shafa bayan ta cike da nazarin maganar da ta gaya masa.

*Billy giro 😊&Futha lurv 💅*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:22PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [ 10/18/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futhalurv.WordPress.com*

*```🏅53🏅```*
Ya jima yana nazari akai ,
ya sauke numfashi a hankali,sannan ya d'ago Afrah yana share mata hawaye yace"daina kukan ya isa tashi muje 6angare na in yaso gobe da safe mayi magana.
Ba musu ta tashi suka tafi sae dai kwata kwata ta kasa bacci sbd yanayin firgicin da ta shiga.
Farhan ya shiga yi mata addu'a daga nan bacci ya fara fizgar ta sae kawai ta tashi firgigit da d'an kukan ta na shagwa6a, farhan ya kunna dim light kafin yace komai ta matso gab da shi ta shige jikin sa ta bud'e buttons d'in rigar sa ta 6oye fuskar ta a ciki, shidai farhan sae kallon ta yake yana shafa bayan ta,har ya zaci ta koma bacci se kawai yaga ta fitar da fuskar ta a hankali tace"uncle bacci nake ji amma bazan iya ba ina gudun kar Abba yazo min a mafarki"insaAllah ba zai zo ba kinji,yi baccin ki kawai ,
da qyar ya samu ta koma bacci daga nan shima ya samu yayi.

Da asuba sae da farhan ya raka ta toilet sannnan ta iya yin arwala.

Zaune suke sun gama sallah tana maqale a jikin sa tana kuka marar sauti .
Farhan yace"Afrah me kika fahimta a maganar da Abba yake gaya miki? Uncle na fahimci so yake naje gare su kafin su zo gareni wata qil idan suka zo zasu cutar da ni ne "ba haka bane Afrah abinda na fahimta shine ba kya qiyamul laili domin ita qiyamul laili ba qaramin bakami bace dake hana duk wani maqiyi cin galaba akan ka da yardar ubangiji,haka ma yawaita yin zikiri wato ambaton Allah wanda na fahimci sam ba kya yinsa gashi kuwa manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yace
_"misalin wanda ya ke ambaton ubangijinsa da wanda baya ambaton ubangijin sa,kamar misalin rayayye da matacce ne. Haka kuma yace "Allah mad'aukakin sarki yana cewa"Ni ina

tare da zaton bawana dani, kuma ina tare da shi idan ya ambace ni.Idan ya ambace ni a cikin ransa zan ambace shi a cikin raina, idan ya ambace ni a cikin jama'a zan ambace shi a cikin jama'ar da tafi su alheri,in ya kusance ni taki d'aya zan kusance shi kamu guda, in ya kusance ni kamu guda zan kusance shi tsawon gaba guda, in yazo min yana tafiya zan zo masa ina gaggawa_

To kuwa kinga idan kina yin zikiri Allah yana tare da ke a duk inda kike ,zai kuma kare ki da duk sharrin maqiya.

Haka kuma ki yawaita karatun qur'ani wannan nasan kina yin sa sosai don haka kici gaba ki kuma qara da yanda kike yi.

yanzu ina ftr kin fahimci cewa ba dole sae kaje wa maqiyanka gaba da gaba ba Addu'a kad'ai ta ishe su domin ita ce takobin mumuni.

To haka Abba yake nufi ki tashi ki daina bacci ki duqufa gurin Allah kina mai neman kariyar sa.

Domin su maqiya ako yaushe cike suke da son ganin bayan ka amma idan ka riqe Allah ba abinda zasu iya maka wanda Allah bai ma ba.

Don haka daga yau kiyi qoqari ki kiyaye yin qiyamul laili da kuma zikiri ,da kuma neman kariya a gurin ubangiji,to inshaAllah idan har hakan Abba ke nufi baza ki qara ganin sa a cikin mafarkin ki ba.

Ajiyar zuciya ta sauke ta qara rungume shi cike da fahimtar abinda ya sanar da ita tace"inshaAllah uncle zan kiyaye "to Allah ya bamu ikon kiyaye wa,Amin.

Nan ya d'auke ta suka koma kan gado sae shafa ta yake a hankali kmr yana shafa qwai tana jin shafar tasan cewa ga yanayin da yake son kasancewa ciki ba wai don tayi bacci yake mata hakan ba,

haka ta lafe tana sauraren duk abinda yake mata,har yakai inda bata jin zata iya jurewa wato nipples d'in ta da yake muzarwa cikin wani salo da qwarewa yayinda take jin wani abu na ratsawa tun daga kan qwaqwalwar ta har zuwa babban yatsan ta na qafa ,daga nan ne ta qara shigewa jikin sa tana mayar masa da martani har suka lula duniyar ma'aurata sae dai iya wahala tasha domin har kuka sae da ta masa fiye da wanda tayi masa na farko sbd wannan karon buqatuwar da yake ciki bata bar ya tausaya mata ba domin har second round sae da yayi.

Lallashin ta yake tayi har ya samu ta daina kukan ya kuma samu bacci mai nauyi ya d'auke ta nan shima yabi bayan ta hakan yasa d'akin yayi tsit baka jin komai sae ajiyar zuciyoyinsu.

Sae guraren qarfe goma suka tashi ,Afrah ta tashi tana son taje toilet farhan sae kallon yanda take taka qafar ta da qyar yake sae duk yaji wani abu ba dad'i had'e da mutuwar jiki,ya tashi da hanzari ya qarasa gurin ta ya rungumo ta yana fad'in"Afrah ashe naji maki ciwo? Cikin muryar kuka tace"ai na gaya ma amma kaqi ka saurare ni,in kana min haka gaskiya gurin gwaggo zan

riqa bacci na,,, yi haquri muje na duba ki idan ba sosai bane,um um nikam bazan iya bari ka duba ni ba kawai ka bani magani nasha,,, to muje ayi wanka tukun .

A tare suka yi wanka har suna cud'anya jikin juna da qarshe ya nemi ya gasa mata jikin ta sae dai yana tsunbula ta a cikin ruwan zafi ta tuma ta d'ale kan jikin sa tana kuka akan dole ya fasa mata gashin.

Kamar mai koyon tata yaje da ita 6angaren gwaggo Afrah taje a hankali jikin gwaggo tana mata ina kwana, bata iya kar6awa ba sae farhan ta shiga yiwa tambaya wata kan wata na ganin yanda Afrah ke takawa da qyar,sosai yaji kunya har yana sosa bayan kansa yace"gwaggo wlh ba da qarfi na mata ba ,,,haba farhan kai fa likita ne ya zaka mata haka bayan kasan Afrah qarama ce kuma kasan yanayin jikin ta,kuma alamu sun nuna wannan shine na farko,shiru yayi yaqi yace bana farko bane domin yasan fad'a zai sha sosai idan taji bashi ne na farko ba amma ya mata hakan,haquri kawai yayi ta bata har kuma ya bata tausayi domin tasan Farhan mai tausayin Afrah ne sosai.
Tace"to inace ka gasa mata jikin ta ko?gwaggo kuka take bata bari, oh ni na rasa me ruwan zafi suka yi ma Afrah da ta tsani shigar su sae kace tare suke da mutuwar ta ,to nikam bazan bar ki haka ba sae kin shiga ruwan zafi, cike da son tayi kuka ta kalli gwaggo tace"gwaggo uncle ya bani magani, gwaggo kam bata saurara mata ba taja ta sae toilet .

Duk wani kuka da ihun da take da kuma yanda take ta faman kiran shi,
farhan naji amma haka ya dake nan gurin da suka barshi zaune ko motsin kirki baya yi sbd abinda yake ji game da kukan da take.

Sae da aka gama gwaggo ta bar ta ta fito tazo gun farhan ta zauna tana kallon idonsa da suka cika tap da qwallah kmr nata .
Kauda idon sa yayi ya jawo ta ya rungume Yace"to ya isa haka tunda an gama.

Bayan kwana biyu da faruwar hakan.
Cikin ikon Allah Afrah bata sake mafarkin Abbanta ba sbd kwana biyun nan tana qiyamul laili tana kuma yin zikiri sosai haka kuma takan yi karatun qur'ani ko wace sallah idan ta gama yayinda ta duqufa da roqon Allah ya kare ta da sharrin duk wani mai sharri mutum da Aljan.

Amma kuma suku suku take yin komai sbd wani tunani da tasa a ranta.

Zaune take kan bed ta had'e kai da guiwa cike da tunanin da tasa a ranta har tana fitar da en

silalin hawaye .
Farhan ya fito daga gurin wanka ya same ta a haka ya zauna kan bedside drawer tare da dafa kanta yace"my Afrah wai tunanin me kike yi a kwanakin nan? A shagwa6e ta d'ago tana kallon shi tace"uncle wani abu nake so"mene ne? Ni bana son na gaya maka kace a'a,,, fad'i kawai ina jinki.

*Billy giro😊&Futha lurv💅*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:22PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [10/18, 9:50 PM] Billy giro 😊 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```~AFRAH KO AMRAH ```*~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*NA Billy giro 😊& Bilqis Sidibe💅*

*Futhalurv.WordPress.com*

*🏅54🏅*
Wayar sa ce tayi qara koda ya duba Abban Amrah ne da kulawa yace "pls Afrah yi haquri na d'aga wayar kinji , gyad'a masa kai tayi tare da jinginawa a jikin sa, yanayin yanda yake waya cikin damuwa yasa ta d'ago tana kallon shi miqar da ita yayi tsaye suka je jikin wardrobe ya zaro riga ya bata ta saka mishi sannan ya d'auko wando dai dai ya qarasa waya ya saka wandon yace"yi haquri Afrah har na dawo sae muyi magana,
Abban Amrah ne ya kira ni Amrah ba lafiya unconsciously har anyi addmitng din su a asibiti.
Dan Allah uncle ina zuwa.... Aa Afrah...sae kuma yayi shiru tuna cewa ta had'a shi da Allah amma yaso ya fara zuwa shi kad'ai tukun .
Yace "shikenan d'auko hjb d'inki muje.

Koda suka je asibiti likitawa ne kan Amrah zasu yi su biyar suna qoqarin ganin sun ceto ranta, Farhan ya cike na shidan su wanda kafin ya shiga sae da ya bawa Afrah makullin office d'in shi yace taje ta zauna kafin su fito.

An kwashi kusan awanni kafin ake ciyo nasara sae dai hana kowa shiga akayi sbd patient d'in ta wahala sosai shiyasa aka yi mata allurar bacci.

Iya kuka Abbanta yayi domin ya firgita sosai da yanda yaga ciwon yazo mata karaf d'aya.

Su Farhan na fitowa ya tafi sauri sauri office d'in sa ya sami Afrah sae bacci take rufe qofar sa ne ya farkar da ita.
Bai zauna ba sae da ya bud'e fridge ya d'auko mata fresh milk ya tsiyaye mata a cup ya bata , bata sha ba sae da taje toilet ta wanko bakin ta, tace "uncle ina son zanga Afrah tukun" Amrah bacci take sae anjima ko za a bada damar shiga a ganta "to uncle me yake damun ta ne? ciwon zuciya ne......ciwon zuciya uncle, kallon yanda ta fitar da hawaye kai tsaye yake kmr wacce tasan abinda ya haifar da hakan yace" ko kin san me yake damun ta ne? ni ban sani ba amma dai Abban ta bai sanar maka ba? Shi kansa bai sani ba amma ba makawa ta jima tana sa wani abu a ranta tana kuma yawan tunanin koma mene har ta kai ga ya haifar mata da ciwon zuciya , to uncle ya kenan? Ba yanda zamuyi sae idan ta farka aji mene ke damun ta idan da yanda za'ayi sae a mata wannan abun domin tunanin abun yaci mata zuciya sosai wanda ci gaba da tunanin sa tamkar tana kusanto lokacin mutuwar ta ne , duk da cewa rai a hannun Allah yake amma akwai sanadi, kuka ta fara yi cike da tausayin Amrah tace "uncle kenan idan bata sami abinda take so ba zata iya mutuwa ? zai dai zama sanadi mutuwa kuwa sae Allah yace,shiru tayi inda ta dai fahimci rashin samun abinda Amrah ke so zai iya zama sanadin mutuwar ta.
Hakan yasa taci gaba da rera kukan ta kamar wacce aka ce yau yau d'in nan Amrah zata mutu, bai hana ta kukan ba domin cike yake ta tausayin Amrah da kuma mahaifin ta wato lebaran sa.

Bata ma iya shan fresh milk ba suka koma gida a cewar zasu koma anjima sae dai har suka isa gida Afrah kuka take.
Gwaggo keta rarrashin ta tana bata baki tana fad'in ta daina kukan mana kar taja ma kanta ciwon kai tace "gwaggo ki bar ni nayi kuka domin wlh ni kad'ai nasan yanda nake jin Amrah a cikin raina" duk yanda kike jinta a cikin ranki ai ba kuka zakiyi mata ba addu'a ya kamata , domin kuka baya magani,
nan tayi ta rarrshin ta har ta samu ta daina kukan
Da dare bayan sun koma sun samu Amrah ta tashi daga bacci sae dai kallo d'aya zaka yi mata kasan tana jin jiki sosai domin ko magana bata cika son yi ba sae dole take yi .
Kuma ba irin tamvayar da likitawa basu yi mata ba kan me ta sa a rai da yawa har yake neman illata ta amma ta nuna sam ba abinda ke damun ta ciwo ne kawai, likitawa basu yarda da hakan ba sbd sun san dole akwai abinda tasa a ranta yaja mata wannan ciwon amma ba su takura ta da tambaya ba sae mahaifin ta suka snr cewa ya lalla6a ta ko zata snr da shi.

Afrah ce kad'ai da Amrah a dakin,
 su gwaggo da farhan duk sun fita dama kuwa haka Afrah taso domin tana son tayi wa Amrah wasu tambayoyi.
  Kallon Amrah tayi wacce tun shigowar su tana kwance  bata ko iya wani  motsin kirki.
  Matsawa tayi kusa da ita tare da riqo hannun ta tana qara yi mata sannu kafin take cewa"Dan Allah Amrah me yake damun ki ne da kika qi sanar da kowa hatta Abba da ya tambayeki naji kince da shi ba abinda ke damun ki,bayan nasan ba gaskiya bane wanda ina fatar zaki sanar dani domin nasan idan kin 6oye ma kowa ni baza ki 6oye min ba sbd mu abokanan shawara ne wata qil idan kika snr dani zan iya shawo kan abinda ke damun ki.
   Shiru Amrah tayi tana kallon ta cike da qwalla a idon ta domin bata jin zata iya sanar da Afrah cewa tunanin farhan ne da take ba dare ba rana da kuma ywan kukan da take akan tsananin son shi dake azazzalar ta mnt by mnt.
   Afrah tace"ina jinki Amrah ki sanar da ni kinji,kauda kanta tayi tana faman danne hawayen da ke qoqarin zubo mata amma duk da haka sae da suka fito tayi saurin sa hannu ta share hawayen,ta qara jimqe hannayen su da ke riqe da juna tace"ba komai Afrah......saurin rufe mata baki Afrah tayi tace"kinsan ba ma haka dake sanin kanki ne ba ma 6oye ma junan mu komai don haka ki cire ba komai a cikin bakin ki,ki sanar dani komai,hawaye ne suka sake cika ma Amrah ido har suna qoqarin zubowa tace aranta
_"kiyi haquri Afrah duk da na d'auke ki tamkar er uwa ta jini  bana jin zan iya sanr da ke abinda ke damuna,domin abu ne dani kad'ai nake son barwa kaina har na koma ga mahlicci na"_
    Afrah dake kallon ta take taji ita ma nata idanun sun ciko tace a ranta
  _"lokaci mai tsawo na fahimci abinda ke damun ki amma na dake akan ban sani ba,sbd son da nake yiwa uncle so ne dani kad'ai nake son zama mallakin sa yayinda nake jin ni kad'ai na dace dashi,but jin da nake miki tamkar er uwa shi yasa na fara jin bazan iya barin ki cikin damuwa ba wanda don haka ne yasa nace ki aure shi ba wai don binciken da nayi niyya ba sae gashi kmr kar wani  abu ya shiga tsakani na da uncle naji na qara son sa  wanda duk matsa ma san da nake kan ya amince ya aure ki ina jurewa ne kawai but still inshaAllah sae naga cewa kin sami abinda kike so  dmn jin da nake  miki tmkr  er uwa bazai bar na iya ganin mutuwar ki ba kan abinda nasan zan iya taimaka miki ki mallake shi_.

 Daga haka suka rungume juna sae kuka suke ba wai don d'aya taji abinda d'aya ta fad'a ba.

*Billy giro😊&Futha lurv💅*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:22PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [18/10/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
       *```~AFRAH  KO AMRAH ```*~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

 *NA  Billy giro 😊& Bilqis Sidibe💅*

*🏅55🏅*
Haka suka ci kukan su kmr wad'an da akayi ma mutuwa sai da suka gaji don kan su suka daina.

Sae guraren tara da rabi suka bar asibitin.
Farhan da gwaggo duk sun fahimci yanda Afrah jikin ta yayi sanyi ko magana bata cika son yi ba wanda duk a tunanin su rashin lafiyar Amrah ne ya sa ta hakan , eh haka ne amma ta had'a da tunanin yanda zata tunkari Farhan da zancen ya amince ya auri Amrah ba tare da ta sanar da shi cewa Amrah na son shi ba kan wani dalili nata .

Bayan sun isa gida sukayi wanka sannan sukayi shirin bacci, Farhan ya kalli Afrah wacce har yanxu akwai damuwa a tare da ita cikin muryar lallashi yace "Afrah nasan dole ki damu sosai akan ciwon Amrah sbd na fahimci kina jin ta ne kmr sistar ki ta jini wanda ba komai ya kawo hakan ba face yanda kuka taso tare tun kuna yara, kuma kukayi matuqar shaquwar da kesa idan d'ayan ku ya shiga wani hali dole d'ayan ya shiga,amma ina son kiyi haquri ki rage wannan damuwar ki mata addu'ar samun sauqi domin ita ce mafita .

Marairai ce fuska tayi cike da qwallah tap a idon ta tana kallon shi tace "uncle pls zan roqe ka wata alfarma wacce bana son sautin a'a ya fito a bakin ka na fiso kawai kace min ka amince pls and pls uncle"
Ina jinki Afrah gaya min indai har bai fi qarfina ba InshaAllah zan miki amma kuma ya kasance ba sa6on Allah bane domin kinsan babu d'a a ga abokin halitta a gurin sa6awa mahalicci. Uncle ko kad'an ba sa6o a cikin abinda nake son kamin, to fad'i ina jinki, inda inda ta shiga yi ganin yanda ya tsure ta da kallo ta samu da qyar ta fara da cewa "dama ba komai bane uncle maganar dai da ka sani ce ta xancen auren Amrah da nake son kayi" qyar yake kallon ta har ta gama zancen, yayi d'an gutun tsaki had'e da girgiza kansa yace "akan wannan maganar ne kika sa na 6ata lokacina na saurare ki"
Hawaye ne suka silalo a hankali kan kumatun ta, da kulawa Farhan ya riqo kumatun ta yana kallon cikin idon ta yace "Afrah kuka kike yi bayan kinsan baki da gaskiya a cikin zancen nan ina ce dalilin da yasa kike son na aure ta yanxu babu shi an wuce gun, ryt? gyad'a masa kai tayi sbd yanda ya tsure ta da ido yana son yaji amsa tace "amma uncle.....rufe mata baki yayi ya kwantar da ita tare da ja musu blanket yana fad'in "har yanzu baki san lokacin da zaki fara rigimar ki ba muyi bacci haka ya isa,
duk yana maganar ne rungume da ita yana share mata hawaye yace " idan kuma so kike zuciya ta ta fashe sae kiyi ta kukan.
Akan dole tayi shiru ya kashe dim light suka shiga bacci .

Washe gari bata yi masa zancen ba har suka je asibiti koda suka je ciwon Amrah ya

tashi sosai da qyar aka shawo kai,
ba Abban ta kad'ai ba har likitawa sun fara sarewa da yanda ciwon keyi mata wanda har suna tunanin idan ya sake motsawa sae dai wata ba ita ba amma basu sanar da Abban ta haka ba domin so suke suyi iya qoqarin su na ganin hakan bai faru ba.

Kuka Afrah keyi sosai duk tabi ta katse har bata iya tsayuwa da qafafun ta sbd duk wanda ya kalli Amrah baya tunanin zata qara scnd a duniya.
Amma cikin ikon Allah har ta iya kama hannun Afrah ta zaunar ta samu da qyar ta bud'e baki tace "Afrah ki daina min kuka addu'a nake so kimin Allah ya yaye min abinda yasa nake fama da wannan ciwon idan kuma na mutu shikenan Alhmdlh domin ina ganin kmr za tafi zama hutu a gare ni .... Hava Amrah dan Allah ki daina zancen mutuwa zaki tashi InshaAllah har ma ki sami abinda kike so.......da kmr wuya Afrah shiyasa nafi son na mutu kan na rayu domin kamar zanfi wahala wahalar da ban san lokacin da zata yaye min ba.
Kuka ne yazo ma Afrah sosai ta tashi ta fad'a jikin Farhan dake tsaye akan su tace "uncle kaga Amrah ko ce ta daina gaya min haka wlh bana son tana fad'in zata mutu, ta qarashe mgnr cikin kuka sosai , Farhan ya kalli Amrah wacce kejin kmr zuciyarta ta fito ta had'e da ta farhan su zamo guri d'aya ko xata ji sassaucin abinda take ji,
yace" Amrah ki daina zancen mutuwa kinji ai ciwo ba shine mutuwa ba domin sau nawa zaki ji an kwanta da mutum lafiyar sa qalau amma a wayi gari ba tare da shi ba amma sae a wayi gari da marar lafiyan da yayi nisa nisan da ba a ta6a tunanin xa a wayi gari da shi sbd lokacin sa bai yi ba domin ita rayuwa sae idan lokacin ka yayi ne ake zare ta.
Hawaye ne suka cika mata ido har ma bata ganin shi sosai tace "na gode uncle zan kiyaye"
Ya kalli Afrah wacce har yanxu ke kuka tace "uncle dan Allah ina so muje gida" meyasa Afrah ? Baza mu jima ba zamu dawo.
Ba musu sukayi sallama da Abban Amrah suka kama hanya.
Suna zuwa gida suka sami gwaggo har ta rufe 6angaren ta zata fito tace "A'a lafiya kuka dawo gashi sai sauri nake har na kammala abinda nake zan ja tawa motor na tafi" Afrah ce ta nemi mu dawo ban san me yasa ba, to ga makullin sae ku shiga domin ya kamata naje na qara ganin ya jikin nata yayi,, Afrah tace "gwaggo dan Allah magana nake son zamuyi mu duka.

Bayan sun shiga sun zauna Farhan da gwaggo sae sauraren Afrah suke suji maganar da zata sanar da su wanda kafin ta fara sae addu'ar samun nasara take sannan tace "uncle, gwaggo , zan so kuyi haquri da maganar da zanyi zan kuma so kuyi haquri ku amince da buqata ta kuma kuyi haquri da yawan naci na domin magana ce wacce kuka santa wato mgnr ita ce,
" ina son uncle yayi haquri ya janye ra'ayin sa na zama dani kad'ai a matsayin matar sa zan so ya taimaka min ya had'amu mu biyu wato nida Amrah wanda ina son haka ne a bisa wani dalili ba don wancan dallin farko ba amma don Allah kar a tambaye ni wane irin dalili ne .
Farhan yace "Afrah kin fiye naci , kin fiye naci sosai wanda na kasa fahimta shin so na

ne ba kya yi da har ba kya jin komai idan kina amvatar na auri wata keda kanki,kuma haka kawai zan auri Amrah bayan naji ta sanar da ke tana da wanda take so,kuma me ya kawo zancen nan a cikin wannan yanayi da Amrah ke fama da rashin lafiya ? Kayi haquri uncle rashin lafiyar ce tasa na damu sosai akan ka aure ta....sbd me? Shiru tayi tana tunanin a yanda ta fahimci Amrah sam bata son a san tana son uncle tunda har ta iya ciwo kmr ta mutu amma taqi fad'a, hakan yasa ita ma zata ajiye mata sirrin baza ta sanar da kowa ba.....dake nake ki gaya min meyasa? Sbd ina ganin kmr kad'ai ci ne ke sata yawan tunani
har ta kai ga ciwon zuciya,
kad'ai ci? Eh uncle kasan cewa Amrah ita kad'ai ce gun Abban ta Kuma ba ya tare da mahaifiyar ta sannan kuma bai yi wani auren ba gashi tun safe idan ya fita aiki sae dare yake komawa,
shiyasa nake son ka aure ta ta dawo cikin mu da zama ko zata ji sauqin kad'ai cin da take ciki,babu wata hujja a cikin zancen ki... Niko nake da hujja uncle sbd wanda tace tana so bai ma san tana yi ba bare a tuntun6e shi da zancen aure Kuma idan yaji ita ke son shi ba zai riqe ta da wata daraja ba amma nasan kai zaka iya tausaya mata ko don Abban ta, don girman Allah uncle kar ka ce a'a ina son ayi ayi auren nan ne tun kafin ciwon ya illata ta don Allah uncle kaji.
Nan ta shiga kuka tana roqon sa tana Kuma had'a shi da sunayen ubangiji kala kala sae duk ya rasa ma me zai ce mata domin ji yayi kmr ta d'aure shi tamau da sunayen ubangiin da ta had'a shi, sae dai qwarai yayi baqin ciki na ganin kwata kwata Afrah bata kishin sa.
Ke kuwa Afrah..... A'a gwaggo barta kawai na amince zanyi auren! kuma a cikin kwanakin nan wata qil Amrahn ma zata fi sona domin na fahimci sam ba sona a tare da Afrah bare har ta iya kishina!
Nan ya fita cikin 6acin rai.
Haka ita ma gwaggo ta tashi tare da jefo mata keys tace idan kin tashi ki rufe min 6angare na, ya zamo ita kad'ai suka bari sae kuka take mai cin rai ta rasa inda zata sa kanta taji sanyi tasan har ga Allah tana matuqar son uncle kuma tana kishin sa, haka kuma tana matuqar son Amrah bata iya barin ta cikin damuwa ko don kasancewar su aminan juna tun suna yara.
Sae da taci kukan ta har ta gode Allah sannan ta tashi ta rufe 6angaren gwaggo ta fita ta nemi napep taje asibiti.

Amenity ward ta nufa ta shiga room number 2 wato d'akin da Amrah take
Tana shiga ta sami gwaggo sai dai ko zama bata yi ba gwaggo ta bar d'akin kallon gwaggo take har ta fita sannan ta d'an qirqiro murmushin dole ta zauna tana mai kallon Amrah ta d'an qara sake fuskar ta kafin take cewa "Amrah InshaAllah a cikin kwanakin nan za'ayi auren ki da uncle,..... Zumbur Amrah takai zaune wacce tunda aka kawo ta asibiti bata ta6a tashi ba sae yanxu, bata san lokacin da tace" da gaske? Da gaske nake Amrah,,, amma meyasa, bayan yanxu ba wani zancen binciken da zakiyi? Haka kawai nake son mu auri miji d'aya nida ke sbd amintakar mu ta qara qulluwa.
Wani irin farin ciki Amrah taji kamar wacce akayi wa bushara da gidan Aljannah har ma ta nemi ciwon da ke jikin ta ta rasa,sae kuma nan take taji farin cikin ya ragu har tana magana

a  ranta  cewa
_"meyasa zanyi farin ciki don xan auri mijin aminiya ta wacce a duk duniya bani da kamar ta“_

Kamar Afrah taji me take fad'a tace " kar ki ta6a tunanin don kin auri uncle kinyi abin kunya ga auren mijin aminiyarki, ko d'aya babu  kunya a ciki domin ni na  buqaci hakan ba snatching kika min ba,don haka don Allah daga  yau ki cire a ranki cewa kinyi rashin kyautatawa kuma ki daina tunanin zamu iya samun sa6ani don kin auri uncle kisa  a ranki cewa wata shaquwa ce zata qara qulluwa a tsakanin mu.
Komai Amrah ta kasa cewa sae hawaye da suka silalo a hankali kan kumatun ta.
Nan suka ji sallamar Farhan wanda sau d'aya ya had'a ido da Afrah ya kauda kai, hawayen da ke qoqarin zubo mata ne yasa tayi saurin tashi ta bar musu d'akin.
Farhan  ya  nemi  guri ya zauna wanda sae da yayi gyaran murya kafin yake cewa "nasan Afrah ta sanar da ke abinda ake ciki,sae dai nasan zaki  ji  zancen wani iri sbd tun a Oman naji kina sanar da ita baza ki amince ba amma ina so kiyi haquri wannan karon ki amince sbd na samu ta daina damuna akan zancen auren nan,duk da cewa nasan kina da wanda kike so, haka kuma baza ki so ki auri wanda ba kya so ba,idanun ta ne suka ciko da qwallah yaci gaba da cewa,sbd shi so wani abu ne wanda in baka yiwa mutum shi baza ka ji dad'in rayuwar aure da shi ba shiyasa nake son wannan auren ya zamo na wata biyu ne kacal tsakina na dake ba tare  da  Afrah ta san da hakan ba, sannan ba wani abunda zai shiga tsakanin mu na auratayya sbd na yarda da yin auren ne a  bisa sanin halin Afrah kan idan taso abu hankalin ta baya ta6a kwanciya har sae an mata,haka kema nasan baza kiso wani abu ya shiga tsakanin mu ba. Sosai nake guje mata wannan auren ba don komai ba sae don sanin irin halin kishin ku na mata wanda komai amintakar ku da mutum idan kuka had'a miji d'aya sae kun sami sa6ani har ma kuzo Kuna nuna qiyayya wa junan ku,gashi sam bana fatar amintakar ku da Afrah ta koma qiyayya, amma nasan kona snr da ita hakan baza ta gane ba sae idan anyi auren ko zata fahimta.
Then kar ki samu damuwa domin auren za a yi shi ne a asirce ba wanda zai sani sae waliyan mu kad'ai wanda koda mun rabu ba mai tunanin cewa ke bazawara ce.
Amma don Allah Amrah idan har da takurawa a cikin al'amarin nan ki sanar dani.
Hawayen da suka cika mata ido ne suka gangaro  kan  kumatun ta tace  a  ranta
_" ba abinda zance sae godiya ga ubangiji na da yasa zanyi rayuwa da kai har ta tsawon wata biyu a  matsayin  miji da mata,koda kuwa ba abinda zai shiga tsakani na da kai bani da wani sauran baqin ciki  a duniya, fatana  d'aya  Allah yasa har na gama wata na biyu ban kawo sa6ani a tsakanin ku ba_.

*Billy giro 😊&Futha lurv 💅*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:22PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [20/10/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```~AFRAH  KO AMRAH ```*~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*NA  Billy giro 😊& Bilqis Sidibe💅*

*Futhalurv.WordPress.com*

*🏅57🏅*
Tana zuwa d'aki ta fad'a ruf da ciki tana kuka tana kuma mamakin halin d'a namiji, ita fa ta nemi ayi auren don taimakon aminyarta har yana zillewa baya so amma shine ana yin auren ya wani zaqe har yana nuna wani abu ya shiga tsakanin su a gaban ta "lallai ma uncle " shine abinda ta fad'a yayinda take share hawayenta wasu na sake fitowa .

Shigowa yayi d'akin tayi saurin share hawayen ba tare da ya lura ba,
yazo gab da ita tayi saurin matsawa sbd qamshin turaren da taji a jikin Amrah, shi taji yanayi,
nan take taji ya qara bata haushi.

Kwanciya yayi kan gadon da take zaune yace "waih Alhmdlh ashe dai mata biyu ni'ima ne ban sani ba sae a daren jiya"ya jawota jikin sa yana wasa da tsorayen kalbar da ke saman kanta yana ci gaba da cewa," sae yanxu naga ashe ba qaramin taimaka min kika yi ba da kika sani nayi auren nan,kinga duk byn kwana biyu se mutum ya riqa canji idan yau nasha kankana gobe sai naci Apple domin kinsan shi yanayin rayuwa komai idan ana yin canji yafi,ryt haka ne ? Wani irin abu take ji kmr ta cije la66ansa dake maganar sae dai bata nuna masa komai ba se ma murmurshi ta qirqiro tace "ai shine nake son ka fahmta uncle kaqi ka gane sae yanxu wanda naji da d'in hakan sosai daka fara fahimta" ransa ne ya d'an 6aci sbd ya xaci taji haushin maganar da yayi, amma yaga akasin haka sae dai zai ci gaba da yi mata irin hakan dole yau da gobe ta fara kishin sa har taji haushin auren da tasa yayi.

Haka ya raya a ransa.

Sannan shima yayi murmushi yana miqa yace "waih kina da maganin ciwon jiki? da kulawa ta kalle shi ta fahimci gayya ce tace "eyyah uncle sannu bari na maka tausa domin kmr maganin zai yi wuya"

A hankali ta yunqura zata fara masa tausa sae qoqarin danne xuciyar ta take, yaje gun wata amma ita ce da tausa ,
ya dakatar da ita da cewa"barshi kawai zan nemi magani domin tausa baza ta min magani ba"yana gama fad'ar haka ya fita cike da tunanin abubuwan da zai riqa yiwa Afrah wad'an da zasu sanya ta kishin sa har ta nemi rabuwar auren da kanta kafin wata biyun da ya d'iba suyi sbd shi ko kad'an baya ra'ayin mata biyu.

Yana fita Afrah ta rufe qofar da key ta hau wani sabon kuka sae kace mutuwa aka mata.

** ** **

Leesa ce zaune da mom Farida suna cin abinci kan dining leesa ta ajiye spoon ta d'auki lemu ta kur6a tayi sassanyar ajiyar zuciya kafin take cewa " mom Farida lokaci ya kusa da zan tura en fashi a gidan Farhan su kwashe duk wata dukiyar dake cikin gidan tun daga kan 6angaren gwaggo har 6angaren sa, takardun kadarorin sa,keys d'in motors, gold, diamond, ke duk dai wani abu da kika san dukiya ne, indai akwai shi a gidan baza'a bar

masa ba,har ma phone d'in hannun sa bana son su barshi da ita domin ita ma kud'i ce After that sea kuma nasa a kore shi daga gurin aikin shi......ke kuwa tayaya zaki iya sa a kori Farhan a gurin aikin sa?Abu mai sauqi wai cire wando aka, zan sa ayi kisan kai ne a cikin office d'in sa na kuma san yanda zanyi a laqa masa wannan kisan, ba kuma kowa zansa a kashe ba sae na nemo mafi kusanci dashi a office wanda ko yaushe yana cikin yi masa hidima,na masa zafi biyu kenan domin wlh tuggun da zan qulla a wannan kisan ba mai iya fitar da Farhan sae ni dana qulla, kinga kuwa har abada ba zai ta6a fita ba.

kuyi haquri da wannan.

*Billy giro 😊&Futha lurv 💅*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:22PM, 11/30/2016] Billy Geeero: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```~AFRAH KO AMRAH ```*~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*NA Billy giro 😊& Bilqis Sidibe💅*

*Futhalurv.WordPress.com*

*🏅58🏅*
Bayan kwana d'aya da faruwar hakan Afrah ce a kitchen tana girka abincin yamma duk tabi ta yanyanke hannun ta sbd har yanxu bata wani gwane sosai a girki ba son jiki tasa a koyon abincin sbd a Oman maman Amir na koyar dasu duk suka je 6angaren ta. sae dai sauqin ta d'aya abincin na dad'i amma sae ta wahala sosai kafin take samu ta kammala.
Kmr tayi kuka taga ta kammala abincin sae ga Farhan ya shigo kitchen d'in yace "ina ce ke kad'ai kika girka abincin bada mu ba? Meyasa uncle? to me amarya zai zauna ne basu je yawon shaqatawa ba ai sae zaman gidan ya fara isar ta,gashi ni kuwa bana son aminiyar taki ta fara jin haka har dai yanda na fahimci kina matuqar sonta shiyasa nake son faranta mata sbd kema kiyi farin ciki,ryt?ya fad'i haka ne yayinda ya rungumota ta baya ya riqo hannuwan ta yana wasa dasu ta samu da qyar ta danne kukan da take ji na takaici tace "yanxu uncle har abinci kunci a can? Qwarai kuwa duk wani abin marmari da kika sani sae da muka ci shiyasa cikin mu yayi tap.....kash at all na manta fa mu d'an riqo miki wani abu but kar ki damu zan bawa mai gadi ya sayo miki, bai tsaya jin me zata ce ba ya fita sae dariya yake a ransa sbd ba wani gun suka je ba face asibiti domin qara duba lafiyar Amrah idan zuciyarta tayi sauqi ba sae anyi aiki ba sbd sunyi tunanin yi mata aiki kafin ciwon ya sake tasowa sae suka ga ta fara jin sauqi shine suka sallame ta acewar bayan kwana biyu ta dawo.

To shine fa suna dawowa suka je 6angaren gwaggo ya samu tana yanka kayan marmari yayi zaune yasha son ransa ya bar Amrah tana taya gwaggo qarasa aikin sae dai sae sauri take ta samu tazo ta taya Afrah aiki sbd tasan yanda Afrah ke wahala gurin aikin abinci.

Tana shigowa ta samu Afrah zata fita da basket d'in abinci Amrah tace "wai har kin gama abincin ne ina ta sauri nazo na taya ki" har na gama kuma har zan kyautar wa masu gadi , meyasa? kuda kuka sha 'ya' yan marmari me kuma zakuyi da abinci? A sanyaye Amrah tace " Afrah kayan marmari dake narkewa kai tsaye"

Cikin tsiwa taso yi mata magana sae kuma ta fasa da ta tuna xancen ta na asibiti kan baza su sami sa6ani ba.

Ta danne 6acin ranta tace "gashi idan kina buqata sae ki d'iba, sauran se ki kaiwa masu gadi, da kulawa Amrah tace" ke baza kici bane " d'an guntun murmushi tayi mai ciwo ta wahala a girki amma baqin ciki ba zai iya bari taci ba tace" uhm a'a ni freshmilk zan sha "tana gama fad'ar haka ta haura sama wanda har taso ta tamvaye ta uncle fa sae taga ita da mijinta baza ta so ta mata shisshigi ba ,domin shisshigi nasa a fara jin haushinka har azo a sami sa6ani ita kuwa duk wani abu da tasan zai iya kawo sa6ani a tsakanin su guje masa take.

Afrah kuwa kan ta qarasa d'aki kuka ya fara zo mata tana shiga taji sallamar Farhan ya shigo tayi saurin zuwa gun wardrobe ta bud'e tana qoqarin had'iye kukan ta sbd ko kad'an bata son ya fahimci tana kishi domin kunya zata ji amatsayin ta na wacce ta tursasa ayi auren.

Bata iya d'agowa jikin wardrobe ba har ya qaraso gurinta, ya rungomo ta a hankali ta baya yace "kuka kike ko? uncle hannu na ne ya yanke , ya riqa hannun yana dubawa yaga tabbas ta yanke d'in amma ysn ba kukan yanka kawai take ba, yasan ko bata ji ciwon fitar su ba zata ji haushi kan wahalar girkin da tayi ba a ci ba, sbd yasan yana d'aya daga cikin abinda tafi tsana, Afrah kuwa ita ba abinda ma yafi qona mata rai irin yawon shaqatawar da yace mata sun tafi .

Yace "sannu amma ba cutting board ne da ba kya using dashi gurin cutting d'in abubuwa? to uncle ai da shi nake aiki kawai dai dana zo yanka albasa ne na rufe ido na sbd yaji shine na yanka hannu na.,

Sannu ya qara yi mata sannan yaja hannun ta suka zauna kan bedside sae hura mata iskan bakin shi yake kan gurin da ta yanke, taji dad'in hakan har tana qoqarin qwanciya kan jikin sa sae Kuma ta fasa sbd duk ta matsa kusa dashi sae taji qamshin turaren Amrah wanda ba komai kesa yana qamshin ba sae don yanayin turaren da Amrah ke sawa wanda duk yanda kaje kusa da ita ko kad'an ne sae ka kwashi qamshin kuma ba wai sae kunyi very close kake kwasar qamshin ba.

Yace "tashi ki d'obo mana abinci muci" turo baki tayi tace "wane abincin kaida kace baka ci har na kyautar wa masu gadi " amma ke kinci kafin ki kyautar? Aa ni banci ba,Amrah kawai nace ta d'iba, meyasa bayan daji yunwa kike ji gashi d'an zaman nan da nayi har inajin yanda cikin ki ke qugi.

shiru tayi dmn qara mata takaici kawai yake yace" yi haquri laifi na ne, yanxu kisha

freshmilk kafin na fita na siyo miki wani abinda zaki ci kinji ,gyad'a masa kai tayi sbd bata jin zata iya d'ora wani girkin, gashi su ke kaima gwaggo abinci bare ta nemo gurin ta, na marecen nan ma ba ayi da ita ba sbd tace kar a girka da ita dmn kona ranan ta bata cinye ba.

Shi ya tsiyaya mata freshmilk da kansa ya bata tasha sannan ya wuce zuwa masallaci jin anata kirayen kirayen sallar magrib.

** ** **

Yau kusan sati biyu da yin auren, sosai Amrah ke kiyaye duk wani abu da tasan zai iya kawo sa6ani a tsakanin su. kuma yanxu kullum ita ke aikin gidan da dutyn ta, da ba nata ba, sbd ita ta buqaci hakan ganin yanda Afrah ke wahala gun abinci gashi ita nan take da ta d'ora abinci bata wahala kuma ba jimawa ta kammala shine duk rnr girkin Afrah take taya ta, Afrah da son jiki sae ta sake mata aikin gabad'aya iyakar ta taje ta mata zaune a kitchen suna fira har ta kammala wanda in sun gama abincin, sake zama suke a falo suna ci gaba da fira amma duk yanda firar tayi ma Afrah dad'i da Farhan ya shigo gidan zata tashi ta koma d'akin ta ne sbd cikin azanci yake sake mata maganar da kesa kishin ta ya motsa sosai har taji kamar ta had'iye zuciya ta mutu, wani lokacin ma har hawaye ke qoqarin zubo mata sae tayi saurin danne su, tana faman wayencewa kmr ba komai .

Farhan kuwa tashin da takeyi ganin yake kmr tana yin haka ne don ta qulla wata shaquwa tsakanin sa da Amrah, domin shi har yanxu bai fara ganin alamun Afrah na kishin sa ba, duk da cewa yanxu ko kad'an bata bashi damar ya kar6i haqqin sa a gurinta , ita kuwa har ga Allah ko taso bashi da ta tuna cewa fa yasan wata bayan ita kuma still yana ci gba da mu'amalar aure da ita, sae taji baza ta iya ba, akan dole yake haqura ya barta.

A cikin sati na uku ne Afrah ta fara jin jikin ta ba d'adi sae wani nauyi yake mata da ke sa taji bata iya aikin komai domin ko wanka da ba dole bane da sae dai tayi kwanciyar ta.

Yau koda ta tashi da safe taji abin sae qaruwa yake yafi na kullum, da qyar ta samu tayi wanka ta je d'akin Farhan ta same shi kwance kan bed ya rufe jikin sa da blanket. A iya bakin qofar d'akin ta tsaya , sai da ta mishi ina kwana sannan tace "uncle so nake naje asibiti a duba ni bana jin dad'i" hm Afrah kenan gani kuma sae kinje asibiti, zo naji jikin naki may be ma malaria ce da ta addabi mutane, um um nidai nafi so naje asibiti, kin fara rigimar ki kenan gashi ni yau jikina ciwo yake min bana son damuwa,takaici maganar shi ta bata sbd duk girkin Amrah haka yake ce mata sae dai shi a gurin shi da gaske jikin nasa ciwo yake masa sbd gajiyar aikin da yayi jiya a office, yace "zo kinji na duba ki, ki daina zancen zuwa asibiti, nifa uncle nafi so naje asibiti sbd ni kad'ai nasan yanda nake ji, kin fara ko, ni kuwa gsky yanda jikina kemin ciwo bazan iya driving yanxu ba but zo a nan bedside drawer xaki ga malaria tablet kisha qwara d'aya kinga zuwa anjima dai dai jikina ya sake min sae muje,

jin tayi ya soma kawo ta iya wuya da ciwon jikin nan da yake amvata mata tace"ai bance maka malaria ke damuna ba kuma ni ixini nake so kaban tunda yanxu na iya driving sae naja kaina, rufe idanun sa yayi a hankali sbd kansa dake sara masa sosai haka kuma surutun Afrah ya fara isar shi yace "wai ma na tambaye ki da izinin wa kika shigo d'akin nan?
uncle ka manta sae da na maka sallama ka amsa min ka kuma bani ixini kafin nake shigowa, ba wannan nake nufi ba, sanin kanki ne u are not on duty , kuma kinsan yanda tsarin komai yake domin na sanar da ku don haka koma gun Amrah ki nemi izinin ta idan har ta baki damar zowa kiyi magana dani wannan ba laifi bane, bcs in yanxu ta shigo ta ganki baza taji dad'i ba , ba izini kin shigo mata d'akin maigida kuma da sassafe haka,komai kasa ce masa tayi domin baqin cikin da take ji ma baza ta iya magana ba ta yaya ita da mijinta ace sae ta nemi izinin wacce ta la6a har ma yana kiran kansa a maigidanta.
Tsawa ya daka mata ta fita cikin kuka, tana zuwa d'aki ta d'auki mayafi da makulli ta fita sae kuka take tana jan mota har hawaye nasa ta ganin hanya bishi bishi Allah ne ya nufa zata kai asibiti lafiya .

Ba yabo ba fallasa ta dawo gidan taci karo da Farhan yana saukowa kan staircase sae faman dafe kansa yake dake masa masifar ciwo.
Tsayawa tayi cike da fargaba sbd wani kallo da taga yana yi mata, qarasowa yayi yazo gab da ita, gabanta sae dukan uku uku yake tana tunanin matakin da zai d'auka,
a natse cikin yanayin muryar da rai ya 6aci yace "Afrah yanxu fita kikayi without my permission shin ko kinsan tun fitar ki har dawowar ki mala'ikun Allah na kan tsine miki, kuma tabbas kin sani amma kika take sani sbd rashin ji irin naki,kunnen ta ya kama riqo ba mai zafi ba yace" ki saurareni da kyau kiji daga yau kinyi na farko kinyi na qarshe idan kuma kika sake zan d'auki matakin da baki ta6a tsammani ba, ture hannu sa tayi cike da kukan shagwa6a tace "to shine sae ka wani riqe min kunne" yace "wai meyasa yanxu duk kin rainani ko ce miki akayi duk mutuncin ki da mutum da girman sa idan ya zamo mijinki kika san sirrin sa sai ki raina shi, nan ya shiga yi mata fad'a sosai domin ko kad'an ya tsani raini,ita kuwa ko kad'an ma bata ga wani laifi da tayi ba kan ture masa hannu, sae duk taji ranta ya qara 6aci, tayi saurin ra6ewa ta gefen sa zata bar gurin domin bata son 6acin rai yasa ta masa wani abun da zai sa ya qara mata fad'a.
Kiran sunan ta ya shiga yi ita kuma sai sauri take zata hau staircase wanda garin saurin ne ta zubar da takardun asibitinta dai dai Amrah ta sauko ta gani tayi saurin d'auka ta kira sunan ta domin ta bata, wani gigitaccen mari taji ya sauka akan kuncen ta wanda ya fitar mata da hawaye kai tsaye, Afrah wacce ita ce tayi marin tace "meye ruwanki dan ya kirani naqi na amsa mai! uncle d'inki ne ko nawa!daga yau kinyi na farko kinyi na qarshe kar ki sake ganin muna abu nida uncle kisa bakin ki, ki bari har idan an kasa dake!
Daga nan ta fashe da wani irin kuka ta tafi d'aki tana fad'in " wlh bazan sanar da kai wannan cikin ba zubar da shi zanyi tunda ko na bar shi baqin ciki ba zai bar shi.
Nan ta shiga yamutse d'akin ta ko'ina tana neman abinda zata sha kai tsaye cikin ya xube.

*Billy giro 😊&Futha lurv 💅*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:22PM, 11/30/2016] Billy Geeero: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futhalurv.WordPress.com*

*```🏅59🏅```*
Sosai Farhan ya shiga bawa Amrah haquri sannan ya haura sama zuwa d'akin Afrah.
Ya samu duk ta yakuce wata er kit da yake ajiyewa nan d'akinta ta magunguna, sae duba magungnan take tana karanta qa'idojin su ko zata sami wanda keda qarfin da mai ciki bata shan shi.
Hannun ta ya riqo ta fizge hannun tace"ni ka rabu dani"
qarfi yasa ya jawota ya manna ta a jikin sa, sae kuka take sosai tana son qwace kanta, ganin ta kasa yasa tayi tayi mai kuka kan jikin sa tana dukan qirjin sa.
Hannayenta ya kama ya riqe tana ta fizgar jikinta kmr wacce tayi qaramar hauka, ya qara matseta gam a qrnsa yace"Afrah ki daina jijjiga mu haka kaina ciwo yake sosai ki natsu ko kuma wlh na hukunta ki"wani marayen kuka ta fashe ta sulale qasà kàn guiwoyinta, ta kama qafafun sa ta rungume kmr wacce ke shirin roqon sa gafara sae kuka take tana ambatar iyayenta da suka rasu, a sanyaye farhan ya durqusa bakinsa na rawa ya kama kumatun ta yace"me na miki haka da kike ambatar su Abba da suka jima da rasuwa?, ni ka rabu dani baka sona ai dole na kira su,kuma duk abinda kake min baka gani ne Allah ma yasa na bisu na huta da takaicin da kake d'ura min kullum,wani abu yake ji marar misaltuwa wanda yafi kuka ciwo sae dai kuma kai tsaye yayi d'an guntun murmushi yace"au wai dama duk abinda

nake miki yana 6ata miki rai kenan,yaushe kika fara kishi na ne ban sani ba Afrah?.....ni Allah ya tsare ni nayi kishin wanda baya sona ,murmushi kawai yayi ya bar d'akin yana tuna marinda Afrah tayiwa Amrah wanda ko kad'an bai ji dad'i ba domin shi baya da nufin had'a su fad'a.

Afrah kuwa yana fita ta tafi 6amgaren gwaggo cikin kuka, gwaggo tace"oyo oyo zo naji wa ya ta6a min ke "sae da ta fad'a kan jikinta sannan tace"ba uncle bane tunda akayi auren nan kullm sae yayi ta 6ata min rai har ya guma min wani a yau wai daga naje d'akin shi ina so ya bar ni naje asibiti bana jin dad'i shine yace na bari ya duba ni nace masa nafi so naje,da qarshe wai ma na fitar masa d'aki tunda bani keda duty ba sae naje na nemi izinin Amrah sannan ko zan dawo muci gaba da magana"eh mana Afrah ai haka abin yake...kmr ya gwaggo uncle d'inane fa la6ata kawai nayi sae ace sae na nemi izinin ta,, da kika la6ata ai ta zama mata, kun zama d'aya keda ita a gurin uncle d'in naki don haka dole ne ya bata haqqinta na matar sa ya kuma yi adalci a tsakanin ku.....wai ni Allahna gwaggo wai baza ki fahimce ni bane shike nan don na taimaka na la6ata aka ce bazan je gun uncle d'ina ba sae da izinin ta don ita ce mai duty,wai kuma shine ma har da raba kwana daidai daidai nida ita, Allah ya kawo mu yau nida Afrah,to da duk a tunaninki don kin la6a ta kinfi ta kaso agun miji ne.... Eh mana, dariya gwaggo tayi tace "Allah ya shirye ki Afrah"uhm uhm wato ma gwaggo haka zaki ce sae kace wani abu nake yi mara kyau, bayan akan daidai nake ,tashi tayi tana fad'in "inda ma nasani banzo gurin ki ba tunda ba kya d'ebe min takaici sae ma qara min da kike.
Tana kawai nan taga farhan tsaye a bakin qofa yana kallon ta, tayi saurin kauda fuskar ta gefe cikin fushi,yayi dariya yace"wai ashe yarinyar nan kishi ne da ita haka gashi har takai ga marin Amrah don kawai ta d'auki takardu zata bata.....ta mari Amrah fa kace.... Wlh kuwa,,,Afrah da hankalin ki kuwa? to aini gwaggo bansan abu zata bani ba.... Ina zaki sani kishi ya rufe miki ido...wane kishin byn duk kaine kamin fad'a da dawowa ta asibiti baka ko tambi me akace yana damuna ba,,Aa farhan ba kyauta ba...gwaggo haka kawai fa ta fita ba izini na,lallai baki da gaskiya Afrah kuma ko kad'an banji dad'in yanda kika mari Amrah ba ,tun farko abinda ake duba miki kenan kan auren nan amma kinqi ji gashi tun ba aje koina ba kun fara samin sa6ani... To gwaggo ai 6acin raine yasa na mata haka ba wai da niya ba.... ba wani tun da da kuna yara har girman ku ko kunyi fad'a ba kwa dukan junan ku amma sae yanzu zaki sa mata hannu don kina ganin kin taimaka mata ta auri farhan ai inace itama taimakon naki tayi sbd tana da wanda take so ba kuma ita tace tana buqatar auren farhan d'in ba kece kika tilasta ta amma har kike ikirarin la6a ta kikayi ,to ai wanda take so d'in bai fa san tanayi ba,shine naga gwara ta auri uncle domin wancan zai iya mata walaqanci ba lallai bane ya riqe ta da daraja.....
ai gwanda shi d'in da ace tana tare da aminiyar ta tana sata baqin cikin da gwara ace wanda bata taso tare dashi bane yake mata hakan.....oh oh gwaggo na gaya muku ba a son raina bane kuma ni shike nan bani da inda zanje naji sanyi uncle fad'a ke fad'a,nan ta fita tana ci gava da cewa"Allah yasa yau yau d"in nan ma na mutu na huta da takaici, duk tana magana ne cikin kukan shagwa6a har ta fice daga 6angaren tana mitar ba a sonta .

Farhan yayi murmushi ya sami guri ya zauna yana fad'in "Afrah iyayen rigima ni na rasa a ina ta kwaso rigimar nan gwaggo" shine fa ga kuma saurin fushi kuma nan take ne idan an mata abu ranta ke 6aci "naga dai ba haka mahaifiyar ta marigayiya hajiya maryam take ba "ai kinsan gwaggo sae ka haifi d'a baka haifi halin shi ba" haka ne fa.

Sai da suka d'anyi shiru gwaggo ta katse shirun da cewa shin wai ta sanar da kai abinda ke damun ta? Ai rigimarta baza ta bari ba kawai dai zan duba ta da kaina koda bata so ko kuma na kar6i takardun da ke hannun Amrah na gani.
To Allah yasa muji alheri ,da jin kunya yace"Amin "sannan ya fita yana tunanin ko ciki ne ba zai kai wata d'aya ba"amma sae ganin yake kmr ma malaria ce da zaman banzan da take yi bata aikin komai .

Afrah na komawa 6angaren su ta tu6e zata yi wanka sae ga Amrah tazo ta same ta har d'aki tana bata haquri kan cewa "Don Allah Afrah kiyi haquri wlh ban miki magana don komai ba sae don na baki takardun ki da kika zubar a rashin sani kuma ni ban san wani abu kukeyi ba dmn saukowata kenan,amma kiyi haquri inshaAllah hakan ba zai sake faruwa a tsakanin mu ba.
Afrah komai ta kasa cewa sbd kunya ta cika ta har ta matsu Amrah bata var d'akin ba,Amrah kuwa na ganin ko kallon ta Afrah taqi ta ajiye takardun a kusa da ita zata fita, Afrah taji kmr ta mata magana idan bata bud'e takardun taga meke ciki ba domin ita bata son kowa ya sani har sae ta zubar da cikin, sae dai kuma tasan halin Amrah baza ta bud'e takardun ba amma duk ta haka hankalin ta bai kwanta ba,tace"kinga ina fatar baki bud'e min takardu ba? Ko d'aya Afrah kinsan ba hali na bane, sae duk ta qarà jin bata kyuata mata ba domin da gani tasan Amrah taci kuka kuma ko yanzu kukan take ji.
Afrah tace"kiyi haquri Amrah nima ba a son raina bane dan Allah kiyi haquri kinji"ba komai Afrah ya wuce.
Daga haka ta fita Afrah kuwa ta yiwa takardun 6oyon qwarai sannan ta shiga wanka.

Da fitowar ta wankan d'aure da towel taje d'akin Amrah ta nemi izinin ganin farhan Amrah ta bata dama.

Tana shiga d'akin shi ta same shi yana shan magani bayan ya gama yazo har inda take nan bakin qofa yace"ya akayi ne? na nemi izininta kafin na shigo,to ina ce kin bata haquri ?eh ,yaushe? da tazo d'akina ta ban haquri, to kema kije har d'akin nata ki bata haquri, kuma wlh kar na qara ganin irin haka a tsakanin ku, idan kuma kika qi wlh Afrah zan miki huknci mai tsanani,kayi haquri uncle nima ban so haka ba sharrin shaid'an ne, naji Allah ya mana katangar qarfe da sharrin sa, Amin
yauwa ina jinki me ya kawo ki?,dama ina so anjima zan fita ne da yamma ,,zuwa ina? nidai kawai kayi haquri ka bani izini,keda ba kya da lafiya kike zancen fita bayan kuma d'axu kinje asibiti ,don Allah uncle kar kace " Aa",,naji amma ina so zanga wani abu a jikin ki, bani fa keda duty ba,, ai na sani dmn aikin da zanyi ba zancen duty bane, idan kuma kince Aa fitar ki ce Aa, ba yanda ta iya tace"to shike nan duba abinda xaka duba.
Qara matsawa yayi kusa da ita har suna shaqar numfashin juna sannan yakai hannu a hankali yana yaye towel d'inta ,tayi saurin kallon shi yace"ba dole kina iya tafiyar ki amma ki sani ba fitar ki, kmar zata yi kuka tace "to uncle me zakayi?nima gaya min inda zaki je sae na gaya miki abinda zanyi,, um um duba kawai, wani shu'umin murmushi yayi sannan ya qarasa bud'e towel d'in wanda hakan ya bayyanar da kyakkyawan qirjinta a fili har sae da yaji wani abu

kasancewar ya jima bai gansu ba,haka ya dake yaci gaba da kallon qirjin nata da kyau sannan ya riqo hannayen ta yana kallon en yatsunta daga nan ya kalli fuskar ta wacce taqi yarda ta kalle shi yace"ur eyes "a hankali ta d'ago suka had'a ido,yace"yayi kyau sae ki rufe qirjin naki ki bani guri"a sanyaye ta rufe qirjin ta tace"to ka bani ixini? Sae da ya lumshe idon sa yace"eh na baki u are free to go"
cikin jin dad'i ta fita d'akin ba tare da ta kawo tunanin abinda yasa ya mata binciken  ba.

Bayan ta saka tufafi taje har d'akin Amrah kamar yanda yace, ta qara bata haquri cike da nadamar abinda ta mata ,
Amrah tace "wlh har ga Allah Afrah nasan a yanda muke yin kanki ba zai sa kimin haka ba sae dai sharrin shaid'an wanda nake fatar Allah ya shiga tsakanin mu dashi kar ya sake bashi cin nasara a tsakanin mu, amin Amrah ako yaushe ina alfahari dake sbd haqurin ki da kuma tunanin ki shiyasa nake son ki a rayuwa wlh, amma ai nafi sonki domin ni bazan miki yanda kika min ba, tayi maganar ne cikin wasa, Afrah ta rufe idonta cikin jin kunya ,ta kama kunnen tace"gsky ne yi haquri dan  Allah ,Amrah tayi saurin d'auke hannayen Afrah da ta kama kunnuwanta ta rungumeta ,tace"kefa da wasa nake miki.
  Daga haka sukayi zaune suna fira cike da nishad'i kmr basu ba.

Sun kwashe awanni suna fira har Afrah taji sat kmr bata da wani  sauran baqin ciki har tayi tunanin fasa zubar da cikin da tayi niyya.

Sea dai  yamma nayi tayi tunanin zuwa ta zubar da cikin ba don komai ba sae don ganin idan tayi haka zata rama takaicin maganganun da farhan ke saka mata domin idan yana mata maganganun ji take tamkar wata wuta ce mai kaifin bala'i yake rura mata a zuciya.

Shirinta tayi  tsaf ta fita sae dai tafiya mai nisa tayi zuwa wata asibiti inda bata sa ran wani  ya santa ko ta had'u da wanda ta sani.

Har ta isa wani abu take ji kmr ta fasa,amma bata bawa zcyr ta dmr hakan ba.

Cikin sauqi ta samu ganin likita kasancewar private asibiti ce,da shigarta office d'in taji wani dad'i ganin likitan ba musulmi bane a cewar idan ta had'u da musulmi zai tsaya ja mata aya ko hadisi tafi son kai tsaye ayi mata abinda taje nema.
   "Hajiya have a seat,ko kina da lalaura zama ne"kallon sa tayi had'e da girgiza masa kai tana mamakin yanda ko kad'an bai yi kama da mai jin hausa ba amma sae gashi yana hausa kamar jakin kano.
  Basarwa tayi ta nemi guri ta zauna tana tunanin qaryar da zata shirga masa ya mata aikin ta kai tsaye.
  Yace"Uhm meye matsalarki? sae da ta qirqiro hawayen qarya suka cika mata ido tap ta fara magana cikin murya kmr wacce ke cikin matsananciyar damuwa tace"doctor juna biyu ne dani kuma wanda a bisa qaddara na same shi ba wai ina nufi banyi aure ba na same shi, a'a ina da

aure, amma miji na baya son mu sami haifuwa da wuri shiyasa yake bani pills ina sha amma kwatsam sae gani d'auke da ciki wanda na tabbatar idan yaji kashe ni ne kawai ba zai yi ba domin nasan zan sha dukan tsiya sbd zai d'auka ko bana shan pills d'in da yake bani,kuma kullum ce min yake idan na yarda na d'auki ciki mun rabu dashi kenan har abada ,ba zai qara waiwayata ba,cikin kuka sosai ta qarasa maganar tace"gashi ni kuma ina mutuwar son shi bana son mu rabu kuma shi kad'ai ne gare ni a duniyar nan bani da kowa duk iyayena sun rasu, share hawayenta take wasu na sake zubowa,ta zame kan kujera ta durqusa kan guiwoyinta tace"pls doctor ka taimaka ka bani abinda zan sha cikin nan ya zube cikin gaggawa pls and pls am begin u"

Ajiyar zuciya dr ya sauke ya cire eyeglass sannan yace"ya isa haka Hajiya zauna muyi magana"

Bayan ta zauna yace"mijin naki yasan kin fito?eh amma bai san asibiti zan zo ba shiyasa nake son nayi sauri na koma,shike nan zan taimaka miki dmn matuqa kin bani tausayi,amma ina fatar ba kwata kwata bane baya son haifuwa? Aa yace da mun shekara biyu yana son mu haifu,ok cikin naki wata nawa ne?ko wata d'aya ma bai qarasa ba, that's gud domin abu ne mai sauqin zubarwa.

Nan ya tashi ya d'auko mata wani magani tablet ya zauna kafin yake cewa"zaki sha qwaya d'aya tak by 30mint cikin zai zube tas"bai kai ga miqa mata ba wayar sa tayi qara ,ya d'aga wayr cikin fara'a,

yana cikin wyr ya shiga kallon Afrah bcs ba da kowa yake waya ba face farhan wanda duk zunzurutun tafiyar nan da Afrah tayi yana biye a bayan ta haka kuma duk abinda ta fad'a yana ji a bayan window.

Amma sae da ya bar kusa da window sannan ya kira Dr wanda ba komai yake snr da shi face"ka canza mata wannan maganin ka bata na bacci dana qarin jini da qarfin jiki ga masu ciki,amma ka bata su a matsayin na zubar da ciki ne idan ta fita zan shigo muyi magana."

Nan Dr ya katse wyr ya kalli Afrah kafin yake cewa bari dai na baki wanda yafi wannan qarfi, kmr kuwa kasan tunanin da nake yi kenan ka bani wanda koda 15 mnt keyi cikin ya zube tas, ok to cewar Dr sannan ya tashi ya d'auko mata magungnan da farhan yace a bata ,ta kar6a tana godiya yace"kowanne kisha qwaya d'aya "ok to, nawa ne kud'in nan ya fad'a mata kud'i ta biya shi ta fita sae murna take a ranta.

Tana zuwa gida bata wani duba qa'idojin magungunan ba bare ta fahimci na mene ne ,sha kawai tayi,taje ta dauko pad ta saka a cewar koda yazo mata da matsanancin ciwon mara ta shirya,taje ta nemi gado tayi kwance sae jin wani abu take cikin cikinta na tsoro kmr wacce tayi babban laifi tana tunanin idan aka kamata ya zatayi ,haka take ji sosai har ma ta kasa samun natsuwa ta yanke shawara zata je 6angaren gwaggo koda yazo mata da mutuwa sae tayi wasiya kafin ta mutu.

Nan ta garzaya sae 6angaren gwaggo ta haye gado ta rufa jikin ta da blanket fuskar ta kad'ai ta bari.

Farhan kuwa tafe yake hanyar dawowa sae mamakin Afrah yake a ransa ,yayinda ya yanke shawarar ba zai nuna mata yasan komai ba zai zuba mata ido yaga iya haukarta tukun.

Yana shigowa gidan 6angaren gwaggo ya nufa koda ya shiga d'aki ya sami Afrah idon ta qyar kan agogon bangon d'akin sae qidayar lokaci take ,dariya ta soma bashi wai a haukar ta zubewar cikin take jira har tana wani qidayar time baki sae motsi yake kmr wata mai salati.

*Billy giro😊 &Futha lurv💅*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:22PM, 11/30/2016] Billy Geeero: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futhalurv.WordPress.com*

*```🏅60🏅```*
Gyaran murya yayi domin ya fahimci bata san da shigowar sa ba.
Da fargaba take kallon shi abu ga marar gaskiya.
Shi kuma ya sake mata fuska kmr ba komai yace"ina gwaggo take ne? koda na shigo ban ganta ba may be tana bayi tana wanka,yace"OK" kafin yake fita.
Ajiyar zuciya ta sauke ta qara shigewa blanket sae ga gwaggo ta fito daga bayi tace"assha kaddai ciwon ne yakai ki ga kwanciya,ina farhan yake ne bai duba ki ba? Aa gwaggo amma yanzu ya fita, to qoqarta kiyi sallah kinji an fara kiraye kiraye ,ba musu ta tashi amma ta fara mamaki da har yanzu bata fara jin komai ba sae bacci,

may be yanayin maganin ne sae idan tayi bacci koda zata tashi ta samu cikin ya zube.
Haka tunanin nata ya bata.

Da qyar taga ta samu tayi sallar magrib sbd bacci ,tana kammalawa ta maida pant d'inta da ta cire mai d'auke da pad taje ta hau gado ta sake qudundunewa cikin blanket daga haka bacci yayi awon gaba da ita.

Sai bayan sallar isha'i farhan ya sake dawowa 6angaren ya sami gwaggo tana lazimi ya nemi guri ya zauna ta taqaita tace"inaga fa kmr Afrah na jin jiki sosai ka duba ta kuwa? eh gwaggo, to me yake damun ta ne? shiru yayi baya son snr da gwaggo ciki ne da Afrah wanda ya fahimci haka ne kafin ma yabi bayanta wato lokacin da ya duba qirjinta da yatsunta da kuma idanuwanta ,yafi so ko zai sanar da gwaggo sae ya gama ganin haukar Afrah tukun.
Yace"d'an zazza6i ne"to Allah ya mata sauqin shi yace amin "ya tashi ya fita.

Koda Afrah ta farka daga bacci ta ganta d'akin farhan yana zaune a bedside yana wani aiki da laptop bayan sa kad'ai take gani hakan yasa tayi saurin sa hannu ta ta6a pant d'inta bata ji alamar komai ba ,ta shiga dube dube akan gadon ma haka, ta tashi domin zuwa toilet ta qara duba kanta ,farhan yace"ki d'oro arwala kafin kike fitowa kiyi sallar isha'i"kallon agogon d'akin tayi qarfe 9:40pm ta shiga tunanin ko dai cikin ya zube har farhan ya mata wanka bata sani ba, to idan haka ne ai ba zai ce tayi arwala ba kuma ai kayan jikin ta ne a saye da ita farhan dai se kallon ta yake har ta qaraci banzan tunanin ta ta shiga toilet.
Tana shiga ta ciro pant taga shi d'in dai ne ba wani canji kanta yayi mugun d'aurewa ya akayi cikin bai zube ba ko dai doctor ya manta ba guda guda ake sha ba lallai zata je ta duba qa'idar maganin ta gani.

Sae da ta watsa ruwa sannan tayi arwala ta fito taje d'akinta tayi sallah tana gamawa ko azkar d'in da take bata iya yi ba ta tashi ta jajimo jakarta da ta fita da ita sae dai kaf ta zazzage jakar bata ga maganin ba, tunani ta shiga yi to ina takai maganin ko ta bar su a mota,no nazo dasu tunda har nasha kawai dai nasan ina da niyyar musu 6oyon qwarai ban kuma riga nayi ba amma zan bincika .
Ta kwashe kusan rabin awa tana neman maganin duk ta wahala amma bata gan su ba nan ta yanke shawarar zata je cikin motarta ta bincika.
Sum sum take tafiya kmr wata 6arauniya har ta sauko downstairs ta murd'a key tare da riqo handle d'in qofar taji farhan yace"ina zuwa da dare haka? wani irin abu taji na fad'uwar gaba duk la6a6en nan da take don shi kawai take amma sae gashi ya kamata dumu dumu zata bud'e qofa, ynx me zata ce masa ,har ya qaraso gurinta ta kasa ko qwaqqawaran motsi kanta qasa cike da fargaba sae 6al 6al zuciyar ta keyi kmr zata fito, yace"ina magana wani abu kike so ne? Da qyar ta iya bud'e bkinta tace"dama wani abu zan duba a mota"mene ne wannan abun da baza ki haqura har da safe ba koda yake jeki ,kallon sa tayi ta kuma yi saurin duqar da kanta yace"jeki man ko so kike na raka ki ? saurin girgiza kanta tayi tace"Aa zan iya zuwa ni kad'ai"

Tana kawowa nan ta bud'e qofa ta fita farhan ya girgiza kansa domin yasan ba komai take nema ba face magungunan da ya d'auke ,wanda ya d'auke su ne sbd yasan da zarar taga cikin bai zube ba sae ta nemi ganin qa'idar su.

Sosai take jin tsoro duk da hasken da ke harabar gidan haka taje ta bud'e motarta,tayi iya binciken ta bata ga komai ba.

Jin take kmr tayi kuka duk takaicin kanta take da ta manta inda ta sa su, domin a tunaninta tasan ba wanda yasan da su bare tayi tunanin d'auke su akayi.

Ba yanda ta iya ta rufe motar ta koma daga ciki ,sae dai bata sami farhan ba ya komawar sa d'aki .

Tana shiga d'aki tayi zaune qasan tiles bayanta na manne a jikin gado ta had'e kai da guiwa ta fara rera kuka tana tunanin yanzu ya zata yi idan bata ga magungunan ba gashi cikin bai zube ba tasan da kmr wuya farhan ya sake bari ta fita nan kusa.

Bud'e qofa taji anyi tayi saurin d'agowa dai dai hawaye na zubowa kan fuskar ta, tayi saurin share hawayen farhan yazo yana taya ta ta yace"kukan na me"cikin muryar kuka tace"ba komai"amma kike kuka ko yunwa kike ji?girgiza kanta tayi byan kuwa tana jin yunwa sosai amma bata jin zata iya cin abinci a yanayin da take ciki yanxu.

D'aukar ta yayi suka je d'akin shi ya zaunar da ita kan bed yaje ya bud'e frigde ya d'auko fresh milk ya tsiyaya a cup yazo ya zauna kusa da ita,ya jawota jikin sa yana shafa bayanta a hankali yace"Afrah yi haquri kisha wannan kafin ki kwanta kinji"

girgiza masa kai tayi, nan dai ya lalla6a ta ya shiga bata har sai da tace ta ishe ta,tana gama sha ba jimawa bacci ya kwasheta,wanda shi ya saka ta baccin ta hanyar qwarewa gun shafar jiki dmn bacci.

Kallonta yake yanda ta wani lafe a qirjin sa, yakai hannu a hankali ya shafo cikinta,sae kawai hawaye suka silalo kan kumatun shi yana mai jin baqin cikin yanda Afrah ta tashi zubar mai da cikin,ya rasa meyasa take da niyar hakan da har ta shirgawa doctor uwar qarya haka byn kusan ko yaushe yana nuna mata illar qarya amma sae gashi ta gwane a gurin.

Motsin da tayi ne yasa yayi saurin d'auke hannun sa a kan cikinta .

Washe gari ta gama sallah kenan taji amai da sauri ta nufi toilet ta saka key sbd d'akin farhan take bata so ya shigo yaga amai take ya fahimci ciki ne da ita, sauqin ta d'aya ammanta baya da sauti,

ta kintsa kanta kmr wani abu bai faru ba ta ta fito.

Da ta fito komai bai ce mata ba ,
nuna ma yayi bai lura da yanayin da ta tashi ba .
Sosai taji dad'in da bai fahimta ba ta zauna tana yin azkar.

Zaune suke suna break fast su uku guraren qarfe goma spoon d'aya Afrah tayi taji alamar amai hakan yasa bata sake saka wata lomar ba gudun kar tayi aman.

Magana farhan ke musu yana tambyar abinda zai dawo musu dashi sbd fita zai yi,komai Afrah

taqi yarda tace domin tasan tana bud'e bakinta za a sami matsala.
Amrah kam tace"bata buqatar komai,
Farhan ya kalli Afrah domin yasan duk zai fita sae ta fad'i kalar chocolate d'in da take so, yace"kefa"girgiza mishi kai tayi wanda ya duk san dalilin kasa maganar sbd yana lure da ita tun lokacin da ta saka loma.
Fita kawai yayi abin shi ba tare da ya ske cewa komai ba yasan dai tana da aiki domin duk yanda taso 6oye cikin yau da gobe sae ya bayyana dmn ba zai ta6a sakacin barinta ta zubar dashi ba.

D'aki Afrah ta shige domin ta samu taci abinci amma da taje zuwa bud'e baki sae taji amai ,ta sake gwada bud'e bakin taji still ta kasa ,
kuka take sonyi sbd yunwa take ji sosai ,nan dai ta danne kukan tayi ta gwadawa ko zata samu ta bud'e bakin bata ji amai ba  wanda tayi hakan kusan sau biyar taga duk d'aya,kuka ta shiga yi ciki ciki ta rasa yanda zata yi taga dai ba wai amai ta bari a cikin bakinta ba kawai dai yunqurin amai kezo mata da zarar taje zuwa bud'e baki.

Haka ta yini ba ci ba magana ko gwaggo da tazo dubata da hannu take bata amsa idan na gyad'a kaine  ta gyd'a kai in kuma girgizawa ne ma haka.
Hakan yasa hankalin gwaggo duk ya tashi domin ganin take kmr matsalar Afrah ce ta dawo mata wato kurmanci,sae duk ta kasa zama ta kasa tsayi tana kiran wayar farhan da taqi shiga, tace da Amrah"tun yaushe ne rashin maganar  yazo mata ?nima gwaggo ban sani ba sae yanzu sbd tunda safe ta shige d'aki bata sake fitowa ba kawai dai d'azu da safe da uncle zai fita, as usual tana fad'in abinda take so a dawo mata dashi amma sae naga ta girgiza masa kai wanda hkn ya ban mamaki amma sae na basar.

Afrah da ko kad'an bata son a kira farhan ta kar6e wayar gwaggo tana nuna kar a kira shi ita fa lafiyar ta qalau, gwaggo tace "to Afrah kimin magana mana naji"
Shiru Afrah tayi domin bata jin zata iya yiwa gwaggo magana .
Suna cikin haka sae ga farhan ya shigo , gwaggo tace "yauwa farhan dama kai nake son kazo ka duba Afrah idan ba matsalar tace ta dawo ba,dmn bata magana sae dai tayi wa mutum maganar kurame,yace"Afrah yiwa gwaggo magana mana taji,girgiza mai kai tayi yace"me yasa?shiru tayi ,yace"gwaggo jeki abinki kawai lafiyar ta qalau kar ki damu"farhan ina fa lafiya bata mgna nikm ba inda zanje sae naji tayi min magana,,rau rau Afrah ke kallon Farhan dake kallonta ko kad'an bata son tayi magana tayi amai har su fahimci ciki ne da ita ,shi kuwa farhan ransa ne yayi mugun 6aci dmn sak ya fahimci irin laulayin da take d'auke dashi ya kuma gano dalilin da yasa bata son yin magana,wanda hakan ya qara bashi  tabbacin tana kan bakar ta na ganin ta zubar mai da ciki, duk da yaso ya basar har sae yaga iya gudun ruwanta amma 6acin rai ya mantar dashi har bai san lokacin da ya daka mata uwar tsawa tare da jawota jikin sa yace"kiyi magana aka ce !Afrah da gabad'aya ta rud'e bata san lokacin da ta bud'e baki zuwa magana ba kan tace komai ta shiga kwara amai kan jikin farhan.

*Futha lurv&Billy giro*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:22PM, 11/30/2016] Billy Geeero: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```~AFRAH KO AMRAH ```*~
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*NA Billy giro 😊& Bilqis Sidibe💅*

*Futhalurv.WordPress.com*

*🏅61🏅*
KO kad'an ransa bai 6aci ba kan amman da take kwara masa sbd yasan sae tayi aman ne zata ji sauqi,
da qyar ta samu ya tsaya mata duk tabi ta galabaita sae numfashi take fitarwa.
Qoqarin zamewa take daga jikin sa sbd tsayuwa na son gagararta hannun ta yaja ya tafi da ita d'akin shi suka je bayi, ya riga ta tsaftace jikinsa ya fito ya barta ya dawo downstairs ya samu Amrah ta gyare gurin tsaf gwaggo tace " anya farhan baza ayiwa yarinyar nan test ba kuwa" zan gwada hakan, haka ya fad'a a taqaice sbd 6acin randa yake ciki baya ko son yin magana sosai.

Da dare Afrah ce kwance sae tunani take Farhan bai ce mata komai ba har yanxu kuma tasan ya fahimci abinda kenan.
Bud'e qofa taji anyi ta tashi a hankali tana kallon Farhan wanda fuskar sa ba alamar annuri yaje ya zauna kan gadon da take , ta matso gab dashi tare da jinginawa a jikinsa ta kwantar da kanta kan kafad'ar sa wanda tana yin komai ne tsoro tsoro yace "gaya min meyasa kike son zubar min da ciki,na miki wani laifi ne ko kuwa ra'ayin cikin ne ba kya yi? fad'uwar gaba taji sosai ta san bone ya cita tunda ya gano ta amma ya akayi ya sani shine abinda take tamvayar kanta, tace "uncle wa yace maka zan zubar da ciki? Ki bani amsar tambaya ta tukun,ba zai yu na miki tambaya kimin ba,shiru tayi ta rasa me zata ce masa sae qoqarin kuka take yace" Afrah ba kuka na tambaye ki ba don haka kar ki soma" shiru tayi yace"Afrah kar ki bari 6acin raina ya yawaita ki bani amsar tamvaya ta ina saurarenki "
cikin muryar kuka sosai,tace "uncle ni abinda kake min ne bana so" name kenan? na maganganun da kake gaya min, sosai suke qona min rai shiyasa naga ba abinda zan maka na rama face zubar da cikin "tsantsar wauta ya hango a tare da ita ,
dmn shi ya d'auka ko qatoton wani abu ne sae dai ya tuna cewa Afrah yarinya ce she is only seventeen yrs bata kammala hankalin kanta ba tukun,
Yace" amma Afrah ai ni na miki laifin ba cikin ba meyasa baza ki d'auki mataki a kaina ba,

kuma kin manta cewa kwata kwata kin daina bani kulawa akan haqqina ai ko shima wata axaba ce kike min,uncle kana fa da wata mata, Afrah dan ina da wata matar sae aka ce ki share ni,ko kuma haka aka ce miki idan ana kishi har haqqi daina ba miji ake...turo baki tayi tace"ai ni ba kishi bane kuma nida nace a auro ta sae kuma nayi kishi", naji ba kishi bane gaya min dalilin ki naqin bani haqqina,to ni uncle ba komai,kenan yau zaki bani? maqale kafad'a tayi tace "ni bazan baka ba tunda d'azu kamin tsawa don kawai naqi magana" ai kad'an ma kika gani don banzo gun zancen qaryar da naji kin shirgawa doctor ba "da sauri ta tashi kan jikin sa har tana hard'e qafafu sae wani soshe soshen rashin gsky take.

Tace " uncle waya snr da kai nayiwa doctor qarya? Ni naji da kunne na ko Kuma kina tunanin haka kawai zan barki ki fita ba tare da kin sanar dani inda zaki je ba,, kenan uncle baka yarda dani ba,yarda ma kuwa amma ke ke shirin 6arar da yardar sbd tun da kika zo nemn izinin fita na fahimci ba kya da gaskiya na kuma sami kaina da jin fad'uwar gaba kmr wani mummunan abu zai same ni shiyasa na kasa haqura sae da nabi bayanki wanda tabbas 6arna ce ke shirin afkuwa dani se Allah ya kare ni da sharrin shad'aninki,,kuka ta fashe dashi ko kad'an bata ji dad'in kalmar ba tace"me yayi zafi haka uncle? Au to ba shaid'anin naki ya ingizaki ba, wani kukan ta sake fashewa sosai kuwa ,farhan yace"baki fahimce ni ba fa zo na fahimtar da ke.

Nan ya jawo hannun ta ya zaunar da ita yace"ba ina nufin ke shaid'an bace ,kuma shaid'aninki da kika ji nace kowa na duniya Allah ya halicce sa dashi haka ma Annabi Muhmd( s . a. w), amma shi Allah ya taimake shi ya musulntar mai da nashi baya sashi aikata munanan ayukka, mu kuma namu da ba a musulntr ba shike ingixa mu wani lokaci muna aikata abinda ba dai dai ba,haka kuma idan muka biyewa son zuciya tana sa mu aikata munanan ayukka ,ma'ana kinsan abu marar kyau ne amma kika yi don kawai biyan wata buqatar ki,shine kinyi son zuciya shiyasa ake son mutum ya tsalkake zuciyar sa idan kikayi hakan to kin gyara dukkanin jikin ki,

Idan zaki iya tuna a cikin arba'una hadith, a cikin qrshen hadith na shida inda annabi Muhammad (S.A.W)yake cewa sahabbansa

_"Ala,Ku saurara,wa inna fil jasadi mudgatan izan salahat salahal jasadu_

_Kullihi,wa iza fasadat fasadal jasadu kullihi_. _Haqiqa a cikin jiki akwai wata tsoka idan ta gyaru dukkan jiki ya gyaru._

_Idan kuma ta lalace dukkan jiki ya lalace._

_Yace"Ala ,Ku saurara ,wa hiya qalbun ,ita ce zuciya_"

Buhari da muslim ne suka ruwaito shi.

Kinga kenan abinda hadith yake fahimtar damu anan shine idan muka tsalkake zuciyar mu ,mun ku6utar da ga66an jikin mu ne daga aikata miyagun ayyukka,sbd dama duk wani abu daga zuciya ne yake fitowa sannan ga66an jiki su aikata.

Ina fatr kin fahimta? Na fahimta uncle kasan mnyi wannan hadith a islamiyya....ai ba yi ba aiki dashi, inshaAllah zan kiyaye.

Yace "yayi kyau na kuma dawo zancen doctor, kisani ko kad'an banji dad'in qaryar da kika yi masa ba, nasha gaya miki Afrah qarya ba kyau,qarya takan iya sa mutum wuta,tana kawo xubewar mutunci a kuma daina ganin kimar mutum da darajar sa,

yanzu da ace na sanar da doctor cewa qarya kika masa ba zai qara ganin kimar ba ,ba kuma

zai qara yarda da abinda zaki sake gaya mai ba koda kuwa ya kasance gaskiya ne.
Kayi haquri uncle sharrin shaid'an ne amma zan roqi Allah ya bani ikon rinjayar shaitan ya kuma bani ikon tsalkake zuciyata,
,tada ta yayi kan durquson da tayi masa sbd ta fahimci ko kad'an abin bai masa dad'i ba.
Share mata hawaye yake yace"shike nan ya isa na haqura amma kar ki sake aikata hakan kinji"
"inshaAllah uncle"
kimmin alqawari ko bayan idona ne ?nayi maka alqawari inshaAllah, amma uncle me kace da doctor ?ce masa kawai nayi na san waye mijinki ,zanje na masa magana.
yace"amma Afrah dan Allah na roqe ki kar ki sake gigin cewa zaki zubar da ciki don kawai mai shi ya 6ata miki rai sam ba hujja bace,kuma ba qaramar wauta bace domin ba kisan irin alherin da ke tattare da wannan cikin ba wanda idan kika haifeshi Allah kad'ai yasan matsayin da zai kai shi tayu shine mai tausayin ki da taimakon ki duk baki sani ba.
Don haka ko nan gaba koda bani ba,mijinki ya 6ata miki rai kiyi tsalkakakken hukunci ba irin wannan ba..... uncle me kuma ya kawo zancen wani mijin, Afrah idan na mutu ai dole kiyi aure baza ki zauna haka ba....cikin kukan shagwa6a ta rufe mai baki tace,"haka kawai ana zaune qalau ka d'auko zancen mutuwa,,ai ko banyi zancenta ba zata xo min sbd dole ce.....Aa ka daina uncle baza ma ka mutu ka barni ba "
idan Allah ya rubuto tare mutuwar tamu take ba, amma idan ya rubuto ni zan fara mutuwa kinga dole na tafi na barki.
Kuka ta ajiye mai sosai kan ya daina mata zancen mutuwa bata so,yace "to na daina sae kuma me?sae muyi bacci, wane baccin wai nikam ce miki akayi ni dtse ne da zan yi ta bacci kullum,bana rage sha'awa,kunya taji tayi saurin rufe mai baki had'e da 6oye fuskarta a qirjin sa, ya shafo cikinta yace"gobe zan sanar da su gwaggo qaruwar da muka samu...Aa uncle kunya nake ji dan Allah kar ka fad'a wa gwaggo ,to ai idan kika snr da Amrh dole gwaggo taji,ai ni bazan gayawa Amrah ba sae idan ta gani da kanta.
To shi baban babyn fa? to ai ya sani ,um um da ace ban sani ba wai, tace"a rnr jy ko,da naje asibiti aka sanr dani ina d'auke da ciki tun kafin na baro asibiti nake ta farin ciki har ma na manta 6acin randa kasa min yayinda na tsara a raina cewa ina zuwa gida zan baka takardun na kuma rufe idona na fita da gudu, as i imagined idan ka krnta tkrdn zakayi farin ciki sosai sae kawai da dawowata ka ajiye min fad'a ka juyar da farin cikna izuwa baqin ciki.
Cikin shagwa6a ta qarasa maganar yace"yi haquri ftr ki ba izini ce ta 6ata min rai dmn bana son mala'ikun Allah suna tsine miki,amma ai yanzu komai ya wuce"
um um saura d'aya ,meke nan? Amai ne bana son inayi uncle,kaga yau na wahala sosai tun fitarka ban sake cin abinci ba da da magana.
Dama kuwa zan miki magana akai idan kika ji amai kiyi amn domin zai fi miki sauqi kan kice barin shi zakiyi, zai yi ta damun ki ne ba kuwa zai daina ba har sae kinyi shi,kinga yanzu da kika yi ,kinci abinci gashi yanzu har muna magana dake.
Murmushi tayi tace"ni ina nasan haka ne"ya lakato hancinta cike da murmushi yace"ya zaki sani kina fama da rashin jinki"
Yana kawo nan ya shiga cire buttons d'in rigar sa ,ta kai hannu a hankali tana shafa sumar qirjinsa tace"uncle yaushe sumar qirjin ka ya fito haka?ya zaki sani kin share mijinki d'an bawan Allah kin barshi da yunwa, d'an guntun murmushi kawai tayi ,yace"nikam meyasa kike son

sumar qirji? tace"ba ita kad'ai ba har ma na nan ina so,ta fad'i haka ne yayinda ta shafo sajen fskrsa sannan ta koma kan qirjinsa tana ci gaba da shafa tace"luf luf dashi yana matuqar birgeni shiyasa kake matuqar birgine har bana so naga ka aske"qara rungume ta yayi yace"ni kuma a jikin ki ina matuqar son wa'anan har bana fatar ganin zubewar su shiyasa a duk lokacinda na gansu nake alfahari sbd Allah yayi miki su masu fad'i da tsayi ta yanda basa saurin zuvewa.
Duk maganar nan da yake yi kanta a qasa tana d'an murmushi jin kunya sae kallon hannun sa take dake yawo a hankali kan qirjinta,daga nan ya kashe bedside lamp ya kwantar da ita tare da fad'in " yau a nan zamuyi yaqin kashe arna, anan d'in? Eh man kinga munyi a Oman mun sami ciki, munyi a d'aki na mun sami ciki,yanzu sae muyi a d'akin ki mu sami ciki, kinga mun sami 'ya'ya uku kenan, idan mun sake yi mu sami na hud'u... dariya tayi sosai tare da fad'in"cabd'i! idan haka ne da bone yaci matar jarababbe....kuf ta buge bakinta tayi saurin 6oye fuskarta a kirjinsa sbd wata irin matsananciyar kunya taji har dai da taga yayi mata kallon mamaki ,sae duk taji kmr ta 6ace 6at ta huta da kunyar .
Lallai yaran zamani ba abinda baku sani ba"cewar farhan wanda ke kallon Afrah dake ta faman cusa fukarta a qirjinsa kmr zata fasa qirjin ta shige ,yayi2 ya d'ago fuskarta ya kasa yace"d'ago fuskar ki man ko so kike nayi fushi? a hankali ta girgiza kanta yace"to d'ago , da qyar ta iya d'agowa sae dai fuskarta rufe take da tafukan hannyenta ya jaye hannunwanta but still idonta a rufe suke .
Nan ya sami damar qarewa kyakkywar fuskarta kallo musamman kan d'an qaramin bakinta da shima yake matuqar birge shi,fuskarsa yakai gab da tata ya goga hancinsa akan nata yace baza ki bud'e idon naki ba,kan tayi wani abu ya had'e bakinsu guri d'aya sae tsutsar lips d'inta yake kafin yake fara wasa da harshenta,yana kuma wasa da d'ayan hannunsa akan qirjinta yayinda d'ayan hannun ke shafar gadon bayanta ,daga haka ya shiga aika mata saqonni masu nauyin gaske da suka mantar da ita komai wato har Amrah,inda ta shiga nuna mai tata qwarewar ta hanyar mayar masa martani hakan yasa d'akin yayi tsit ba a jin komai sae numfashin su kad'ai.

"A hankali uncle kar naji zafi pls"
shine abinda ta furta cikin kasalalliyar murya, sbd addu'ar da taji yayi yana qoqarin shigarta.
Yace"olryt"

Da haka suka lula duniyar ma'aurata wacce tayi bala'in nishad'antar dasu.

Gurаren qarfe uku farhan ya farka sae kallon Afrah yake da ta wani qudundune cikin jikin sa kmr mai shirin shan mamma cike da murmushi ya shafo fuskar ta domin yau ta faranta mai rai sosai ya kuma ji dad'in kasancewa da ita har dai yanda bata nuna gajiyawar ta ba.
Tashi yake qoqarin yi domin zuwa toilet ya d'oro arwala yayi nafila sae kawai yaji wani motsin da bai kamace shi ba a harabar gidan, hakan yasa ya tashi a hankali ya bud'e window,
sosai ya firgita da abinda ya hango ,
da sauri yaje gun wardrobe ya bud'e ya d'aukowa Afrah wata doguwar rigar bacci mai kauri da tsawo har qasa ,yayi kan Afrah ya tada ta zaune yana saka mata rigar sae innalillahi wa inna ilaihi raji'un! ke fita a bakinsa,sbd yanda yake jin motsin yazo gab da d'akin su,yana gama sa mata rigar kuwa aka turo qofar d'akin da qarfin tsiya har sae da Afrah dake cikin bacci ta farka a

firgice ta daka uban tsalle ta koma bayan farhan ta qanqame shi tana kallon bakin qofar d'akin,cikin muryar firgici tace"innalillahi wa inna ilaihi raji'un!uncle su waye wa'anan"?

*Futha luv💅&Billy giro😊*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:22PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [ 10/25/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futhalurv.WordPress.com*

*🏅62🏅*
Uwayenki ne !ko kinada wata magana ne! saurin girgiza kanta tayi sbd bindigar da ta gani a hannun sa sae duk ta qara qanqame farhan tana kallon halitta irin tasu wacce bata ta6a gani a fili ba sae dai ko film domin girman jiki ne dasu sosai da kuma tsayi kmr samudawa ,haka ko maganar su abin tsoro ce kan kaurin muryar su wacce har vibrate kake ji idan suna magana.

D'aya daga cikin su ya daka ma Afrah tsawa sbd amboton Allahn da take ta faman yi cikin muryar kuka,Farhan kuwa tunda suka shigo ya duqar da kansa yana ta addu'oi'n da duk suka fad'o masa a rai sbd kallo d'aya yayi musu ya fahimci sam ba irin wad'anda zai iya fafatawa dasu bane .

Sbd shi kanshi ya bala'in tsorata da ganin yanayin su.

wanda ya dakawa Afrah tsawa ne yace"ki mana shiru ba tashin hankali ya kawo mu ba,don haka kajata ku 6ace mana da gani daga d'akin nan idan kuma kasa wasa mu fitar da ku daga duniyar nan gabad'aya,

A rikice afrah taja hannun farhan tace"uncle muje dan Allah kar su kashe mu"

Suna  xuwa downstairs farhan yace "Afrah yi sauri kije 6angaren gwaggo kafin su fito na samu na tada Amrah, pls uncle ni tsoro nake ji muje tare, da sauri kuwa farhan yaja hannun ta har yana had'awa da gudu gudu sae kawai suka ga an 6alla wutar falon suka ga mutane su uku sae tafi suke ga tulin 'ya'yan fruits da suka ciro a fridge suna sha ,d'yan su yace "weldone 6angaren gwaggo ko, kuje man ai itama tana da nata baqin sae ku tayata tarbar su."

Koda yake Ku jira d'ayar sae kuje tare"rufe bakinsa keda wuya sae ga Amrah cikin kuka tana saukowa da gudu a firgice sae kama wuyan rigar baccinta take da ta yage wacce idan ta sake kai tsaye qirjinta ne zai bayyana ,wani  daga cikin su ya kalli wanda ke bayanta yace"meye haka aikinda muka zo yi kenan? oga yarnyar ce da taurin kai taqi ta sauko ko kan gadon da take shine na jawota har aka sami akasi rgr ta yage.

Yace"naji jeku qarasa aikin mu samu mu kammala da wuri,

kar kubar komai da kuka sani na dukiya .

Sannan ya kalli su farhan yace"malam bana son ganin mutum a tsàye idan ina zaune don haka ku zauna Ku taya mu shan fruit idan kuna ra'ayi.

Idan ba kwa ra'ayi ku zauna kuyi shiru da bakin ku bana son sake jin maganar wani  a cikin ku har mu bar gidan ,doka ce idan kuka taka muma zamu taka ,ba mu zo da niyar ta6a lafiyar kowa ba sae wanda ya taka mana doka.

Wannan kenan.

Sunyi kusan minti 20 ashirin zaune a gurin ba wanda yace qala domin kowa na gudun a ta6a lafiyar sa .

Bayan en fashin sun gma duk abinda suke a cikin gidan suka had'u falo d'ayan yace"oga a wancan 6angaren da mukaje matar ta sa6a doka hakan yasa muka harbe ta a qafa,da kyau amma ya akayi ka tausaya mata ai ba a qafa ya kamata ka harbeta ba ka mata harbin da zata bar duniya domin shine hkncin wanda ya taka mana doka, ai ko yanzu oga bata da maraba da matatta dmn tunda na harbe ta bata sake motsi ba har muka gama abinda muke muka fito.

Ba qaramin tashin hankali farhan ya shiga ba har ya tashi tsaye yana qoqarin cewa dasu wani abu, ogan yace"wlh zan harve ka ynzu idan baka zauna ba.

Cikin kuka da firgicin jin an harve gwaggo Afrah ta jayo shi tana fad'in "uncle dan Allah ka zauna kai ma kar su harbe ka"da qyar farhan ya iya durqusawa kan qafafun sa idanun sa sunyi jajir yana ji kmr ya fasa ihu.

Wani  daga cikin su yace "oga ai sai mu tafi kafin a fara kiraye kiraye,tkuna wani  saqon ya riske ni a waya yanzu.

Ya kalli farhan yace"Ku bani takardun kadarorin sa da kuka kwaso "

Suna miqa mai ya miqa ma farhan yace"sa mana hannu a kan kowace takarda kuma bana son musu "ko kallon takardun farhan yaqi yayi ya kauda kansa gefe wanda shi kad'ai yasan abinda yake ji game da harbin gwaggo da akayi,ogan ya jawo Afrah da qarfin tsiya har sae da ta fad'a kan jikinsa,

ya d'ora mata bindiga akai tare da buge mata baki kan ihun da yaga zatayi, yace"ka sa mana

hannu ko kuma na harbeta idan kuma kaqi kaima na had'a da kai"
A kan dole farhan ya sa musu hannu kan kowace takarda.
Sannan ogan ya saki Afrah da ke ta faman kuka ciki ciki.
Yace"then wace ce matar ka a cikin en matan nan? Kai tsaye ya nuna Afrah sbd sanin alqawarin da yayi ma Amrah na ba wanda zai san da auren su,,, Afrah kuwa kallon mamaki take yiwa farhan tace"uncle..... Shiiii!ba sai kince komai ba ai na fahimci ba gsky bane...da gaske yake yi oga domin tare muka same su d'aki d'aya, nop ai naga lokacin da ya leqo mu ta window ba mamaki shi ya sameta a d'akinta ya sanr da ita abinda ya gani.
Ya kalli Amrah yace"ke baiwar Allah gaya min gaskiya wace ce matar sa a cikin ku"shiru tayi tana tunanin in ma mugun abu zasuyi wa Afrah gara kawai tace ita ce"tsawa ya daka mata yace"dake nake magana! a rikice tace"nice matar sa"da sauri farhan ya kalleta tayi saurin had'e tafukan hannayenta alamar don Allah kar yace komai,ogan yace"laifinta kake gani don ta fad'i gaskiya,ai kuruwa kayi dmn da ace munje da wannan muka samu ba itace matarka ba zamu kashe tane kaima mu dawo mu kashe ka mu kuma d'auke matar ka,duk yana magana ne yayinda yake nuna Afrah.
Sannan yace da yaransa "kuja matar tasa kuzo mu wuce "a rikice farhan ya miqe ganin sunja Amrah yace"Dan Allah ku bar mu haka mana meyasa zaku tafi da ita wannan wane irin rashin imani ne..... qarasa zancen sa keda wuya yaji harbi ,ihu Afrah ta saki tayi kan farhan da ya fad'i tana kuka cike da firgici,da qyar ya iya nuna mata Amrah wacce har sun fita da ita daga cikin falon  yace"Afrah kije Amrah na magana, da gudu ta tafi ta riqo hannun Amrah da take miqowa,kuka take sosai tana so zatayi wata magana ta fasa tare da saurin cewa"Afrah ki koma ki fitar da uncle sun saka wuta"
gudu take har tana hard'e qafafu ta samu ta koma daga cikin falon tana jijjiga farhan da kad'an ya rage ya rufe idonsa tace"uncle don Allah kar ka rufe idonka ka tashi mu fita sun saka wuta uncle "Afrah ki fita kawai kinga wutar ta kawo a bakin qofa ki tashi ki fita !a rud'e ta kalli bakin qofa wanda hakan ya bata tabbacin zagaye gidan sukayi da wuta.
Cikin kuka sosai ta juyo tana fad'in "uncle ka tashi mu fita kar wutar ta fara yawa"
ta fad'i hakane yayinda   take qoqarin tallaboshi yayi saurin dafe inda aka harbeshi yace"Afrah bazan iya d'agawa ba ki tafi kawai ,wani  irin kuka ta fashe dashi tace"uncle ni bazan fita ba sae tare da kai,idan kuma baza ka iya ba sai dai mu mutu a tare"Afrah ko na fita ba lallai bane na rayu ,sbd sun harve ni inda bana tunanin zan rayu....a'a uncle zaka rayu ka tuna kaifa ka ce min ba a yanke qauna daga haramar ubangiji,,haka ne Afrah amma.... sae kuma ya kasa iyar wa sae idanuwansa dake qoqarin rufewa ,
murya can can qasa yace"pls Afrah ki fita nace"shine abinda ya furta na qarshe se idanuwansa suka rufe ruf..... Wayyo Allahna uncle dan Allah ka bud'e idonka kar ka tafi ka varni!.
Kuka ta shigayi sosai tana jijjiga shi tàna kiran sunan shi amma ba alamar zai motsa ga wutar duk ta zagaye gidan tana ci gaba da ci.

*Billy giro😊&Futha Luv💅*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:22PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [ 10/25/2016] Billy giro😊: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futhalurv.WordPress.com*

*```🏅63🏅```*
Rungume sa tayi qam a qirjinta tana ta kuka a cikin kukan ne taji yayar mutane a waje sae taslima suke .

Da hanzarinta ta tashi domin ganin wanda ke shigowa wato JB da mahaifin sa taje ta rungume Abban Jb tana kuka tana fad'in"Abba sun kashe min uncle ,sun kashe min gwaggo sun kuma tafi da Amrah,

ta qarashe maganar cikin kuka sosai.

Mahaifin jb wanda ba kowa ya sanar dasu halin da ake ciki ba face mai gadi da ya samu ya farfad'o kan wata powder da suka shaqa masa ya some shine yana farfad'owa ya lalubo er wayrs da en fashi suka manta basu kar6e ba ya kira mahaifin JB kasancewar yana da numbar sa ,sbd shike masa gadi da rana sannan yazo nan yayi na dare.

Komai Abban Jb ya kasa cewa sbd jimamin da ya shiga ciki,en sandan da ya kira ne suka zo suna fad'in Alhj kunyi gigin shigowa fa wutar tana ci sosai, yace "dole ne dmn duk na rud'e naga na ceto ran 'yayana.

Yana gama fadar haka en sanda suka kama aka fitar da farhan wanda da qyar suka iya tsallake wutar suka fito sannan aka nufi 6angaren gwaggo wacce still tana nan yanda take, ita ma d'aukar ta akayi aka sata cikin mota.

Asibiti aka tafi dasu wanda cikin gaggawa aka kar6e su .

Bayan an shiga theater room dasu ne Abban JB ke waya da commissioner en sanda yana

sanar dashi halin da suke ciki yayinda yake son ayi gaggawar tura motar en sanda  a tare hanyar fita gari da ta shiga a kuma yad'a en sanda ta koina ko za'ayi nasarar gano su kafin su illata Amrah. Haka kuma yayi waya da en kashe gobara kan suje su kashe wutar da ke ci gidan farhan.

Sannan ne ya samu er natsuwar kallon  Afrah da JB keta faman rarrashi,shima ya saka nasa bakin suna kwantar mata da hankali.

Ba qaramin jimawa akayi ba domin tuni gari ya waye sannan aka fito daga theater room ,Afrah ta tashi da hanzarinta ta nufi gun fu'ad dake cire hand gloves tace"uncle dan Allah kar kace sun mutu"kwantar da hankalin ki dmn ba wanda ya mutu a cikin su ,zama ki iya zuwa gun farhan sbd har yanzu gwaggo bata farfad'o ba but anyi mata aiki an cire harsashin da ke cikin qafarta, haka nan bada jimawa ba inshAlh zata farfad'o.

Da gudu take zuwa d'akin da ya nuna mata farhan yake, sae dai ba qaramin tausayi ta bashi ba domin ko farhan d'in ba wai ya farfad'o bane.

Da shigar ta d'akin ta nufi gadon da farhan yake se ta tsaya cak duk wani  kuzarinta ya rage, sae kallon sa take da tsoro  sbd bashi da maraba da gawa,gashi duk a tunaninta zata zo ta same shi ya farka.

Wani tunani ne ya fad'o mata a rai wanda yasa ta fashe da wani sabon kuka, taje a hankali ta kwanta kan jikin sa tana ci gaba da kukan.

Ta kalli fu'ad da ya shigo shida  JB da kuma Abban JB tace"uncle fu'ad ya naga uncle bai farka ba kwata kwata baya motsi har yanzu?zai farka kinji... yaushe?shiru yayi sannan yace"idan allurar da aka masa ta sake shi,inshaAllah zai farka indai har aikin da aka masa bai zo da wata matsala ba, don haka ki daina ta6a sa hka sbd kinga kusa da zuciya ne aka masa aiki akwai had'ari sosai ga ta6a gurin.

Tace"to zan iya zama kusa dashi ?eh ba matsala ,nan ta share hawayenta  taja kujera kusa dashi ta zauna tana jiran farfad'owar sa.

*Billy giro& Futha luv😊*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:22PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [10/26/2016] Billy giro😊: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futhalurv.WordPress.com*

*```🏅64🏅```*
Tana nan zaune sae kallon farhan take har dai gunda aka masa aiki wato inda aka cire masa harsashi, haka tayi ta bin jikin sa da kallo sae tunanin rayuwar su ta jiya take kafin suyi bacci sae gashi yanzu shine a kwance komai baya iya yi wanda idan aka ce mata ya mutu bata san ya zatayi ba.

Hawaye ne ke silalowa a hankali kan kumatun ta ,ta share hawayen tana tuna ko sallah bata yi ba gashi se tayi wanka wanda kan tunanin rayuwar su ta jiya ce ta tuna mata da hakan,sae kallon rgr jikinta tayi tasan ba wanda ya saka mata ita face farhan,Allah yaso ta farhan mutum ne mai yawan ibadah da bai maida dare domin bacci kad'ai ba,
da ba don hakan ba da sun riske ta a yanda take, da baqin cikin zai fi mata yawa a rayuwa wanda har ta mutu bazata ta6a manta hakan ba ,still baza ta ta6a manta hakan ba domin ko a tahiri bata ji wanda irin wannan mummunan abu ya faru dasu irin yanda ya faru dasu kai tsaye ba,,haqiqa Allah mai jarabatar bawan sa ne ga wanda yaga dama ga kuma wanda yafi so domin ya qara gwada imanin sa,hakan yasa baza tayi kuskuren tunanin cewa don Allah baya son su ne ya musu haka.

JB ta kalla wanda tun d'azu yake ta faman kallonta yayi saurin kauda idonsa sbd ba a son ransa ya tsare ta da ido ba.

tace"uncle jB ina son nayi sallah amma bana da hijab kuma.....sae tayi shiru tana qarewa d'akin kallo ganin toilet yasa ta sauke ajiyar zuciya,yace"sae kuma me Afrah?ta duqar da kanta tace"sae kuma tufafi "yace "to"ya kama hanya zai fita Abban shi yace"gidan nasu zaka tafi ne?Aa wai da zan tafi gida na kar6o mata a gurin Nina ,Aa muje gidan nasu kmr wajen gidan kad'ai ya qone, shiyasa nake son a rufe musu d'akuna kasan wasu na zuwa da sunan taimako alhali ba haka bane, marasa imani ne wad'an da basa tsoron had'uwar su da ubangiji bare suji tausayin halin bayinsa da suka shiga ciki,sae ma qoqarin qara saka su wani halin suke na ganin sun qarasa kwashe d'an abunda ya rage musu.

Suna fita Afrah ta fad'a toilet tayi wanka

tana fitowa ta nemi guri ta zauna jiran dawowar su,wanda bata jima da xama ba sae ga JB ya dawo ,ta kar6i kyn tana masa godiya, har zai fita sae kuma ya tsaya ya d'an juyo kad'an yace"shike nan kike buqata ko da wani abu? Aa bana buqatar komai,, but ya kamata kici wani abu Afrah,bana jin yunwa...Aa bari dai naje na kar6o miki a gida nasan sun isa kammala break fst.

Bata iya ce masa komai ba ta barshi ya fita ,
amma sam ita bata jin zata iya cin wani abu, domin tashin hankalin da take ciki ko yunwa ma bata ji, fatar ta d'aya Allah ya farfad'o da farhan da gwaggo ya kuma sa a gano Amrah ba tare da sun mata komai ba.

Bata damu da hawayen da taji suna sauka kan kumatun ta ba ta nufi toilet domin saka tufafi. Bayan ta fito tayi sallah, ta jima tana kai kukanta a gurin ubangiji wanda ako yaushe yana kusa da bawansa musmman mafi kusa dashi wato mai yawan ibadah da kuma yawan ambaton sa,wanda tasan yana jinta kuma zai share mata kukanta inshaAllah.

Bayan ta gama taje kan kujerar da ke kusa da farhan ta zauna tana tunanin ko ya Amrah take ciki yanzu.

** ** **

6angaren Amrah kuwa tunda suka tafi da ita kuka take tana tunanin wane hali Afrah ,gwaggo ,Farhan suke ciki yanzu,ko Afrah ta sami fitar da farhan? shin ita gwaggo fa tana raye ko kuwa ta mutu?,ya mahaifinta zai ji idan yaji an tafi da ita a kasancewarta na 'ya qwaya d'aya tal a gunshi ?haka take ta yiwa kanta tambayoyin da ba amsa, sae kuma ta sake fashewa da wani sabon kuka wannnan wace irin musiba ce ta same su haka a lokaci d'aya.

Duk tana wannan tunanin ne a cikin wani d'an qaramin d'aki mai duhun gaske da komai bata gani hatta tafin hannun ta ,ga gurin very stationary ,
motsin komai ba a ji hakan yasa ta kame guri d'aya cike da tsoro har bata son yin wani dogon motsi.

Yini akayi zungur ba wanda ya farfado tsakanin gwaggo da farhan iya damuwa Afrah ta damu domin yinin ranar ko abinci taqi taci sae kuka take tana magana da fu'ad da ya shigo d'akin dmn ya qara kwantar mata da hankali bata bar yace komai ba ta tashi tana kuka cikin dasasshiyar murya tace "uncle fu'ad dan Allah ka snr dani gsky wai ko basa raye ne ake 6oye min"Afrah kiyi haquri ki kwantar da hankalin ki lokacin farfad'owar sune bai yi ba,uncle fu'ad wace irin allura ce da tuni an gama masa aiki amma har yanxu bata sake shi ba,gashi nan tun safe still bai motsa ko qaramin yatsan sa ba at all ma ko numfashi bana ganin yana yi,haka ma gwaggo har yanxu ko damar ganinta ba'a bani ba.
Cikin kuka sosai ta qarashe mgnr.

Shiru fu'ad yayi cike da tausayi domin tuni gwaggo ta farfad'o amma wani tashin hankali ne idan Afrah ta ganta sbd numfashi take sama sama kmr wacce zata mutu kan hawan jinin da yayi mata mugun kamu shiyasa aka mata allurar bacci.

Da alamar rarrashi fu'ad ya kalli Afrah wacce kallo d'aya xakayi mata kasan a galabai ce take da jin yunwa duk ta wani hargitse ta fita hayyacinta kmr ba ita ba.

Da sauri ta kai xaune sbd jirin da ya d’ebe ta ,ba shiri ta riqo hannun farhan gam sbd yanda

take ganin komai na d'akin na juya mata.
  Sulalewa take qoqarin yi sae kawai taji hannun farhan da ta damqe yana motsawa a hankali.

*Billy  giro 😊&futha lurv💅*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:22PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [8:36PM, 10/27/2016] Billy giro😊:  10/27/2016
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futhalurv.WordPress.com*

*```🏅65🏅```*
_muna Allah ne,kuma haqiqa mu masu komawa ne zuwa gare shi.Ya Allah ka bani ladan haqurina akan wannan masifa, kuma ka mayar min da abinda yafi alhairi._
  _Ya Allah!babu wani  abu mai sauqi sae abinda ka sanya shi ya zama sauqi,kuma kai kana sanya tsanani idan kaso ya zama sauqi. Da haka nke rqonka Allah ka sauqaqa mana wannan al'amari_
  Duk maganar tana fitowa ne daga gurin farhan wanda bai riga ya bud'e idon sa ba ,bai kuma bud'e bakin sa ba, a cikin zuciyar sa ne yake magana da ubangijin sa.
  Afrah kuwa tunda taga hannun sa ya motsa ta qara matsawa kusa dashi tana kiran sunan shi a hankali.
  Kad'an kad'an ya shiga bud'e idonsa har ya sauke su a kanta, bai ce komai ba sae yunqurin tashi yake se yayi saurin dafe inda aka harbe shi yace
  _"Bismillahi!Bismillahi! Bismillahi!_
  Sannan yace" _A'uzubillahi wa qudratihi min sharrama ajidu wa uhaziru_"

Ya fad'i haka sau 7.
Sannan ya kwantar da kansa kan qirjin Afrah wacce ta tashi da niyar taimaka masa ta shiga shafa sumar kanshi tana fad'in"sorry uncle"
murya can ciki yace"Afrah gwaggo fa?uncle fu'ad yace tana raye amma Amrah har yanzu ba labarinta,ga Abbanta sosai ya damu har ma kuka yake "ta fad'i haka ne tare da share hawayen da suka zubo mata.
Yace"haqiqa Allah ba azzalumin bawan sa ba ne,kuma yafi mu sonta shida yasa hakan ta faru da ita ,kuma ba abinda zasu iya mata wanda Allah bai mata ba, da yardar Allah zata dawo lafiya qalau ba tare da sun iya mata komai ba.
Allah yasa haka uncle, Amin.
Afrah ta zauna kan gadon a hankali kusa dashi dmn yaji dad'in qara kwanciya a jikinta, tana zama kuwa ya qara gyra kwanciyar sa akan qirjinta ya shafo cikin ta yace"what about my unborn child?lafiya and u? am fine, ba inda wuta ya ta6a ki ko kika ji ciwo? Alhmdlh ko d'aya, "Alhmdlh" haka shima ya fad'a sannan yace"Haqiqa Allah shine abin godiya domin babu wanda yafi cancanta ama godiya sae shi.
Fu'ad da ke tsaye sae yaji d'an uwan nasa ya qara birge shi sbd tawakkali irin nashi.
Ya matsa kusa da su yana masa sannu da kuma jajantawa akan abinda ya same su.
Sannan ya duba shi ya umarci Afrah da ta bashi fresh milk ya sha.

Shi ya d'auko mata fresh milk ya tsiyaya a cup ya bata sbd ganin yanda farhan ya samo kwanciya a jikinta ba zai so ta tashi ba.

Bayan ya fita ne Afrah ta shiga bashi wanda sae da ya tilasta ta ita ma tasha sbd ya fahimci yunwa take ji.

Bayan sun gama sha ta zaro tissue dake kan bedside drawer ta goge mishi bakin sa yace "Afrah ina son nayi wanka nayi sallah"tace zaka iya uncle? zan iya .

Da taimakonta yayi wanka yazo yana sallolin da ke kanshi wanda yana yin komai ne cikin juriya.

Bayan ya kammala Afrah ta taimaka mishi ya koma kan bed tare da jinginawa a jikin pillow,ta d'auko grapes tana bashi yana ci.

6angaren leesa kuwa zaune suke ita da mom farida tana"fad'in gaskiya mom farida naji dad'in haraka da mutanen nan sun iya aiki sosai matsala d'aya ita ce harbin farhan da sukayi wanda shi zai kawo mana tsaiko game da sa hannun da zai mana a kan takardun Afrah,wanda hakan yasa nace suje da Afrah sbd muyi garkuwa da ita ta yanda dole zai sa mana hannu akan takardun sbd sae da sa hannun sa ne ko zata koma hannun shi..... Ai kuskure mu kayi da kuma mantuwa dmn da en fashin muka bawa da yanzu har dasu ansa hannu amma ko dukiyar sa kad'ai ta ishe ni facaka in yaso na bawa wad'an can mutanen su san dabarar da

sukayi suka mallaki dukiyar (cewa da en uwan mahaifin Afrah).....Hm mom farida kenan kema dai zancen kike so, nida na mallakawa en fashin komai da suka kwaso.....zumbur mom Farida ta miqe tace"kina hauka ne! Kmr ya mom  farida ai banyi da ke zan baki wani  abu ba kuma kinsan ni ba abinda zanyi da dukiya tunda mahaifina yana da ita,,,haba leesa amma kinsan ya kamata a bani wani  abu ko...a gsky banyi wannan tunanin ba sbd takardn Afrah ba qaramar dukiya bace idan kika mallake su ba wani  abn da ya rage wanda xaki nema, kuma kinsan wannan karon ba makawa zaki mallake su dmn tuni Afrah na hanun su, ba kuwa za a sako ta ba sae idan farhan yasa hannu akan takardun ko kuma abu mai sauqi ma zanje da kaina tasa hannu a takardun sannan ko za a sake ta.
 Nida da kaina ma idan tasa hannu sae na maida ta har qofar gidan nasu tunda naji ance bai wani  qone ba aka kawo musu taimako but ba mtsala ta bane domin yanzu ban kai ga Babban burina ba  tukun wato ganin bayan farhan....wai da gaske keda kanki zaki sa a kashe farhan? Uhm mom farida kenan ba dai da naji bazan mallake sa ba,kuma kinsan wani  at all yanzu bana jin son sa bashi kad'ai ba ma bana jin zan sake son wani  d'a namiji ba don  komai ba sae don sabuwar harakar nan da na fara nida qawata ta Oman to tunda nayi nisa a wannan harakar sai naji duk wani d'a namiji ya fita a raina domin ba wani  abun da zai min wanda mace baza ta min ba,sbd mace da mace yafi dad'in haraka har nake ji ina ma ace ana auren mace da mace da ina d'aya daga cikin wad'an da zasuyi hakan amma ko haka ma ba matsala bace tunda muna had'uwa a duk lokacinda muka so..oh leesa wata harakar kuma kika samu?Uhm mom farida a bar xancen kawai har idan na dawo mayi maganar ,mom farida ta girgiza kai tace"kedai ko wace harka sae kin shiga,, to mom farida ka zauna ayi ta baka labarin komai ai gwanda mutum yayi ya xamo cikin masu bada labari.
   Tana gama fad'ar haka taja makullin mota da mayafi ta fita.

Bata zarce koina ba sae ma6oyar da Amrah take suna bud'e dakin ta shiga ,a mamakinta sae taga Amrah tace dasu"ya haka ai wannan ba matar sa ba ce qawar matar ce? ogan ya kalli Amrah yace"ke!dan gidn ku ya mukayi da ke ba ce mana kika yi kece matar sa ba...... Hm kaga barta fita kawai ka bani guri nasan yanda zanyi da ita.
  Yana fita taje gaban Amrah,wacce sae màmakin gnin leesa take.
 Lessa na qare mata
 kallo tace"show d'in ya birgeni fa dmn kin nuna ke aminiyar ta ce ta gaske ,da kmr zai yi wuya a samu wacce zata iya yin hakan, sae dai kinyi kuskure babba da kika sako kanki a cikin inda ba a saki ba,abinda ba amin kenan wai shigar tsugula,amma ba wani  hukunci da zan miki zaki fita lami lafiya sae dai da sharad'i ,
bazan shaqo motar banza naxo ba dmn kin 6arar da abinda ya kawo ni don haka samun lafiyar ki shine  kimin abinda nake so,ta zaro takardu ta miqa mata had'e da biro tace"so nake qawar ki ko kuma mijin qawar ki wato farhan,ki san yanda zakiyi d'ayan su yasa hannu akan takardun" Amrah ta kalli takardun wad'an da ke yawo da sunan Afrah kuma sak ta fahimci takardun mene ne,hakan ya qara mata tabbacin cewa da sa hannun leesa aka yi fashin tunda har kadarar Afrah taje hannun ta dmn ita a tunanin ta a cikin fashin ne aka d'auke su .
A sanyaye  tace"ya zance musu idan na kai takardun?oho miki ke kika sani,ni muradina kawai a

samin hannu idan kuma kinqi ba makawa zan maido ki ne.
Amrah tayi shiru tace" yanzu farhan da Afrah suna ina ne hln? Suna asibiti, can zan kaiki yanzu idan kuma baza ki iya ba sae na barki dmn ni ina da hanyoyi da dama ba wai dole sae da ke ba,me kika ce?
Amrah tayi shiru tana tunain gara kawai ta yarda tabita in yaso tana zuwa ta sanar da farhan azo a kama ta.

Tace"na amince zan biki"

Tafe suke cikin mota Amrah sae kallon leesa take da mamaki me farhan da gwaggo suka mata da tasa aka musu haka,lallai kuwa yau xata sa a mata kamun wulaqanci,sbd dama can leesa bata birge ta bata kuma yarda da ita ba dmn tun lokacin da ake je musu visiting da leesa ta fara ganin wasu alamomi a tare da ita.
6angaren leesa kuwa waya ta jawo bayan ta gama ta tsaida motar suka kwashi kusan minti talatin a zaune,sannan taji shigowar waya tayi sh'umin murmushi tare da d'aga wayar tace"kaddai kace min har an samo shi, yayi kyau bani shi, nan ta saka speaker tace da Amrah "ki saurari muryar kiji ko zaki iya fhmtr ta waye"
Hankalin Amrah ne yayi mugun tashi da jin muryar mahaifinta yana ta basu haquri "leesa ta katse wyr tace"kin gano muryar waye ko na qara sa miki? cikin muryar kuka tace"Abbana ne don Allah meyasa kika sa aka kama shi? Uhm lallai ma to ke a tunanin ki haka kawai surnugudu zan bar ki ki shiga asibiti ba tare da na riqe wani abu naki ba,ko kin d'auka ban san mahaifinki bane? Nidai kiyi haquri dan Allah kisa a sake shi,,,sa hannu a takardun nan tamkar an saki mahaifinki ne, kuma kar ki kuskura ki sanar da farhan nice na aiko ki dmn nasan kinyi banzan tunani ki snr da farhan a kama ni,idan kuma kinyi hakan wlh mahaifinki ba zai ta6a fita ba dmn ko kashe ni za'ayi bazan fad'i inda yake ba, kuma bazan ta6a bada damar a sake shi ba koda na fito kuwa ,don haka sae ki san yanda zakiyi ki fitar da mahaifinki ba tare da kowa yasan wanda ya aiko ki ba.
Hawaye ne suka zubo zar a kumatun Amrah ta kalli takardun tana tunanin ita ta yaya tasan zata yi haka❓

*Billy giro😊& Futha luv💅*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:22PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [10/28/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futhalurv.WordPress.com*

*```🏅66🏅```*
Wani  tunanin ne ya fad'o mata a rai ta share hawayenta ,ta kalli leesa tace"shike nan muje,, Uhm ashe dai kina son mahaifinki sosai but me zaki ce musu idan kinje?kedai kawai kince hannu kike son a saka miki a takardun ba tare da sun san wanda ya aiko ni ba,,,eh haka ne,,, to kawai muje ni nasan yanda zanyi da su.

Sunyi tafiya mai nisan gaske kafin suke shigowa cikin gari,Leesa ta parker dai dai gurin wani shagon tufafi da takalma  taje ta siyo ma Amrah Arabian gown da takalmi ta dawo, ta bata tare da fad'in "kar6i kisa kuma kiyi sauri karki 6ata min lokaci"cikin qanqanin lokaci kuwa ta shirya .
  Suka je sae asibiti,leesa ta gaya mata ward d'in da zata je da kuma room .

Cikin sallama Amrah ta tura qofar d'akin dai dai Afrah ta tsiyaya ruwa a cup  zata ba farhan ta saki cup cike da murna ta maqalqale Amrah.

 Bayan sun gama murnar su ta en mintina ,farhan da Afrah da, fu'ad sae tambayoyi suke jefowa Amrah idan en fashin basu mata komai ba tace"ba abinda suka min"
   "Alhmdlh"shine abinda kowanen su ya furta.
  Sae tayi shiru tana mai kallon su kafin take snr dasu abinda ya kawo ta ,ma'ana duk yanda sukayi da leesa da kuma mahaifin ta da tasa aka d'auke duk ta sanar da su.
   Sosai suka shiga tashin hankali da mamaki , farhan yace"muga takardun na mene ne"

Yana kar6a ya miqe zumbur dmn sam ya manta da ciwon da ke jikin sa sae da Afrah tayi saurin kama shi.
   Yace"Afrah dukiyar ki ce fa da Abbanki ya bar miki ,kenan dama can leesa en uwan Abbanki ne suka tura ta,,impossible wannan dukiyar baza ta ta6a ciyuwa gare su ba wlh"Amrah yanzu ina leesan take? Tana daga waje can gurin  parking space,,,da hanzari yake qoqarin fita d'akin, Amrah tayi saurin dakartar dshi tace"uncle idan kaje fa Abbana ba zai fito ba"
a sanyaye ya dakata yace"yanzu ya kenan?ni a tunani na....sae kuma tayi shiru bata san me zata ce ba tace"uncle mu zauna ayi maganar.

Nan suka zauna su dukan su suna sauraren me zata ce tace"me zai hana a sa mata hannu in

yaso idan ta sako shi sae a kama ta"
wani  tunani farhan ya shiga yi yace"bana son kuskuren saka hannu a kan originals d'in nan....sae ayi fake mana cewar fu'ad, farhan yace"da wane lokacin kasan fa jiran ta take, Amrah tace"yanzu kmr wane lokaci abun zai d'auka? Fu'ad yace"baza a d'auki wani  lokaci ba sbd ina da wanda zai min akin cikin gaggawa sae dai gaskiya aikin ba zai samu yau ba sbd dare yayi sae dai ko gobe,farhan Yace"to Abbanta da yake hannun su fa sannan kuma me zata ce ma leesa idan ta koma  ba tarardun? Fu'ad yace takardu mai sauqi ne,sae a canza takardun a zuba wasu a cikin file d'in...hm fu'ad hakan ba zai yi ba....zai yi uncle....ta yaya Amrah?kawai dai da yardar Allah baza ta bud'e file d'in ba,,to idan har Allah yasa hakan what about ur father zai kwana a hannun su kenan?ai ko ni kaina nasan zata maida ni inda ta d'auko ni,,,fatana kawai Allah yasa kar suyi ma Abbana komai,ko basu masa komai ba, ba dad'i ya kwana hannun su,abubuwa zasuma Abbanki yawa ga tunanin an d'auke ki sannan kuma shima an tafi dashi,hawaye ne suka zubo mata tace"ba komai uncle inshaAllah Abba zai jure kuma zan roqeta kar ta bari a masa komai"to yanzu idan kinje me zaki ce mata?zan nuna mata ba a bari a ganka sbd anyi maka allurar bacci ana son ka sami hutu da zai iya d'aukar 1hur or 2 then about Afrah zance ba inda ban duba ba amma ban ganta ba.... kina ganin hkn zai sa ta yarda? Eh uncle bcs Abbana fa yana hannun su tasan dole na matsu a sake shi,tunda nace mata banga Afrah ba zata d'auka da gaske ne d'in, kuma ni kaina ina hannun ta ba dawowa zanyi ba ko hkn zai sa ta yarda da zance na,fu'ad ya nisa yace to shike nan kawo file d'in a canzo takardun.

Nan ya kar6a ya fita zuwa office dinsa Amrah tace "gwaggo fa?Afrah tace muje ki ganta amma bacci take bata jima da komawa ba.

Bayan sun dawo suka samu fu'ad ya dawo ya bata file d'in tare da zaro er qaramar wyr Nokia a aljihun sa yace"ki riqa in case off,but ki barta a silent kar ta san kina tare da ita"

Bayan ta fita ne Afrah ta kalli farhan kmr zata yi kuka ya jawota jikin sa yana lallashi tace"uncle Amrah ta ban tausayi yanzu fa Abbanta yana a rufe ita ma zata je a rufe ta kan abinda ba nata ba,bana mahaifin ta ba,gashi mutanen basu da imani abu kad'an se su harbi mutum yace"ki kwantar da hankalinki Allah yana tare damu inshaAllah ba abinda zai sami ko d'ayan su"

Amrah kuwa tana zuwa ta sami leesa sae kallon agogon hannunta take jiki sanyaye ta bud'e motar ta shiga tace"kiyi haquri kinga na jima sosai koda naje ba a bari a shiga aga uncle yana bacci kuma ana buqatar ya huta shiyasa aka hana kowa shiga....Afrah fa?a kan nemanta ne ma na jima amma duk inda nake sa rai ban ganta ba,kuma duk su uncle JB basa nan bare na tambesu ,,,ya za'ayi kenan?sae abinda kika ce,, sanin kanki ne bazan sa a saki mahaifinki ba kema haka dole zan myr da ke,ba komai ki maida ni d'in in yaso gobe da safe ki sake d'auko ni mu dawo,amma don Allah kar a ma Abbana komai.
"Kar ki damu"tayi mgnr a taqaice
taja motar  suka kama hanyar inda suka fito,har sun fara nisa, sae kawai ta juyo motar da

alama cikin gari zasu koma ko me dalili oho.

Bata zarce koina ba sae gidan su,bayan ta parka mota tace"bani file d'in takardun, ta kar6a tace"oya zo muje daga ciki.

*Billy giro😊&Futha Luv💅*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:22PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [ 10/28/2016] Billy giro😊: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futhalurv.WordPress.com*

*```🏅67🏅```*
Har suka shiga gidan ba abinda Amrah keyi sae addu'a Allah yasa kar leesa ta bude file din.
Da shigar su ta nuna mata d'akin da zata zauna ta fita ,Amrah tabi d'akin da kallo sannan ta nemi guri ta zauna.

Leesa kuwa d'akin mom farida taje ta same ta tana cin abinci tana ganinta ta ture plate tare da fad'in "Allah yasa anyi nasara"

Leesa ta sauke ajiyar zuciya ta cire mayafi ta zauna tace"kwantar da hankalin ki gab muke da yin nasara dmn yanzu haka ina tare da Amrah a cikin gidan nan....Amrah ko dai Afrah? Amrah dai qawar Afrah.
Nan leesa ta kawo labari ta bata duk yanda akayi,,,mom farida tace "ke yanzu kin yarda ba wata qulalliya ce ta shirya miki ba? Mom farida ta ma isa mahaifinta fa yana hannu na kuma har ga Allah idan har qulalliya ta shirya min na azo a kama ni wlh bazan fad'i inda Abbanta yake ba

koda kashe ni za'ayi kuwa,shiyasa ma tun a asibiti ina ganin ta shiga na kira su na sanar dasu koda sunji an kama ni su kashe shi kawai su jefar sannan su ma su sani inda dare yayi musu,ni kuma dole ko don kud'in Abbana za a fitar dani lami lafiya ba duka ba zagi, kinga kenan wa gari ya waya...su,, aha mom farida shiyasa kika ga hankali na a kwance,nasan indai naira ke aiki to kuwa bani da matsala.

Mom farida tace"wai kinsan wani abu? Aa sai kin fad'a,wai su Hajiya luba zasu shigo gari gobe (idan baku manta ba Hajiya luba ita ce kishiyar mahaifiyar Baban Afrah wato Alhj sadiq)

leesa tace"au su tun basu ji an sa hannu ba zasu kwaso jiki suzo... Inafa ban sanr dasu ba ai, wai cewa sukayi sun gaji da jiran tsammani idan bazan iya ba,su zasu zo suyi da kansu,shine nace Allah ya kawo su lafiya... Kika ce musu?eh man to so kike har su gano ni bayan kin san basu da imani komai suna iya aikatawa akan kud'i tunda har suka sa aka kashe d'an uwan su Alhj Sadiq bare ni da en uwan takan bai kai can ba, hm Mom farida kenan ai su en uba ne don sun masa wani abu ba mamaki, kedai bari kawai mutanen ne sae a hankali ,kenan raba dukiyar zakuyi... da wa hm Allah kad'an zan basu nace ba a sa hannu a sauran takardun ba in yaso na 6alle na tafi zuwa cin duniyata bisa tsinke sae a lafira ko muna had'uwa dmn nida dawowa Nigeria sae kuma wanda ya gani.... Hhhh mom farida ashe dai zanyi missing ,ba wani missing idn kin buqaci gani na ai kya hau jirgi, haka ne fa.

Ni kuwa mom farida akwai wani lkc da naji kince wai Afrah en biyu ce ,shin wai d'ayar ta mtu ne da naga takardun da sunan Afrah kad'ai suke yawo ?, hm leesa wannan zancen sam ban ta6a yinsa da kowa ba, ko a rnr kuskure nayi na d'auko miki zancen shiyasa nayi saurin daina shi na d'auko wani zancen,,,mom farida ni har akwai wani abu da zaki 6oye min ,,leesa wato zancen ina matuqar jin tsoron a jishi sbd abinda ban ta6a yi bane a rayuwata, amma ke nasan zaki iya 6oye min sirrin .

Wato tun kafin Abbn Afrah ya auro ni en uwansa suka so ya aure ni shi kuma yaqi yarda da hakan sbd irin matuqar son da yake yiwa maman Afrah wato Hajiya Zarah wanda su suna nuna mishi don ya sami qaruwa ne suke son ya aure ni,

amma gskyr abun so suke na aure shi sbd dukiya,sae gashi Hajiya Zarah ta sami ciki bayan tuni na kwad'aitu da son na aure shi ba don komai ba sae don dukiyar sa,ina jin matar sa ta sami ciki na san ba yanda za'ayi ya aure ni tunda dama can baya so en uwansa ne keyita son tursasa shi har su samu ya amince,shiyasa sukayi baqin ciki sosai da jin Hajiya Zarah ta sami ciki dmn ganin suke plan d'in su ya watse, ni kuma a gurina sam na kasa haqura har dai idan na tuna irin d'inbin dukiyar sa, wacce nasan bazan ta6a nasarar cinta ba indai Hajiya Zarah na raye,daga nan ne fa na shiga tunanin yanda xanyi na kawadda ita duniya dmn na samu na aure shi,wanda banyi nasarar kashe ta ba sae bayan ta haifu, inda sam ba haka naso ba, naso ace kafin ta haifu ne na kashe ta,sbd bana son Alhj Sadiq ya kasance yana da magaji ,da wannan tunanin ne naga ko 'yayan ma bazan iya bari ba,shine na samo wata mata akan zan biya ta kud'i masu yawa idan ta taya ni d'aukar 'ya'yan har mu bar asibitin ba tare da an gan mu ba,d'ayar kawai muka iya d'auka sbd ina kashe Hajiya Zarah gabad'aya na rasa natsuwa ta wanda ni ya kamata ace na d'auko d'ayar amma rud'u bai barni ba, ni dai kawai naga na fito asibitin ba tare da an kama ni ba.

To bayan fitar mu ne matar ta roqe ni idan har kashe er zanyi tana son na bar mata ita,kai tsaye kuwa nace ta d'auka sbd ni kaina ban san ma me zanyi wa er ba muradi na kawai na raba ta da mahaifin ta,nan na biya mtr jingar da mukayi ta tafi da er wacce har yau ban qara sata a

ido ba.

Kinji yanda abun yake wanda ko su Hajiya luba basu san yanda aka yi ba kawai dai sunga abun ya faru.

Leesa ta nisa tace "lallai mom farida dole ki damu da dukiyar nan tunda kikayi abinda baki ta6a yi ba a kanta"hm kedai bari kawai amma na roqe ki wannan abun ya zama sirri"

Kar ki damu indai nice to ko a lafira da ace baki ke magana da baza aji wannan zancen ba.

Wani abu da basu sani ba shine duk wannan zancen da suke yi sak a kunnen Amrah dake la6e tana jinsu.

A rikice ta koma d'akinta ta shige toilet ta kira fu'ad ta sanar dashi duk abinda taji komai bata rage ba.

Hakan yasa ,Uncle Basheer, JB ,Fuad,suka had'u a d'akin farhan dake nan asibiti suka tsara duk yanda za a kama su leesa gove da safe.

Bayan sun fita ne farhan ya rufe d'akin da key sbd yana son ya rarrashi Afrah wacce tunda taji labarin take ta kuka dmn jin take kmr yanzu ne abin ya faru,qarin kukan ma bata san cewa ita en biyu bace sae yau.

Jawota yayi ya rungumeta yana ta rarrashi cikin natsuwa amma kmr qara mata yake duk tayi zufa zufa kan kuka.

Nan ya cire mata komai na jikinta ya d'auke ta sae zuwa toilet ya mata wanka suka fito suka zauna kan sofa yana ci gaba da rarrashinta dmn har yanxu kukan take.

Kallon ta yake ya rasa me zai mata ta daina kukan ,nan ya riqo kumatun ta yana kallon hawayenda ke sauka,ya d'ora harshen sa ya lashe hawayen tas ya kuma had'e bakinsu guri d'aya yana mata light kiss da yasa ta shiga sulalewa a hankali kan sofa shi kuma yana binta har suka kai qasa,ya zare mata towel yana ci gaba da aika mata manyan saqonni masu nauyi da rikitarwa.

Sae da ya tabbatar ta sami natsuwa sannan ya barta,ya d'auke ta suka koma kan sofa ta wani lafe a qirjinsa tare da lumshe idonta tana fitar da numfashi a natse,hannunta takai sannu a hankali tana yawo dashi a kusa da inda aka masa aiki kmr tana shafa qwai shiyasa yake jin dad'in abun kmr susar qadangare .

Murya can qasa yaji tace"uncle towel"

ya d'auko towel d'in ya rufa mata jiknta.

*Billy giro😊& Futha luv💅*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

[10:22PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [9:17PM, 10/29/2016] Billy giro😊: [10/29/2016] Billy giro😊: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futhalurv.WordPress.com*

*```🏅68🏅```*
Uncle yanzu dama ni twins ce shine baka gaya min ba,tayi maganar ne cike da qwalla a idonta ,qara rungume ta yayi yace"yi haquri bana son ki sake wani kukan dan Allah"Amma uncle ai dole ne wannan abun da naji ta yaya zan iya ajiye kuka"

Nan ta miqe daga kan jikinsa tana qara rufe jikinta da towel ,ya riqo towel d'in yace ina zuwa? Zan tafi na saka kaya naji kmr za a shigo "kai ya gyad'a mata dmn yaji alamar hakan ,ta shiga toilet sannan ya bud'e qofa.

Fu'ad ne ya shigo tare da fad'in "Alhmdlh gwaggo sauqi sae abinda ya qaru har ma tana son ganin ku zata yi magana daku,
a kasin d'auxu da ta farka bata iya cewa komai ba, sosai farhan yaji dad'i yace"Allhmdlh"

But kar a mata zancen su leesa yafi sae anyi settling din komai tukun sbd kar jinin ta ya koma hawa.
cewar fu'ad

Frhn yace"Ai nima nayi tunanin hakan bare idan taji Abban Amrah na hannun su,zata shiga wata damuwa ne,haka kuma bana son taji Amrah na hanun leesa".

Sae da Afrah ta shirya sannan suka je d'akin da gwaggo take .

Suka mata ya jiki tace"Alhmdlh naji sauqi ,ta kalli qirjin farhan tace"kai kuma a nan suka harve ka?eh wlh gwaggo Allah ma yasa inada qarin kwana,,oh to Allah ya qara tsare gaba, yace"amin

amin.
Ta jawo hannun Afrah ta zaunar da ita kusa da ita tace"inace ba abinda suka miki? Allah ya tsare, ba abinda suka min gwaggo, to Allah ya qara tsarewa, Amin, Amrah fa?ita ma ba abinda suka mata,,,to ya ban ganta ba? Ai ta shigo daxu kina bacci.
kmr an d'inke bakin gwaggo bata sake cewa komai ba .
Afrah ta tashi ta d'ebo mata abinci ta shiga bata ,taci kad'an tace ya isheta.

Sun jima sosai a d'akin gwaggo,kafin suke komawa d'akin farhan .
Da shigar su farhan yaja hannun Afrah yace"muje ki taya ni wanka"

Bayan sun fito ne fu'ad ya shigo d'akin ya sami Afrah lafe a gefen qirjin farhan hannunta na yawo a qasan inda aka masa aiki,fu'ad yace"wai kai farhan baka jin ciwo ne idan tana ta6a kusa da inda aka maka aiki,,, kai fa ba zafi baka ga yanda take ta6a gurin bane?uhm to ai yawan ta6a gurin nasa kumburi? Eh to haka ne, amma ciwon rage min yake idan tana ta6awa shiyasa ko bata kai hannun ta ba da kaina zan kai,Sa'a dai kaci jikin naka mai kyau ne sosai kuma harsashin bai fasa jikin ka da yawa ba,amma duk da haka gskiya ina ganin qoqarin yanda kake yin komai lafiya lau kmr ba ciwo a jikin ka.
Ya kalli Afrah yace"ko yau ke zaki masa dressing ne na baku guri?kunya taji ta tashi daga jikin farhan dmn sam ta mnta yanda suke,murmushi kawai fu'ad yayi ya fara cire bandage d'inda ke jikin farhan.

Bayan ya gama masa dressing ya fita,Afrah tace"sannu uncle"
gyad'a mata kai yayi ya miqa mata hannu alamar tazo.
Tazo ta zauna kusa dashi nan bisa gado, ya kwantar da kan sa a kafad'adar ta yana yawo da hannun sa akan qirjinta yace"Afrah bacci nake ji ,idan nayi bacci sae kije gun gwaggo ki kwana kinji,, dama nayi tunanin haka amma kai wa zai kwana da kai ya kula da kai? Ni kinga Alhmdlh ina iya yima kaina komai ba matsala bane,amma ita gwaggo bata iya tashi,,,amma me zai hana uncle fu'ad ya kwana a nan ?sbd naga ba abinda yafi damun sa irin gove a samu a kammala takardun,kuma ai zan iya bacci ni kad'ai ba wani abu bane tunda ba abinda bazan iya ba, turo baki tayi tace"Aa gsky uncle ashe gurin yana duk maka zafi sosai jurewa ne kawai kake kana abubuwa,dmn d'azu na fahimci ba qaramin zafi kake ji ba da uncle fu'ad na maka dressing, my Afrah dole naji zafi ta6a gurin ake ana wankewa fa,to amma shine kake bari ni ina ta6a kusa da gurin, cikin muryar kuka ta qasara mgnr yace"Afrah meye na kuka wlh har ga Allah bana jin zafi don kin ta6a gurin wani abu ma nake ji mai sanya ni bacci da natsuwa,ko kin manta hannun ki kmr auduga yake? Ba wani nan... Haka ne man.
Hannun sa ta kalla da yake turawa a cikin rgr ta tace"kuma kaida zaka yi bacci uncle"ai baccin zanyi"
Shiru tayi tana jin yanda hannun sa ke shafa qirjinta kmr wani mai shafa mata Vaseline,daga haka kuwa yayi bacci abinsa.
Ta tashi a hankali tare da zare hannun nasa a cikin rgrta ,ya bud'e idon sa a hankali yace"zaki tafi kenan? Eh uncle amma ka koma bacci tukun, ta fad'i hk ne yayinda ta koma ta zauna ta d'ora kansa a cinyar ta tana shafa sumar kanshi.
sae da ta tabbatar baccin sa yayi nauyi ta tashi tare da d'ora mai kiss a hankali kan lips ta fito

ta tarar da securities a bakin qofar d'akin kasancewar tunda aka kawo shi asibiti aka zuba matakan tsaro da d'akin sa har na gwaggo.

6angaren leesa kuwa.
Mom farida ce ta shigo d'aki ta same ta kwance tace"wato bacci ma kike qoqarin yi baki bi shawarata ba kenan,no mom farida nabi fa, har na kira su sae dai sunce min suna abuja gun wani operation amma by tomorrow morning zasu biyo jirgin safe.
Oh har naji sanyi a raina na d'auka ko share ni kikayi ,na ma isa mom farida, ai ko banza ina son su zo su min garkuwa sbd tsaro.

Washe gari sae guraren sha biyu fu'ad ya samu aka kammala takardun.
6angaren leesa kuwa bacci tayi abinta sae 11 ta farka taje ta umarci Amrah da ta shirya by 12 zasu fita.

12:20 su leesa suka isa asibiti Amrah na zuwa ba 6ata lokaci aka sauya takardun wato aka saka fake d'in da Afrah ta yiwa signing.

Ta fito ta sami leesa sae addu'a take kada Allah ya ganar da ita komai duk da cewa takardun an yisu tmkar original.
Leesa ta kar6i takardun cike da shu'umin murmushi tana kallon ko wacce takarda an mata signing,tace"kin ceci ubanki yarinya da sae dai wani ba shi ba.
Da haka taja motar sukayi zunzurutun tafiya kmr zasu fita gari,sannan suka keta cikin daji,inda shima sae da sukayi tafiya mai nisa leesa ta Parker motar ta.
Ta kira waya ba jimawa sae ga wani ya fito da Abban Amrah ,Amrah taje da gudu ta rungume shi tana kuka,shima haka leesa tace"kinga ba kuka zaku mana ba, oya ja uban naki ku bamu guri idan kuma kuka sa wasa yanzu nasa a harve ku wlh sae kuyi kukan da tushe.
Da sauri Amrah taja mahaifin nata suka bar gurin.
Sae da leesa ta bar hango su ta shiga tafa hannyenta tana wata irin kafirar dariya ,
sae kawai gardawan en fashin ta suka shiga firfirtowa tace"aikin ku na kyau baku ga alamar ana biye da mu ba dai ko?suka ce kwantar da hankalin ki ba wanda ke biye damu tun daga cikin gari har isowar mu nan,tace"yayi kyau sai.....wayr ta ce tayi qara ta d'aga tare da fad'in"ummana..sae kuma tayi shiru tàna mai sauràren mhfyrta sai duk wani farin cikin ta ya tafi nan take.
Tace"umma komai fa kika ce,gabad'aya kaf kadarorin mu har na Abba!umma garin yaya...kuma!na shiga uku!no umma nasan baza ki gaya min mutuwar Abbana da bakin ki ba, dan Allah umma.....
wayyo na shiga uku na lalace.....ta katse wayar cikin tsananin rud'u ta kalli en fashin da ke zagaye da ita tace da ogan
"operation d'in da kuka tafi jiya a abuja gidan waye kuka tafi?lafiyar ki? Dan Allah gaya min kar ka 6ata min lokaci? Gidan wani Alhj muktar mai dala.... What!!Abbana ne fa!
in a shrug manner yace"and so what!aikin mu ne yazo da hakan!ko kuma don haraka ta had'a

mu dake sae aka ce baza muje muyi wa ubanki fashi ba!
cikin kuka sosai tace"amma Jago kasan hakan yaja mutuwar mahaifina kan baqin cikin kwashe masa dukiya da kuka yi....ai da yanzu har da uwarki dmn da kad'an tsautsayi ya hau kanta mun harbe ta a ka.....U are all under arrest! shine abinda suka ji kai tsaye kmr daga sama.

*Billy giro&Futha Luv*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:22PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [9:34PM, 10/30/2016] Billy giro😊
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futhalurv.WordPress.com*

*```🏅69🏅```*
Tashin hankalin da leesa ta shiga da kuma en fashin abu ne da baya misaltuwa musamman yanda suka ga irin tarin en sandan da ke zagaye dasu kowanen su ya saita bindigar sa suna jirn wanda zai yi yunqurin guduwa su harbe shi.

Bayan leesa ta gama zagaye idonta da kallon police snan ta fad'a kan.

Farhan, Afrah, Amrah, Fu'ad, JB, Uncle Basheer da kuma Abban Amrah.

Ji tayi kmr ta fasa ihu, ta rasa da wanne baqin ciki zata ji, mutuwar Abbanta ko kuma halin da ta tsinci knta a yanzu.

Ba 6ata lokaci aka tasa qeyar su gaba,sae dai suna isa cikin gari akayi hannu biyu dmn zuwa gun su mom farida.

Amrah ce tayi jagorancin nuna musu gidan.
Da isar su suka samu Hajiya luba ita da 'ya'yanta isowar su kenan ko zama ba suyi ba,sukayi arba da police yayinda sukà shiga sanar da su cewa"gabad'ayan ku ana tuhumar ku da sa hannun a kan kashe marigayi Alhj Sadiq mahaifin Afrah wanda ya jima da rasuwa a bisa dalilin en fashinda ake zargin ku kuka tura a gidan sa,dmn tun daga wannan rnr da abun ya faru kuka gudu kuka bar gari aka neme ku aka rasa.

Dam! kowanen su yaji fad'uwar gaba musamman mom farida,da ta saki glass cup din hannun ta,yayinda kowanen su tashin hankali bai bar sun iya cewa komai ba,
sae Hajiya luba ce tayi qarfin halin cewa "kmr ya don mun bar gari sae a zarge mu!bayan lalaura ce tasa muka bar gari!koma yaya ne dai idan munje can kwayi bayani.

Daga haka basu sake tsayawa sauraren su ba suka tasa qeyar su gaba ,
daga mai taslima sae mai d'ora hannu aka har suka isa station,nan suka taradda su leesa wacce baqin ciki ya hanata kuka sae tunanin mafita take inda tana ganin har mom farida an kamo tashin hankalin ta ya yawaita dmn tasan yanzu bata da wata mafita ,mahaifinta dai ya mutu kuma dukiyar da take taqama da ita an kwashe bare mahaifiyar ta tayi tikaniyar ftr da ita.

Ihu ta fasa mai had'e da kuka  sae kuma nan take tyi shiru tana wani  tunanin da take sa ran in tayi hakan zai fitar da ita.
Da yamma su farhan ne suka dawo daga station Afrah tayi saurin tashi tana tambayar farhan ya ake ciki, ajiyar zuciya ya sauke yace"mutanen akwai su da taurin kai dmn ba irin wahalar da basu sha ba amma sun kafe kan cewa su sam basu da sa hannu a mutuwar Abbanki haka kuma basu ne suka tura masa en fashi ba,,but uncle ai Amrah taji komai har dai mutuwar ummana ba zancen tace ba ita bace tunda matar ita ke bada labari da bakinta,ba a fara zancen na ummanki ba tukun sae an shiga kotu... Kotu kuma uncle ?eh man ai dole ne har dai yanda suka dake kan basu da masaniya akan abinda ake tuhumar su ,ita leesa fa da en fashi?duk kotu za'a  yanke ma kowanen su hukunci.

then ki harhad'a komai zamu koma gida yanzu,,har da gwaggo?eh har da gwaggo fu'ad zai riqa zuwa yana dubata kafin naci gaba da kula da ita, ina Amrah take? Tana can gurin gwaggo ko ni nazo d'aukar wayata ne da na manta.

OK to hurry up and pack evrtng,zanje na snr da Amrah ita ma ta packer ma gwaggo komai.

Da isar su bakin qofar gidan Afrah  ta shiga kallon yanda aka gyara wajen gidan aka fente shi tsaf kmr ba wani  abun da ya faru,tace"uncle ya naga har an gyara wajen gidan kmr ba abinda ya faru? Uncle Basheer ne yasa aka gyara mana gidan.

Da dare guraren qarfe goma farhan ne ya shigo gidan sae ga Afrah ta fito da gudu daure da towel ta rungume shi tana kuka ,farhan yace"lafiya Afrah me yake faruwa?qra qanqameshi tayi tace"uncle tsoro nake ji ni kad'ai Amrah ta tafi 6angaren gwaggo kai kuma tunda ka fita se yanzu ka dawo"am sorry ,ita Amrah a can zata kwana ne? Eh nace ta bari ni na kwana a can tace a'a,to shike nan muje daga ciki.

Suna shiga d'aki ya xauna kan bed yana cire kayan jikin sa  yana cikin cire kayan ya kalli Afrah

dake ta faman kallon shi yaje a hankali kusa da fusakar ta ya qesta yatsun shi yace"haka aka ce miki anayi ayi ta kallon miji ba a taya shi cire kayan,uhm uncle bafa kai nake kallo ba tunani nake idan anje kotu baza a kira ni ba dai ko? Ya danganta but lafiya?matsawa tayi kusa dashi tare da fad'in ni tsoro nake ji,shine nake tunanin ya zanyi gobe idan aka kira ni,ai ba gobe bane sae ran monday wato jibi ,tsare su za'a ci gaba dayi kenan?eh idan kuma kafin Monday sun fad'i gsky ba sai anyi wani  cece kuce a gaban shari'a ba hukunci kawai za a yanke musu.

To uncle....bakinsa taji cikin nata ya zare yace"wai ke baki san mijinki qishirwa yake ji bane na dawo baki tarbe ni da ruwa ba sae surutu,, yi haquri uncle hankalina ne yana kan tunanin kotu, kar ki fa tada hankalin ki kotu ba lallai bane ma a kira ki sae idan ta kama, ruwan ta kawo masa,cikin muryar kuka tace"ai idan ta kama nake yiwa gudu  dmn na gani a wani  film aka kira wata shaidu  dn ta fad'i gaskiya sae kawai mai laifin yayi saurin cafke bindigar police d'in da ke tsare da shi ya harbeta ta fad'i kai tsaye ta mutu,ni shine nake yiwa gudu uncle, ta qarashe maganar cikin kuka,farhan ya qara rungume ta yana lallashi yace"hakan ma bazai faru ba inshaAllah kinji ki daina  kuka,nan ta share hawayenta ta d'auki cup d'in ruwan da ya ajiye bai sha ba, ta bashi yasha ,ta ajiye cofin tare da qara maqalqalewa a jikin sa ya shafo bayanta yace"ina son na tashi na d'an watsa ruwa kinji,pls uncle tsoro nake ji ,ka bari  idan nayi bacci sae ka tafi,yace"to tashi ki saka rgr baccin ki, nan ta tashi ta sako rgr ta dawo jiknsa ta kwanta bata jima ba tayi bacci.

Ya tashi ya shifed'e ta a hankali kmr wata er baby ya rufa mata blanket sannan ya tafi toilet.

Yana gama wankan kenan yaji ihunta ta shigo da gudu bayin ta qanqame shi ta baya sae kuka take tana fad'in "uncle tsoro nake ji idan na tuna wani  abu ya faru a gidan nan ganin nake kmr zai sake faruwa gashi ynx har mafrki nkeyi sun dawo.

towel ya xaro ya d'aura sannan yace"muje na miki addu'a kiyi bacci ba abunda zai faru kinji"

nan ta gyad'a masa kai tare da sassauta riqon da ta mishi, suka fito suka kwanta kan bed ta wani  shige jikin shi sosai,shi kuma yana mata addu'a, inda duk wani  motsi da take tana kule kar taji masa ciwo ,

da haka har  bacci yayi awon gaba da ita.

*Billy giro &Futha Luv*.

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

[10:22PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [9:59PM, 10/31/2016] Billy giro😊: [7:2 10/31/2016] Billy giro😊: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```AFRAH KO AMRAH ```*

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futhalurv.WordPress.com*

*```🏅70🏅```*
 Washe gari  bayan sun gama sallar asuba tana maqale dashi sae wani  kukan shagwa6a take masa da ya kasa gane kanta ya tada ta zaune yace"Bacci ko yunwa ko kuma duka ne?  To ba kai bane kafin muyi sallah wai kace kar ta6a ka byn ni bansan laifin da na maka ba,yi haquri abu nake ji a lokacin wanda in kika ta6a zaki ja na tsaya wasa da jikin ki ni kuma ba so nake nayi missing jam'i ba.
     Ko ke duk ta6a niñ da kike baki ji komai bane tun tashin mu kafin asuba har zuwa yanzu? um um ni kam me zanji,dan baki sa abun a ranki bane shiyasa, can qasa sosai tace"cab wannan abun mai wahala har ma zan sashi a raina"mene abu mai wahala? shiru tayi dn bata tsammaci zai ji ba,ya d'ago fuskar ta yace"meye abu mai wahala, ba dai abun da dk mukayi sai kin nemi second round a kanshi ba,ta zaro ido cikin muryar kuka tace"ni kuma yaushe?oho koma yaushe ne ai kin fini sani, tashi tayi cike da qwallah a idonta tace" wlh Allah nikam hakan bai faru tsakani na dakai ba"
dariya ta soma bashi ganin da gaske kuka take har hawaye na d'iga kan hijabinta yaje ya rungumo ta yana fad'in "amma Afrah ai kinsan da wasa nake miki,kawai dai nasan a yanda kika fad'i abun nada wahala ba haka bane,,amma ai kasan da zafi ko....wane zafin ai shima kad'an ne kuma da kin saba zaki daina ji har dai idan kin haifu,ya fad'i haka ne yayinda yake share mata hawaye sannan ya shafo cikinta yace"daji babyn mu najin yunwa ,wane babyn nidai kejin yunwa kuma bazan ci komai ba tunda kake sani kuka kan abunda bnyi ba,to naji yi haquri ,maqale kafad'a tayi taje kan bed tayi kwanciyar ta, fridge ya bud'e ya tsiyayo fresh milk a cup yaje ya ajiye kan bedside drawer ya zauna tare da jawo Afrah jikin sa yana lallashi kan ta tashi tasha but still sae maqale kafad'a take.

Yace "ko sae nayi tsallen kwad'o ?kallon sa tayi a shagawa6e tare da gyad'a masa kai.
  Nan ya zare jikin sa ya sauka kan gadon tare da kama kunnen sa,tsalle ta daka ta sauko kan gadon  ta miqar dashi tsaye tace"lah ilah! uncle wai da gske zakayi wlh da wasa fa nakeyi"tayi mgnr ne cikin yanayi na kmr wacce taga tayi wani  sa6o,shima ya lura da hakan kan yace komai, sae kawai yaga ta fashe da dariya ta rungumo shi ta gefensa tana ci gaba da dariyar kuma sosai har da su tara qwallah a idonta sae kallonta yake da ya d'ago ta yace"Ifyr ki wannan dry haka, sae da ta goge er qwallarta ta dariya tace"ance wai tuna ka dara shike kawo hauka, wani  abu na tuna a school uncle wata senior ta ce ta zubar min da kaya by mistake har ma tana bani haquri da yake haushinta nake ji kan seniorityn ta kawai na kaita qara na had'e qarya

da gaskiya na fad'i ,uncle Frank ya kira ta yasa ta tsallen kwad'o,gashi qiba ne da ita sosai uncle baka ganta ba har nishi takeyi ,
in tana tsallen kuma komai nata rawa yake kuma in tayi tsallen sae kaji dum kmr qasa zata fad'a,nan ta ci gaba da bashi labrin da ya kasance mai cike da dariya dmn ko shi sae da abin ya bashi dariya sosai a cikin dariyar ne yace "wato Afrah ashe da na kai ki bording bai sa kin daina rashin ji ba,nafa daina uncle dmn ba ruwan mu da kowa nida Amrah,ko ita senior dan inada cikinta ne sbd da wannan jikin nata take punishment din juniors duk wanda ya mata laifi zaune shi take kuma sae taga dama take tashi suyi ta kuka suna roqonta wasu har da fitsari suke yi a wando, ai shine da ta zubar min da kaya naji wani irin dad'i jikina har mazari yake banje na kaita qara ba,to da kukaje hostel bata miki komai ba... cab hm ta ma isa,in tamin ramawa zanyi wlh,zaki iya da ita ne, to uncle ai dabara tafi qarfi,dmn da tayi cikina ba wata wata zan kwashi qafafunta ne kafin kace me na cika mata baki da qasa da ido na kuma sami dutse na fara darzar bakinta sae yayi jini.
Hm my Afrah Allah ya shirya min ke,,Amin uncle.
Waih uncle bacci, ta fadi hakane tana kallon shi da idanunta da sukayi kalar jin bacci yace"in kin gama shan fresh milk d'in kya yi bacci"ba musu tasha sannan ta kwanta .

Sae guraren qarfe goma ta fito taji gidan ya qamsashe da qamshin break fast ,kicin ta nufa ta 6ata rai a shagwa6e tana kallon Amrah tace"Amrah shine kikayi break fast d'in ke kad'ai bayan kinji nace ina son na riqa kallon yanda kike aiki dmn nima na iya aiki a sauqaqe,, murmushi tayi tace"yi hqr naje nayi knocking naji shiru nace may be ko bacci kuke,
shiru Afrah tayi ta d'anji er kunyarta wacce bata bayyana ba bcs tabbas taji knocking amma kmr a mafarki taji abun sbd ta lula duniyar romance d'in da farhan ya tafi da ita inda ko yanxu da qyar ta samu ya barta ta fito,Amrah tace"shine nikam nazo na d'ora sbd kinsan gwaggo ya kamata a kai mata abinci da wuri ,da sauri Afrah ta kai hannu a baki tare da fad'in "lah har yanzu gwaggo bata karya ba kenan? Aa na mata kunun gyad'a tun da safe tasha,amma Amrah duk da haka ba dad'i har goma ba a kai mata break fast ba, kuma wlh duk laifi na ne tun da ni nace miki zanyi"ai shiyasa na miki knocking naji idan kinyi sae naga kan dining ba alamar anyi komai ,am sorry pls bari na kama miki muyi saurin qarasa kammalawa.

Tana cikin aikin ne Amrah ta shiga store dai dai farhan ya shigo ya rungumo Afrah a hankali ta baya yace"wa ya gaya miki ana fitowa da towel idan wani ya shigo gidan fa? To ai ka san sae an bawa mutum izini yake shigowa, duk da haka dai ki kiyaye, ok naji kayi hqr.... Ah meye haka uncle pls ka fita har na kammala ,Allah zaka shiririta ni ne kuma ka ga yanda mukayi lettin break fast,uncle Amrah fa na store kar ta fito ta same mu haka,farhan kam kmr baya jinta sae abubuwa yake mata ,ta samu da qyar ta qwaci kanta ta tura shi waje tana dariya tana fad'in "kayi haquri uncle har na kammala kaji" tana gama fad'ar haka ta rufe qofar ta saka key, Amrah ta fito tace"ikon Allah lafiyar ki kika rufe mu ko so kike zafi ya kashe mu,ah ah kuma wake knocking... um um kar ki bud'e dan Allah, to waye? Uncle ne,, tsaki Amrah taja zata bud'e qofar tace"ni na d'auka ma wani ne da ba kya so ya ganki haka...nidai kar ki bud'e pls, meyasa Afrah?murmushi kawai Afrah tayi tace"kedai nace miki kar ki bud'e, Amrah tace"to shikenan kawo aikin na qarasa may be kiran ki yake, bafa magana yake dani ba dmn yanzu ya fita, daga

haka Amrah bata sake cewa komai ba suka ci gaba da aikin su sae labari suke har suka kammala.

Da yamma guraren qarfe biyar Afrah tayi kwalliya cikin kayan da sukayi matuqar d'aukar ta sae qamshi take,taje d'akin farhan ta same shi gaban mirror yana cire buttons d'in rgr shi ,ta rungumo shi ta baya suna kallon juna ta jikin mirror tace"uncle daga police station ka fito ne? Haka kawai ba sannu da zuwa bayan kinsan yanzun ne dawowata ,yi haquri sannu da zuwa, a taqaice yace "yauwa sannu"ya jayeta daga kan jikin sa yaje kan bed ya zauna zai cire takalma ta durqusa zata taya shi yace"um um ki bar shi kawai, jiki sanyaye ta saki takalman da ta riqa ta riqo kumatun shi tana kallon cikin idon shi yayi saurin kauda fuskar shi tare da sauke hannyen ta dake kan fuskar shi,take idanun ta suka ciko da qwalla tace"uncle wai fishi kake dani shine tun safe da ana break fast baka sake ce min komai ba har ka fita"
Yace"wa gaya miki fushi nake dake kawai dai I'm not in mood pls ki tashi ki fita, maqale kafad'a tayi taje kan jikin sa tana kuka tana fad'in"ni nasan fushi kake yi dani don kawai d'azu da safe na ftr da kai a kitchen"
ai shine naga rainin naki yayi yawa, uncle bafa raini bane wlh ina sauri ne mu qarasa break fast sbd gwaggo,kallon bakinta yake tana magana da kulawa ya d'ora yatsan sa yana shafa gefen lips d'inta da yaga yayi ja, yace"me ya ji miki ciwo Afrah?kaiñe d'axu da safe a kitchen lokacin da ina maka magana baka saurare ni ba, amma meyasa baki gaya min ba kin san dole na dakata ai, to uncle a wannan lokacin zaka ce ba gsky bane don dai kawai ina so ka fita ne.
Rungume ta yayi yace"I'm really sorry "ya sake d'agota yana shafa gurin yace"da zafi sosai? um um ba sosai ba, sorry kinji ,ta gyad'a masa kai ta tashi tana fad'in bara na kawo maka ruwa kasha,hannunta ya riqo yace"yi zamn ki bana jin qishi ,to lemu fa ?um um wanka nake son nayi tukun, nan ta shiga taya shi cire kayan jikin shi yace"my Afrah wai kin san me? um um sae ka fad'a uncle,, wai tamvaya leesa keyi wai da wane dalilin ne aka kamata ,,driya Afrah tayi mai cike da mamakin leesa tace"uncle ko dai zafi yayi mata yawa ta zauce ba a sani ba? Ba wani da hankalinta take zancen akwai wani abu dana fhmci take son qullawa shine ta fara da hakan,kuma wai ma da en fashi suka ce itace ta turo su gidana cewa fa tayi qarya suke,hhhh shin uncle ko ta manta cewa Amrah tasan komai ne wai? Oho mata, fita batunta ma akayi tukun dmn yanzu so ake aji inda en fashin suka ajiye mana kadarorin mu da duk wani abu da suka d'auka but sunqi fad'a har yanzu shine nagaji na bar en sanda na ci gaba da aikin su na ganin sun fad'a,Allah yasa su fad'a ni a ma fasa shiga kotun nan... to ai ba a kansu kad'ai za'a shiga kotu ba,da akwai manyan cases guda biyu na kashe Abbanki da ummanki,then about ur twin sister,to Allah yasa su fad'i komai wanda da anje kotu hukunci kawai za'a yanke musu,to Allah yasa.

uncle, ta rufe fuskar ta tare da fad'in"kai yi haquri gsky bazan iya gaya miki labarin zancen mu ba"
sbd me?a yangace Afrah ta kalleta tana wani  karkad'a jiki tace"sbd na manya ne masu aure kad'ai keyin shi yarinya matso da aurenku kusa ko kema zaki shiga layin manya,Amrah tace"ni ko"gwalo Afrah ta mata tace "eh in kinyi zuciya ki matso da auren mukan musha biki!oh don shi ne to naqi d'in ,wata magana Afrah tasa mata a kunne  ta tafi da gudu ,Amrah tasa hijabi ta bita, tana ganinta tayi saurin komawa bayan gwaggo tana fad'in "gwaggo ki hanata wai dukana zata yi don kawai na fad'a mata gaskiya"
  Ni ba dukanki zanyi ba amma ki maimaita abinda kika fad'a a gaban kowa, to ai gaskiya na fad'i,ko ba gaskiya bane?amma ke ki fad'a aji idan qarya nayi,Amrah ta kama hanya tana dariya tace"Allah Afrah baki da kunya, Allah dai ya shirye ki"

Bayan ta wuce
  Farhan yace"zo nan Afrah,
 ba musu tazo kusa dashi ta zauna yace"meyasa kike gudu bayan kin san matsalar ki ,so kike ki 6arar mana da baby? Aa bana so kayi haquri, to naji amma ki natsu ki zauna kurum kinji, a natse ta gyara zamanta tace"to uncle na natsu na zauna kurum"yayi murmushi yace"wane rashin kunya ne kika gaya ma Amrah a kunne ko baki san ina hango ku ba"dariya tayi tare da 6oye fuskarta a qirjinsa tace"uncle kawai abar kaza cikin gashinta.

*Billy giro&Futha Luv*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:23PM, 11/30/2016] Billy Geeero: *[11/15/2016]* 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
       *```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futhalurv.WordPress.com*

*```🏅81🏅```*
To idan ana buqatar a yanka ta aci fa? Wannan lalura ce ta kama dole a fige ta...yauwa uncle pls ina son yau muje shopping kaga weekend ne kanada time,gaya min me kike so idan na fita sae na sayo miki, um um pls ni nafi son mu tafi tare sbd undies dina sunyi qasa ina son a siya min wasu har da wata bz ma nake so mai had'e da half vest, haka kuma ina son half vest da kuma panties n under skirt then... Then bazanje dake ba kawai dai kije ki samu biro da paper ki rubuto duk abinda kike so ki kawo min, a shagwa6e ta juya gun da gwaggo take zaune bata ganta ba, yace"gwaggo kike nema ta roqa miki ni,ai ina kiranki ta shige, je daga ciki,ko na raka ki? Girgiza kanta tayi ta wani marairaice tace"pls uncle ka tafi dani kaji" naji amma da sharad'i ko munje baza a d'auko komai na sweet ko chocolate ba, ko kada'n bata damu ba sbd tasan tana da su a lots a d'aki tace"na amince to shike nan ki gaya ma Amrah anjima da maraice za'a fita.
OK uncle tank u,ta d'ora masa kiss kan kumatu kafin take tashi ta shiga daga ciki shi kuma ya fita.

Da dare Afrah ce sanye da farar savuwar vz mai had'e da half vest sae d'an guntun farin wandon da ya d'ara pant da kad'an,sae neme neme take a cikin drawers d'in d'akinta bata gani ba ta koma d'akin Farhan nan ma bata ga abinda take nema ba, ta tashi cikin 6acin rai ta nufi Farhan da ya fito daga gurin wanka d'aure da towel, yace "mene ne? Uncle ina chocolates da sweets da biscuits dina dake daki? Na kyautar... haba uncle meyasa basu fa yi expire ba ,sbd nasan baki san ya kamata ba har yanzu dmn da ace kin gansu ban ko sani sae dai ki kama kiyi taci, to uncle don me ka saya min su? don kici, to meyasa ka kyautar ?sbd juna biyun da ke jikin ki bana son kina cin zaki,oh oh uncle wai kai juna biyun nan ka d'ora komai akan shi ,gashi yau ji nake kmr zan mutu idan banci chocolate ba ,ta qarashe maganar cikin kuka ta juya zata bar d'akin ya jawota jikin sa yace"ke komai crying crying da abinda ya kai na kuka da wanda bai kai ba"uhm uhm uncle dole nayi kuka wlh abinda nakeji idan banci chocolate ba ni kad'ai na sani, ni wlh dana san ka kyautar d'azun da muka fita sae na siya ko a 6oye ne kuwa ,ko yanzu kuwa kina iya fita ki siya ba ma zancen 6oyo ni da kaina zan baki kud'i har da makullin mota,kar6i, nan ya riqo hannunta ya damqa mata kud'i da makullin mota yace"jeki ko a yanda kike ma zaki iya fita ba matsala bane,then koda nayi bacci idan kika dawo sae ki rufe mana gida.
Daga haka yaja Vaseline yaje ya zauna ya bar Afrah tsaye tana kuka marar sauti.
Ta jima tsaye a gurin har ya gama shafa Vaseline ya zare towel tare da sa d'an guntun wando ,nan taje ta zauna kusa dashi tana ci gaba da kuka a jikinsa ,yana jin yanda hawayenta ke d'iga kan qirjinsa ,takai hannu tana share masa hawayen snn ta share wad'an da ke kan fuskarta.
Tace"to uncle don Allah ko chewing gum ne idan kanada ka bani"oya bring my briefcase" cikin jin dad'i ta qara share hawayenta taje ta d'auko ya bud'e jakar ya d'auko orbit ya 6are ya sa mata a baki "ta d'ora masa kiss a kumatu tare da fad'in "luv u uncle"murmushi yayi yace"luv u more, shike nan kuka ya qare? Rufe fuskar ta tayi da tafukan hannyenta ta fad'a kan qirjinsa tana fad'in "eh ba ka bani chewing gum ba".
Shiru sukayi yana kallon bz half vest dinda ke jikinta ana hango rabin mammanta ta jikin net sae ta mata kyau sosai.
Fira sukeyi har tayi bacci kan jikinsa yasa yatsan sa a hankali ya ciro chewing gum din da ke

bakinta ,
ya zaro tissue ya dunqule shi ya kad'a dustbin snn ya dauke towel din da ya cire ya kai inda ya dace ya dawo kanta ya cire mata Bz half vest yaje har d'akinta ya d'auko half vest ya saka mata tare da gyra mata kwanciya ,
ya nemo jallabiya ya saka yaje kan prayer mat ya fara sallah as usual.

2 weeks later
Afrah wai baza ki tashi ki had'a mana breakfast ba kinsan fa ina fita aiki, zumbur Afrah ta yaye bedsheet din da ke jikinta ta sauko kan gadon da sauri tana fad'in "sorry uncle wlh na d'auka ko yau weekend"
Zama d'aya taji jiri ya d'ebe ta Farhan yayi saurin jawota kan qirjinsa ya kwntr da kañtà yana shafa bayanta a hankali yayinda Afrah ke dafe da goshinta sbd had'e da ciwon kai take jin jirin,sun d'au 4mnt a haka Farhan ya d'agota yace"jirin ya daina? Eh ,ok lemmi tell u abinda baki sani ba shine ba'a tashi kai tsaye daga bacci kmr yanda kika tashi d'in nan shiyasa kika ji jiri, ki kiyaye kinji, thank u uncle.
No p,pls ki d'ora abu mai sauqi wanda baza ki yayyanke hannunki ba,like what?Arish but kuma fa zaki soya mana qwai sae ki kiyaye gurin yanka albasa pls dnt pain ur hand kinji,inshaAllah uncle.

Bayan sunyi wanka sunyi breakfast Afrah ta raka Farhan har mota ta miqa masa briefcase tare da fad'in Allah kiyaye, yace"Amin ya riqo briefcase taqi saki ta marairaice fuska tace"dan Allah uncle nazo mu tafi"ina Afrah? Asibiti mana,, Afrah...pls uncle kar ka ce Aa, ok hurry up n bring ur hijab amma banda gudu ki tafi a hankali, ai kuwa kmr ya sani dmn da gudu tayi niyyar barin gurin don murna.
Ta tafi da sauri ta d'auko hijabi mai hula da hannu har qasa kausar yard da ba a ganin jikin mutum.

Tafe suke cikin asibiti riqe da hannunta duk inda suka gifta sae kallon su ake sbd baqon al'amari ganin Farhan da mace kuma riqe da hannunta.
Kan dole ya sake mata hannu ganin yanda ido suka mai yawa duk da yaji en gulma na fad'in "ah wannan dole matar sa ce ko qanwar sa tunda har kika ga ya riqe mata hannu"
Da shigar su office ya bata kujera ta zauna shima yaje kan kujerar sa mai shillo ya zauna, nan wayrsa tayi qara ya d'aga wayar bayan ya gama yace"Afrah zan d'an fita idan wata ta shigo kice ta jirani ba jimawa zanyi ba"to uncle sae ka dawo.
Yana fita Afrah ta koma kan kujerar da ya tashi ta jawo eyeglass dinsa ta saka,ta ciro orbit chewing gum zata 6are sae kawai taji knocking ,qara hakincewa tayi kan kujerar kmr ita keda office din ,cikin yanga tace"yes come in"
A hankali wata mata da vazata wuce 30 yrs ba ta bud'e qofa ta shigo ,Afrah da ke jingine tana d'an juyawa a hankali kan kujera tace"malama have a seat"bayan ta zauna tace"uheem meye matsalar ki? Sai da matar ta gyara muryarta snn tace"rashin lafiya nake fama da ita yau kusan wata d'aya kenan ina shan magani amma a banxa ga yawan amai musamman idan na shaqi qamshin abinci"Afrah ta d'ago tare da nisawa tace"malama ai wad'annan alamomin ciki kenan"

um um bana tunanin ciki ne,meyasa?sbd yau shekarun mu goma da yin aure nida mijina amma ko 6ari ban ta6a yi ba kuma dama idan bana da lafiya amai nake yi sosai kuma bana son warin abinci sbd magungunan da nake sha kesa naji haka, but ban ta6a wata da zazza6i ba gsky sbd dana sha magani a take nake jin sauqi amma wannan sae abinda ya qaru"Afrah ta 6are orbit chewing gum d'inda ke hannun ta ta saka a baki snn ta sake jinginawa jikin kujera tana ci gaba da juyi a hankali  tace"wannan watan kinga al'adar ki kuwa? Aa ina tsalleken wata dama bazan iya ganewa ba,, well a jikin ki ba wani  abu da kika ji ya canja ko kuma a lokacinda kuke mu'amalar ku ta aure mijinki bai sanar da ke cewa kin d'an sauya masa ba?gsky bai gaya min ba amma  my body skin look so smooth n fresh ya qara haske ba kamar da ba kuma qirjina sae qara cikowa yake d'anyi,,oh ryt i think ciki ne dake but take dis PT strip,byn ta kar6a Afrah tace" zaki sami er kwalba kiyi fitsari a ciki sae ki tsoma shi a ciki,after  some minutes sae ki duba idan ya baki layi d'aya negetive kenan wato ba ciki  bane idan kuma  ya baki layi biyu  positive kenan ,i congratulate u bcs u are going to be a mother, kina d'auke da ciki kenan, then bari na rubutu maki irin magungunan da zaki fara sha koda hakan ta kasance.

Kai tsaye ta jawo biro da paper ta fara rubutu akai, ta miqa mata haka tayi ido hud'u da Farhan yana jingine a jikin qofa wanda kan idon shi akayi komai, cikin dariya Afrah ta rufe fuskarta da tafukan hannayenta ,haka ma Farhan cikin dariya ya qaraso gurinta tare da kama kunnenta ya mird'e.

*Bilkeesu giro😊&Futha luv*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:23PM, 11/30/2016] Billy Geeero: *```[11/16/2016]```* 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futhalurv.WordPress.com*

*```🏅82🏅```*
Er qara ta saki tace"wayyo uncle! wlh da zafi sosai,ah! wayyo gwaggo uncle zai kashe ni"
zaki sake? ah ah wlh bazan sake ba na tuba dan Allah kayi haquri! ai bani zaki bawa haquri ba, to ka sake min kunne zan bata, sae kin bata tukun,ihu ta fara yi tana tsalle tace"wayyo uncle zaka 6alle min kunne wlh da gaske nake uncle"ai nima da gaske nake tsararki ce da zaki zauna kina tsara ta,oya bata haquri ,don Allah Aunty kiyi haquri bazan sake ba wlh ni ba doctor bace tsaraki kawai nayi asali ma secondary school kawai na qare ko 5 months ma banyi da gamawa ba.

Sai da matar tace ta haqura sannan Farhan ya sake mata kunne .

Tazo gun matar tace"dan Allah anti duba min kunne na yayi jini ko?
matar ta gwalo ido tace"kai kai kai jini kuwa har da su gudaji subhanalillahi!a tsorace Afrah ta qarawa kukanta qarfi tana yarfi da hannu,bata nan bata can kmr a yanke kaza tana d'aukar rai , da Farhan har matar ba wanda bai yi dariya ba ,matar tace"kinga da kin daina tumami kina tsalle yanda kika min ne na miki,kunya Afrah taji ta shige bayi.

Matar ta gaisa da Farhan tace"Wlh har yarinyar nan tasa naji dad'i sosai a raina ashe ba likita bace "kiyi haquri bata ji ne wlh ,
amma kar ki damu inshaAllah yanda naji kinyi bayani da alamun juna biyu a tare da ke.

Nan ya rubuta mata test din jini da na fitsari.

Bayan matar ta fita ne Afrah ta fito taje kan jikin Farhan ta zauna tare da kwantar da kanta a qirjinsa tana sauke numfashi cikin sanyin murya tace"pls uncle duba min kunne na inaga fa yayi jini da gaske,ya duba yace"oh no har ma kuwa jinin  ya cika miki kunne ,bani tissue tun kan jinin yayi nisa ,
da sauri tasa yatsanta a ciki ta ciro bata ga komai ba, ta turo baki tana kallon shi tace"wai uncle meyasa kake qarawa miya gishiri ?sbd tayi dad'i, in banda abinki ina kunnenki ya isa jini da har kike tambaya, baka san zafin da nake ji bane uncle, daga jinin ki ne fa amma ni ba wani  kama kunnen nayi sosai ba,duk da haka dai yayi ja ko uncle?bai yi komai ba fa  ,nan ya gyara mata hijab d'inta ya 6oye kunnen.

Yace "ya akayi kika san yanda ake amfani da pregnancy test strip?ina matar doctor kuma, hm naji amma wane  irin magani ne kika rubuta mata? Wanda kake bani ne na rubuta mata, ce maki akayi cikin nata yana da matsala irin nki ne? To ai dai maganin yana qara ma baby lafiya da kuzari, to naji tashi kan jikina next person zata shigo tun jiya ya kamata ace na duba su aka samu akasi bana jin dad'i nace suyi haquri har ga yau.

Afrah tayi dariya tace"wai uncle ita matar nan da ta yarda ni likita ce bata ga nayi qanqanta ba,kuma kafin ta shigo ma ai akwai sunanka a rubuce,
To waya sani ko ta lura da sunan kuma idan kin lura a matse take taji meye matsalar ta shiyasa bata wani  kula da qaramcin ki sosai ba.

Knocking suka ji yace "kije daga ciki akwai sofa ki kwanta akai idan bacci kike ji ma kiyi.

Tace"lah uncle wai office dinka ciki da falo ne ?eh mana ,wow! amma har naji kwad'ayin zama babbar likita ,nan ta shiga daga ciki taga gurin d'an midi room don hutawa kawai akayi shi,Ac ta kunna ta kwanta daga nan kuwa bacci yayi awon gaba da ita.

Sae guraren sha biyu ta farka ta fito ta sami Farhan shi kad'ai jingine jikin kujera ya lumshe ido kmr mai bacci ,zaman da tayi kan jikinsa ne yasa shi bud'e idon shi yace"ya akayi kin tashi? Gyad'a masa kai tayi tare da fad'in uncle muje gida yunwa nake ji, ai dama ke nake jira ki tashi mu tafi, amma bari bacci ya qarasa sakin ki tukun,tace"uncle a lokacinda nike er qararrama idan kazo dani office ina kake ajiye ni? A inda kike zaune, a nan kan jikinka? Eh, ko kuma na kwantar dake kan kafad'ata idan kina bacci, meyasa baka ajiye ni kaji dad'in aiki? Sbd ba kya yarda kuka kike inna sauke ki,to idan zanci abinci fa?daukarta yayi ya d'ora kan desk yace"haka nake miki snn na bud'e food flask na fara ciyadda ke har sae kin qoshi snn na baki ruwa kisha na zaro tissue na goge miki d'an qaramin bakin nan naki ,after that zan baki sweet ko chocolate dmn ko ban baki ba zaki tamvaye ni ne.

To idan ina bacci kan jikin ka bana maka fitsari?Aa duk yanda kike jin fitsari sae kin farka kin ajiye kuka a kaiki toilet bcs at that time ba kya iya magana sbd matsalar da ta same ki ta rashin ji.

To uncle ka ta6a dukana a lokacin da ina qarama? Har yau ban ta6a dukan ki ba Afrah, amma na kusa farawa,meyasa ?sbd rashin jinki hkn zai sa bazan qara zowa dake asibiti ba, he uncle nice fa Afrah,,oh Afrah Zarah Sadiq amanata wacce na raina tun tana er qanwanuwa ko, ai ban manta ba amma idan rashin jinta ya wuce guri sae na dake ta,ai idan ka dake ni babyn ka shima zai yi kuka ,sae na rarrashi babyna na qyale wacce bata ji.

Nidai uncle maganar gaskiya kar kace baza ka qara dawowa dani ba...yauwa uncle ya baka fara mana process din makaranta ba?sae kin haifu tukun, pls uncle kar ka min haka so nake kafin na zama babba na zama doctor,kinga tashi mu tafi lokaci na tafiya yau Friday.

Nan ta sauka kan desk suka fito.

Tafe suke cikin mota tace"uncle dan Allah fruits nake so"to bari idan zamu koma gida, ina zamu je yanzu? Gidan JB ,nifa Maman sa bata sona ,to ai ba gun maman shi zamu je ba gun matar shi... Chabd'i! hm wai ka kai kuka gidan mutuwa kenan, har dambe fa mukayi a school ,to ai yanzu ya wuce, nifa uncle gsky bana son a tafi, nayi ma JB alqwarin yau zan kai ki ya kenan? Kawai ka kirashi ka bashi haquri, sbd ga Anti Afrah ko? Ba haka bane uncle wlh bana shiri da ita ko yanzun ta min maganar banza zamuyi ta ne,ai ba sae ta miki maganar banza ba ma,muna shiga ki same ta ki fara duka tunda ke ba a zumunci dake.

Shiru tayi bata sake ce masa komai ba har suka iso.

Bayan sun iso yace"gaya min fruits kawai kike so ko da wani abu? Ni na fasa ,ai ba don ki zan siyo ba wa babyna,to wa ke d'auke da babyn, wa kuma keda bakin kaiwa babyn? jawota yayi ya rungume yaja hancinta yace"kece amma sai nasa kan dole ki aikawa babyna,ko ban isa ba?ta lakato hancinsa tace"ka isa har ma ka yi yawa, ta koina zaka iya aika saqon ka a jikina ba tare da na hanaka ba ,dmn kai keda mallakin shi,banda kai ba wanda zai qara zama mallakin shi koda baka raye kuwa sbd inaso har a lafira ka kasance kaine mijina,,

Yace"nima haka fatana kenan "

yauwa uncle wai a lafira idan mutum d'an aljanna ne dole sae ya auri matan fura'aini ?eh,uhm uhm gsky da ace ba dole bane wlh baza ka aure su ba mu kad'ai zamuyi ta zaman mu, dariya

yayi yace"ai a aljanna ba a kishi kuma kece uwargida za'a qara miki kyau da komai kiyi mulki yanda kike so ba mai hana ki.

Turo baki tayi tace"nidai nidai"kedai kedai kiyi shiru haka kar ki wuce gun.

Murmushi tayi ta riqo yatsunsa tace"uncle idan kaje sayen fruits ka siyo min grapes da yawa dan Allah"kar ki damu ummul aulad ko mai grapes kike so zan kawo miki,dariya tayi tace"hm uncle kenan ai nasan mgnr ka a iya ftr baki ta tsaya, ya shafo fuskarta yace"to so kike ya gane min kyakkyawar fuskar nan taki ,ai sai dai na siyo abinda yake siyarwa amma shi kam qwalelensa da ya shigo min gida.

Yatsine fuska tayi sbd cikinta da ya juya mata kan yunwa ,ya shafo cikin yace"yunwa ko? Eh wlh, to muje daga ciki muci abinci ,anan gidan? Eh mana ai tun dazu mu kad'ai ake jira aci liyafar juma'a kafin mu tafi masallaci.

Nan ya fita ya zagaya ya ja hannunta suka shiga daga ciki.

Da dare guraren qarfe goma Farhan ne ya fito daga wanka ya sami Afrah kwance qasa sanye da er fincikar rgr bacci rungume da robar grapes a qirjinta ,

A gefenta kuma empty robar grapes ne guda biyu a ajiye wad'anda ta gama dasu zama d'aya.

Durqusawa yayi kusa da ita yakai hannu ya zare grapes dinda ke kan qirjinta a hankali,snn ya d'auke ta zuwa kan bed inda kan sanyin ruwan wankan da ke jikinsa yasa ta fara juyi a hankali,ba tare da ta bud'e idonta ba takai hannu tana shafa sumar qirjinsa ,cikin muryar bacci can qasa tace"uncle wanka kayi?eh Afrah, sae kuma ta shiga lalaben qirjinta har da qoqarin sa hannu ciki, ya riqo hannun yace"mene ne? My grapes,yana nan na ajiye miki, ka bani zanci,, to naji, shine abinda yace ba don zai bata ba sae don ya huta dmn yasan bazata iya cinsa ba kan bacci,qara mannewa tayi a qirjinsa sbd dad'in sanyin ruwan da ke jikinsa ,tace"uncle kayi zamanka ma jikinka yamin dad'i da ruwan wankan nan,kallonta yayi yaga har lokacin idonta a rufe yace"kina son nayi miki wankan, um um na jikinka ma ya isa ,daga haka yayi shiru yana shafa bayanta yana mata addu'a har tayi bacci.

*Billy giro😊&Futha Luv*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:23PM, 11/30/2016] Billy Geeero: ```[ 11/17/2016]``` 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futhalurv.WordPress.com*

*```🏅83🏅```*
Guraren qarfe biyu na dare farhan ya sallame sallah  yana kallon Afrah dake ta faman juyi tana kiran sunan shi cikin muryar kuka.
   Tashi yayi yaje
kusa da ita ya kwanta yace"lafiya Afrah ?uncle zafi ba Ac ,Afrah sun d'auke nepa kuma na kira mai gadi yace min wai gen d'in yaqi tashi shiyasa aka kunna inverter,zafi zai kasheni uncle,to muje kiyi wanka,ba musu ta tashi suka tafi ,
bayan sun fito ta kalle shi tace"gsky bazan iya bacci da towel ba yana da zafi"to ki saka rgr ki mana, maqale kafad'a tayi, yace"to bani towel d'in tunda kinada pant a jikinki sae ki kwanta na rufa miki bedsheets ai kinga shi bai da zafi sosai ko, ta gyad'a masa kai tare da zare towel d'in ta bashi snn ta kwanta ya rufa mata bedsheets ba jimawa bacci yayi awon gaba da ita.
   Duk da haka bata yi wani  baccin kirki ba kusan sau uku tana tashi tana sake wanka.

Washe gari bayan sunyi break fast Afrah taje 6angaren gwaggo ta bar Farhan yana wani  aiki kan laptop.

Tana zuwa 6angaren gwaggo taji d'akin ya mata sanyi mai dad'i kan Acn da ke kunne gashi Amrah ta gyara gadon very need ai kuwa kai tsaye ta fad'a gadon, Amrah tace"ke daga shigowa sae kwanciya?bari kawai jiya ban sami baccin kirki ba ko kad'an kusan sau uku ina tashi wanka sbd zafi gashi kinsàñ iskan fanka komai qanqantar sa mura yake sani shiyasa ba a kunna ba ga en NEPA da Gen sun mana tsiya.

Amrah tace"Hmm kar alaqawa zafi may be uncle ne bai bar kinyi bacci ba shine kike wani wayance wa" yaushe kika fara rashin kunya ke kuma Amrah? Ke kika koya min ko kin manta har lecture kike min, murmushi kawai Afrah tayi dmn ita bata ko iya tuna rabon Farhan da ya kar6i haqqinsa tunda aka fara harakar kotu ita akai.
  Tayi kwanciyar ta ba tare da ta sake cewa Amrah komai ba har tayi bacci.

Baccinta bai ko yi wani  nisa ba taji Amrah na tashinta ,ta tashi cikin 6acin rai tace"Amrah wai meye haka ina bacci ki tashe ni gashi har kin saka min ciwon kai,to uncle ke kiranki kar ki ga laifi na ,to ko shine baza ki ce masa bacci nake ba ,mtsw ni wlh kar ki koma min haka, Uhm Allah ya huci zuciyar ki.

kallon agogon d'akin tayi cikin muryar kuka tace"wai shi uncle ba kuma yace tun jiya na gama shan magani na ba"

Tazo ta same shi falo cike da son tayi kuka ,ya riqo hannun ta ya zaunar yace"mene ne kuma? To uncle ba Amrah ce ta tashe ni ba ina bacci ,kasan jiya bnyi baccin kirki ba kuma da asuba bnyi ba, afwan ya naji jikin ki yayi zafi sosai? Abu biyu mana da rashin baccin jiya da ciwon kai kan tashina da akayi daga bacci ynz.

hannunta yaja suka je 6angaren su ,ya cire mata kayan jikinta yace"jeki d'an watsa ruwa kafin na gama had'a alurar da zan miki...oh oh uncle wlh bana son allura ,to naji jeki watsa ruwa ,ni bacci nakeji ,but Afrah baki ji zafin jikin ki bane da har zaki iya kwanciya a haka, koko so kike na miki da kaina?um um,to shike nan zauna muga.

Bayan ya zare towel dinta ya shiga tura hannusa a hankali cikin pant dinta ,wani abu taji tayi saurin riqe masa hannu tare da jan cikinta yace"dakata mana Afrah abu zanyi"

A iya qasan cikinta ya tsaya tare da matsa gurin, ba shiri ta saki er qara, yace"wai ciwo? Eh uncle, kinga kenan da sauran ki,Aa uncle kad'an ne fa kuma yanzu ko nayi dogon motsi gurin baya ciwo, to xan baki magani kisha idan kuma allura kike so to, saurin girgiza kanta tayi tace"Aa nafi son magani"

Ya d'auko magani ya bata tasha ,ta marairaice fuska tace "gsky uncle yanzu ko nice pharmacy a daina d'ura min magani hakan nan"murmushi kawai yayi yana kallon qirjinta sae duk taji wani iri har tana qoqarin kai hannu ta rufe ya riqe hannayen yace"sbd me zaki rufe min kayana? to ba kai bane keta kallo kmr yau ka fara gani,to meye a ciki? kana sani ina jin kunya, buttons d'in rgrsa ya 6alle gabad'aya yace"ni kiyi ta kallon nawa bazan ji kunya ba, uhm uncle kenan to ai naka ba irin nawa bane,yatsansa yakai kan d'ayan mamman ta yana zagaye nipple dinta,yace"inace kan wannan abun ne ke qara sa kiji kunyar naga mammanki to nima ina dashi,jaye yatsan nasa tayi tace"nidai na gaya maka ba d'aya muke ba ,ba kuma zamu ta6a zama d'aya ba,kwantar da ita yayi ya mata rumfa yace"zama d'aya kuma na yaushe bayan gashi har Allah ya bamu qaruwa ,
ta riqe hannunsa da yake shafa cikinta tace"ni ba wannan nake nufi ba ai kasani, murmushi yayi ya matsa fuskar sa gab da qirjinta cike da son ya saka mamman a cikin bakin shi,tayi saurin bashi bai ta rungume qirjinta da hannu tana dariya,shima dariyar yayi ya juyo da ita yace"Kin raina ni ko Afrah? Ba haka bane uncle bacci zanyi,gashi ni kuma wasa nake son muyi ya kenan ,uncle na fika uzuri ,ji bakinta ba kunya kinfi ni uzuri,tsuke bakin tayi tace"eh mana"

Hancin sa yakai ya goga kan nata yace"yanzu zanyi maganin bakin nan naki,hannu takai ta rufe bakinsa da yake qoqarin had'ewa da nata tace"yi haquri uncle ka barni nayi bacci, kan mammanta taji ya maida bakin nasa,lumshe idonta tayi tana sauraren abinda yakeyi a qirjinta wato aikin jarirai ,
daga haka taji hannunsa yakai inda bata yi tsammani ba wato pant dinta da yake qoqarin raba ta dashi, tayi saurin dago fuskarsa da tafukan hannayenta ido rau rau tace"pls uncle kar ka cire min bacci nake ji wlh,wasa fa kawai zanyi Afrah ba abinda kike tunani ba, to ai zaka watse min bacci na ne, zan sa kiyi baccin so nake jikin ki ya rage zafi tukun kinji,rufe idonki bazan takura ki yanda kike tunani ba sae dai ma kiji kinyi bacci,nan ta rufe idonta a hankali tana jin yanda yake wasa da jikinta har bacci yayi awon gaba da ita.

Sae guraren byn zuhur ta farka ta ganshi zaune kan bedside ya bada bai yana aiki da laptop

dake kan stool,  tazo a hankali ta bayan shi ta rungume shi tare da kwantar da kanta a bayan nashi  ,yakai  hannu ya shafo fuskarta yace"my Afrah kin tashi? Bata ce komai ba sae dawowa tayi ta gefensa ta zauna ,ya kalli yanda tq rufe jikinta da bedsheets har wuya ,yace "tashi kije kiyi arwala ,ina son zan watsa ruwa tukun ,um um sae kinyi sallah ko zakiyi sbd nasan halinki da jimawa gurin wanka gashi lokacin sallah ya tafi.
  Ba musu taje ta d'oro arwala tayi sallah,tana gamawa ta kishingida tace"me za'a dafa mai sauqi?um um bana buqatar abinci yau,amma yi wanka muje 6angaren gwaggo kici abinda suka dafa.

Bayan tayi wanka suka je ,da zuwanta ta zarce sae kici ta dawo rai 6ace tana kallon Amrah dake mata dariya tace"shine kika barni naje bayan kinsan ba abinda zanci bane ,kinji ki ni nasan abinda kika jeyi kicin ne?indai zaki daina abu d'aya ki daina don uncle fu'ad bazai yarda da wannan shirmen ba, hhhh shi faten doya ne shirme? Eh mana, to ai gwaggo keso bani ba kuma ni banda matsala duk abinda nayi zan iya ci, to wake da matsala? Oho.. Nima ai banda matsala yanzu kuwa zaki gani dn zan cinye shi kaf bazan raga miki ba, ba ruwana dai in kikayi amai ke kika ja,yaushe rabonki ai na daina wannan yayin kema kin sani,tana gama fad'ar haka ta nufi hanyar kici Amrah ta bita da ido tana murmushi, sae gata ta dawo dauke da plate d'aya da spoon biyu ta zauna kusa da Amrah tace dake fa na d'ebo ,au kin tausaya min kenan? Ai Amrah kinsan bazan iya cin abu na hana miki ba wasa nake, ta kalli Farhan da ke fira da gwaggo tace"uncle ko na d'ebo maka zaka ci? Alhmdlh Afrah.

Tsoro tsoro Afrah kecin faten dmn ko Amrah ta lura jurewa ne kawai take har suka cinye plate kaf, sae a sannan Afrah ta sauke ajiyar zuciya ta tsiyaya ruwa tasha ,ajiye cup dinta keda wuya ta fara jin tashin zuciya ,zama d'aya taji yawu ya cika mata baki inda kai tsaye taji ta fara yunqurin amai ta tafi da gudu sae toilet,sae da ta amaye kaf abinda taci sannan ta samu aman ya tsaya mata,duk ta galabaita tana neman gurin zama a cikin bayin,  gwaggo ta jata suka fito Amrah ta tsaya gyara toilet .

6angaren su Farhan ya koma da ita sae lalla6ata yake kan ta fad'i me take son ci yanzu?ji take kmr baza ta iya sake cin komai ba sbd still zuciyar ta bata daina tashi ba, Farhan bai matsa mata ba sae bayanta ya shiga shafawa a hankali, ta lafe sosai a qirjinsa kmr wacce tayi bacci, sun d'auki lokaci a haka Yace"ynz fa zaki iya cin wani  abu?
girgiza masa kai tayi, daga hk bai sake ce mata komai ba.
  Bayan sunyi sallar la'asar ya qara tamvayar ta tace"grapes kawai zan iya ci, kuma ina son dabino"to shike nan,ya dauko grapes ya bata Yace"kici zanje na siyo miki dabino, pls uncle ina zuwa, Afrah kiyi zamanki ba jimawa zanyi ba kinji,gyad'a masa kai tayi snn ta dauki qwarar grapes d'aya tasa a baki.

Bai wani  jima sosai ba ya dawo ya sameta kwance  qasan tiles ta cinye robar grapes d'inda ya barta dashi.

Ya ajiye kayan hannun shi ya durqusa yana kallonta Yace"Afrah ga center carpet kya kwanta a qasan tiles, sanyin tiles din dadi yake min uncle, tada ita yayi zaune snn ya ware ledodin da ya shigo dasu, dabino ne kusan kala uku ciki har da na makka wato na kwali,snn kuma ya qaro mata grapes, dad'i taji har ranta tace"nagode uncle"
ya shafo gefen fuskarta yace"no vex ai aikina ne dmn haqqi ne a kaina na kula da matata yanda ya kamata ko ba haka ba?
murmushi tayi tace"duk da haka kana qoqari sosai uncle dmn ba kowane namiji keyin haka ba ,sai dai nace nikam nayi dace da samun irin namijin da sae an tona a qasar hausa,
ta riqo kumatun shi tana kallon cikin idonshi tace"ko uncle ?murmushi kawai yayi ya zauna qasa kusa da ita  yace"ni kuma sae nace nafi kowane namiji sa'ar samun kyakkyawar mace er qarrama mai dad'in sha'ani"
kunya taji sosai tare da shigewa qirjinsa dmn ta gano inda ya dosa bcs tun ba yau ba yasha yabonta a duk lokacinda suke mu'amalar su ta aure.
Tashi yayi ya wanko mata dabino byn ya zauna yace"ko na kwali zaki ci ,a 6alle packet d'in? Duka zanci,yakai  hannu zai bud'e kwalin yace" to da sharad'i sae idan zaki haifo min en ukku tunda kika ci dabino kala uku a zama d'aya, ware ido tayi tana kallon shi tace"uncle ni haka dani na haifo en uku ai sae mutuwa, ko goma kika haifo zama d'aya ai baza ki mutu ba sae idan kwanan ki sun qare, um um nidai gsky bana so d'aya ya isa.
To Allah dai ya bamu rayayye mai albarka ,amin uncle.
Uncle pls na rage kayan jikina?rage man ba zafi kike ji ba,wai uncle meyasa nake jin zafi byn ga Ac a kunne, daga babyn mu ne,dama akwai cikin da ke farawa da zafi tun yana sabo wani kuma sae ya tsufa,ko zaki watsa ruwa ne? um um sae na gama cin dabino tukun, kice sae kin gama kwad'ayi....um um nikam bana da kwad'kayi.
Daga haka tayi shiru ta fara cin dabino kmr ta samu abinci, Farhan yayi zaune sae kallonta yake ,ta dauko dabino zata saka mishi a baki, ya riqo hannun suka saka dabinon a tare snn yace "ya baki rage kayan jikinki ba? sae idan zanyi wanka sbd na tuno ba bz a jikina,meyasa baki sa ba? rgr ta zauna min ba sae nasa ba idan nasa matse min zatayi.
Ya kalli qirjinta ya tatta6a yace"kmr yau naga qirjin ya qara cikowa ko? Nima haka nagani da naje wanka.
Nan suka tsaida srtn nasu sbd wayarsa da tayi qara.

After 2 weeks,
murna Afrah keyi sosai jin ansa date d'in auren Amrah da Fu'ad nan da wata d'aya .
Ta koma 6angaren su da murna tana kiran uncle! uncle!!... Afrah zo gani ,mgnr ta fito daga bayi, Afrah ta shiga kai tsaye dmn ta d'auka ba wani  abu yake ba,tayi sauri zata fito ganin yanda yake ,yace"dawo ai ba dodo kika gani a toilet d'in ba, kinaji na fa ko so kike mu 6ata?kan dole ta dawo rufe da fuska, ya jawota qirjinsa tare da jaye hannuwanta,yace"bude idonki mana ta bude idon ta sauke su iya qirjinsa yace"lafiyar ki na komawa sae kace yau kika saba gani na haka?hasken ne yayi yawa uncle, towel ya jawo ya d'aura a qugunsa yace"baki ga aikin da nakeyi bane dole sae da haske,kema cire kayan jikin ki na miki, idonta ta jaye kan nashi tace"aini banda suma a jikina, ban yarda ba ai duk wankan da kike zuwa ban ta6a ganin kin

d'au shaver zuwa gyaran jikin ki ba, to uncle suman baya fito min.
To naji cire kayan muyi wanka ,to a rage hasken a bar dim light ,ba musu ya rage hasken ya shiga taya ta cire kayan kaf bai bar mata komai har shi kanshi ya cire towel d'in da ya d'aura, ya rungumeta qam a qirjinsa bakin sa saitin kunnenta yakai hannu yana shafa qasan cikinta a kasale yace"ki shirya yau zan kar6i abuna sbd babyna ya zauna yanda nake so,qam ta qara rungume shi sbd hannunsa da taji ya wuce gun, murya can qasa tace"uncle wanka fa zamuyi tukun "nan ya d'auke ta suka shiga gun wanka wani qamshin dad'i ne da ruwan sbd turaren wankan da ke cikinsu, sabulu ya d'auko yana bin jikinta dashi a hankali kmr mai shafa qwai,ta rufe ido tana sauraren yanda yake bin jikinta da sabulu can taji ya riqo hannunta ya saka mata sabulu , ta shiga yimai duk yanda yake mata can ya kar6i sabulan ya ajiye ya miqar da ita tsaye tare da sake musu shower ruwan na fara saukowa kan jikin su suka had'e bakinsu gam suna cud'anya jikin juna ta hanyar romance ,
lungu da saqo ba inda hannun kowanen su bai kai ba na ganin koina ya wanku a jikinsu ,
sae dai hkn ba qaramin tsima su yayi ba dmn har tsayuwa na qoqarin gagarar su.

Farhan ya kashe shower ya d'auki Afrah cak suka fita yaje da da ita sae kan bed ya kwantar tare da fara bin koina na jikinta da shafa musamman kan qirjinta inda cikin wani irin sabon salon da bai ta6a mata irinsa ba take jin yana bin qirjinta da shafa hkn yasa take fitar da numfashi sannu a hankali,
ta kama nasa qirjin ita ma tana shafa,tare da laluba bakinsa ta zira harshenta a ciki,can ya zare bakinsa ya maida shi kan qirjinta.
da haka har suka lula duniyar ma'aurata .

Sosai suka jima a wannan duniyar sbd jin dad'in ta ,
ba ga Farhan kad'ai ba har ga Afrah.
A hankali ya sauka kan jikinta ya jawota ya rungume ,idanuwansu a lumshe suna jin saukar numfashin juna.
Farhan ya kira sunan ta tare da shafo qasan cikinta yace"baki ji ciwo ba dai ko?girgiza masa kai tayi tare da qara shigewa jikinsa sbd baccin da take ji sosai.

*Billy giro 😊&Futha luv💅*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:23PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [ 11/18/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futhalurv.WordPress.com*

*```🏅84🏅```*
Time ya duba yaga 11:30 na safe yana da time d'in da zai yi bacci kafin zuhur,hakan yasa ya biyewa Afrah sukayi bacci mai isar su sae dai ya rigata tashi yaje yayi wanka koda ya fito ya sami Afrah ta tashi ta had'e kai da guiwa.
Yaje ya zauna kan bedside drawer tare da dafa bayanta ta kwanto mai a hankali kafin yake cewa "lafiya me yake faruwa ko gajiya ce? Girgiza masa kai tayi tace"so nake baccin ya kammala saki na sae na tashi"
Olryt kinji ana kiraye kirayen sallah bari na tashi ko, kema kije ki samu kiyi wanka kafin lokaci ya tafi ,then idan na fita bazan dawo da wuri ba zan iya kai dare ,sae kije 6angaren su gwaggo kafin na dawo kinji, kai ta gyad'a masa snn tace "a dawo lfy uncle"
ko da wani abu da zan dawo miki dashi? um um bana buqatar komai.
Daga haka ya fita snn ta tashi ta fad'a toilet.

Da 'ya'yan fruits a plate ta tafi 6angaren gwaggo tana ci, sae da ta gaida gwaggo snn ta nemi guri ta zauna, ta kalli Amrah dake game da waya tace"Ke ba magana? Ya zan miki magana byn tun d'azu kinsan jiranki nake kin wani je kinyi zaman ki gashi kin tafi da wyr ki bare na tura games d'in da nace,yi haquri gani na dawo kawo na tura miki, bana so ki barshi,Amrah fushi kikayi, hm ba kya kyau ma in kika yi fushi gara ma ki daina ,tana magana ne sanye da kankana a bakinta, Amrah ta qwace plate din tace"kinji yanda kike magana sae kace wani gardi kin wani cika baki da kan..kana, Afrah ce ta katse ta tasa mgnr ta fito iri biyu sbd slice d'in kankanar da ta cusa mata a baki,tace"yeah munyi iri d'aya"murmushi kawai Amrah tayi tace"bani wyr nidai na tura"ta miqa mata wyr tana qoqarin tashi, Amrah tace"kuma ina zuwa baki bud'e min code d'in ba?Afrah wacce taje gun gwaggo ta zauna tace"to Anti bala'i na cire code d'in ai"hmm wai kwando kece ma rariya na yoyo ke waye bai sanki ba a school kan fad'a da tsokana? Afrah tace"ni banda fad'a ko gwaggo ina dai da tsokana?gwaggo dai ta gyad'a kanta kawai tana ci gaba da lazimi ,Afrah kuwa taci gaba da shan 'ya'yan fruit d'inta ,ita kuma Amrah ta maida hankali kan wayoyin da ke hannunta.

Sun jima a haka ba mai magana can Afrah tace"dan Allah Amrah muje ki raka ni 6angaren mu na maida plate snn kuma ina son zan d'auko wani abu"
Amrah bata ce mata komai ba sbd hankalinta na kan waya tana chat.
Afrah tace"wai ke naga sae wani shan qamshi kike don kinga zakiyi aure" da sauri Amrah ta

d'ago tana kallonta tace "oh oh yi haquri wlh hankali na ya d'auku ne a kan chat"
hmmm yayi har ma chat kike bayan saura wata d'aya a miki aure abin ki ajiye komai kiyi ta kukan rabuwa damu,ashe ko tausayina ma ba kya ji zaki tafi ki barni banida abokiyar fira shike nan kuma sae idan kinxo ganin gida, Amrah tace"ai nice abin tausayi nida aka cire cikin en uwa ban kuma san ya zanje na sami nashi en uwan ba, wlh kuwa har kin ban tausayi, don Allah bari kar ki sani kuka Afrah, na daina dmn bana son kiyi kuka ,taja hannunta tace "muje .

Tafe suke Afrah ta kalli Amrah, tace"zakiyi kuka da yawa rnr aurenki kenan,dmn naga ynx har jikin ki yayi sanyi kan er maganar nan da mukayi "dole nayi kuka kam ko yanzu jinsa nake sosai na danne ne kawai,amma ji nake kmr nayi naji sauqi,um um kar ki fara kuka tun yanzu bcs kukan zai ginshe ki ne,koda rnr auren zata zo sae kiga kin kasa ba kya iya yi,amma kar ki damu er uwa yi abinki ko zaki sami relief in yaso rnr kaiki koda kukàn ya qare miki sae na maye gurbinki nayi ta kukan kamar nice amarya har a kaini d'akin ki amma fa ina tsoro kar ango yazo ayi dai dai an d'auke nepa bai ga fuskar waye ba yaje yaja gwazi da mtr mutane ,Amrah ta kai mata duka tace"Allah ya shirye ki ba ma tausayina kike ji ba shine har da min tsare tsaren kuka...to so kike ace an kai amarya bata yi kuka ba,koda yake meye a ciki ai zamani ne yazo da hakan... Kanki ake ji dai.
Dai dai sun iso knn Afrah ta kai plate kici snn ta haura sama ta d'auko robar grapes da Apple qwara biyu ta sauko .
A byntà ta 6oye hannun ta da ke d'auke da robar grapes, ta miqawa Amrah hannunta mai dauke da Apples tace"d'auki d'aya a ladan rakiya kuma kar kisa ranki a na bayana sbd kuma naga fridge d'inku cike yake da 'ya'yan fruits ba abunda babu a ciki"Amrah tace" ni kuwa grapes d'in nake so a ladan rakiya", ta fad'i haka ne tare da kar6e robar grapes d'in zata bar falon cikin sauri, Afrah tace"kut haaaae! Yarinya jeki na matan aure ne in kika ci sae kin kasa bacci,Amrah ta fita da gudu tana dariya tace"er wayo koma dai yayane sae naci.
Tana fita taja birki ba shiri sbd cin karo da ta tashi yi da wani ba tare da ta d'ago ta kalli wane ne ba tace"yi hqr uncle fu'ad"
da mamaki ya kalleta ya akayi tasan shine kai tsaye ba tare ta kalle shi ba, yace"ya akayi kika gane nine? Murmushi kawai tayi inda ba don komai ta gane shi ba sae don qamshin turarensa ,ya kar6i grapes d'in da ke hannuta ya bud'e ya d'auki d'aya yaci,tare da miqa mata robar sae da ta kalli Afrah tana dariya tace"d'auka kawai na baka halak malak"ta bar gurin cikin sauri tana dariya Afrah tace"ba nata bane fa ,amma tunda kaine na baka,Allah Afrah naci ne kawai don na ganshi a hanunta ,bcs koda na iso nan a mota cikin cinsa ma nake,ya miqa mata tare da fad'in "Farhan fa?ya fita tun dazu ,yace"OK bari na kira shi a waya"kafin yake wucewa.

Cikin sauri Afrah ta cimma Amrah dake gab da shiga 6angaren gwaggo tace"tau! wata walle bone ya ciki yau uncle fu'ad sae ya lalubo ki cikin dare, bare kinsan yau yana nan tafe fira, A tsorace Amrah tace"wai don Allah na matan aure ne kika sa na barshi yaci"hhhh matsoraciya kawai wasa nake wlh,ita ma Amrah dariya tayi tare da girgiza kanta tace"Allah ya shirye ki"

Sae dare Farhan ya dawo gidan dmn har goma tayi koda yazo da nyr kiran Afrah su koma gawaggo tace"har tayi bacci tun dazu take ta jiran dawowar ka"

to shikenan gwaggo abarta kawai taci gaba da baccin,
to da ka d'an duba ta kafin ka tafi dmn naji jikin nata yayi zafi sosai,
tace wani abu na mata ciwo ne?um um lafiya lau fa ta kwanta,yaje ya tatta6a jikinta har zuwa goshinta yace"body temperature ne dole zai farkar da ita sbd yayi yawa,idan ta farka d'in sae kice tayi wanka da ruwan d'umi zafin zai sauka.
Tace "to shikenan"
nn yayi mata sae da safe ya fita.

Da safe ya fito daga wanka yana tsaye a gaban dressing mirror yana taje gashin kanshi ,Afrah ta shigo dakin taje da sauri ta rungumo shi a hankali ta bayan shi tare da fad'in "i missed u uncle"missed more my Afrah,ya juyo da ita ya zaunar kan dressing mirror ya jawo stool ya zauna yakai hannu kan cinyar ta tare da riqo en yatsunta ya sarqe da nashi yana kallon fuskarta yace"honey better ya baccin jiya body temperature d'in ya barki kuwa?eh tunda na tashi nayi wanka shikenan sae asuba na sake farkawa.
To mu gaisa ,
yana fad'ar haka ya lumshe idon shi ta duqa a hankali taje gab da fuskar sa ta d'ora masa kiss kan kumatu ta kowane gefe,snn ta d'ago tana murmushi tare da fad'in "nayi nawa saura kai"
Ya bud'e idon shi tare da fad'in"babyna zan fara gaidawa ko maman baby? Duk yanda ka gani amma kayi adalci, to shikenan zanyi Allah kaini gidan akwai,
nan yakai yatsan sa ya ta6a ta ya ta6a cikinta yana fad'in"
_Allah kaini gidan akwai gidan akwai nika fad'awa ga masara ga kudaku ga inda Allah yannufa_" cak yatsan shi ya tsaya kan cikinta, Afrah ta buga ihun shagwa6a tace"wlh bazan yarda ba nice a gabanka ni zaka fara gaidawa"cikin dariya Farhan ya rungumota yaje saitin kunneñta yace "a tare dai zan gaidaku tunda a tare kuke"maqale kafad'a tayi tace"um um gsky ni zaka fara gaidawa ai ni ka fara samu kafin shi, to naji,nan ya d'aga ya koma hugging d'inta tare da kai mata kisses kan kumatun ta, snn yaje a hankali kan cikinta ya yaye rgr jikinta ya d'ora lips d'insa a hankali kan cibiyar ta ya furta a hankali kmr mai rad'a"good morning my child"
Yana d'agowa ya bar gurin yana dariya sbd wani kallo da yaga tayi mishi mai cike da rigima har da wani turo baki,ta sauko kan dressing mirror tana fad'in"gsky nima sae kace min good morning"dai dai ta iso gurin shi ya lakato hancinta yace"ai nima baki ce min good morning ba"a shagwa6e take kallon shi tana bubbuga qafafunta a qasa tace"to ai shima bai ce maka ba amma kace mishi"

*Billy giro😊&Futha Luv*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:23PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [ 11/19/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futhalurv.WordPress.com*

*```🏅85🏅```*
Kinga zo na gaya miki wani albirish ,
ya jawota suka zauna kan gado yace"yau ki shirya zamu fita yawo a duk inda kike son zuwa kuma ki siyo duk abinda kike so.... Wayyo Allah uncle har da chocolates? Rufe idon shi yayi alamar ya manta da yace komai, Afrah ta shafo fuskar sa cikin sanyin murya tace"uncle mene ne bada shi ba ko?da shi amma kad'an ,
ihu ta saki tana murna sae rawa take a jikinsa ya dakatar da ita yace"saura kuma kiyi rashin alqawari kije ki kwaso da yawa nako kyautar dasu gabad'aya"
To da kanka ma zaka d'auko iya abinda kake son naci, to naji ,yes! ta fad'i hk ne tare rungume shi qam a qirjinta had'e da bashi peck.
Yace"to jeki snr da Amrah ki kuma snr mata har da fu'ad za'a fita ,da gudu tayi niyar barin gurin yayi saurin riqota yace" be careful my unborn child d'ina fa"wato ni baka ma damu ba idan naje na fad'i,zan damu ba sosai ba sbd ke kikayi gudu ba saki aka yi ba, lallai uncle unborn child d'inka ya fini nsn ma in na haife shi shikenan ni shara ce a gurinka,yace"ko d'aya ki daina tunanin hk kinji...ai da alama...jawota yayi yana rarrashi sbd yanda yaji sautin muryarta kmr zata yi kuka
yace"zan fa damu sosai kin sani Afrah na fad'a ne kawai"
Ta tashi tana murmushi ta fita.

Ba qaramin dad'i ftr tayiwa su Afrah ba dmn duk abinda suke so sun kwaso.
Ana gama sllr isha'i Afrah tayi bacci nan kwance kan sallaya sbd a gajiye suka dawo kuma da isowarta ta d'ora girki qarshenta bata ma ci ba bacci yayi awon gaba da ita.
Koda Farhan ya dawo ya sameta kwance ya d'auke ta ya mayar kan gado tare da cire mata hijab ya had'a da carpet ya linke yasa a wardrobe.
Kan dining yaje yaci abinci sbd yunwa yake ji sosai.
Bayan ya gama ya koma sama d'auke da kular abinci da plate a cewar koda Afrah ta farka

taci.
Wanka yayi yazo yayi kwance yana kallon labarai ba tare da sautin tvn yayi yawa ba sbd kar ya tashi Afrah.
Har guraren qarfe goma baiyi bacci ba yana jiran tashin Afrah taci abinci, juyin da take yi ne yasa ya matsa kusa da ita wani irin zafi yaji a jikinta,
"zafi uncle"
shine abinda yaji kafin ya iya yin komai ,
d'agata yayi yace"wani abu na miki ciwo"ba tare da ta bud'e idonta ba ta girgiza masa kai,snn tace"pls Ac uncle"Afrah d'akin nan yayi sanyi ba kad'an ba sbd Acn da ke kunne "to kai uncle baka ji zafi yayi yawa ba har ya ba jikina kodai baka da lafiya ne shiyasa baka ji zafin ba?lfy ta qalau Afrah kece jikin ki yayi zafi tashi kiyi wanka zafin ya sauka ,a hankali ta bud'e idonta ta tashi ta fad'a toilet ,sae gashi ta dawo daure da towel ta bud'e freezer ta d'auki qanqara yace"me zakiyi da ita ?zan sha ne,bai ce mata komai ba har ta koma toilet da qanqara a hannunta.
Kusan awa d'aya yana fmn jiran fitowar ta amma ko motsin alamar fitowar ta bai ji ba.
Ya tashi yaje ya mata knocking yaji shiru ya murd'a qofar a hankali ya shiga ya sameta kwance abinta cikin bahon wanka sae bacci take ,garin d'aukar ta ne yaji sanyi ga ruwan da take kwance cikinsu,ysn ba makawa ciki tasa qanqarar da ta d'auka dama yayi mmki ga ruwa me ya kaita daukar qanqara.
Yana sanya mata towel ta tashi tare da cire towel d'in a jikinta tace"uncle bana so ka maida ni cikin ruwa"Afrah kin jima sosai a bayi har kika yi bacci"nasani uncle nan zanyi baccina cikin ruwa har safe"
Lallashinta ya shiga yi inda da qyar ya samu ta yarda suka koma d'aki.
Ba yanda bai yi ba kan taci abinci amma taqi sae fresh milk tasha mai sanyi ta kwanta.
*~~~~~~~~*
Sannu sannu lokaci keta tafiya inda ynx har auren Amrah ya matso gab sauran kwana d'aya a fara bukukuwa.

Afrah ce zaune ta tasa 'ya'yan fruits tana ci dmn ynx su tafi bawa qarfi kan abinci ,
sae ta yini tana cinsu ba tare da taci wani abincin kirki ba.
Ta kalli Farhan dake zaune kusa da ita tace"uncle zaka barni nayi rawa a bikin Amra? um um , shine abinda ya fad'a a taqaice sbd labarun da yake kallo baya son srt, tace"pls uncle wlh in banyi rawa ba ai ba'ayi komai ba"kallon ta yayi yaci gaba da kallon labarun sa ,Afrah kuwa ta hau bakinta sae roqon sa take,yace"Afrah bazan barki ba fa ki daina damuna ina sauraren labarai"tashi tayi cikin fushi ta bar gurin tana magana ciki ciki yabita da ido kawai har ta shige.
Sae da ya gama kallon labaran ya bita ya hango ta zaune tsakiyar gado ta lanqwashe qafafu tana cin pringles tana kallo sae dariya take kasancewar comedies ne take kallo.
Yaje yayi
zaune kusa da ita kmr yanda tayi irin zmnta ya kar6i Pringles yana ci ,ta d'auki remote ta rage volume ta kwanta a hnkl kan jikinsa tare da tura hannun ta cikin rgrs tana yawo dashi kan qirjinsa ,yakai hannu ya 6alle buttons d'in rgr gabad'aya snn ya shafo gefen fuskarta yace"bacci?gyad'a masa kai tayi inda bata jima ba bacci ya d'auke ta.
Zafin da jikinta keyi ne ya tashe ta ,koda ta duba Farhan ya fita ,toilet ta fad'a tayi wanka tana

fitowa daure da towel ta nufi downstairs ,saurin juyawa tayi hango fu'ad ,JB da kuma Farhan suna tsaren tsaren yanda za'ayi biki, ba wanda ya ganta a cikin su face Farhan da shi kad'ai ke facing d'in gurin.

Bayan sun gama abinda suke ya haura sama zuwa d'akinta ya sameta ruf da ciki tana kuka ya zauna tare da jawota jikinsa yace"mene ne? Cikin muryar kuka tace"uncle wlh zafin jikin nan yana takura ni ace duk na kwanta bacci ba halin nayi awa biyu kwance sae zafin jiki ya tara min har sae na tashi nayi wanka kan dole,kuma da alama abin bai dame ka ba sae dai kawai kace wai naje nayi wanka ba wani magani da zaka bani nasha"
Sae da ya nisa a hnkli snn yace"Afrah ai wankan da nake cewa kiyi shine maganin abun, ko baki ga da kinyi wakan ba shike nan, kuma laulayi ne yazo miki da haka bynda zanyi,amma sannu sannu zai daina miki kinji,gsky ni ngaji ,daga kawai kinci sa'a Afrah ba amai kike yi ba kuma cikin bai wani sa miki tada ba, to uncle naji amma qirjina fa?a hankali ya bud'e towel d'inta yana kallon qirjinta yace"me yayi? Towel tasa ta rufe abinta snn ta share hawayen kan fuskar ta tace"ni bana son cikowar da yake yi kar yaje ya zama babba da yawa har yazo ya 6ata min body structure ,ai kad'an kad'an ne yake qarawa bazai yi girman da kike tunani ba.
To uncle wai da gaske kakeyi baza ka bar ni nayi rawa ba a bikin Amrah? Dagaske nake yi dmn ko ba don cikin jikin ki ba bana so,dan haka kar ki sake tambayata zancen rawar nan, to uncle na haqura, ta fad'i haka ne a sanyaye ta tashi ta d'auko Vaseline zata shafa ,sae duk yaji ta bashi tausayi ganin yanda tayi sanyi, yace"zo na taya ki"ba musu taje ta zauna kusa dashi byn ya gama tayata yace"wane klr kaya zaki sa?kallonsa tayi snn tace"irin na jikin ka zansa inada irin su kasan"
nan suka je jikin wardrobe Afrah ta ciro kayan tasa, riga da wando ne rgr polo sky blue a jikin kwalar rgr akai ratsin baby pink haka ma a qasan hannun rgr akwai ratsin baby pink rgr dai dai jikinta takai cinyar ta da kad'an.
Wandon ma baby pink ne in colour za'a iya kiran shi skin tight dmn ya kama jikinta ,taje ta feshe jikinta da turarukka ta d'an gyara fuskarta da kayan kwalliya er simple makeup da tasa tayi kyau sosai,
ta qara gyara tsorayen kalabarta en qanana dasuka sauko har kan kafad'ar ta snn ta juyo cikin yanga tare da riqe qugunta tace"uncle ya ka ganni? Kinyi kyau sosai kmr na sunkuce na gudu da ke kowa ya daina ganin ki sae ni kad'ai.
Murmurshi tayi yayinda yazo ya riqo hannunta yace"muje mu kaiwa su gwaggo yawo"suna fitowa compound d'in gdn Afrah tace"uncle muyi photo,kai tsaye kuwa ya shiga camerar wyr shi ya saita ,Afrah ta rungumo shi sukayi murmushi su duka ya d'auke ,kallon photon sukayi da yayi mugun kyau har dai yanda dimplse dinsu ya bayyana kan murmushin da sukayi,sake d'aukar wani sukayi wnn karon kiss ta d'ora masa kan dimple shi kuma yakai hannu ya zagayo dashi ta bayan qugunta ya rungumota yana murmushi.
Kai tsaye ya saka photon a screen wallpaper snn ya tura ma Afrah a phone d'inta yace"amma kar ki sashi screen wallpaper "a shagwa6e ta kalle shi tace"meyasa byn kai kasa?ni dake ba d'aya bane bcs ba mai kar6ar wayata amma ke duk inda kika samu jefar da waya kike, gashi cikin wata biyu ma bansan iya wyr da kika sake ba,,uhm uhm pls uncle zan kiyaye,ai dama na gaya miki in kika yadda phone d'in nan bazan qara saya miki wata ba tunda sakaci ne dake,yi haquri kaji nima bada son raina bane,gefen fuskarta ya shafo ya kar6i wyr yasa mata second

photon da sukayi a screen wallpaper ,dad'i taji sosai tana fad'in "yeah wyr mu iri d'aya n our screen wallpaper ma iri d'aya"

Sae da yaji jikinta ya daina rawa snn ya shafo bynta yace"kin gama wankan? girgiza masa kai tayi ba tare da ta d'ago ba yace"to tashi kije ki qarasa"
riqe da gaban rgr ta tashi taje toilet .
Bayan ta fito ko mai bata iya shafawa ba taje kusa dashi ta kwanta,frhn ya kalli yanda jikinta yayi very weak yace"Afrah kin tsorata da yawa ko?bata ce dashi komai ba sae hannun sa ta jawo ta rungume tare da lumshe idanuwanta ,
nan da nan bacci ya d'auke ta.

A qarshen satin su Amrah suka dawo,murna Afrah tayi ba kad'an ba inda ba don dare ba da sae taje.
Tunda ta fito daga wanka take waya da Amrah har ta shirya tasa kayan bacci basu aje wayar ba, Farhan ne ya shigo d'akin yaje kan gado ya kwanta yana mai kallon Afrah ta jikin mirror da tun shigowar sa waya ke laqe a kunnenta amma bata cewa komai sae ma yanayin 6acin rai ya hango a tattare da fuskar ta,katse wayar yaga tayi tazo ta kwanta,ya kalle ta da da kulawa yace"Afrah ya akayi na shigo na katse muku waya ko?"no uncle"iya abinda tace kenan takai hannu ta rage hasken d'akin"
Jawota yayi jikinsa yace" gaya min to me ya 6ata miki rai?uncle ba komai kawai gobe da safe ina so zanje gidan Amrah ,meyasa bayan sunce su zasu zo, zan kirata su fasa zuwan sbd akwai abinda zai kaini,shike nan Allah kaimu gobe da safen.
Tace "amin tare da gyara kwanciyarta ta shiga bacci.

Washe gari da qarfe goma sha d'ai ta tafi gidan koda ta shiga falon ta sami fu'ad zaune kusa da Amrah kmr wani  mai lalla6a ta ita ko tana tirje mai,hkn yasa ran Afrah ya qara 6aci ,ta danne zuciyarta suka gaisa da fu'ad ya fita ya basu guri.
  Da taikaci Afrah ke kallon er uwar ta ta,ta fizgo hannunta suka haura sama zuwa d'akinta ,Amrah tace"Afrah lafiya kika shigo cikin fushi? kallon tufafin jikin Amrah take da basu da maraba da tsiraici tace"kin cuce shi wlh wad'anan wane irin kayane kike sawa haka bayan kinsan ba kya iya bashi haqqinsa! Wlh Afrah yau kad'ai na ta6a sa irinsu kuma shi ya matsa min ni kuma ina gudun 6acin ransa shiyasa na saka,but in kin lura a takure nake...qarya kike ba kya gudun 6acin ransa tunda har ya iya neman haqqinsa kika hana shi! Pls Afrah wai waya gaya miki ,nasan dai uncle fu'ad baya iya gaya kowa, kin manta kenan jiya muna cikin waya ya shigo d'akin ki ,baki kashe wyr ba kika ajiye shiyasa naji duk wata magiya da yake miki cikin lalama yana roqonki kan ki bashi haqqinsa kika qi,abinda ma ya qara qona min rai wai ace tunda aka yi aure baki ta6a bashi haqqinsa ba,wnn wane irin abu ne da cin zali,kinyi islamiya kmr bakiyi ba! kinzo d'aya da wacce tayi zaman banza a gida,kina kuma sane da tsinuwar mala'iku dake hawa kanki!kuma kinga tafiyata idan kinga dama ki gyara idan kuma kinqi ke kika sani....da sauri Amrah ta riqo hannunta tace"Pls Afrah ki tsaya kiji wlh tsoro nake ji sbd ban san yanda zanji abin ba,da qarfi Afrah ta fizge hannunta tace"sae kiyi ta jin tsoron tunda shi zai fishsheki.
  Nan tasa kai ta bar musu gidan.

 Da Afrah ta koma gida gabad'aya Farhan ya kasa gane kanta sae tambayar ta yake me aka mata amma taqi ce mai komai yajata suka je gurin gwaggo nan ma bata ce dasu komai ba , da ma suka matsa mata tace bata jin dad'i ne.

Washe gari guraren qarfe 11 na safe Afrah na qoqarin rufe windown living room d'in farhan ta hango motar fu'ad ta kunno kai cikin gidan kallon sa take har ya parker mota ya zagaya ya fito da Amrah da yake lalla6awa kamar qwai.
  Ya jawota suna tafiya a hankali kmr masu tausayin qasa amma ba don komai suke tafiyar ba sae don Amrah wacce kallo d'aya za'ayi mata a fmhci cikin juriya take taka qafafunta yayinda fu'ad ke kallonta cikin tausayi da nuna so da kulawa.

 Ganin ta daina ganin su yasa ta rufe window ta koma d'akinta ba jimawa taji knocking ta bada izinin shigowa ba tare da taje ta bud'e qofar ba.
  Amrah ta turo qofar a hankali ta shigo.
  Cikin rashin sakin fuska Afrah ke kallon Amrah tace"me ya sami qafar ki da ba kya iya tafiya sosai? Sae da Amrah ta kauda idonta da kallon da Afrah ke mata snn tace"haqqinsa na bashi shine hakan ta faru dani"

*Billy giro😊&Futha luv💅*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:23PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [11/24/2016]  🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
      *```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futuhatulkhair.WordPress.com*

*```🏅90🏅```*
Kuma shine kuka zo abin ki snr dashi sae kinji sauqi tukun, nice nace mai sae munzo sbd banajin zan iya qara kwana d'aya banzo mun sasanta nida ke ba tunda ko na kiraki a waya ba kya d'agawa.
Amma amrah da gani kina jin jiki fa ,ai uncle yamin allura ya kuma bani magani nasha,, kin shiga ruwan zafi? Eh ya sani a ruwan zafi.
Taja hannunta tace"to muje ki d'an kwanta ki huta ko"
Ba musu Amrah taje ta kwanta sbd tana buqace da hutun.
Afrah ta fito ta nufi d'akin Farhan ta same shi ya gama walha yana karatun qur'ani taje kusa dashi ta zauna, har sae da yakai aya ya juyo gareta yace"ya akayi ne Afrah ?murmushi tayi had'e da rungumo shi a hankali tace"uncle karatun ka da dad'i kmr kar ka daina, na ma d'auka fa kayi bacci naga na jima da barinka kana sallah, Yace"Afrah ai kinfi ni zaqin murya gun karatu dole ne fa in kinayi sae mutum ya tsaya ya bada natsuwar sa, hm uncle kenan nagode da zolaya... Au kenan nima zolaya ta kikeyi? Ah ah wlh kaima kasan da gaske nake, ni kuma kinsan da qarya nake, da sauri ta rufe mai baki tace"yi haquri ba haka bane wlh,murmushi yayi yace"to me ya kawo ki kika katse min karatuna?baqi mukayi uncle fu'ad da Amrah, shine nazo nagaya ma nsn uncle fu'ad na downstairs yana jiran fitowar ka, hannunta yaja suka tashi suka fito.

Banyan sun gama gaisawa da fu'ad yake cewa da Afrah taje ta kira Amrah su je su gaida gwaggo.
Afrah taje ta dawo take snr dashi Amrah tayi bacci, Farhan Yace"ashe kun jima da shigowa kenan, cikin jin kunya fu'ad ya d'an sosa byn kanshi yace"bata samu baccin kirki bane bari naje na dubata,nan ya haura sama, Afrah ta wani riqo Farhan ta qanqameshi tana murmushi mai

cike da nuna jin dad'i ,Farhan yace"ke Ifyr ki wannan jin dad'in fa"uhm uncle ba komai.
Fu'ad yana shiga d'akin ya zauna kusa da ita yakai hannu ya shafo gefen fuskarta a hankali ya furta"dear"
Amrah ta bud'e idonta a hnkli ta sauke su akan nashi sae kuma tayi saurin kauda idonta tana qoqarin tashi, da taimakonsa ta tashi zaune ya d'an jawota jikinsa ,ya matsa fuskar shi gab da gefen fuskar ta har suna shafar juna yace"zamu je mu gaida gwaggo ne zaki iya?gyad'a masa kai tayi ,yace"to tashi kiyi tafiya nagani"kawai dai muje zan iya"to tashi muje ,cikin juriya ta tashi ta fara takawa sannu a hankali yana janye da ita a jikinsa har suka fito gurin staircase tayi saurin janye jikinta daga nashi sbd hango Farhan da tayi,taci gaba da takawa kmr ba wani abu har suka sauko ta gaisa da Farhan snn suka d'unguma su duka zuwa 6angaren gwaggo.

Ba qaramin murna gwaggo tayi ba da ganin su sae tambayar su take anzo Ify ya kuma bayan rabuwa ?Alhmdlh shine abinda Amrah da fu'ad suka ce,gwaggo ta qwalawa Raheema kira cewa da mai aikinta sae gashi tazo cikin hanzari gwaggo ta umarce ta da ta kawo lemu da kayan marmari.
Nan take taje ta kawo ta ajiye gaban su fu'ad da Amrah kmr yanda gwaggo ta umarceta.
Amrah ta tsiyaya lemu ta bawa fu'ad ya kar6a yasha ita ma ta tsiyaya tasha, sae da suka d'an jima har an soma fira fu'ad yace"Amrah muje mu d'auko kayan tsarabar su gwaggo kar naje na manta mu koma dasu"
Ba musu Amrah ta tashi suka je suna isa gun mota ya bud'e mata gidan baya yace"shiga ina so zamuyi magana tukun"byn ta shiga shima ya zagaya ya shiga ya ta6a jikinta yace"kinga jikin naki yayi zafi shiyasa naso ace kin haqura mun bar zuwan nan har sae kinji sauqi amma kika qi"to uncle munzo gari kuma ajimu shiru ba muzo ganin gida ba, to amma ai lalura ce, sae ace ba kya jin dad'i kinga za'a mana uzuri ai, ni bana son ace haka dmn za'a min wani tunani na daban, to ai gara hakan da ace duk kika taka sae an fhmci abinda kenan, saurin kallonsa tayi tace"duk jurewar nan da nake yi?lumshe idonsa yayi snn ya ware mata su a hankali yace"eh" kauda idonta tayi da suka ciko tap da qwalla tace"ai duk laifinka ne da kamin da zafi kmr wacce baka so"
Amma Amrah it's ur fault da kika tara min desire har tsawon wata d'aya shiyasa a daren jiya na kasa controlling kaina but i'm really sorry i dnt mean to hurt u , ya fad'i haka ne tare da jawota jikinsa ya kwantar da kanta a qirjinsa sae lallashin ta yake,
cikin sanyin murya tace"to ni ynz uncle ina jin kunyar na koma a sake ganin yanda nake tafiya kuma"to bari naje nace da gwaggo mu zamu tafi...sbd me gsky ah ah gani nake kmr ma don kasan abinda ya faru shine kake ganin kmr ba dai dai nake tafiya ba,kin jure a lokacinda na taso ki daga bacci amma wnn karon da muka fito kin kasa har sae da kowa yayita kallonki, kuka ta fashe dashi tace"ai duk kaine da baka tausaya min ba,dmn wasu amare da dama ba'a gane wani abu ya shiga tsakanin su da mijinsu,amma ni gashi har kallona ake, ta qarashe mgnr cikin muyar kuka sosai ,jin Hawaye sun d'iga kan hannun shi ya d'agota cikin damuwa yana kallon fuskarta yace" dear wai dgske kuka kikeyi Allah wasa nake miki ba wanda ya kalle ki a lokacin da muka fito, na fad'i haka ne kawai don kice mu koma gida sbd ina son ki samu ki huta"
ya zaro handkerchief ya share mata hawayenta yace"is ok fita mu koma kar aga mun jima,nan yakai hannu ta gefensa ya d'auki ledodin da ke ajiye kan seat ,
da suka fito Amrah ta miqa hannu zata kar6a yace ta barshi tace"pls ka bani ko d'aya ce na

samu tamin kara kar a gane tafiyata, murmushi yayi ya miqa mata d'ayar ledar tare da kai babban yatsan sa ta gefen idonta ya share mata en guntayen hawayen da ke gurin tace"thank u,amma ana gane nayi kuka ko? girgiza kansa yayi yace"ko d'aya"
um um uncle nifa inaji kmr ana ganewa, ciro wyrsa yayi a aljihu ya shiga mirror ya bata yace"duba kiga kmr ma yanzu kika gama kwalliya da zafinta sae qyalli kike "bashi wayr tayi byn ta duba tace"uncle kenan baka rabo da wasa.

Anan suka yini gidan har dare shiyasa farhan bai fita koina ba sbd ya samu abokin fira sae fira suke tayi da fu'ad, haka ma Afrah da Amrah d'aki suka shige suna ta firar su.
Bayan sun tafi ne Farhan yaje d'akin Afrah ya sameta ta fito daga wanka d'aure da towel tayi tsaye sae kallon cikinta take tana murmushi ,Farhan ya qaraso yace"keda wa hk? ur unborn child mana sae motsi yake min wai shi baya iya zama kurum,hannu yakai ya shafo cikin ta jikin towel yace"sae kuma naga har ynzu cikin yaqi tasowa but na lura ta jikin ki ya fara nuna girmansa bcs tun daga waist d'inki zuwa hips ya qara fad'i kmr yanda qirjinki yake qara cikowa ,hips d'inta ta kalla tace wai dgske uncle nifa ban ta6a fahimta ba sae da ka fad'a ynz, yajata suka zauna kan gado yana kallonta yace"shiyasa shape d'inki ya qara fitowa kika qara kyau har dai er kibar nan da kikayi ga hasken da kika qara da fresh"hm uncle wai ni yanzu na qara kyau kenan? Sosai kuwa....kaji uncle ba wani dama kyau nane ba unborn child d'inka ya qara min ba"er dariya yayi yace"na yaushe kuma sae dai idan ba kya so sae mu kar6e abin mu nida yarona"
ku kar6e mana ai ni nafison haka kar ku 6ata min tsarin jiki, ta ina kike tunanin zamu 6ata miki tsarin jiki? Nan mana cewa da qirjinta da ta nuna mai,hannu yakai ya yaye mata towel ta iya qirji yace"wnn qirjin fa ki gode Allah in banda tsayi da fad'i da kyau ba abinda yake qarawa"um um ya matse yana ta6a juna,to ai shine mamma mai kyau, but uncle kana ganin inna haifu bazai lalace ba kuwa? Ko d'aya nonon fulani ne dake bare kuma kina tare da doctor mijin doctor, qirjinsa ta bugo
bugu ba mai ciwo ba tace"bayan kayi shiru har yanzu baka ce komai ba game da makaranta ta, ita Amrah gashi har zata fara zuwa.... Au haba!?
wasa nake ba muyi zancen school da ita ba,amma nsn in ta gaya ma uncle fu'ad zai sata cikin time ba kmr ni da aka share ba, ba hk bane Afrah duba maki nake idan cikin nan ya tsufa zaki wahala ne amma da kin haifu ba sai kin yaye ba sae ki fara karatun kawai, to Allah nuna mana lokaci muna masu rai da lafiya, yace"amin tare da gyra mata towel d'inta ya d'aure,snn ya kishingid'a kan gadon yace "yi kisa kayan bacci mu
tafi yau bacci nake ji sosai"ai dole ne uncle tun 3 o'clock na dare da naga ka tashi baka sake kwanciya ba kuma hk kake kullum baka hutawa"to meye amfanin zuwa na duniya ba ibada ba... But bawa nason hutu ,ai ina hutawar sae in kin manta, to ai hutun kad'an ne,to Afrah idan ban gyara lafirata tayi kyau ba me zan gyara ?shine kuma fa ,Allah dai yasa mu dace,yace"Amin,yauwa uncle.....pls Afrah sa kayan baccin ki in munje can mayi magana kinji,"ok to"shine abinda tace taje ta bud'e wardrobe ta d'auki rgr bacci. ,tana gama sa kayan yaja hannunta suka tafi zuwa d'akin shi.

Washe gari Afrah ce ta fito da gudu tana dariya Farhan na biye da ita sae gwalo take masa tana fad'in "yeah na cinye ka!ba shiri taji ya cafko ta duk irin gudun da take yi kuwa bata yi

yunqurin qwatar kanta ba sae qanqame shi tayi tana kallon fuskar shi tana dariya,shima dariyar yake ya shafo cikinta yace"be careful akwai had'ari gudu ga mai juna biyu kuma kin sani"sorry uncle inshaAllah zan kiyaye  murna ta mantar dani abinda ke jikina,takai hannu tana wasa da sajen fuskar shi tace"wai uncle ya akayi ka bari na cinye ka kuma wai tseren mota ne fa,meye abin mamaki kinsan ba ruwana da wata shiriritar games shiyasa ban iya ba, to uncle zaka dai cika min alqawarina da kace inna cinye ka zaka tafi dani  yawo musha ice cream kuma zaka goya ni, to ai ynx 6angaren gwaggo mukayi mu gaishe ta, eh mana ba sae ka goya ni ba da munkai bakin 6angaren sae ka sauke ni,hancin ta ya lakato yace "er wayo to ai nima kisan kince zaki ciyadda ni popcorn kuma kimin tausa,a shwagwa6e tace"ah ah gsky uncle kasan cewa nayi sae idan kayi winning,amma zan maka d'in tunda iyawa ne baka yi ba but ynz goya ni idan mun dawo daga 6angaren gwaggo sae na maka, nan ya zare jikinsa daga nata ya juya bayanshi tare da duqawa sosai ta yanda zata hau bayan nashi cikin sauki,
Dad'i taji har ranta sae murna take ta haye bayanshi ya d'aga da ita cak takai hannyenta duka biyu kan qirjinsa tare da kwantar da kanta a bayanshi sae srt take mai suna tafiya har suka isa a bakin qofar 6angaren gwaggo,
ya sauke ta ta riqa hannunsa suka shiga ciki.

*Billy giro😊&Futha luv💅*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:23PM, 11/30/2016] Billy Geeero: [11/25/2016] 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futuhatulkhair.WordPress.com*

*```🏅91🏅```*
Basu wani  jima sosai ba suka dawo.

D'akin Farhan suka nufa da shigar su ya cire rigarshi tare da kwantawa rub da ciki yace"oya it's ur turn"
baka gama naka ba ai, kinsan ai saida yamma ko muna fita.

Ba tare da tace komai ba ta hau kan gadon ta durqusa kan guiwoyinta ta fara mishi tausa tun daga kan kafad'un shi har zuwa qugunshi cikin salon da tasan zai ji dad'in tausar sosai take bin lallausan jikinsa tana tausa mai,ta jima tana mai tausar shiru ba mai cewa komai sbd wani yanayi da Farhan ya shiga na jin dad'in tausar yasa ya lumshe ido tamkar mai yin bacci,
a kasale ya jawota jikinsa sosai har tsinin hancinsu na ta6a juna ya riqo hannunta ya d'ora mai kiss yace"ya akayi yau kika min tausa mai dad'in gaske haka da har ta janyo min bacci mai dad'i"ba kai ka koya min ba rnr, gud! kin d'auki karatun kenan, ya qara mannata a qirjinsa yace"to taya ni muyi bacci,ba musu ta kar6i tayin da yayi mata, sukayi bacci sae da suka gode Allah .

Sallar zuhur ce ta tashe su bayan ya dawo daga masallaci ya sami Afrah ta gama sallah tayi kwance kan sallaya yaje gab da ita ya durqusa yace"zaki qara yin wani baccin ne? Tashi tayi had'e da cire hijab tace"wane baccin nida ko girki ban mana ba" je dafa mana indomie kawai ta isa ,cikin en mintina goma ta dafo ta dawo cikin d'an qaramin tray ta zuba musu ita sukayi zaune suka ci,suka koma kwanciya ,
ba bacci sukayi ba sae fira kawai har la'asar ta kusa suka tashi suka fad'a wanka suna fitowa Farhan ya shirya ya tafi masallaci ya bar Afrah na shirin fara sallah bayan ta gama ta jawo wyrta sae ga Farhan ya shigo ya kar6i wyr yace"shirin fita zakiyi ba zancen waya ba ,wai Amrah naso kira na qara jin ya jikinta tun safe da mukayi waya bamu sake ba, meya same ta ne?kallon sa tayi tace"ba komai just headache amma taji sauqi, to Allah qara mata sauqin tace"amin" ya miqa mata wyr ta kirata ba su jima ba ta ajiye wyr ta tafi d'akinta zuwa nemn kayan da zata sa. Bayan sun shirya ne suka biya 6angaren gwaggo suka snr da ita zasu fita.

Guraren shaqatawa da dama Farhan ya tafi da Afrah.

Snn kumà ya tafi da ita gurin shopping ta tsinto duk abinda take so iya son ranta sae chocolate ta tsinto kad'an sbd Farhan ya hanata.

Kan hnyr su ta dawowa ne Amrah ta kira Afrah inda cikin farin ciki Afrah ta ajiye wyr ta qanqame Farhan ba tare da ta damu da driven d'inda yake ba,tace"uncle dan Allah mu biya gidan su Amrah naga motar ta da aka saya mata....mashaAllah mota fu'ad ya saya mata? Aa Abban shi ne ya aiko mata kuma tace sak iri d'aya da mota ta shiyasa naji mugun dad'i sbd tana mutuwar son motar ba kad'an ba,kai amma naji mata dad'i fa Allah ya kare ta da shairinta ya sada ta da alhairinta ,Amin uncle.

Gidan su Amrah suka nufa koda suka kunna hancin motar su cikin gidan suka hango fu'ad da Amrah riqe da hannun juna yana qoqarin shigar da Amrah driver seat ya hango su hakan yasa ya washe bakinsa zuwa murmushi kan su qaraso suka isa gurin su ,Afrah ta qanqame Amrah sosai tana tayata murna kmr ita ce aka siya ma motar ,Farhan kuwa hannu ya miqawa fu'ad suka gaisa yayinda ko wannen su ke d'auke da murmushi a fuskar shi.

Sae da suka qarewa motar kallo suna sa Albarka snn suka shiga daga ciki, Amrah ta ja hannun Afrah suka haura sama zuwa d'akinta ,
suna shiga Afrah ta hango glass cup gun fridge ya fashe an tara guri d'aya ba'a riga an kwashe

ba, ta nuna tace"ya haka kin bar abu, hmm uncle fu'ad ne fa zai sha ruwa yaji na saki ihu a bathroom sbd fad'uwar da na tashi yi shine ya saki glass cup d'in ya tafi da gudu,eyyah baki ji ciwo ba ko?um um ko fad'uwar banyi ba fa tsoro ne kawai amma dai naji kunya ba kad'an ba da ya shiga bayin ya same ni ba kaya naji kmr na tsune wlh sbd bai ta6a gani na haka ba ,kinji ki wanda ya saki a ruwan zafi meye naki bai gani ba, uhm Afrah kenan wlh qin yarda nayi na cire ko towel d'in jikina sae d'aga towel d'in na d'anyi da zan zauna a cikin ruwan, hmm zaki daina ne yarinya tun kina jinta har a cire miki ita gabad'aya sbd su ba kunya ne dasu ba sae kiga sun saki jikinsu a gabanki basu damu ba,hm ai haka ya min last night kawai naga mutum ya fito bayi daga shi sae d'an boxer...mtsw baki ga komai ba yarinya sae zuwa gaba,Amrah tace" hmm lallai wani abu sae rayuwar aure nifa kinsan har yau na kasa had'a ido dashi ko na minti d'aya sbd da na kalle shi sae na tuna abinda ya shiga tsakanin mu, shine nake ta mamaki yanda mata da miji ke had'a ido da safe bayan kuma wani abu ya shiga tsakanin su da dare,nikam gsky komai dad'ewar mu bazan iya haka ba.... hhhhh kika ce dai nida uncle duk kallon en iska kike mana da muke had'a ido,rufan asiri cewa fa nayi mamaki mata da mijin da ke had'a ido ke ban,to meye a ciki Allah ne fa yace ayi kuma sunnar annabi ne kawai kedai u are jaki just comin shiyasa kike jin kunya....Amma Afrah kinsan na tsani kalmar J J C ko,dariya kika ban ne yi haquri tashi bani ruwa nasha.

Nan Amrah ta tashi taje gun fridge wacce sam ta manta da fasasshen class cup d'inda ke gurin inda gab take da d'ora qafar ta akai Afrah tayi saurin dakatar da ita tace" kin gani ko da ynz fa kin taka, ya akayi ma wai da aka tara ba a kwashe ba?zai kwashe kenan Abba ya kira shi,shine kan tsananin murnar jin abinda Abba ya gaya mai ya mantar dashi ,ni kuma yana gaya min alherin da Abba yamin ya mantar dani kunyarsa da nake ji na gani na da yayi a bathroom sae qanqameshi ma nayi ina murna,snn na nemi ya kira min Abba na masa godiya har ummansa ma sae da na ma godiya,to kin kira Abban ki kin sanr dashi? eh na kira shi so nake ma na tambayi uncle naji yaushe zai kaini na nuna ma Abbana motar ,gsky kam har mu azo a sake nuna mana, ku da kuka gani zan dai je na nunawa gwaggo ,shin wai jiya ya barki kinje gun abbanki naga kmr dare yayi ,wane dare bayan isha'i ne fa ko tara bata yi ba, da naje ma sae goma da rabi na baro gidan, har ma yake min wani albishir amma bazan gaya miki ba sae maganar ta xaunu....yayi nida banda wani Abba shine kike min kuri, lah!wlh Aa halin Abba na sani yasha min albishiri d'in tun ba yau ba amma har yanzu shiru ba wani bayani.

To Allah yasa muji alhairi ,amin.

Knocking suka ji Amrah taje ta bud'e, fu'ad dake tsaye yace "snr da Afrah ta fito zasu koma"

Amrah ta snr da Afrah ,Afrah ta wani 6ata fuska tace"shi kuma uncle yanzu da shigowar mu zai wani ce mu koma,"nan ta tashi ta nufi downstairs ta bar Amrah na qoqarin nemo mayafin rakiya.

A shagwa6e ta qaraso gurin shi ta zauna tace"pls uncle ka bari har bayan isha'i ko zamu koma kaga ynz magrib ake qoqarin yi"

Kallonta yake kmr ba zai amince ba tace"Dan Allah dai uncle"dariya yayi ya riqo kunnenta yana fad'in "wai ke kin ganki ko mugun wayo kin san bana taka klmr Allah shine kikayi saurin had'a ni da ita"wash uncle sorry" shine abinda tace lokacinda ta riqo hannun sa da ke riqe da kunnenta byñ ya saki kunnen ta fad'a jikin sa tana dariya tace"na tafi ka yarda? Eh jeki kar kiyi

gudu amma ,murmushi tayi tace"thank u"snn ta d'ora mai peck ta tafi inda kai tsaye ta shiga d'akin Amrah ta sami fu'ad zaune close to Amrah gefen fuskar su na ta6a juna ya had'e tafukan hannyensu yana murzawa a hnkli yana mata magana kmr wani mai rad'a yayinda kan Amrah yake done qasa tana murmushin jin kunya daga bisani su duka suka fashe da er dariya suna kallon juna Amrah tayi saurin kauda idonta kan nashi dai dai Afrah ta juya zata bar d'akin,Amrah tayi saurin zare hannunta da yake fmn murzawa tace"Afrah ya zaki koma ko tafiyar kenan? kuyi haquri ban san kana ciki ba, ta fad'i hkne yayinda fu'ad ya tashi zai fita, yace"no ba komai wlh .

Bayan ya fita Amrah ta rufe fuskarta tace"har naji kunyar ki kin riske mu bamu ganki ba har zaki fita, ya zaku ganni kun lula duniyar soyayya sae fmn murza miki hannu ake, wlh tabi'ar sa ce haka duk muna tare ya kama murza min hannu kenan ko gurin kwanciya hakane sae idan yayi bacci zanji ya daina shafar hannun, kuma bashi da wani buri da ya wuce in muna zaune yaji gefen fuskata na shafar tashi ko meye dalilinsa oho,hk ne kowane namiji da salon iyawar sa ni uncle kullum sae na ganshi da wani sabon salo har mamaki yake ban da idean sa bata qarewa sae kace malamin fiqihun soyayya..... Hhh Afrah baki da dama,

wai ya barki har bayan isha'i d'in ko yaya? Eh ya amince baki ga da zama na ba na cire mayafi muji dad'in fira ,wai ban tambaye ki ba Amrah ya jikin naki kinji sauqi,hm bari kedai jin sauqin dole dmn tun da muka dawo uncle fu'ad ya tasa ni gava sae famn yawon shiga ruwan zafi nake duk na fito sae ya maida ni wai bayyi ba na koma da qarshe sae da na masa kuka snn ya barni nayi bacci bayan ya bani magani nasha,koda na tashi da safe kmr bani ba Ify lau,to ai kin gode masa gàshi yanzu kina komai Ify lau, ke ya damu ne sosai ganin yanda nake tafiya duk na taka idonsa yana a kaina haka cikin dare duk na motsa sae yace mene ne ba dai gurin bane ko.... Dariya sukayi harda tafawa sbd yanda Amrah tayi
magana kmr ita ce fu'ad Afrah ce ita, harda wani rungumo Afrah a hnkli taje saitin kunnenta tana magana cikin rad'a had'e da kama hannunta tana murzawa, Afrah tace"wai ke ko farkawa kukayi sae ya murza hannun ki?ai kafin yace komai yake fara murza hannun sauqi na d'aya bana jin takurawa tuni ya riga ya saba min dmn da haka yake tashina bacci, shine kike koyon acting d'insa ko sae na gaya masa nace Amrah ta raina ka har kwaikwayon acting d'inka take, hm wlh ina mugun son acting d'insa komai nasa a natse idan yana magana kyace wani ne kusa damu baya so yaji ,
kwata kwata baya d'aga murya kuma duk yanda yayi magana zanji.

Like my uncle kenan cewar Afrah kafin take cewa"ina ga fa abin daga jinin su ne baki ga ko gwaggo haka take ba?eh wlh su kam Allah ya basu.

Shin Afrah ya ainihin alaqar uncle d'inki da uncle fu'ad take? harara ta dalla mata tace"wannan tamvayar fa? Ni dai gaya min in zaki gaya min,, kinga uncle fu'ad da uncle en wa da qani ne uwa d'aya uba d'aya, Baban uncle shine babba snn baban uncle fu'ad then gwaggo ita ce last born d'insu, uncle bashir kuma yayan mahaifiyar uncle d'ina ce hope getit ,yes haka ne i knew,,er rainin sense kin duk sani kika sani bayani,, sorry kinga anyi magrib ta shi muyi sallah snn muyi zancen cin abinci.

Ana gama sallar isha'i su Farhan suka fito zasu koma ,
har bakin mota fu'ad da Amrah suka raka su basu bar gurin ba sae da suka ga fitar su snn fu'ad

yaja hannun Amrah suka koma daga ciki.

Su farhan kuwa suna isa gida suka fad'a wanka sukayi shirin bacci sukayi zaune suna kallon TV a living room yayinda Afrah ta jawo popcorn tana ciyar da Farhan na alqawarin da ta masa, sae dariya take tana tsoron kai hannu zuwa saka masa popcorn a baki sbd idan taje bashi da yatsunta yake had'awa yad'an ciza cizo ba mai ciyo ba sae ma dariya da cizon ke bata sbd jinsa take kmr yana mata cakulkuli kan yanayin salon cizo irin na Farhan.
Yana cinye popcorn d'in yace"ta qaro mai bai qoshi ba tace "ba wani sae in yatsu na zan baka ka cinye ,ziruf taji ya kama yatsunta guda biyu yasa a bakin shi yana wasa da haurun sa akai ita kuwa tana jin abun kmar cakulkuli sae dariya take tana qyaqyatawa har da su ftr da qwallah , ya d'aga ta cak suka je bedroom ya kwantar da ita yace"wnn dariya haka ya kike ji ne wai yi min naji ,
sae ka qara min tukun ,dariyar bata miki yawa ba Afrah,bari dai gobe na miki ,uhm Uhm nidai kamin, to naji kawo hannun naki da na miki sae mu shiga bacci dare yayi,ya mata rumfa had'e da riqo en yatsunta biyu ya fara mata tana ta fmn dariya.

2 months later
Afrah ce ta shigo d'akin Farhan sanye da half vest sae dogon wando da ya d'an kama jikinta tana riqe da robar ice cream tana sha ,ga d'an cikinta da ya fito a waje, Farhan ya bita da wani kallo har taje ta zauna kusa dashi
tace "kallon fa uncle ?
Yace"ban gane ba nayi sati uku bana gari kuma kizo min bacci da dogon wando, wani irin murmushi tayi tace"nida babynka ne fa muke shan iska tukuna kafin nayi shirin bacci"oh na d'auka ko yau tausayin uncle d'in ne ba a ji,ta wani lumshe ido ta ware su akanshi tace"ni kuwa idan banji tausayin uncle d'ina ba na wa zanji"
Uncle d'inda aka yi ta fushi dashi kan yayi tafiya, to ai dole ne wai kai sae kace baza kaje dani ba,
ta qarashe maganar kmr zata yi kuka,
Yace"am really sorry inshAllah zan tafi dake next time,dagske uncle? Gyad'a mata kai yayi,
tayi murmushi tare da jawo wyrta da ta ajiye kan bedside drawer yace"me zaki yi da waya yanzu ba dai chat ba? No Amrah zan kira mai min gorin miji kullum har tana kiramin gauruwa to yau ga nawa mijin ya dawo,nan tayi dialling numbar Amrah dai dai Farhan ya kishingid'a yana kallon d'an cikinta da ya taso ya qara mata kyau sae motsi yake a hnkli, murmushi yayi yakai hannu yana shafa cikin.
6angaren Amrah kuwa wayrta sae ruri take kan bed yayinda take bathroom sae kwarara amai take fu'ad da ke gefenta duk ya shiga damuwa sae sannu yake mata,ta samu da qyar aman ya tsaya mata sae neman gurin zama take sbd jiri dake shirin d'ibar ta,fu'ad ya riqota ya wanke mata bakinta har fuska snn ya tallabeta cak suka fito sae kallonta yake cike da son ya gane ainihin abinda ke damunta.

*Billy giro😊&Futha luv💅*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

[10:23PM, 11/30/2016] Billy Geeero: ```[11/26/2016]``` 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futuhatulkhair.WordPress.com*

*```🏅92🏅```*
Afrah na ganin kiran har ya katse ba a d'aga ba tace"well ba mamaki tayi bacci naga yanzu saurin bacci ne da ita"
Ta ajiye wayar tana mai kallon Farhan da ya daina yawo da hannunsa ya kuma rufe ido kmr mai bacci, ta kai hannu ta shafo fuskar sa a hankali tace"uncle kayi bacci?
Hannunta ya riqo dake kan fuskar shi yace"baccin lafiya ina sauraren unborn child d'ina ne dake miki yawo ta koina"ta kalli cikin ta shafo tana murmushi tace"ji nake kmr ace ba zai yi qatoto ba yayi zaman sa haka yafi kyau"girma kan dole tunda babyn girma yake qarawa, wlh bana son ya min qatoto sosai na tsani qaton ciki, ai sae dai kiyi haquri...gsky nikam belt zan siya na riqa sawa....da izinin wa, da izinin uncle, to nikam ban amince ba, ta wani 6ata fuska tace"sbd me uncle? Sbd bana ra'ayi ,uhm uhm to uncle so kake idan yayi qatoto in fita ta kamani na fita dashi haka nan, meye a ciki haramun ne ko kuma cikin shege ne?kuka ta fashe mai dashi tace"ba shege bane amma nayi qanqanta a ganni d'auke da ciki, ai sae mutane suyi ta kallona suna nuna ni,abinda yafi nuni ma su miki amma baza ki sa ba.
Cikin fushi ta tashi ta bar mai daki ya bita da kallo har ta fita ,ya gyra kwanciyar sa ya rage hasken d'akin.
Afrah ta jima sosai kafin take dawowa sanye da er fincikar rgr bacci a jikinta sae qamshi take zubawa
ta samu har Farhan yayi bacci abinsa ko kad'an bata ji dad'i ba sbd haqqinsa dake kanta gashi kuma har ya nuna mata yana buqata,
jiki sanyaye ta zauna tana tunanin yanzu zai ce bata tausayin shi gashi ita ko kad'an fushin da

tayi bada  niyyar hana masa haqqinsa tayi ba, taje ne kawai don tayi shirin bacci.
Kwanciya kusa dashi tayi tare da ja musu blanket ta rufa musu jikinsu.

6angaren su fu'ad kuwa zaunar da ita yayi kan bed ta jawo pillow ta kwanta sbd bata jin zata iya zama.
Yace"dear meke miki ciwo ne da kike  faman yin amai haka, ko kinci wani  abu ne da bai kwanta miki ba?ko d'aya uncle haka kawai ina fesa turare naji amai amma bansan meyasa ba, yanzu me kike ji da kika kasa zama ?jiri nake ji but ka bani abu nasha may be yunwa ce,ya tashi yaje ya had'a mata tea mai kauri yace "oya wakeup"da taimakon sa ta jingina a jikin sa ya shiga bata tana sha bata wuce kur6i uku ba tace"nagaji da sha ka bani abu mai sanyi, ,fresh milk ya tsiyayo ya shiga bata sae sha take har tayi rabin cup tace"uncle is ok i wnt sleep,no kar ki kwanta just sleep d way u are, why can't u leave me to lay down on d bed?,bcs laying immediately after eating yana kawo matsaloli ba kad'an ba,shiru tayi sbd baccin ya mata yawa, nan tayi abinta kan jikin sa sae da baccin yayi nisa snn ya kwantar da ita sae kallon yanayin jikinta yake har ya hango hasken da ta qara mussaman yatsun hannunta da na qafa.

Washe gari Farhan ya tashi Afrah tayi sallah tana tashi zaune tace"pls uncle kayi haquri ystday night naje canza kaya ne shine koda na dawo har kayi bacci"ba komai Afrah shine abinda yace snn ya fita.

Ta d'anyi mamakin ganin baiyi fushi da ita ba ta dai basar taje zuwa bathroom.

Koda ya dawo tana kan sallaya tana addu'a bayan ta tofa tayi mishi ina kwana ya amsa ba yabo ba fallasa ,ya d'auko qur'ani taje kusa dashi ta zauna tace"yauwa uncle saukar da mukeyi a sati sati kaga munyi missing 3weeks ba muyi ba na d'auko nawa qur'ani mu fara ta satin nan? A natse ya kalleta yace"meyasa ba ruwanki da damuwa ta Afrah?qwalla ne suka ciko mata ido tayi saurin duqar da kanta yaci gaba da cewa"na fahimci rayuwarki ko shekara nayi ban neme ki ba ba ruwanki harkar gabanki kawai kike ,ba haka ake rayuwar aure ba Afrah ki gyara kinji.
Daga haka yayi shiru yana kallonta sae hawaye take yace"meye na kuka kuma ko baki ji dad'in magana ta bane?girgiza kanta tayi tace"ba haka bane nasan na shiga haqqin ka da yawa pls kayi haquri uncle,ya jawota jikin sa yace is ok ki daina kuka ba komai ya wuce bari mu karanta ko sura d'aya ce sae ki bani abuna ko? Murmushi jin kunya tayi tare da gyad'a masa kai.
Shima murmushi yayi snn suka fara karatun.

Sha biyun rana suka farka daga nannauyan baccin da sukayi sae miqa suke Afrah ta rungumo Farhan a hnkli tace"uncle muje muyi wanka  kar zuhur ta same mu dmn qila d'aya tayi, sha biyu ne yanzu bansan dai wane tunani gwaggo zata yi ba yau bamu je mun gaisheta ba da safe kmr yanda muka sava ko yaushe ,nifa uncle a d'azun har knocking naji...yaushe? shiru ta mishi tare

da kauda kanta gefe hkn yasa ya gano time d'inda take nufi, yayi murmushi yace"to ya akayi baki snr dani ba ko ba kya iya magana a wnn lokacin? Tashi tayi tare da bedsheets a jikinta tace"nidai ban iya yanda ka iyaba kuma ma ai gara ni har naji knocking d'in,yayi miki kyau akwai rnr da zan kama ki ne ai,dariya kawai tayi ta shige bathroom ya bita sukayi wanka suka fito sun gama shiri kenan suka ji knocking Afrah taje ta bud'e ,Raheema mai aikin gwaggo ce a tsaye riqe da kula ta gaida Afrah snn ta miqa mata kular tare da fad'in"gashi gwaggo tace a kawo snn tace ko lafiya taji ku shiru yau? Kice
mata lafiya lau bacci mukayi amma gamu nan shigowa.

Koda ta shiga ciki ta bud'e kular tace"kai gwaggo na sona wlh abinda nake so shine tamin mayemayen shinkafa da ganyen sure,ta rufe kular ta kalli Farhan tace"uncle muje muci don ni yunwa nake ji sosai bazan iya jira har ayi sallah ba,yace"nima yunwar nakeji nan suka je downstairs kan dining suka ci.
Bayan sunyi sallah ne suka je 6angaren gwaggo suka gaishe ta tare da yi mata godiya kan abincin da ta aika musu.

3weeks later Afrah ce keta roqon Farhan kan yaje da ita asibiti bazata yi rashin ji ba ta samu da qyar ya amince suka tafi.
Tafe suke cikin asibiti suka had'u da matar da Afrah ta ta6a tsarawa d'auke da cikinta da har ya soma fitowa Afrah tace"lah Anti kin gane ni? Matar tace"ai bazan manta ki ba,kodan hasashenki da ya zamo gaskiya a gare ni ba qaramin farin ciki nayi ba na kuma gode Allah sosai dmn ya bani abinda na jima ina nema, ta kawo qarshen zancenta kenan idonta ya fad'a kan cikin Afrah tace"ikon Allah ciki ne nake gani a tare dake ko kuwa? Mugun kunya Afrah taji tayi saurin zuwa bayan Farhan ta 6uya ,mtr tace barkalla wnn cikin da gani tun lokacin had'uwar mu kina d'auke dashi wato kenan da auren ki er yarinya dake abin gwanin sha'awa ,matrka ce kenan doctor? Farhan yace"eh matata ce, to Allah ya baku zamn lafiya da zuri'a d'ayiba Farhan yace "amin mungode"
Tayiwa Afrah sae anjima ta wuce.

Bayan sunje office Farhan ya kalli Afrah da ta wani sha toka cike da son tayi kuka, yace"me akayi kuma? Ba kai bane kafin mu fito na tambaye ka ana gane cikina ya fito kace min a'a,amma Afrah ai kinsan da wasa nake miki inace kinga yanda cikin nan ya qara girma zama d'aya ba sae kin tamvaya ba ma kinsan dole a ganshi, to ba qatoton hijabi na saka ba kuma rgr jikina mai 6oyon ciki ce fa,ni bazan ma qara fita ba daga yau, ta qarashe maganar cikin kuka ta tashi ta tafi daga ciki gurin hutawa ta kwanta tun tana kuka har tayi bacci.
Har ya gama aikin sa Afrah bacci take.
Yaje ya sameta ya durqusa kusa da ita yana kiran sunan ta yace"tashi muje gida "ta tashi tace "ni bazan fita ba sae kowa ya watse ,tashi muje na baki briefcase ki riqa sae ki kare cikin ki da ita ta yanda baza a gane ba, ba musu ta tashi suka fito suna zowa parking space suka had'u da fu'ad shi da Amrah wacce kallo d'aya zakayi mata kasan bata da lafiya dmn wani irin haske tayi da rama, da mamaki Afrah tace"Amrah lfyr ki kuwa, duqar da kanta tayi ta kalli fu'ad ta gefen ido, murmushi yayi ya kauda idonsa sbd ya gano me kallon ke nufi, Afrah tace"Amrah ina magana dake kin min shiru ,ba komai d'an zazza6i nayi amma naji sauqi, shine Amrah duk wyr

da muke yi baki gaya min ba, sorry naga ba wani zazza6i mai qarfi bane, jin abinda tace yasa fu'ad ya kalle ta bai ce komai ba dai dmn ysn bata son tayar da hnklin er uwarta ne amma ta darji ciwo ba kad'an ba ko yau tausayinta yaji sosai ganin bata iya komai ga kuma kad'aici ita kad'ai a gida shine yazo da ita ko abin zai mata sauqi.
Jirin dake shirin d'ibar Amrah ne yasa tace"bari muje gida Afrah ma qarasa maganar kinji,can gidan mu ko kuwa? Eh can mukayi dama.

6angaren gwaggo suka tafi gabad'ayan su,fu'ad na gama gaisawa da gwaggo ya tafi, shima Farhan ya tafi 6anfaren su dmn ya samu ya watsa ruwa.
Afrah kuwa Abinci suke ci ita da Amrah bayan sun gama ne Afrah ta jata zuwa 6angaren su sbd tana son ta d'an watsa ruwa ita ma.
Da mamaki Amrah ke kallon Afrah dake d'aure da towel zata je bathroom tace"kai!barikallah ya naga cikin ki ya girma hk zama d'aya ?hm bari kedai nima na tsorata da girman sa sae wani nauyi da ya qara min shiyasa ko dogon tsayi bana son yi ynx,Amrah tace"ko dai en biyu kika kwaso mana ne? Ko en uku ba, cewar Afrah wacce ranta yayi mugun 6aci ta wuce bathroom ba tare ta sake cewa komai ba.
Har ta fito shaye da toka Amrah tace"ke daga kawai na ambaci en biyu sai kawai ki tsiri fushi dani? To ya zaki ce min haka ,yama zan iya haifuwar en biyu idan ba so kike na mutu gurin haifuwa ba mtsw ni ko da wasa kar ki qara ambata min en biyu bana so, idan Allah ya baki ai sae kice ba kya s.......amai ya hanata qarasa mgnr ta tafi da gudu sae bayi, da taimakon Afrah ta wanke bakinta ta fito ta nemi guri ta kwanta sbd jiri ba zai bar ta iya zama ba,da kulawa Afrah ke kallonta tace"Amrah ciki ne dake ko? Shiru Amrah ta mata dmn tasan ciki ne da ita amma kunya take ji a sani shiyasa ta roqi fu'ad kan kar ya snr da kowa.
Tace"dake nake magana ?haba Afrah wane irin ciki ni ki barni na huta dan Allah,hm yrinya ko kiso ko kar kiso ciki ne dake ko hasken da kikayi kad'ai ya ishi ya fhmtar, nifa ba ciki bane shawara ce dani don kar kije ki snr da gwaggo nasan halinki, hhhh nayi wnn yarinya indai ciki ne baya 6oyuwa gamu gani dai tunda kince bashi bane.

Yinin rnr kafin Amrah ta koma sae da kowa ya fahimci ciki ne da ita sbd yawan aman da take yi da kuma jirin da ke yawan d'ibar ta, gwaggo baki yaqi rufuwa sae murna take.
Afrah kuwa sae tsula ma Amrah tsiya take tana mata dariya.

Tun da labari yaje gun iyayen fu'ad ko yaushe mahaifiyar Fu'ad cikin kiran wyr Amrah take tana tambayar lafiyar jikinta.
A qarshen satin sae da taxo daga Abuja takanas don kawai tazo ta duba Amrah wacce Alhmdlh ynz jiki yayi sauqi.
Sosai suke shiri da gwaggo shiyasa tayo mata tsarava kala kala ta kawo mata ,bayan wacce ta ba su Afrah ,Amrah kuwa ba'a zancenta dmn har kayan wasan baby ta siyo mata kan tsananin farin cikin zata sami jika gun d'anta qwaya d'aya tal da Allah ya basu.

Sannu sannu rayuwa keta tafiya inda yanzu cikin Afrah watan sa tara cikin da yayi girman wuce misali da duk wanda ya gani sae yayi mata tunanin en uku ne a ciki ba ma biyu ba.

Yanzu bata da ikon saukowa downstairs sae da taimakon Farhan gashi tunda cikin ya tsufa wani zafin bala'i ya taso mata da bata jin sanyin Ac zai mata maganin shi ga Farhan ya hanata shan qanqara duk da ba irin kukan da bata yi ba kuwa har tana cewa don bashi ke d'auke da cikin bane, shi kuma ba don komai ya hanata ba sae don gudun kar unborn child d'insa ya kamu da cinyon sanyi sbd shan qanqarar take tmkr Allah ne ya aikota.
Yanzu bata da gurin zaman da ya wuce garden kusan ko yaushe tana can bata da wani aiki sae shan fresh air sallah da komai can takeyin abinta sae ta gama shan iskan tane take komawa daga ciki in ta shiga kuma ba wani aikin take yi ba sae kwanciya tayi kallo sbd bata iya aikin komai hatta girki yanzu a 6anggaren gwaggo ake kawo musu abinci ,kuma idan Raheema ta gama aikinda take yiwa gwaggo, gwaggo ta kan izo ta nan 6angaren su Afrah sbd ta riqa taimakawa Afrah da wani abu.

Guraren bayan la'asar gari yayi luf kmr za'ayi ruwa Afrah ta matsu ta fito taje garden shan iska dmn tasan yanda yanayin garin yayi iskan yau zai fi na kullum dad'i.
Farhan ya fito daga gurin wanka cikin sauri yace"sorry yau na shiga time d'in fitar ki zuwa garden ko? Gasky kam na matsu banje ba sae jiran fitowar ka nake ,ko mai bai tsaya shafawa ba ya nemo jallabiya ya saka yaje ya kamata ta tashi tace"waih!uncle nauyi"kallonta yake da kulawa yace"sannu kinji"ta gyad'a masa kai cikin shagwa6a tace"Allah babyn nan naka nida shine in ya fito ya wahaldani ba kad'an ba wlh duk na tashi tsaye sae naji kmr na fasa ihu don nauyi, cike da tausayinta yake ta mata sannu yayinda suka fara tafiya har suka fito gun staircase Afrah tace"plz uncle kafin mu fara sauka a bari na d'an zauna na huta, bari na d'auke ki..... cab! wlh a'a inada nauyi kbr shi Allah ma ya biyaka don kana qoqari dani ba kad'an ba, murmushi kawai yayi yaje zuwa d'aukar ta tayi sauri zata zauna sbd har ga Allah bata son ya d'auke ta ya wahala,wani irin ihu ta saki kafin takai zaune tace"na shiga uku uncle zan mutu bayana da cikina zasu tsage ah!wayyo uncle zan mutu wlh! dan Allah ka taimake ni uncle!duk Farhan ya rikice yana kallon Afrah dake durqushe tana ihu sae fmn yarfi take da hannu.
Cikin rud'u ya d'auketa ya kaita downstairs ya ajiye ya tafi 6angaren gwaggo ya snr da ita dmn ya fahimci haifuwa ce tazo mata kai tsaye.

Bai jira gwaggo ba ya dawo ya d'auki Afrah ya saka a mota gwaggo na isowa suka wuce asibiti.
iya wahala Afrah tasha har ana tunanin yi mata aiki sbd jikinta kwata kwata ba qarfi bata iya yunqurin haifuwa ,Allah da ikonsa har ana gav da yankata ta suntu6o 'ya'yanta guda biyu boy en girl da sukayi bala'in kama da Farhan tu6ul tu6ul dasu jawur kmr a qwanta jini ya fito.
Byn sun koma gida rungume take a jikin Farhan tana kallon 'ya'yan da ta haifa da idanuwanta da suka qabe kan kuka,Farhan ya kai hannu ya d'auki yaran ya rungume su qam a qirjinsa yana mai gode Allah da ya bashi jinsi biyu at d same time.

*Billy giro 😊&Futha Luv💅*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:23PM, 11/30/2016] Billy Geeero: *[11/27/2016]* 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futuhatulkhair.WordPress.com*

*```🏅93🏅```*
Ya ajiye yaran yana kallon Afrah da ke qoqarin kwanciya, yace"Afrah tashi ki d'anci wani abu tukun kafin yaran nan su farka su buqaci mamma.
Fasa kwanciyar tayi ta zauna ya jawo stool tare da ware ledar da ke saman shi, naman rago ne gasasshe mai kyau da shiga rai, ya d'auko tsoka d'aya yakai a bakinta, bata bud'e bakin ba sae jinginawa tayi a jikin sa tace"uncle ni tea nake son na sha, ba musu ya had'a mata tea mai kauri ya bata tasha.
Sae ga gwaggo ta shigo d'auke da kula ta ajiye tace"ka qoqarta ta cinye abinda ke ciki kaf har romuwar"yace"inshaAllah gwaggo snn ta fita.
Farfesun nmn rago ne da aka had'a shi da ganyen shuwaka.
Ya zuba mata ya fara bata kenan ta wani 6ata fuska yace"mene ne ba dad'i? d'iba tayi ta sa mai a baki yaci yace"wai shuwaka ?tace" eh mana shine har gwaggo ke fad'in na cinye duka gsky ni bazan iya shan farfesun nan ba, amma Afrah ni dad'in sa naji ba wani d'aci sosai, to uncle ai kasan ko ya d'aci yake bana son sa ,haquri zakiyi Afrah shuwaka abu ce da take da matuqar amfani a jiki musamman ga wacce ta haifu,kiyi haquri kisha kinji,maqale kafad'a tayi tace"gaskiya uncle bazan iya sha ba, lallashin ta ya shiga yi taqi kan dole ya shiga bata sae kuka take tana ci har sae da tayi rabi snn ya barta yakai hannu yana share mata hawaye cikin fushi take son barin jikin shi ya riqo kumatunta Yace"kar kiyi fushi mana, bari na rage miki d'acin kallonsa take yana matso fuskar a hankali har ya had'e bakinsu can ya zare yana kallon yaran sa da suka tashi daga bacci ,ya maida dubansa gareta yace"na qara rage miki d'acin? ta sadda kanta qasa tace"Aa d'acin ya rage sae ma d'an wani zaqi da nake ji,, yace"to kinga yaran mu sun tashi suna buqatar su sha mamma, ni ai fushi nake yi dasu tunda suka wahalarda ni sae dai susha madara ba dai mammana ba, cikin shagwa6a take maganar yace"yarana ne fa Afrah ki basu ko don ni, murmushi tayi tare da nuna shi tace"don kai? Ya gyad'a mata kai yana kallon

cikin idonta tace"to zan basu amma ka fita kunyar ka nake ji"kai Afrah ni kike kunya yau? Allah da gaske nake uncle.
Ya tashi tare da fad'in "ok feed them well n secure"

Yana fita ta d'auki mace cikin so da kulawa take kallonta ta samu da qyar ta iya fara bata sbd ciwon da take ji haka dai ta jure ta ci gaba da bata, ta gama bata ta d'auko namiji zata bashi kenan taji za'a shigo tayi saurin mayadda mammanta ta gyara rigar ta, Amrah wacce ta shigo tace"ke nice fa huta da 6oyon mamma "Afrah dai bata ce komai ba har Amrah taje ta zauna kusa da ita ta d'auki baby girl tana kallo cike da sha'awa tace"wow barikalla snn ta kalli Afrah tace"sannu kinji kinsha fama"ta kalli baby boy dake jikin Afrah tace"ki bashi mamma mana kinga kuka yake qoqarin yi, Afrah tace"ke nifa kunya nakeji na shayar a gaban kowa don ko uncle na kasa shayarwa a gaban shi"to wai me? Wlh wai kunya nakeji yau nice uwa ina shayarwa sae kace a mafarki, hm Afrah kenan daga kawai Allah ya kaiki gaba abin kiyi feeling as kin zama babba,au haba to daga yau Anti Afrah sama da qasa, ta riqe kunnenta tace "bari ma na miki hud'ubar da ban miki ba, kar inji kar in gani aure ba abin wasa bane ki bi mijinki sau da qafa,yi nayi bari na bari,kuma shi zamn aure dole sae da haquri dmn duk nan da kika ganmu da haquri mukeyin zaman aure amma fa idan ya 6ata miki rai ki nuna masa 6acin ranki, uncle kike kira masa amma da ya 6ata miki rai ce masa kai fu'ad! dan yasan ranki ya 6aci dgske ehe!dariya Amrah tayi tace"Allah ya shirye ki" gaskiya na fad'a miki fa namiji idan baka nuna 6acin ranka zai maida ke bora duk abinda ya kwaso sae saman kanki,to Anti Afrah naji sae kace ke kiran sunan uncle d'in naki kike idan ya 6ata miki rai, dariya tayi tace"ai kinsan tun tashi na ko da wasa bana kiran sunan uncle dmn sunan babba ne a gurina ina girmama sunan ba kad'an ba,Amrah tace"to ki dai shayadda yaron mutane kinga har ya fara kuka,nifa dagaske bazan iya shayar dashi kina kallo ba sae dai na juya miki baya, ke kunya ne dake hln,na dai ji ko banda ita yau ina jinta.
nan ta juya bayanta ta shiga shayar da yaron har sae da ya qoshi inda cikin wash da komai aka kammala bashi, Amrah ta shinfid'e baby girl ta kar6i baby boy sae ga gwaggo ta shigo d'auke da flask d'in kunu ta ajiye ta kalli Amrah tace"ke kin manta da fu'ad ne da kika barshi yana zaman jiran ki kai masa yara?
gwaggo na samu tana shayadda su ne shiyasa sae ynz ta gama,to d'auke su ki kaimai shi kad'ai ne a falo bansan inda Farhan ya shiga ba ya barshi zaune shi kad'ai.

Kafin ta qaraso gurin shi yayi sauri yaje ya kar6i d'aya snn sukaje suka zauna ya kalli baby boy d'inda ke hannun shi yace"nima zaki haifo min mai kama dani, kinga Afrah ta haifo masu kama da Farhan,murmushi jin kunya tayi tace"ni duk ma na tsorata da jin yanda Afrah ta wahala gurin haifuwa sae tausayin kaina nake ji" kar ki damu kowa da irin haifuwar sa sae kiga kina bacci kin haifo min d'ana tashin ki kawai zanyi na nuna miki mai kama dani,dariya tayi tace"wlh da ana haifuwa haka da na fi kowa farin ciki,wai ina uncle ya tafi ya barka? Baqinsa zai shigo dasu tashi ki koma daga ciki bcs nan zai shigo dasu, ok to na bar yaran ko na koma dasu ?bar su mana ai su aka zo gani, ok bye, yace"bye dear"

koda Amrah ta koma d'akin sae ihun Afrah taji ta fito daga bathroom d'aure da towel gwaggo na

biye da ita Afrah tace"gwaggo fa nayi wanka da dawowar mu,gwaggo tace ai na gaya miki kin d'auraye jiki ne kawai don na tabbatar bada ruwan zafin kirki kikayi wankan ba,to gwaggo wlh ruwan zafin da kika had'a min zafi ne dasu sosai.

Farhan ne ya shigo ya same su yace"gwaggo je zuwa aikin ki nasan yanda zanyi da ita.

Byn gwaggo ta fita yace"Afrah gaya min gaskiya tsakanin ki da Allah da ruwan zafin da ke gasa jiki kikayi wanka d'azun? Cike da son tayi kuka tace"Aa but.... Shiiii!ba sai kin d'ora da wata magana ba muje bathroom,

nan yaja hanunta sae kuka take har suka shiga.

Jiki sanyaye Amrah ta zauna sbd tausayin er uwar ta, bayan ta wahala gun haifuwa kuma rad'ad'in haifuwa na tare da ita ace ta shiga ruwan zafi.

Fu'ad ne ya shigo d'auke da yara ya ajiye su kan bed yana kallon Amrah da tayi suku suku, ya zauna tare da riqo hannunta yana murzawa a hankali yace"dear what happen? Kan tace komai tayi saurin qanqame shi cike da jin zafin ihun Afrah da taji ,fu'ad ya d'ago fuskarta a hankali yana kallon idonta da suka cika tap da qwalla, yace"mene ne na kuka dear ?kana nufin baka ji ihun Afrah ba?naji amma nsn tana tare da Farhan kuma ihun da tayi ba zai wuce raki irin naku na mata ba ,ba wani don kawai abin baya faruwa daku shine komai mukayi kuce raki ne damu ba kwa ko jin tausayin mu, snn ko banza Afrah bata son ruwan zafi duk yanda suke zafin su take ji,qara rungume ta yayi yace"am sorry ai kinji ta rage ihu da alama ya rage mata zafin ruwan,bari na tafi ma kafin su fito,sae da yayi pecking nata snn ya tafi.

Afrah ta riga Farhan fitowa tana zuwa ta fad'a kan bed tana kuka mara sauti.

Da damuwa ya fito yana kallonta yace"sorry Afrah tashi ki shirya kanki kinsan ba zai yu ki zauna haka ba yanzu jikin ki zai iya 6aci"

Cikin shagwa6a ta fizge hannunta da ya riqo da niyyar tada ta zaune tace"ni ka rabu dani"ya kalli Amrah yace"fu'ad fa ko ya koma gida ,Aa yanzu ya fita kuma na maji kafin ya qarasa fita yana waya da uncle JB kan zasu shigo shida maman shi da matar shi nasn zai jira zuwan su,"ok tom"shine abinda yace ya tashi yana mai kallon Afrah ya fita.

Yana fita Afrah ta tashi ta shirya.

Guraren qarfe goma na dare Afrah ce zaune kan bed can nesa ta had'e kai da guiwo ga yara kwance a gefenta sae sharar baccin su suke.

Farhan ya fito daga wanka d'aure da towel a qugunsa ta d'ago tana kallon shi da idanuwanta da suka cika tap da qwallah,

Yaje gab da ita ya zauna yace"poppy luv wa ya ta6a min ke?

ba gwaggo bace bayan ta tasa ni gaba na cinye farfesun en ciki mai had'e da ganyen shuwaka wai kuma shine tace kunnun da ta kawo d'azun a flask na tabbatar kafin safe ba komai, kisha ko kad'an ne ba sae kin shanye ba kinji,ta wani yamutse fuska tana kallon shi tace"uncle da ganyen shuwaka fa aka yi shi"eh amma zan sa miki madara a ciki sae kiji dad'in sha ko? Maqale kafad'a tayi yace"to so kike gobe da safe gwaggo taga baki sha komai ba taji ba dad'i bayan duk wahalar nan da tayi dake yau? um um bana son gawggo taji ba dad'i,to nasa miki

kisha?gyad'a masa kai tayi, ya tashi yaje ya d'ibar mata kunun a cup yasa madara ya motse yazo ya miqa mata yayi zaune had'e da tagumi yana kallon yaransa cike da sha'awa ,
kur6i d'aya tayi ta 6ata fuska ta d'ago tana kallon shi taga sajen fuskar sa ya kwanta luf sae yayi mata mugun kyau kmr wani  balarabe,shafo sajen tayi a hnkli, ya d'ago yana kallonta ta sakar mai murmushi tace"kayi min kyau uncle"

*Billy giro😊&Futha Luv💅*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:23PM, 11/30/2016] Billy Geeero: 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futuhatulkhair.WordPress.com*

*```🏅94🏅```*
Saurin kama cup d'in hanunta yayi ganin kunun zai zuba Afrah tace"sorry"no ai bai zuba ba, ya jawota ya zaunar kan jikinsa ya shiga bata kunun sae sha take tana kallon yaran har ta shanye kunun sbd ba wani  yawa ne dashi sosai ba,ya ajiye cup ya zaro tissue ya goge mata bakinta wacce still idonta na kan yaran yace"kema suna baki sha'awa sosai ko?kunya taji ta kauda idonta tace"nifa uncle don sunyi kama da kaine nake kallon su"ba wani  kedai 'ya'ya na sha'awa suke baki shine har ba kya son qyaftawa idan kina kallon su"turo baki tayi tace"nida mà ba ruwana dasu sunci arziqin kàmar ku shiyasa ma nake d'an kulasu"
to naji dai gaya min meyasa kika ce na miki kyau, nima haka kawai naga yau kamin kyau ,menayi haske na qara ko qiba ko rama? Ammm kayi haske kuma kayi er qiba ,shi kawai?eh, to bari na gaya miki abinda baki sani ba shine
basu suka sani nayi kyau ba farin cikin samun 'ya'yana ne,,, dagaske? Yep haka nake idan ina cikin matsanancin farin ciki baki ta6a lura ba?baka ta6a irin farin cikin nan ba taya zan lura, um

um kin dai manta rnr da na fara samun ki as my wife, that's our first night nayi farin ciki ba kad'an ba,hm uncle kaidai kafi farin ciki akan yaranka dmn ni banga hk a tare da kai ba a wnn lokacin, taya zaki lura byn rnr guduwa kikayi"ni uncle kunya nake ji a daina zancen nan, naji kwanta kiyi bacci bcs u have to sleep.

Ta kwanta ya tashi ya nemo jallabiya ya zuba ya d'auko sallaya tace"uncle ba yanzu xaka yi bacci ba kenan? Taya kike tunanin zan iya bacci yau ai sai dai na duqufa gun godewa ubangijina da ya axurtani da yara har biyu a lokaci d'aya,tayi murmushi tace"that's y i love u but idan ka kai time d'inda ya kamata kayi bacci dan Allah kayi bacci uncle sbd shi Allah har ko yaushe cikiñ gode masa ake baza a ta6a daina gode masa ba dmn yafi da hakan sae dai a kwatanta kawai,, to my Afrah get sleep.

Nan ya fara sallah tun tana kallon shi har tayi bacci.

Bacci take mai dad'in gaske da ta jima bata yi irin shi ba, yara suka tashe ta ta tashi taje bayi ta dawo

Tayi tsaye tana kallon yanda suke qoqarin ftr da sautin kukan su gashi ko kad'an bata son su tada Farhan.

dabara ce ta fad'o mata taje a hnkli ta d'auki yaran sae Allah Allah take kar ta kadasu sbd bata iya d'aukar su su biyu ba wai ita a wautar ta duka su biyu zata runguma a hannunta kmr yanda ake d'aukar jariri d'aya,

ba ma ta d'ora kowanen su a d'ayan kafad'ar ta ba ,ai kuwa kai tsaye taji baby girl ta sa6ule a hannunta ta fad'a kan bed sae kawai ta fashe da kuka sosai kan tsoratar da yayi ,firgigit Farhan ya tashi ya d'auki baby girl da sauri snn ya kalli Afrah wacce ta saki ido kan tsoro yace"me yake faruwa ne? Uncle sorry fad'uwa tayi sbd ban iya d'aukar su ba ,to meyasa zaki d'auke su su duka biyu ?kukan su naga yana so ya tashe ka ni kuma bana so dmn nsn baka jima da kwanciya ba shine nayi tunanin naje dasu living room na shayar dàsu, ajiyar zuciya ya sauke yace"my Afrah kar ki soma yin haka daga yau ki riqa zamnki a nn kina shayar dasu idan sun tashe ni ai yarana ne ba komai "

Oya kar6e ta ki fara bata a samu tayi shiru, ta ajiye baby boy taje zuwa kar6ar baby girl ya kalli yanda idonta suka ciko da qwallah yace"ko ta samu buguwa a wani guri ne? um um kan bed kawai ta fad'a kuma ban ko d'aga dasu sosai ba dn ko miqewa tsaye ban qarasa yi ba,to ya naga kmr zakiyi kuka? tsoro ne kawai da naji.

Ok sorry take her, ta kar6eta ta zauna ta bashi bai tana shayarda ita sae da ta koma bacci snn ta shimfid'ar da ita ta kar6i baby boy da Farhan keta fmn jijjigawa kan kukan da yake.

Bayan ta gama ne suka sa yaran a tsakiyar su suka koma bacci.

Washe gari har qarfe goma Afrah bacci take ita da yaranta .

Gwaggo ta shigo ta ajiye kayan da ke hannunta snn ta kar6o wasu dake hannun Raheema dake tsaye a bakin qofa ta shiga dasu ta ajiye tace da Farhan dake kar6ar kyn yana ajiyewa"wai tashin ta suke tatayi da dare ne ? Sau d'aya ne kawai dai yaran akwai bacci but ita Afrah she deserve it bcs tunda muka dawo daga asibiti bata samu tayi bacci ba sae dare, to nikam zan yiwa yara wanka sbd kar a fara shigowa barka yara ba wanka, haka ne kam gwaggo.

Wankan da akeyiwa yara suna kuka shi ya tashi Afrah ta tashi a hankali ta zauna snn tayi wa

gwaggo ina kwana da gajiyar aiki ,gwaggo tace"lafiya lau ya jikin naki ba wata matsala ko?Alhlmdlh ba komai,to Farhan da ka had'a mata ruwan zafi tayi wanka......um um bana so ni zan had'a abuna da kaina, gwaggo tace"ke ruwan zafi kike had'awa ko abu da kama....uhm uhm gwaggo da zafi yake had'a min,to so kike ki koma tsofuwa ki raku6e zama d'aya jiki bai sami gashin kirki ba,to ai ba dole sae ruwan zafi ba ko magani nasha zan bi normal ,to naji dai jeki kinga har Farhan tuni ya shiga bayi yana had'a ruwan ,kamar tayi kuka ta tashi ta tu6e ta fad'a bayi, Farhan dake cikin bathroom d'in ya kalleta da kulawa ya riqo hannuwnta yana magana cikin rarrashi yace"pls Afrah kiyi wankan qwarai kinji,idan bakiyi wankan kirki ba zan duba ki ne dmn zan gane na kuma maida ke na miki wankan da kaina, to uncle ciwo fa ka sani, jurewa zakiyi my Afrah kuma ki dirza jikin ki sosai kinji, then dan Allah kar kice zaki qara sirka ruwan ,inshaAllah uncle zanyi yanda kamin jiya sbd naji dad'in wankan daga baya, that's gud my dear Afrah kinga amfanin wanka mai kyau kenan,uhm amma uncle zan d'anyi ihu ko zanji damar zafi,murmushi yayi yace" kiyi ihun bada yawa ba amma"

Bayan ta fito ta shirya aka bata yaran ta shayar dasu sbd kukan da suke,cikin kulawa gwaggo tasa ta gaba tayi break fast .

Haka taci gaba da samun kulawa sosai gun gwaggo har rnr suna tazo akayi biki shagali yara suka ci sunan *Suhail da suhailat*

Ana gama biki da bayan magrib Amrah ta koma gida sbd wani  irin zazza6i da ya taso mata ,fu'ad ya shiga damuwa ba kad'an ba don komai bata iya yi sae da taimakon sa ne ma ta samu tayi wanka ,ya tasa ta gaba taci abinci ba don taso ba, ko ruwa bata samu tasha ba bacci yayi awon gaba da ita nan ya dubata ya gano ba komai bane face d'inbin gajiyar aiki da kuma zama da yunwa.

Ba ita ta farka ba sae guraren qarfe goma taje bathroom tayi arwala ta fito ta sami fu'ad zaune ya taso ya riqo hannyenta yana murzawa as usual yace"ba dai zazza6in bane ko, naji jikin naki ba zafi ynz? Eh bashi bane tashi nayi dmn nayi sallah kasan banyi isha'i ba,kallon cikinta yayi da ya fara fitowa yayi murmushin jin dad'i tare da kai hannu ya shafo cikin,Amrah bata ce komai ba sae hannunsa take kallo dake yawo kan cikinta, oops sorry kar na 6ata miki time je kiyi sallar.
  Hannunta ta xare a hnkli cikin nashi snn ta wuce.

6angaren su Afrah kuwa.
Afrah ta fito daga bathroom ta sami Farhan ya shigo d'akinta bcs dama a d'akinta take , bacci ne yake kawo mata kullum.
  Kallon sa take yana ma Suhail da Suhalait addu'a dake kwañce cikin d'an gadon su suna bacci ,taje a hankali ta rungumoshi ta baya ya juyo ya d'aga ta cak suka je kan bed ya kai hannu ya rage hasken d'akin snn ya kwanta Afrah na kan qirjinsa yana shafa bayanta har tayi bacci snn shima yayi bacci.

Sannu sannu lokaci keta tafiya yanzu har cikin Amrah ya shiga wata tara.

6angaren gwaggo suke ita da Afrah suna
fira sbd yau tazo yini gida Suhail da suhailat na hannun Raheema sae wasa take musu gashi sun qara qiba sunyi matuqar qara kyau abin ba'a cewa komai sae kace 'ya'ayan larabawa.
Afrah ta kalli cikin Amrah tace"ke kam kin huta cikin ki ba hayaniya dai dai ke ba kamar ni ba da har fita na daina yi kan girmansa "hm Afrah kenan ke cikin en biyu ne dake fa ni kuma da gani d'a d'aya ne.....wayr Amrah ta shiga ringing kallon wayr kawai tayi ta basar bayan sak taga sunan da ke yawo akai wato switat.
Afrah tace"ban gane uncle fu'ad na kiranki ba kin wani kauda fuska"bari kedai yau da safe fad'a mukayi.... Oh no why?wai shi ba zai barni na dawo gida haifuwa ba a can zan zauna na rasa wa yake son ya kula dani can d'in,ke ko Amrah baki sani ba ko zai nemo wata mai kula dake....Ba wani shi kawai lokacin haifuwar ki ne ya birge shi ganin kinyi zamanki a 6angaren ku ,
taya ma zai had'ani dake keda gida d'aya kuke da gwaggo ni kuma ba ko anguwa d'aya ba kuma ba wani d'an uwa da muke da a anguwar,
Kuma sam ba hujja bace ma yace wai bazan dawo gida haihuwa ba,Afrah ta nisa kan tace komai suka ji sallamar yaro ana kiran Amrah,Afrah tace"ce masa gata nan zuwa snn tace"bawan Allah nasan duk yaji ba dad'i shine har ya biyoki, Amrah dai komai bata ce ba ta nemi hijab ta tafi tunda ta hango motar shi ta qara d'aure fuskar nan tamau taje ta shiga motar ta rufe ba tare da tace dashi uffan ba asali ma ko kallon gefensa bata yi ba, as usual ya riqo hannunta zai fara murza ta fizge hannun ta rungume duka hannayenta biyu a qirjinta, komai kasa ce mata yayi sae kallonta yake can yace"Amrah baki fahimce ni bane bana jin dad'i idan kika tafi kika barni but i dnt mean to hurt u....u mean to hurt me uncle bcs cikin fad'a kake min magana har kana daka min tsawa bayan ni cikin rarrashi nake ma magana, ta qarashe maganar cike da son tayi kuka, hkn yasa fu'ad ya qara shiga damuwa yace"kiyi haquri raina ne ya 6aci ganin kinqi ki fahimce ne shine ma yñz nazo na qara fhmtar dake ni mai iya kula dake ne ba sai kinzo gida ba.... Wato ma ba zuwa kayi kace ka amince ba ,
sae kawai ta fashe da kuka tana qoqarin fita daga motar yayi saurin jawota jikinsa sae zille mai take,
bata iya qwatar kanta ba sbd yanda ya matse ta a qirjinsa hkn yasa ta ci gaba da kuka a jikinsa ,fu'ad ya rufe idanunsa yana jin kukanta kmr wata azaba ce ake mai yace"dear na amince ,wlh na amince idan kin haifu zan maida ke gida"ta d'ago tana kallonshi ta sake komawa kan jikinsa tace"thank u uncle i thank u so much "daga hk suka yi shiru long time fu'ad ya d'ago ta yace"sae kuma me kike son na miki dear? Ba komai ,d'an bakinta yake kallo kmr ya had'e da nashi ,tace"uncle zan koma daga ciki fitsari nake ji"yace"ok zan zo d'aukar ki ,kamanta da mota ta nazo, ban manta ba zan dai zo, to sae kazo, nan ta wuce sae kallonta yake cike da so da qauña har ta 6ace ma ganin sa snn ya furzadda iskan bakinshi a hnkli yaja motar shi ya tafi.

Washe gari Afrah ce cikin kwalliyar ta mai kyau sae zuba qamshi take tayi tsaye tana kallon Farhan da yaran sa kmr masu gasar ado sae wasa yake musu Afrah nata dariya dmn wasar tasu daban dariya take yanda yaran ke qyalqyatar dariya suna rigengeniya gun hawa jikin Farhan sbd duk wanda ya fara hawa shi/ita
farhan ke fara d'auka yayita cilla shi/ta

sama yana mai/mata
wasa.
da murmushinta ta hau gadon ta zauna Farhan ya tashi daga kwancen da yake tare da riqo yaransa yana kallon ta tace"hm Suhail da Suhailat fa sunyi saurin wayo ji fa yanda suke wasar nan wai ba wanda keson a rigashi,
to Afrah meye abin mamaki yaran nan fa sunyi 4 to 5 months kuma kullum fa idan ina gida wasa muke yi dasu ,haka ne kuma. tashi zatayi yayi saurin riqota ya d'ora mata kiss gefen kunce yace"ina zuwa byn kinsan time d'in wasan yarane?
shafo kiss d'in tayi tana murmushi tace"bakaji wayata tana ringing ba ita zan d'auko,tana tashi suhailat ta aza kuka wai ta d'auketa tace"yi haquri Suhailat waya zanyi,Farhan ya d'auketa ganin taqi shiru yace"yi haquri mana Suhailan daddy mommy zata yi waya ne bari ta dawo kinji, ba musu tayi shiru ta kwanta kan jikinsa tana wasa da Suhail da shima yake kan jikin Farhan.
Sae ga Afrah cikin murna ta qanqame Farhan tace"wayyo dad'i! uncle Amrah ta haifu ta sami baby boy"

*Billy giro😊&Futha luv*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
[10:23PM, 11/30/2016] Billy Geeero: *[11/30/2016]* 🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅
*```AFRAH KO AMRAH ```*
🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅

*```Na Billy giro 😊&Bilqis Sidibe💅```*

*Futuhatulkhair.WordPress.com*

*```🏅95🏅```*
Cikin farin ciki sosai yace"mashaAllah tana asibiti ko ansallamo ta? No a gida fa ta haifu, shine nake son nayi sauri naje kafin a maida ta na samu na tsara mata kayan da zata zo dasu.
Ok to muje a snr da gwaggo .

Nan suka je 6angaren gwaggo dai dai ta gama waya kenan sae murna take tace"Afrah sae ki gaggauta zuwa sbd tace tana son kije yanzu, ni yanzu bari naje nayi sauri a had'a mata abincinda zata ci kafin ku dawo,
hahaha yau su Amrah za'a sha d'aci da zaman ruwan zafi,uhm ai ita kinsan ba irinki bace ,Aa gwaggo ai kinsan ita ma bata son shuwaka amma jin qiris yaja mata yau, farhan yace"muje nidai da wannan srtn naki .
To bani yaran a bawa Raheema,
ni da yarana zan tafi, kenan ni zan mana driven? Eh ni wasa zanyi da yarana ,murmushi tayi ta girgiza kai shidai yaransa yaransa.

Suna shiga mota suhailat ta ajiye kuka sae taje gun Afrah, Afrah tace"kai me yake damunki ne yau ga Abbanki kice sae ni zan d'auke ki bayan kinga driven zanyi" ki kar6e ta may be yunwa take ji....haba uncle kaima kasan ba dai yunwa ba ,kasan ita wani lokaci rigima ne da ita ba kamar suhail ba da ko mamma bai damu dashi ba idan yana hannunka .
Ta kalli suhailat tace"kima daina kuka kina taro min hannu ni ba kar6ar ki zanyi ba,
nan ta mird'a key zuwa tada mota Farhan yace"Aa gaskiya ki kar6eta sae ni na jamu,ta wani turo baki tana kallon suhailat dake taro mata hannu tana gwalanniya Afrah tace"yanyanyan kedai na kar6e ki ko? Suhailat ta fashe da dariya Afrah tace"dariya ma na baki to zo muje nan ta kar6e ta,Farhan ya fita d'auke da suhail ya zauna driver seat ita kuma ta zauna inda ya tashi ta rufe gambun mota tana fad'in "kawo suhail ko dashi zakayi driven? Eh mana baki ga har seat belt nasa mana ba, but uncle kasan suhail da wasa da ta6e ta6e ,bacci yake ji ai ko suhailat bacci ne yasata rigimar nan gashi har tayi kwanciyar ta a jikin ki alamar zata yi bacci, ok to muje .

Suna isa gidan fu'ad ya tarbe su da murna ya kar6i suhail a hannun Farhan da tuni yayi bacci kamar yadda suhailat tayi bacci.
Yace"wai kai Farhan ina ka ajiye phone d'inka nayi kira har na gaji na snr dakai an haifi mai kama dani ,au haba ?wlh sak ni yaron ya d'auko har bakina baya rufuwa kan murna,to Allah ya raya mana su akan sunna, sae dai phone d'ina fa ka tuna min kmr na manta ta a bathroom bcs zan shiga wanka aka kirani na shiga da ita kuma vibrate kawai take,, eyyah that's y.

suna shiga Afrah ta shimfed'e suhailat ta kai hannu da bisimillah ta d'auki jaririn Amrah mai kyau dashi kmr ubansa ,murmushi tayi tace"wlcm to d world of Islam Allah ya raya mana kai akan sunna, fu'ad da ya shigo yace"amin"tare da shimfid'e suhail kusa da suhailat ya kar6i jariri kan cewa zai kaiwa Farhan ya ganshi dai dai Amrah ta fito bathroom d'aure da towel yace"dear kinyi wankan yanda ya dace ko sai nazo?nayi shine abinda tace snn ya fita Afrah tace"su Anti Amrah dai an zama babba yau anji qiris .....wlh kmr kin sani naji qiris.... Au da wahala kenan ,bari kedai tunda muka dawo na fara jin naquda nayi shiru ban snr dashi ba ,
yaga na kasa yin bacci kuma sae fira yake min bana iya bashi amsar kirki sae kawai ya tsaya yana qare min kallo inda cikin en mintina ya fahimtar dashi naquda nake yace"na tashi muje asibiti nace masa bacci nkeji sbd kedai wani irin bacci nake jin yana fizgata ,sae kuwa nayi bacci abuna amma yana tashi na sllr asuba sae naqudar ta taso gabad'aya baji ba gani har ya had'a mana kayan zuwa asibiti se na haifu abuna .......huh!sannunki,hm ni ko godiya ban ma

uncle ba, name kenan?ke ko har sae na fad'a na haifu a gida ai kinsan shi zai yi wahalar gyran wuri da yiwa baby boy wanka sauqina d'aya ba wata qazanta tass na haifo yaron ,
kankana da rake sunyi aiki dmn kinsan nasha su kmr hauka kuma kinsan wankin ciki suke had'a da tamarind juice da na mayar kmr ruwan shana,to anti tamarind sae jikin ki ya 6aci kina tsaye, cab!nifa na shirya kaina tun a bayi tufafi kawai zan sa.

Tana gama shiri wayarta ta shiga ringing koda ta duba Abbanta ne bayan sun gama waya, ta ajiye wayar tana murmushi tace"Abba kenan yanzu fa business ya ha66aka har ko waya yake yana magana da mutane"Afrah tace"ai ni naga alamar business d'inda yake ya ha66aka sosai wnn tsadaddiyar motar da naga yana shiga, hm kedai bari wlh Alhmdlh Abba ya gode Allah wasa wasa fa ya fara business d'in nan cikin qanqanin lokaci Allah ya ha66aka abun inda yanzu har Abba zai koma gida ya taradda mutane a bakin qofar gidansa suna neman jiran taimako.....wai don Allah? Wlh kinsan fa Abba kalar manya ne tun baya da komai zaka d'auka ko hamshaqin mai kud'i ne sbd yanayin halittar jikinsa lumui lumui ,to bare yanzu da kud'i ke d'an shigo masa kuma yana shiga babbar mota ai dole ya taradda mutane a qofar gidan sa,Afrah tace"kai amma Alhmdlh amma dai ya daina zuwa asibiti ko don naga zuwanda nayi kusan sau biyu ban ganshi ba? Kai tun ya daina aiki asibiti dmn business d'in nan fa bazai barshi ba sbd yanzu masu kud'i sae siyan kayan gini suke suna ta gina gidaje suna bayarwa haya inda tuni har ya biya banki kud'in su da ya ciyo bashi yaja jari,,hmm kinsan uncle ko kad'an bai ji dad'in bashin nan da Abbanki yaci ba,Aa gaskiya ni banga laifin Abbana ba ,wai shi uncle sae yace komai Abba keso ya tambaye shi zai bashi a kyauta shi kuma Abba baya son haka shiyasa yaje banki ya ciyo bashi ba tare da uncle d'inki ya sani ba,ni yanzu abu d'aya ke damuna da Abba shine tun ba yau ba nake son yayi aure kullum sae yace min yaji zai yi sae kuma naji shiru kmr an shuka dusa ko kwanakin baya ina albishir d'inda nace bazan gaya miki ba? Eh, yauwa to cemin yayi zai yi aure amma wai yanzu kwanaki da na tuntu6e shi kinsan me yace? um um sae kin fad'a ,wai bai ma fara nema ba at all bai ma san taya zai tunkari mace ba,dmn ganin yake duk maccen da ya snr da ita matsalar shi ta rashin haifuwa baza ta yarda ta aure shi ba kmr yadda yasha gwagwarmaya a baya, haka ne fa but kinsan tunanin da ya fad'o min kai tsaye shine y not Abbanki da gwaggo su had'a kansu su auri juna tunda dukkansu basa haifuwa......ke Afrah!...um um to meye a ciki ko so kike Abbanki yayita zama ba aure ne har azo a fara masa wani banzan tunani can dmn kinsan yanda Abbanki yayi kud'i kuma yake da kwarjinin da duk wanda yaji cewa bai da aure sae ya kwana da mamaki,kamar yanda duk wanda yaji gwaggo bata da aure sae ya fita da tsegumi a gidan, dmn da Abbanki har gwaggo ba mai kalar tsufa a tare dashi sbd kyawon jiki da Allah yayi musu kuma sam ba mutunci bane ace cikin su ba mai aure dole kuwa abun ya zamo abin tsegumi, kuma naga akai akai suna yawan waya da junansu suna gaisawa ,Amrah ta sauke numfashi tace "nifa kinsan gwaggo ko maganar aure bata so a mata sbd yanda take matuqar son mijinta marigayi da har ko yaushe ta tuno da mutuwar sa sae ta zubar da qwallah,haka ne fa kin kashe min jiki dmn uncle ba irin nacinda bai mata ba amma taqi tayi aure ko Abban uncle fu'ad da yake yaya a gurinta yayi nashi ya gaji ya daina ya zuba mata ido shiyasa ma baki cika jin tana maganar sa ba sbd fushi yake da ita,amma in Allah ya yarda sae na zamo silar auren gwaggo da Abbanki inshaAllah ,tayaya Afrah? Kedai bari uncle zan fara tuntun6a tukun komai ake ciki zaki sani, to Allah ya tabbatar da Alhairi, Amin.

Knocking suka ji bayan sun bada izinin shigowa fu'ad ya shigo d'auke da jaririn sa a kafad'a yace"ku fito muje"kallon juna sukayi ita da Afrah tace"uncle bamu shirya ko kayanda zan tafi dasu ba fa ,to me kukeyi tun snn...koda yake ai ba sai na tambaya ba nsn da kun had'u bakuda aiki sae srt ,amma yanzu kam don Allah ku ajiye srt a had'a kayan nan na maida ke gida mom ta matsa sae kirana take nayi na maida ki gun gwaggo ki samu kulawar da ta dace, to uncle inshAllah 30 mnt sun isa kaji,
to shikenan ,
ya fad'i haka ne kafin yake fita.

Koda 3omnt yayi har sun kammala shirya komai sae gashi ya sake shigowa baby boy na kuka ya tashi daga bacci dmn tunda aka haifeshi fu'ad ya mai wanka bai ko sha mamma ba yayi bacci shine sae yanzu ya farka yana kukan yunwa.
Fu'ad ya jawo hannun Amrah ya zaunar da ita tare da miqa mata baby boy yace"oya ciro mamma ki bashi yasha .....pls uncle bari muje gida mana.... What!yarona najin yunwa kice sae anje gida keda mom ne inta jiki dmn ina cikin waya da ita yaron ya tashi yana kuka shine tace a kawo shi kuma yanzu zata kira taji in ya fara sha, don haka yi sauri kar ta kira ta ji bai fara shaba ta min fad'a.
Kmr tace wani abu sae kuma ta fasa ta shiga bawa yaron mamma ta yanda ba a ganin mamman sosai sbd d'aga rgr ta tayi ta qasa ba ciro mamman tayi ta saman rigar ba.
Duk irin zafin ciwon da take ji haka ta jure bata nuna ba sbd tsn fu'ad zai iya shiga damuwa ne idan ya fahimci tana jin ciwo.
Wayar fu'ad ce tayi qara ya d'aga yace"mom eh ya fara sha ok to gata"
nan ya d'ora waya kan kunnen Amrah inda cikin ladabi take waya da mahaifiyar tashi kamar suna kusa .
Bayan sun gama fu'ad ya kar6i wayar ya tashi yace"zan dawo na kar6i yarona idan ya gama sha"
kafin ya fita ne Afrah tace"pls uncle fu'ad idan zaka dawo d'aukar baby boy kace da uncle yazo dan Allah ya d'auka min d'ayan yaran nan sbd bacci suke bazan iya d'aukarsu su duka ba kuma ga kaya ,yace"ok to ku bani kayan ma na fara ragewa.

Ya d'auki kayan ya fita dasu.

Tafe suke su Amrah cikin motar su haka ma su Afrah .
Suhailat dake bacci kan jikinta ce ta tashi sae kuka take tana son mamma dmn sae tura hannunta take qoqarin yi cikin rgr Afrah,Afrah ta d'aga ta sama tana fad'in"sorry habibtee suhailateee!Farhan yace"ba wani Habibtee ki bawa yarinya mamma tasha kafin ta tayar da suhail ya hana min driven cikin dad'i "nifa bana son shayawar a mota sae mun isa gida tukun ,idan kuwa ta tada suhail zan baki shine suyi ta miki rigima kin san dai halinsu, naji ba komai zan iya dasu ai ,ta qarashe maganar cikin dariya dmn tasan har kuka take idan suka tasa ta gaba suna mata rigima.

Shima Farhan dariya yayi yace"to wa nasha kamawa a d'aki yara kuka ita kuka ba mai kama wani ? Oho wata qil mafarki kayi......waini waini kaina ga cikin ku ban huta ba kun fito ma ban huta ba,
Farhan ne yayi maganar cikin qwaiqwaiyon murya irinta ta Afrah idan tana kuka yara sun tasa ta a gaba"
Dariya kawai tayi ta ci gaba da yiwa suhailat wasa har suka isa.

Sosai gwaggo ke kula da Amrah da yaronta kamar yanda ya dace,haka ma ko yaushe Fu'ad na zuwa ya kawo ma Amrah da yaron su ziyara.
ranar suna yaro yaci sunan *Najeeb* akayi biki bidiri har umman fu'ad ba'a bari a baya ba dmn sae da taxo.

Bayan kwana 2 da biki.
Afrah ce kwance ita da Farhan suna fira suhail da suhailat na kan d'an gadon su suna bacci Afrah ta birgino a hankali kan jikin Farhan tace"uncle wata shawara nake son muyi"da kulawa yace"tame kenan ?wai gani nayi me zai hana gwaggo da Abban Amrah su had'a kansu suyi aure tunda ba mai haifuwa a cikin su"shiru yayi yana nazairi tace"uncle ko basu dace bane?sunyi matuqar dacewa my Afrah, ba don komai ba sae don kinga Abban Amrah duk wanda ya kalle shi ba zai ta6a tunanin yasan wani abu talauci ba a hakan ne ma lokacin da ya fara min aiki a asibiti wasu suka d'auka ko mahaifina ne kemin sharar office har abun ya zama tsegumi sosai ga wad'an da basu san cewa iyayena basa raye ba hakan yasa nace ya bari na bashi kud'i yaja jari yayi wata sana'ar yace shi sam yafi son aikinda na d'ora shi akai kuma taimakon da nakeyiwa Amrah ya isa ya gode min, nayi nayi dashi yaqi se cewa yayi indai en tsegumi ne na rabu dasu sa gaji su bari.
Haka kuma Abban Amrah mutun ne mai yawan ibadah kamar gwaggo hakan yasa nake tunanin sun dace duk da cewa gwaggo kalar matar manya ce amma ai Alhmdlh tunda shima haka yake kuma gashi yanzu ya kama sana'a mai kawo kud'i nan take ko kuma nace sana'ar ta kar6e shi,sai dai gwaggo ce matsala dmn baza ta amince ba kinsani, but ka dai lalla6ata kuma duk sallah mu riqa addu'a Allah yasa ta amince, to shikenan Allah ya shiga ciki ya kuma sa Alhairi ne,Amin.

Washe gari farhan ne ya shigo d'akin Afrah ya samu tana shirya ma yara, suna ganin shi suka tafi jikinshi kallon yaran kawai yayi ya d'an riqa hannunsu yana shafa bayan su ba kullum da in sunzo jikin sa ba zai d'auke su da murna yana d'aga su sama suna dariya, hkn yasa Afrah ta fahmci akwai damuwa a tare da shi ,jiki sanyaye Afrah ta zauna kusa dashi ta ta6a jikinsa ya kalleta yace"yadai ?uncle baka da lafiya ne? Lfyta lau gwaggo ce tamin fad'a kar na qara mata maganar aure idan har ba so nake koda za'a wayi gari ta bar mana gidan ba, ba kuma zamu qara ganin ta ba.
Wani irin abu Afrah taji da ya qara sa jiknta yayi sanyi tace"shikenan uncle dan Allah kar qara ce mata komai ,tayi hanzari zata bar gurin sbd kukanda ke qoqarin zo mata,Farhan yayi saurin jawota jikin sa sae dai bai hanata kukan ba taci gaba dayin abinta kan qirjinsa can ya d'ago ta yace"duba suhail da suhailat yanda suke kallon ki ita suhailat har da wani le6ace baki kmr zata

yi kuka, mamaki ya kama Afrah had'e da dariya tace"wlh uncle na gaya ma yaran nan sunyi saurin wayo jifa kuka zatayi ganin inayi kuma nayi dariya ita ma tayi dariya,barikallah kin sa ma yarana ido ke baki san yara nada wani abu ba duk abinda suka ga anayi suma qoqarin yinshi suke koda basu san mene ne ba, duk da haka dai uncle suhailat tafi sona ba kamar suhail ba ,Afrah kenan mace ce tafi tausayin uwa kuma kina nuna musu banbanci ba kamar yanda nake musu ba kin fiye kula suhailat ko mamma ita kike fara ba kafin shi wanka ma haka idan kuka suke kinga damar ki d'auki suhailat kice Raheema tazo ta d'auki suhail ,hkn da kike yana qona min rai ba kad'an ba kuma ba abune mai kyau ba wnn dmn raba kan 'ya'yanki kike shirin yi baki sani ba, kmr tayi kuka tace"uncle nifa ba ina yin haka bane don nafi son suhailat sae don ganin ita mace ce tana da rauni kuma idan tana kuka ba lallai bane ta yarda taje gun wani sanin kanka ne suhail ya fita haquri kuma duk wanda ya tara masa hannu zai je, amma kayi haquri zan gyara inshaAllah dmn nafison su taso kansu a had'e .

Farhan yace "to Allah ya had'a mana kawunan su tace"amin"snn ta koma jikinsa ta lafe tana tunanin hali irin na gwaggo, farhan yace "baki gama shirya yaran ba fa kinsa musu waduna ba riga, to basu bane suna ganin ka suka qi tsayi,oya suhail zo a qarasa shiri ko,

ba musu yaje dmn hanunwanta da ta tara tana kallon shi ya bashi damar kiran sa take ,tana d'aukar shi suhailat ta ajiye kuka ita ma a d'auketa Afrah tayi murmushi tace"uncle see ur dota kaga son kai irin nata ko ta nuna suhaila da yatsa tace"kin barin son kai to sae na gama shirya shi ko zan d'auke ki,kuka ta ajiye taje jikin Farhan kmr taji me Afrah ke fad'i, Farhan yayi murmushi ya d'auketa ya cira ta sama yana cewa "suhailan mama bakida gaskiya ai ba ke kadai ce 'ya ba kuma kin sani.

Daga haka yayita cira ta sama yana mata wasa sae dariya take, suhail na gani ya bar jikin Afrah dake qoqarin sa masa hannayen riga ya tafi sae sauri yake yana qyalqyaltar dariya har yaje gun Farhan, Afrah tace"ji kuma ba mai son yaga ana yiwa d'an uwansa wani abu ba a mai ba"Farhan yayi dariya ya qarasa saka ma suhail riga snn ya kar6i ta suhailat ya sa mata.

Yau kusan sati d'aya Afrah da Farhan sun sauyawa gwaggo kmr had'in baki da d'ayansu ya shiga 6angarenta gaisuwa kawai ke had'asu su fito ba wani sakin fuska bare zancen zama ayi fira ,duk da Amrah na gidan ba wani zama Afrah keyi ba take komawa 6angareñta.
hkn ba qaramin rashin dad'i yayiwa gwaggo ba duk da tasan dalilin da yasa suke mata hakan.

Farhan ne ya dawo daga aiki a gajiya Afrah taje ta tarbe shi ya kar6i suhail da suhailat ita kuma ta kar6i jakar hannun shi,suka haura sama zuwa d'akinshi.

Da taimakon ta ya rage kayan jikinsa ya fad'a wanka,

kayan wasa ta zuba akan gadon da Farhan ya ajiye su snn ta tafi downstairs ta d'auko mai abincin sa sbd tasan yanda ya shigo a gajiye ba zai iya sake sauka ba.

Barin yaran tayi suna ci gaba da wasar su ita kuma taje zuwa nema ma Farhan kayan sawa masu sauqi.

Yana fitowa ya kalli yaran sae wasa suke da abubuwan wasan su ita ma Afrah tayi tsaye tana kallon su sae dai kmr wani tunani takeyi ,Farhan ya qaraso inda take ya juyar da ita ta baya ya rungume suka ba yaran bai yakai bakinshi dai dai wuyanta kmr wanda zai mata kiss

yace"tunanin me kike kina kallon yara? Ba komai nima haka kawai na ganni a tsaye kmr mai tunani kuma gsky ba abinda nake tunani,ni kuma na d'auka tausayin su ne kika fara idan kika fara karatu, dmn suna samun kulawar ki ba kad'an ba, idan kika fara zuwa school abin zai rage sosai ,to sae suyi haquri ai gwaggo na nan kuma da na sami time zan dawo ne na shayar dasu,ya juyo da ita yana kallonta yace"ko zaki bari idan sun shekara sae ki fara karatun? kai tsaye taji qwallah sun cika mata ido tana kallonshi ,had'e bakinsu kawai taga yayi, tayi tayi ta qwaci kanta ta kasa ,
yayi saurin sakinta sbd towel d'insa dake qoqarin zamewa ya kalli yanda ranta yayi mugun 6aci ya sake jawota yana qoqarin had'e bakinsu ta fixge kanta da qarfi tana fad'in"wai meye hk dan Allah! yara fa na kallon mu,sake riqota yayi yana kallonta yace"Afrah yau ni kike ma tsawa? Da sauri ta sadda kanta qasa tace cikin muryar kuka ni uncle ka gaya min kawai idan baka son nayi karatun nan sai na haqura,Afrah kinsan nafi kowa son kiyi karatu yaran ne kawai suka bani tausayi amma kar ki damu zaki fara karatun nan bada jimawa ba inshaAllah ,gyad'a masa kai tayi snn taje kan qirjinsa ta kwantar da kanta kmr yanda ya buqata ,sun d'an jima a haka ,ya d'agota yace"bari nasa kaya naci abinci sae muje 6angaren gwaggo tace tana son tayi magana damu.....yes!Allah yasa plan d'in mu ne yayi, hm Allah yasa hln ke kinga ta fara shiga damuwa kan canza mata da mukayi?bazan iya ganewa ba tunda da mun gaisa nake tafiyata kawai dai nasan baza ta rasa shiga damuwa ba duk da cewa still suhail da suhailat gurinta suke yini shan mamma kad'ai ke kawo su ,ko yanzu an maida su kenan ka dawo basu ko sha mamman ba ,ya kalli yaransa yace"to je ki basu mamman kinga har suhail ya fara ta6a kunnen sa alamar bacci yake son yayi.
Nan taje tana breast feeding d'insu shi kuma ya shirya yayi zaune yana cin abinci.

Koda suka je 6angaren gwaggo suka dawo ba qaramin murna sukayi ba musamman Afrah da har tsalle take tana rawa sae kace wacce aka yiwa bushara da gidan aljanna ,tace"uncle ai yau nasan ba qaramin murna Abban uncle fu'ad zai yi ba idan yaji gwaggo ta amince zata yi aure,gsky kam na tabbatar har zowa sae yayi amma fa bazan gaya mai ba sae anji daga bakin Abban Amrah duk da a gurin shi bana tunanin akwai matsala but jekiyi magana da Amrah sae ta fara tuntu6ar Abban nata muji,ai na tura mata text ynz zata shigo 6angaren mu ,yauwa naji door bell inaga ita ce.

Ta sauka downstairs tayi sauri ta bud'e qofa ta qanqame Amrah dake tsaye ,Amrah ta qarasa shigowa suka zauna ta kira Abbanta tana gama wayar ta kalli Afrah tace"Abba baya gari yana Abuja amma yau zai dawo yanzu uncle nake son na kira ko zai barni naje gida yau, ke Amrah wa zai barki ki fita kina biqi ,mtsw meye a ciki kuma ai bazan bari gwaggo ta sani ba idan uncle yazo anjima da dare sae na roqe shi ya kaini,kina ganin xai barki ?inshaAllah.

Da dare Amrah ce zaune da fu'ad a cikin mota yace"ya baki zo min da Najeeb ba ?bacci yake ,bai sake cewa komai ba sae fira da ya sake janta da ita a cikin firar su ne tace"pls uncle ina son ka kaini gun Abba yanzu "kallonta yayi yace"gida yanzu why? Nidai dan Allah kawai ka kaini zan ganshi ne,matsowa yayi kusa da ita tayi saurin jaye fuskarta ganin abinda yake shirin yi ,tace"kace wani abu ba wnn ba"jinginawa yayi a jikin seat yace"kina ganin Najib ba zai tashi

ba har mu dawo? Najib ya riga ya shiga bacci sae kuma cikin dare idan ya farka shan mamma,ajiyar zuciya ya sauke snn yaja motar suka tafi.

Bayan wata hud'u da faruwar haka abubuwa da dama sun faru dmn anyi auren gwaggo da Abban Amrah sae dai a nan gidan yake zowa kafin ya kammala gyara wani gida da ya saye dake gab da gidan sbd baya son d'auke gwaggo kusa da su farhan sae akayi sa'a maqwabcin su farhan yasa gidansa a kasuwa sbd zasu bar garin gabad'aya dmn ba mazauni garin bane shine sae Abban Amrah ya sayi gidan,duk da gidan mai kyau ne amma yafi so ya qara tsara gidan yanda yake so.
Amrah kuwa tuni ta koma gidan mijinta haka kuma a cikin watan nan sun fara zuwa school sae dai sae Amrah tazo gida ta ajiye Najib nan gurin gwaggo tare da su suhail da suhailat.

yau weekend hakan yasa Afrah da Farhan suke zaune gida suna hutawa sae shan fruits suke suna kallo, su suhail da suhailat sae wasa suke da motar su ta wasa .
Afrah tace"ni kuwa uncle gidan nan da Abban Amrah ke gyara banga illarsa ba da har naga yasa an rushe katangar da ke tsakanin mu dasu,wai fa duk don mu yake yi so yake ya bud'e qofar da zata riqa sada mu da gwaggo cikin sauqi ba sae mun zagaya ba, kai amma fa ya kyauta mana, to shi 6angaren gwaggo idan suka tare a nasu gidan rufe shi kawai za'ayi? Eh to za'a rufe qofar da ke sada mu da ita sae a zuba en haya a ciki, en haya kuma uncle? Eh amma ba irin en hayan da kike tunani ba wani shahararren d'an kasuwa ne matashi da kasuwancin sa ya bunqasa a nan garin shine yake so ya tare nan garin shida matarsa da d'ansu qwaya d'aya ,bare kinsan yanayin gida yanayin wanda zai dauki hayar shi ba wai haya duk haya bace,kuma kinga gwaggo yanzu ta samu wata hanya da kud'i masu tsoka zasu riqa shigo mata duk shekara ,haka kuma keda Amrah nake son a raba muku dukiyar ku ta gado sae na samar miki hanyar da zaki riqa juya kud'in ta hanyar business ,um um nidai uncle idan an rava kabar nawa a hannunka kawai na bar ma halak malak, sam hakan bai zai yiyu ba Afrah ,meyasa ? Sae kace Farhan d'in mahaukata... As how uncle, calm down mana Afrah, ina son kiyi business ne shiyasa ,nifa uncle harkar business d'in nan bazan iya ba, to shikenan akwai wani tunani da nayi zamu had'a kud'i mu gina asibiti nida fu'ad idan zaku iya keda Amrah sae mu had'a hannu mu duka hud'u sae mu gina babbar asibiti idan Allah ya nuna mana kun kammala karatun ku sae mu koma can da aiki damu har ku, ko ya kika gani ?gaskiya haka yayi uncle muyi aiki tare da mazajenmu .

Two weeks later tafe suke sun fito da gidan su Amrah sae fira suke abinsu cikin mota, hankalin Farhan ne ya d'auku har ya tashi kad'e wata mata yayi saurin jan birki Allah ya taimake shi bai kad'e matar ba ya fito dmn ya bata haquri cikin tsananin mamaki yake kallon fuskar matar bakinsa na rawa ya samu da qyar yace"mama dama kina raye! Matar tayi saqwarqwatai tana kallon shi ko zata tuna inda ta san shi Farhan yace"mama baza ki san fuskata ba sbd lokacin ba kya gani akasin yanzu da aka miki eyeglass ,mama nine Farhan mijin er ki marigayiya Amrah ,kuka ta fashe dashi tace"Allah sarki kaine ashe kaima kana raye aka ce min har da kai ka mutu "ganin kukanta zai tara musu mutane yace"mama muje na kai ki gida sae muyi magana a can.

Bayan sunje gidan yake cewa "mama waya snr da ke cewa har ni na mutu? Mai gida na ne da ya tafi dani ,
ya gaya min labarin da yaji a gari cewa en fashi sun shiga gidan ku har ma an kashe ka kaida Amrah, ba qaramar nadama yayi ba dajin mutuwar Amrah haka nima ba irin kukanda banyi ba dmn kasan ita kad'ai ce 'ya a gareni haka kuma a lokacin qafata tayi tsanani shiyasa maigidana ya d'auke ni yaje dani qauyen su dmn amin magani ,snn kuma shi yayi d'auwainiya dani har aka min madubin ido na fara gani, amma har ko yaushe ina mai jin baqin cikin yanda ya rabani da Amrah ba tare da yasan halinda zata shiga ba, dmn ba don ka ceceta ba da ban san halin da zata shiga ciki ba,wanda duk zamn da tayi a gidanku kafin ka aureta har zuwa lokaçiñ da ka aureta maigidana ya bani lbr don kawai ya samu na kwantar da hnklina har yana min alqawarin idan naji sauqi zai kaini gurinta ashe ba rabon mu qara ganin juna bane haqiqa Allah baya barin wani don wani ,na yafe miki Amrah na yafe miki duniya da lafira, daga haka tayi ta kuka cikin kukan take cewa don Allah d'an nan nasan baza ka rasa hotonta ba idan ka sami lokaci ka kawo min ko zan riqa ganin fuskar 'yata,
ta qarashe maganar cikin wani irin kuka mai ban tausayi.
Sosai Farhan kejin kuka amma haka ya dake ya ciro kud'i masu yawa a aljihunsa ya ajiye mata yace"ga wnn mu zamu tafi sae gobe inshaAllah zan shigo na kawo miki hoton ,
nan tayi ta yimai godiya har suka fita.

Har suka isa gida Farhan bai qara cewa komai ba.
Da dare Afrah tayi shirin bacci taje d'akin Farhan ta same shi sae kallon photon marigayiya Amrah yake qwallah cike tap a idonsa.
Zama tayi ta kar6i photon ta ajiye snn ta kwantar da kansa a qirjinta tana shafa sumar kanshi a hankali yayinda qwallah ke silalowa a hankali kan kumatunta, har suna d'iga kan fuskar Farhan, yayi saurin d'agowa yana kallonta yace"no Afrah ki daina kuka kinji nima na daina,nan ta sake maida shi kan qirjinta kmr wani d'an yaro tana ci gaba da shafar sumar kanshi.

Washe gari ne ya tafi ya kaiwa Maman Amrah photo kmr yanda ta buqata ,dashi da gwaggo ma yaje sbd ya bata labarin had'uwar da sukayi ta jiya.

Some yrs a go .

Farhan ne ya shigo d'akin Afrah ya same ta kan gado ta jingina bayanta da pillow tare da miqe qafafunta sae chat take da Amrah yaje yayi pillow da cinyoyinta yana kallon fuskarta ta ajiye wayar tace"yadai uncle? zancen asibitin mu ne da aka yi kusan kammalawa amma har yanzu bamu tanadi sunan da zamuyi mata ba, kai ko dai uncle bayan ance sunayen mu ,mu hud'u za'a had'a da kuma na yaran mu, to ai bai yi ba yayi kad'an sbd kinga nida fu'ad F keda Amrah A suhail da suhailat S sae Najib kinga idan aka had'a ba zai bada wani abu ba face FASN hope get it, kinga abu mai sauqi kafin a kammala gini ku sanbad'o muna wasu yaran..... Cabd'i sae mun kammala karatu tukun, ba wani yau d'in nan a yanzu ki shiryi kar6ar babyna ,nan yakai hannu ya xuge mata zip d'in riga ,Afrah ta saki dariya ta tashi ta fita dagudu ta bar shi sae

dariya yake .

Bayan wata d'aya da faruwar haka ne.
Fu'ad da Amrah sunzo musu yini suna zaune kan dining su duka hud'u zasu fara cin abinci.
Suhail da suhailat n Naheeb kuma suna gun gwaggo.

Afrah na bud'e warmers qamshin abincin ya daki hancin Amrah ta rufe hancinta ta tafi da gudu sae toilet d'inda ke nan downstairs tayi amai har ta gode Allah ,fu'ad da ya bita shi ya taimaka mata ta wanke bakinta suka fito.
Kan su qaraso Afrah ta kalli Amrah ta fashe da dariya tace"ba dai ciki ba muna last yr da batun kammala school,wayyo Allahna har kin ban tausayi ,takai har qasa tana dariya tana ta6a ciki tana nuna Amarah tace"wayyo Allah cikina wai ke ya ma akayi kika bari kika sami ciki kuma a shekarar mu ta qarshe,ta sake kwashewa da dariya tace" kai amma har kin ban tausayi ga renon ciki ga karatu Allah sarki baiwar Allah.....suhailat ce ta shigo da gudu ta sami Afrah nan durqushe sae kwasar dariya take tana nuna Amrah wacce ranta yayi mugun 6aci ta kalli fu'ad cike da qwallah a idonta dmn ganin take laifinsa ne.
Suhailat ta katse Afrah da cewa" mommy kinji wani turare mai qamshi da gwaggo ta siyo a lokacinda kuka je makka..... Ture ta Afrah tayi da sauri sbd wani irin abu taji lokacinda turaren ya daki hancinta, ta daka mata tsawa tace"6ace min da gani da wnn qamshin turaren naki! cikin fushi suhailat ta fita,inda har ran Farhan ya soma 6aci yaga Afrah ta tashi da gudu tana yunqurin amai sae toilet ,
tayi amai fiye da na Amrah ta,ta fito wahale rungume a jikin Farhan sae numfashi take fitarwa ta samu da qyar tace" uncle nidai ba ciki ne dani ba ko? Kmr mai rad'a yaje saitin kunnenta yace"ciki ne mana Afrah ke baki lura da yanayin jikin ki bane a kwanakin nan?a tsorace cikin d'aga murya tace"ciki fa kace uncle....zama d'aya su duka ukku suka kwashe da dariya har Farhan d'in dake rungume da ita sbd ba qaramin dariya ta bashi ba yanda tayi tambayar.
Dariya suke sosai musamman Amrah ,Afrah kuwa kuka ta fashe dashi tana qoqarin haurawa sama da gudu, Amrah ta riqota tana share mata hawaye tace"bassu kawai na tabbatar da gayya suka mana cikakkan nan don kawai sunan asibiti ya fito, wata dariyar Farhan da fu'ad suka sake kwashewa da ita sbd yanda Amrah tayi maganar shaye da toka ko kunyar maganar ma bata ji ba,sae da sukayi dariya mai isar su har su Afrah da Amrah suka fashe da kuka dmn ganin suke kamar shikenan sun 6ata musu tsarin karatunsu,hakan yasa kowanen su yaja matar sa zuwa rarrashi da qyar suka samu suka shawo kan matan nasu cikin nuna musu cewa cikin fa daga Allah ne kuma in Allah ya yarda zasu kammala karatun su lami lafiya.

Bayan shekara d'aya har da watanni. Alhmdlh su Afrah sun kammala karatun su lami lafiya kuma result Almdlh yayi kyau ba kad'an ba, inda tuni suka haife abinda ke cikinsu yayinda Allah ya azurta Afrah da haifuwar d'a namiji da suke kira *Sameer* Amrah kuwa ta sami en biyunta duka mata wato *Najwa & Najma*

Kuma har sun bud'e asibitir su mai suna *FASAN SPECIALIST HOSPITAL* da tayi matuqar

kar6uwa gun mutane sbd qwararrin likitawan da aka zuba a ciki.

TAMAT BIHAMDILLAH!
WE DEDICATED THIS NOVEL TO ALL OUR FANS!
LUV U ALL😍

NI BILLY GIRO KECE MUKU SAI MUN HAD'U A LITTAFINA NA GABA MAI SUNA *BAZAN BAR SHI BA!*

NI KUMA BILQIS SIDIBE WATO (FUTUHATUL~KHAIR) KE CE MUKU AFTER KAWATA KISHIYATA DA NAKE YI YANZU ZAKU JINI A LITTAFINA NA GABA MAI SUNA *GIMBIYA BILQEES*

🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅🏅